MATAR MUKHTAR

Written by:

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA 1

01

A shekaru hudu da sukayi da aure basu taba samun wata matsala ba domin domin Safiyya macece mai hakuri da kau da kai, musamman a kan lamarin mutumin da take matukar so. Shi din ma kuma ba daga baya ba, duk wani hakki nasu ita da yaran yana saukewa harda kari sannan kuma shi din ma yana matukar kaunar matarsa.

Ma’aikacin gwamnati ne wanda a yanzu ya kai kimanin shekaru goma yana aiki, da yake kuma duniya ta canza sai ya hada da kawo kwamfutoci daga kasar Indiya yana sayarwa a nan Nigeria. Don haka babu laifi suna rayuwa cikin rufin asirin Allah tare da yaransu guda biyu, Usman wanda suke kira Nurain me shekaru uku sai kuma Khadija wadda suke kira Nana mai shekara daya da rabi.

.....

Bayan ya gama karin kumallonsa ya shirya kamar yanda ya saba ya fita aiki, ya barsu ita da yaran a gida da yake babu mai zuwa makaranta. Nan da nan ta yiwa yaran wanka ta goya Nana yayinda ta mika Nurain wajen kanwarta Hamida wadda tazo musu hutu. Saida suka dauki kimanin awa daya da rabi suna bacci itada Nana sannan ta tashi ta shiga kicin.

Indai bai fita da abincin rana ba ya saba dawowa gidan bayan azahar yaci abincin sannan idan yana da wani abun sai ya sake fita, don haka da wuri ta tashi ta gama komai ta hada abincin rana.

A zaune suke a falo suna kallon tashar NTA Hausa yayinda suke cin abinci, ita tana ci a kwanonta inda Hamida take ci tana bawa Nurain; wayarta tayi kara daga kicin. Kafin tace wani abu Hamida ta mike ta dauko mata wayar daga kicin inda ta mantota.

Da sallama ta amsa wayar tayi kasake tana sauraro, ko da bata da lambar amma ta dauki murya; Mustafa ne abokin Abban Nurain wanda waje daya suke aiki.

Kafin su gaisa yace

‘Kin gane ko Safiyya, wallahi abokina ya sami minor accident ne gamu nan ma a emergency na asibitin Nassarawa yanzu. Ya ma damuna yayi ne a kan lallai sai na kirawo ki na sanar dake amma kar ki wani daga hankalinki buguwa ya danyi sai kuma firgici gashi nan likita yana dubanshi.’

‘Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun, Subhanallah bari na taho yanzu.’

Magana Mustafan yake yana kokarin yace ta zauna zai kirawota in akwai bukatar tazo amma ko sauraronsa batayi ba ta jefa wayar kan kujera ba tare da ta katseba.

Ta mike ta dubi Hamida tana nuna mata Nana tace

‘Rike min ita, babansu yayi accident yana asibiti zan je na gani.’

Kafin ta bata amsa ta wuce daki da sauri ta barsu a nan. Hijabi ta saka sannan ta dauki jakar hannunta, ta tsaya a tsakiyar dakin tana duba jakar, bata da ko sisi sai naira dari biyu wadda ya bata shekaranjiya da zai fita ta sa katin waya ta sayi data na whatsapp. Ta zaro dari biyun ta kalleta, ta danyi lissafi a kwakwalwarta ta tabbatar dari biyu zata kaita asibitin Nassarawa sannan ta mayar da ita cikin jakar.

Ta fito falon tayiwa Hamida sallama sannan ta fice.

Tana zuwa ta tarar da Mustafa a wajen da ake jiran ganin likita wanda ya sanar da ita an shige da Mukhtar din ciki, ta sami guri itama ta zauna. Tana ta addu’a Allah ya sa dai a hayyacinsa yake, tana son tayi waya gidansu ta sanar da Hajiyarsa amma ta daure taga an fito da shi tukunna don taga yanda jikin nasa yake.

Jimawa kadan aka leko aka kirawo Mustafan, cikin sauri ta bi bayansa suka wuce dakin likitan.

Yana kwance a kan gadon duba mara lafiya idonsa a rufe kamar mai bacci yayinda likitocin su biyu da ma’aikacin jinya daya suke tsaye a kansa.

Likitan ya dubi Mustafa yace

‘Kaine kazo da shi ko?’

Ya jijjiga kai alamar e. Likitan yace

‘A yanzu dai bamu sami wata babbar matsala ba sai dai kawai ya firgita kadan sannan kuma ya buge a hannunsa na dama. Yanzu haka an yi masa allurar da ka kawo gashi nan har ya sami bacci, za a tura shi a kan wannan gadon kuje da ma’aikata ayi masa x-ray a hannun sannan a nuna muku daki, sai zuwa gobe idan muka ga hoton hannun nasa kuma muka ga ya sami natsuwa za a sallameku.’

‘To likita mun gode.’

Ya amsa yayinda ma’aikacin jinya ya hadasu da wani ma’aikacin wanda ya tura gadon da Mukhtar yake kwance a kai yana bacci har zuwa dakin hoto.

Gaba daya Mustafan ne ya biya kudin akayi komai, sai da aka basu daki sannan Safiyya ta kirawo kaninsa Saifullahi ta sanar da shi halin da suke ciki.

Tunda taga la’asar tayi ta kirawo Hamida ta sanar da ita ta rufe gidan ta kwashi yaran su tafi gidan Umma da safe sa yi waya.

Nan suka zauna da Saifullahi da daya kanin nashi Aminu har dare yayi; sau daya ya farka ya dan ci abinci kafin wani lokaci kuma ya sake komawa bacci.

Bayan sunyi Sallar isha’i a masallacin asibitin suka dawo dakin suka sameta, har yanzu dai baccin yakeyi. Saifullahi ya dubeta yace

‘Anti Safiyya ki taso na mayar dake gida sai Aminu ya kwana da shi.’

Da sauri ta jijjiga kai

‘Ai babu komai zan kwana, yaran duk sun tafi gidan Ummanmu.’

Ya kalleta ta jijjiga masa kai tana sake bashi tabbacin hakan za ayi babu wata damuwa.

Don haka suka wuce suka barta a nan inda ta tashi ta rufe musu kofa tunda Saifullahi da Aminu sun riga sun kawo musu duk wani abun bukata.

Cikin dare ta kasa bacci, shi kuwa yana ta bacci saboda allurai da magungunan da aka bashi.Nan ta tashi ta shiga bandaki ta yi alwala ta tada salla. Kafin ta kai raka’ar farko wayarsa da Mustafa ya bata wadda ta saka nasa a chaji ta dau ringing. Ta cigaba da sallar ta, kafin tayi raka’a biyu an kira ya kai sau biyar.

Tana sallamewa ta dau wayar ta duba.

Mahaifiyarsa ce Hajiya.

Nan da nan ta danna wayarta don ta kira hajiya sai akace bata da credit a wayar, ta san baya rasa credit a tashi wayar don haka ta dau wayarsa don ta kirata.

Tana dubawa taga an kulle wayar wanda dama ta san da haka, ta san da hoton yatsansa yake kullewa don haka ta tashi ta kama yatsan ta dangwala nan da nan kuwa wayar ta bude.

Take ta dannawa Hajiyan kira tana dagawa ta ce

‘Safiyya ina kuka shiga na ke ta kiranku shiru, ya jikin nashi kuwa? Aminu yace min yana ta bacci, bai farka ba?’

Ta yi mata bayani halin da suke ciki da abinda likitoci suka ce. Sukai sallama ta ajiye tana ta fargabar halin da Mukhtar din yake ciki.

Ta mayar da wayar chaji ta idar da sallarta, ta kashe fitilar ta koma ta kwanta. Ta fi awa daya tana juyi bacci yaki daukarta har ta gaji ta tashi ta kunna fitilar. Ta dubashi ta tabbatar yana numfashi ta janyo kujera ta zauna ta zuba masa ido tana kirga numfashinsa tana fatan ya tashi lafiya domin dazu da ya farka baya son bude ido kuma baya son magana.

Ta riga ta san bata da data shi kuma kullum wayarsa da data don haka ta tashi ta dauko wayarsa ta kunna data ta jona da tata wayar ta hau yawo tsakanin Whatsapp da Facebook, haka ta dauki lokaci har kallo tayi a youtube wai ita ta sami data.

Ta gama ta kashe tata datar ta dauki tashi wayar zata kashe ta sai wani message ya shigo wayar ta Whatsapp, ta karanta layin farko da ya nuna ta saman wayar kamar haka

“missing your beautiful lips my love”

Taji kamar an buga mata guduma a tsakar ka nan da nan rufe ta duk da babu zafi ko daya a garin, ko tunani batayi ba ta bude WhatsApp dinshi domin ta karanta message din.

‘Sucre’ shine sunan da akayi saving lambar da shi, ta karanta sunan nan ya kai sau goma kafin ta cigaba. Ta fara yin kasa don taga ko da akwai wasu chats din masu kama da wannan, tana yi tana gumi kwakwalwarta a tsaye cak don ta kasa tunani. Har ta gaji da yin kasa bata samu wani sako daga mace mai kama da wannan ba don haka ta koma sama don ta karanta sakon Sucre.

Tayi ta yin sama tana kokarin ganin lokacin da ya fara musayar sakonni da Sucre amma ta kasa zuwa saboda yawan sakonni, don haka sai kawai ta fara biyo sakonni a hankali.

Da fari har tana tunanin aure yake nema ya boye mata amma hirarrakin ba suyi kama da na me neman aure ba, irin wadannan zantukan da hotunan sun fi kama da wadanda akeyi da karuwa.

Shi dai bai tura mata hotonsa ba amma ita ta turo masa hotunanta kalakala; wani da kayan bacci tana shan ice cream, wani daga ita sai towel da ruwa a jikinta alamar wanka, wani kuma ta yi kasa da wuyan rigar nonuwa a waje, wani video ma daga ita sai breziya da pant tana zaune a gefen gado tana ta faman lashes lebe kamar wata mayunwaciyar mayya. Hirarrakin kuma yawancinsu na batsa ne domin zata iya cewa har saduwa an yi a wadannan hirarrakin kuma wasu shi yake fara su balle tace ko yarinyar ce take masa kutse.

Idonta ya rufe saboda hawayen da suke fitowa tana ta faman gogewa, tana yin kasa kadan ta ga hotunansu shi da ita a bakin wani swimming pool ya rungumeta daga shi sai gajeran wando ita kuma da kayan swimming irin na breziya da pant din nan, ga wani kuma bakunansu a manne da na juna. Ta share hawaye ta ajiye hannun da ta rike wayar da shi a cinyarta yayinda ta dafe kirjinta da daya hannun, ta dago ta dubi fuskarshi. Har yanzu bacci yake hankalinsa a kwance, ta zura masa ido kawai tana bin fuskarsa da kallo. Ta kawar da kanta ta sake share hawaye

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta dubi wayar dake hannunta, ta tabe baki tare da ajiyar zuciya. Ba zata iya cigaba da karanta sakonnin ba saboda yanda zuciyarta take kuna idonta yana zubar da hawaye. Ta kashe datar sannan ta kashe wayar ma gaba daya sannan ta mike ta ajiye a kan durowar da take gefen gadon.

Ta koma kan daya kujerar da take daga gafe jikin bango ta zauna jagwaf kamar wadda aka tunkuda.

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta fada a karo na babu iyaka. Ta ja tissue wadda take ajiye a kan jakarta ta face majinar da ta cika mata hanci, ta goge hawayen da ke fuskarta sannan ta mayar da tissue din ta ajiye.

Ta daga idonta ta dubeshi tana cike da tsananin mamaki, tabbas da wani ya bata labarin wadannan sakonnin da ta gani a wayarsa cewa zatayi ana sone a kashe mata aure. Ko daya bai taba yin wani abu da zai saka mata zargi a zuciyarta ba shi yasa ma ta zata ita kadai ce a zuciyarsa. Da ace ma aure zai kara abun ba zai

dameta sosai ba domin ta san shi din yana da damar auren mata hudu, amma sam wannan sakonnin basuyi kama da na neman aure ba.

Tabbas zina sukeyi da wannan yarinyar domin ko a cikin hirararrakin da ta gani sun kai a kirasu da zinar sannan kuma ga hotuna da suke nuna cewa a aikace ma an aikata zinar. Ga shi shi din mutum ne mai ilimin addini balle tace bai san hukuncin hakan ba, to me hakan yake nufi? Gashi dai ita kadai ce lamabar da taga ana wannan hirar da ita, duk ragowar hirarrakin wadanda suka shafeshi ne na aiki da kullum.

To kenan ba wai neman mata da yawa yakeyi ba wanna Sucre din ita kadai yake nema? Ko kuma dai itace wadda yake yayi yanzu? To yaushe Mukhtar ya zama haka?

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta fada a fili saboda tambayoyin da take bukatar amsarsu sun fara cika mata kai. Nan da nan zuciyarta ta karye, ta muttsuke ido tana fatan ya zama mafarki take amma ta gane idonta biyu.

Bata san tsahon lokacin da ta dauka a haka ba sai ji kawai tayi ana kiran assalatu, ta gyara zama ta kafa tagumi tana kallon fuskar Mukhtar. A hankali ya bude ido ya dan bi dakin da kallo har ya hangota a kan kujera, ya yi mata murmushi ya fara kokarin tashi zaune.

Ta mike tsaye cikin sanyin jiki ta karasa kusa dashi tana fatan Allah ya taushi zuciyarta kada ta yi abinda bai dace ba a halin da suke ciki.

Ta dafe shi tana fadin

‘Ka tashi a hankali Habibi, likita yace kada kayi motsi da karfi har sai an tabbatar babu inda yake maka ciwo.’

Ya karasa zama ta saka masa filo a bayansa tana yi masa sannu. Ya gyara zama sosai yayinda ta janyo kujerar kusa da gadon ta zauna tana kokarin kaucewa hada ido dashi. Jim kadan ya kira sunanta

‘Safee.’

Ta dago ta kalleshi ba tare da ta amsa ba

‘Kuka kika yi ko?’

Ta goge kwallar da ta makale a idonta tana murmushi tace

‘A’a don dai yanzu na tashi daga bacci ne.’

‘Wani mai adaidaita-sahu ne ya shigo min garin na kauce masa na je na daki fitilar dake gefen titi. Ina jin dai babu wanda na juwa ciwo ko?’

Ta gyada kai tace

‘Eh, kai kadai ne kuma muna fatan da sauki.’

‘Alhamdulillah, babu ma inda yake min ciwo yanzu sai hannuna, ina jin kuma buguwa ce kawai.’

‘Eh haka likitan yace da aka kawo masa x-ray din hannun.’

Ya zuro kafafunsa kasan gadon ya mike tsaye, nan da nan itama ta mike ta matso. Yayi murmushi ya mika hannu alamar ta bashi hannunta, tana saka masa hannun ya jata jikinsa yana dariya

‘Ai zan iya tsayawa da kaina, kuka ya kare ko? Tunda mijin Safiyya bai mutu ba.’

Ta zame jikinta tana fadin

‘Ka bari dai na kirawo likita ya dubaka.’

Ta kakalo murmushi tayi masa sannan ta wuce kiran likitan tana share kwalla.

Haka dai suka karasa jinyar tana ta yake tana daurewa, da ya daga wayarsa Sai gabanta ya fadi balle ma taga yana murmushi yana duban wayar. Sai taga kamar da Sucre suke zantukan banza. Sai bayan azahar sannan aka sake dubashi aka sallamesu.

Suka tattara suka koma gida.

MATAR MUKHTAR

Written by:

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA BIYU

02

Tunda suka koma gida take ta daurewa amma zuciyarta ta kasa sakewa da shi, yake kawai take shi kuma yana harkokinsa kamar yanda ya saba. Idan ya ganta cikin damuwa sai ya zata ko don bashi da lafiya ne take cikin damuwa don haka yake ta kokarin nuna mata ya sami lafiya.

Bai san ta bude sakon Sucre ba don bai ma kula da sakon ba, bayan ya bude wayar dai tayi masa sako tana tambaya

‘ni ka share ko?’

sai yayi mata bayanin ya yi hatsari a mota. Suka cigaba da hirarsu daga nan don haka bai ma san da wancan sakon da Safiyyan ta bude ba.

Kwanansu biyu da fitowa daga asibiti ya koma aiki.

Haka suka cigaba da rayuwa, shi bai ce mata komai ba ita kuma bata ce masa komai ba. Gaba daya ma tsoron ta tayar da zancen take musamman da ya cigaba da rayuwarsa kamar babu wata mace sai ita.

Bata taba jinsa yana waya da wata mace da sunan soyayyaba kuma bai taba nuna mata akwai wani abu da yake boyewa ba shi yasa ma bata damu da kulle wayar da yakeyi ba, yana bude wayar ne da yatsansa ko kuma ya zana pattern. Cikin kwana biyu ta faki idonsa ta haddace pattern din da yake bude wayar don haka da ta sami dama sai ta bude wayar ta duba sakonnin shi musamman da Sucre.

Suna nan suna cigaba da hirarrakinsu na batsa yayinda ita take cigaba da turo masa hotunta na rashin kunya a duk lokacin da ya bukata.

Duk wanda ya kalleta ya san tana cikin damuwa amma banda Abban Nurain, kallonta ne baya yi ko kuwa tsabar ko-in-kula ne oho. A haka har akai sati biyar da fitowarsa daga asibitin.

.....

Kamar kullum ta jera masa abincin safe a kan kafet wajen karfe takwas da rabi na safe. Yana shan shayi ita kuma tana zaune a gefensa tana kallon kasa tana kuma wasa da kafet da yatsunta.

‘Safee.’

Ya kira sunanta.

Ta dago suka hada ido alamar amsa kiransa.

‘Wai me yake damunki ne?’

‘Babu komai, me ka gani?’

Ta bashi amsa tana murmushi.

‘Kwana biyun nan baki da wani aiki sai tunani, jikinki ne kawai a nan zuciyar tana can tana wani wasiwasi na daban.’

Ta dan yi yake kadan

‘Umm! Babu komai, yau da gobe dai kawai ka san jiki da jini’

‘Yau da goben nan dai Allah ya sa ta lafiya ce, ko kuma na ce idan tayi wari ma ji.’

Ta dan yi dariya yayinda shi kuma ya sa yatsa ya lakace mata hanci yana dariya, ta tashi ta fara kwashe kwanukan da ya gama cin abinci. Tana yi tana jin zafinshi a ranta; wato don rainin hankali ma sai yau ya kula bata cikin walwala tunda shi yane tare da masoyiyarsa.

.....

Kamar yanda ya saba duk shekara yana zuwa taron karawo juna sani wanda ake yi duk shekara wato ICAN annual conference, wannan karon ma shirin tafiya taron yakeyi. An riga an basu kudin registration da kudin mota daga office don haka ya gama duk wani shiri na zuwa taron wanda za a yi a Abuja. Ta riga ta san da taron kuma ta san bai taba zuwa da ita ba, wanda akayi tana amaryane ma ta so yaje da ita kuma tun lokacin ya nuna mata ba zai iya ba saboda transport ga kudin kama hotel sannan kuma baya son ya dinga tafiya yana barinta ita kadai a hotel room wuni guda; haka dai ya tsarata ta hakura. Don haka wannan ma bata sa rai ba, tana kallo yayi registration a computer dinsa.

Ya riga ya sanar da ita gobe litinin zai tafi don haka tun da rana ta hada masa jakarsa kamar yanda ta saba idan zai yi tafiya, duk wani abun bukata ta hada masa a jaka. Hatta kayan da zai saka da safen ma da takalminsa duk ta ware tunda ya gaya mata karfe bakwai na safe Aminu zai zo ya kaishi airport saboda jirgin karfe takwas da rabi zai bi.

Wajen karfe goma na dare suna kwance a daki, da yake bai gama abinda yake ba fitilar a kunne take. Hankalinsa yana kan wayarsa yanata ‘yan karance-karancensa yayinda ita kuma take kwance ta rufe idonta amma ba bacci take ba, yanayi yana sosa mata tafin kafarta da yatsunsa na kafa.

Hankalinta baya wajen saboda yanda kwakwalwarta take caji; yanzu haka ma wannan tafiyar tare da Sucre din zasu je, ko kuma sai yaje can zai nemi wasu matan oho. Ta dai san masu neman mata sun saba yin tafiya su bar iyalansu a gida su tafi su kama hotel su kwana da matan banza, ta sani ma ko ‘yan matan nasa suna da yawa.

Ta gyara kwanciyarta a karo na babu iyaka, ya rankwafo kadan ya hura mata iska a kunne, tayi firgigit

‘Aaah!’

Yayi dariya

‘Haka kawai zaki dinga yi min labe da sunan bacci.’

Ta sake gyara kwanciyar

‘To kanata sosa min kafa ina zan iya bacci.’

Suka sake yin shiru ya mayar da hankalinsa kan waya.

Jimawa kadan ta mike zaune ta dubeshi, shima ya dubeta yana dariya yana fadin

‘Kin fasa baccin kenan zaki taya ni hira ko kuma kewata kika fara tun yanzu kike kare min kallo?’

Ta sunkuyar da kai tace

‘Hmm! Don Allah kai da wa zakuyi tafiyarnan?’

Ba tare da ya kalleta ba yace

‘Ni da sauran ma’aikata mana.’

Suka sake yin shiru na dan lokaci.

‘Mukhtar.’

Ta kira shi da sunansa wanda ba haka ta saba kiranshi ba. Ya sauke wayar da yake dubawa a kan cikinsa ya dubeta sannan ya amsa

‘Yes.’

‘Ita Sucre din sai kun je can zaku hadu kenan?’

Tambayartata ta shammaceshi don bai san ta san da Sucre ba balle har ya sa rai ta san tare da Sucre za su tafi, nan da nan fuskarshi ta canza. Ya tashi zaune da hanzari har wayar da ya ajiye a kan cikinsa ta fado kasa, ya dauke wayar ya ajiye a kan durowar gefen gado tare da tattaro nutsuwarsa sannan ya juyo ya kalleta. Yayi wani gyaran murya kamar na mara gaskiya tare da kara tsuke fuska

‘Me ya hadaki da wayata har kika yi min bincike? Daman shi ya sa kwana biyu kika sa kanki cikin damuwa ko?’

Ya tsagaita yana saurarenta.

Ta tashi zaune sannan tabe baki da kyar cikin tsananin damuwa ta dubeshi tace

‘Idan ka amsa min tawa tambayar in sha Allahu nima zan amsa maka taka.’

Ya kalleta a wulakance ya ja tsaki mai cike da takaici sannan ya bata amsa

‘Tare da ita za mu sai me, me zaki iya yi a kai?’

Ranta ya kara baci, zuciyarta ta harzuka kwarai, take hawaye ya fara bin fuskarta ta fara hasbunallahu wa nimal wakeel a zuciyarta.

‘Babu abinda zan iya yi a kai sai dai nace Allah ya kiyaye hanya kuma na tuna maka itama ‘yar wanice ubanta yana sonta yana son ya kare mutuncinta kamar yanda kake son kare mutuncin Nana, sannan malamai sun tabbatar mana zina bashi ce idan ka shiga zuri’ar wani da ita sai an shiga taka.’

Ta kalleshi da idanunta da suka riga suka ciko da hawaye, suka hada ido, zai yi magana ta daga masa hannu sannan ta mayar da hannun ta dafe kirjinta da a yanzu yake mata zafi tace

‘Allah ya yafe maka, kada Allah ya nuna min ranar da wani zai yiwa Nana abinda kakeyi da ‘yar wasu.’

Ya harzuka sosai ya mike daga kan gadon ya tsaya a jikin wardrobe yana mata wani kallon wulakanci da takaici

‘Kin yi min bincike a waya kuma kin sani a gaba kina gaya min maganganun banza kina nema ki aibata min ‘ya saboda tsabar wulakanci ko Safiyya. Toh Allah ya baki sa’a ki cigaba da bincika min waya watarana za ki ga abinda zai sa zuciyarki ta buga.’

Ta bude baki zata yi magana ya nuna mata kofar yace

‘Ki fice min daga daki tunda kin gama rashin kunyar kafin yanzu ki sa na buge miki baki.’

Itama da yake ta gaji da jan zancen kuma ba son ganinshi take yi a halin yanzu ba kawai sai ta sauko daga kan gadon ta dauki wayarta ta fice daga dakin tana share hawaye.

Dakinta ta wuce kai tsaye, tana shiga ta turo kofar ta sa mukulli ta rufe da yake yaran suna wajen Hamida suna baccinsu a dakin baki.

Ta zauna a gefen gado ta zuba fuskarta a tafukan hannunta tana kuka, hotunan da ta gani na tsiraicin Sucre ne a wayarsa suke dawo mata da kuma maganganun batsar da yake aika mata da su. Yanzu wannan mutumin da take kallonsa a matsayin mutumin kirki shine ya aikata wannan badalar kuma wai ita yake son ma ya dorawa laifi.

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta share hawaye ta cigaba da kuka, sai da ta gaji da kukan sannan ta mike ta yiwo alwala. A kan dadduma ta zauna ta dauki kur’ani ta bude don ta karanta domin bata jin kafafunta za su iya daukarta tayi tsaiwar Sallah.

Duk yanda take son tayi karatun kur’ani ta kasa saboda yanda bata gani sosai, gaba daya hawaye ya hanata gani sosai. Dole ta rufe kur’anin ta ajiye, ta cigaba da share hawaye. A hankali ta mike tsaye ta kabbara Sallah, tana yi tana kuka har ta samu nutsuwarta ta dawo. Nan a kan daddumar bacci ya dauketa bayan ta idar da sallar.

…….

Tana fita daga dakin ya ja tsaki ya koma ya zauna a kan gadon ya dafe kansa. To yaushe Safiyya ta duba masa waya har taga sakonnin Fatima wadda yayi saving sunanta da Sucre don ya badda kama, in dai yana cikin gidan baya kiranta itama bata kiransa don haka ya san tabbas sai dai idan ta Whatsapp Safiyya taga sakonnin su. To yaushe ta gani?

Maganar da suka yi jiya ma ya tura mata kudin jirgi don ta sameshi a Abujan suna gamawa ya goge, don haka yake mamakin yanda akayi Safiyyan ta san tare za su tafi.

Yayi tsaki ya dunkule hannunsa ya naushi daya hannun dashi.

Maganganunta sun so suyi tasiri a kansa musamman da ta sako batun Nanansa, amma shi wane irin sakaci ne zai sa ya bar Nana ta yi jami’a a wata jihar da ba a nan yake ba sannan ya barta ta zauna a hostel. Ya jijjiga kai, ba yadda za ayi ya bar Nana tayi nisa da gida kamar Fatima(Sucre).

Shekararsa daya da auren Safiyya ya hadu da Fatima. Yar Zariya ce karatu ya kawota jami’ar Bayero ta Kano, basu da dangi a Kano don haka dole ta kama hostel ta zauna duk da ba haka mahaifiyarta ta so ba amma da yake mahaifinta ya goya mata baya dole ta kyaleta. Tun bata saba da Kano ba suka hadu da Mukhtar don haka shi ya dinga daukarta yawo yana nuna mata gari har ta saba.

Soyayya mai karfi suka kulla har yayi mata alkawarin aure, don haka ta saki jiki da shi matuka.

Ita din ba lalatacciya bace don haka da fari soyayya suke mai tsafta, duk inda take so zai je da kanshi ya kaita kuma duk abinda take so zai saya mata. Har Zariya yake kaita gida idan aka yi hutu don haka ya gaisa da mamanta sun san juna.

Bai taba boye mata yana da mata ba itama kuma bata da matsala da auren mai mata musamman da yake tana tsananin son Mukhtar din.

A hankali ya saba da rike mata hannu daga nan ya saba da rungumarta yana tsostsar bakinta yadda yake so. Sai da ta saki jiki ta saba da wannan sosai sannan ya fara daukarta su fita da daddare, idan suka gama cin abincinsu sai ya kama daki a hotel ya lallatseta sannan ya mayar da ita hostel. A haka har ya kai ga biyan bukatarsa a kanta inda shi kansa ya san a budurwa ya sameta.

Ta so ta daga hankalinta amma da yake shi din mutum ne da ya iya tsara zance sai ya lallabata ya nuna mata ai shine zai aureta wanda jira kawai yake ta gama karatu

kafin nan aurenshi da Safiyya ya kwana biyu don haka ba za a ce komai ba. A hankali ya mayar da ita kamar matarsa, sai dai kawai ya kama musu daki idan ya gama da ita ya mayar da ita hostel. Da yake yana amfani da condom sai ya zama a bata tsoron samun ciki.

Bai san tsawon lokacin da ya dauka yana zaune yana tufka da warwara ba har dai ya gaji ya tashi ya kwanta, ba zai canza tsarin da yayi ba don ya riga ya gama komai itama yayi mata booking jirgin, sai dai ita jirgin karfe goma ya kama mata don ko daya baya so a gansu tare. Haka ya kwana yana juyi yana tunani, bai so ba Safiyya ta gane alakarsa da Fatima sai dai babu yanda zai yi. Idan ya dawo ya san yadda yayi ya tsarata, amma dole sai ta daina yi masa bincike don ya san in dai bata daina ba to zasu cigaba da samun matsala.

.....

Duk da bata yi baccin kirki ba kuma ranta a bace yake amma haka ta tashi tun kafin karfe shida don ta hada masa abincin safe. Idan zai fita da sassafe baya iya cin abinci da yawa don haka ruwan shayi kawai ta dafa ta soya masa kwai ta hada da burodi wanda ya siyo tun dare ta ajiye masa a falo inda ya saba cin abinci.

Wajen shida da rabi ta ga kamar lokaci zai kure bai fito ba don haka ta wuce dakin don ta duba kada taje ko makara yayi. Da sallama ta shiga dakin, yana zaune a kan ‘yar kujerar gaban mudubi ya gama shiryawa tsaf yana dube-dube a waya. Bayan ya amsa sallamarta ya dubeta sau daya ya dauke kansa ya cigaba da abinda yake yi a waya, ta karasa ta zauna a gefen gadon ta inda yake zaune. Ta kakalo murmushi tace

‘Ina kwana Abban nurain.’

Ba tare da ya kalleta ba ya amsa a takaice

‘Lafiya.’

Ta kula shi a dole fushi yake yi da ita, bata so yayi tafiya suna halin fushi da juna don haka ta sake kakalo murmushi tace

‘Baka fito kayi breakfast ba, kada ka makara.’

Ya kalleta zai yi magana sai kuma ya fasa ya cigaba da abinda yake yi, jim kadan ya ajiye wayar a kan mudubin ya dubeta yace

‘Kin dafa ne?’

Ta daga masa kai alamar eh. Ya mike ta bi bayansa suka fice daga dakin. Bayan ya zauna ta kunna socket din TV da yake akwai wuta, ta mika masa remote sannan ta zauna a gabansa tana hada masa shayi.

Yana cikin cin abincin ya ajiye kofin shayin ya dubeta yace

‘Nurain da Nana basu tashi ba?’

‘Eh.’

‘Za su tashi kenan suga bana nan.’

Tayi murmushi tace

‘Ma yi maka waya.’

Bayan ya gama cin abincin ya dubeta yace

‘Akwai kudi a cikin durowa, idan kuna bukatar wani abu sai kiyi min waya ko ki kirawo Saifullahi ko Aminu.’

‘To.’

Ta tashi ta fara kwashe kwanukan, kafin ta gama kwashe kwanukan wayarsa tayi kara bayan ya gama amsawa ya mike ya shige dakin.

Tana fitowa daga kicin shi kuma ya fito daga daki yana rataye da jakarsa ta matafiya da wayarsa a hannu.

‘Aminu ne ya zo, za mu wuce.’

Ta karasa inda yake tana murmushi ta danyi dage da yake ya fito tsawo sosai; ta sumbaci lebansa tace

‘Allah ya kiyaye hanya.’

‘Amin.’

Ya fada yana yi mata murmushi a karo na farko tunda garin ya waye. Ya ja hannunta suka fito har kan baranda sannan ya dan tsaya ya dubeta yace

‘Ki kula da gidan da yaran kuma ki daina sawa kanki damuwa, sai munyi waya.’

Tayi murmushi, suka yi sallama ya nufi waje ita kuma ta koma ciki.

.....

Gaba daya ranar haka ta wuni a kwance, zuciyarta babu dadi. Duk da ta san taro ya tafi amma zuciyarta tana gaya mata da wata zai kwana, ta kasa cire tunanin daga zuciyarta kuma ta kasa gamsar da kanta cewa shi kadai zai dinga kwana a hotel.

Sunan Sucre kawai zuciyarta take maimaita mata, ta kasa ganewa ma yarinyar musulmai ce ko kuwa? Tunda duk hotunan da ta gani nata tsirara take. Haka tayi ta gyara kwanciya tana share hawaye, zuciyarta sai tafasa takeyi ta rasa wanda zata gayawa taji sanyi. Har azahar bacci yaki ya dauketa duk da yanda take jinsa, kuma da yake ta gayawa Hamida bata jin dadi duk ta rike mata yaran babu wanda ya nemeta.

Sai wajen karfe biyu da ta tabbatar bacci ba zai iya saceta ba ta tashi ta zauna a kan gadon ta tankwashe kafafu ta zuba tagumi.

Gidansu take son zuwa ta gayawa Ummanta ko zata ji sanyi a ranta, sai dai kuma bata son ta dorawa Umman damuwa. Don haka ta fasa, gara ta je ta gayawa Yaya Hajiyayyaye tunda ta san duk wata shawara zata samu daga gareta.

Take ta sauko daga kan gadon ta shiga bandaki domin tayi sallah ta shirya ta tafi.

MATAR MUKHTAR

Written by:

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA UKU

03

Saida ta idar da sallah ta ci abinci sannan tayiwa Hamida sallama ta bar mata yaran ta wuce gidan Yaya Hajiyayyaye.

Da yake karfe uku ta wuce lokacin da ta isa tana shiga taci karo da yaran gidan suna tafiya islamiyya, sukayi mata sannu da zuwa suka wuce. A falo ta sami Yaya Hajiyayyayen tana jin rediyo. Bayan sun gaisa ta dubeta tace

‘Ya na ganki ke kadai ina yaran nawa?’

Tayi murmushi

‘Suna gida, da yake Hamida tana nan kuma ba dadewa zanyi ba.’

‘To Allah ya sa dai lafiya, na ganki firgai-firgai.’

Tayi dariya ta kau da kai

‘Lafiya kalau Yaya, zuwa dai nayi.’’

‘Cikine dake ko?’

Tayi dariya

‘Wallahi ba wani ciki Yaya.’

Kiran sallar la’asar ne ya katse musu hirar, suka tashi gaba daya sukayi sallah.

Tana zaune a kan daddumar da ta idar da sallah a dakin Yaya Hajiyayyaye yayinda Yaya Hajiyayyayen take zaune a kan daya daddumar inda itama ta idar da tata sallar. Ta shafa addu’arta bayan ta idar da azkar ta dubi Yaya Hajiyayyayen tace

‘Bari na tashi na koma.’

Ta kalleta tana murmushi

‘Uhm, ai baki gaya min abinda ya kawo ki ba.’

Tayi yar dariya. Tana mamakin yanda Yaya Hajiyayyaye take karantarta sosai, ta san ko da tace mata babu komai bazata yarda ba duk da ita din ma bazata tafi ba tare da gaya mata ba. Sukayi shiru na dan lokaci, jimawa kadan ta dubi Yaya Hajiyayyaye tace

‘Dama Abban Nurain ne?’

Ta mayar da hankalinta gaba daya kan Safiyyan sannan ta bata amsa

‘Me ya faru da Abban Nurain din?’

Ta kau da kai ta share kwallar da ta taru a idonta, ta rasa dalilin da yasa in dai ta tuno wannan bakin cikin sai tayi hawaye.

‘Yaya wai ashe Abban Nurain yana neman mata ban taba sanin ba sai kwanakin nan.’

Ta kama haba tana mamaki

‘Ke Safiyya, kin san me kike fada kuwa? Kada fa kije ki bata aurenki a kan wani zargi na banza da wofi.’

Ta sake share kwalla sannan ta bata amsa

‘Yaya wallahi ba zarginsa nake ba, da idona na gani a wayarsa kuma dai wadannan abubuwan da na gani basuyi kama da na mai neman aure ba wallahi sai dai mai aikata zina.’

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta taso daga tata daddumar ta dawo daddumar da Safiyyan take zaune ta zauna a gabanta tana kallon fuskarta

‘To ai kinga abinda ake gudu ake hana mata duba wayar mazajensu, yanzu da can tunda kuka yi aure da baki duba ba kinga kuna zamanku lafiya. Haka kawai yanzu kinje kin bincikowa kanki abinda zai hanaki sukuni.’

‘Ni fa ba bincike nayi masa ba Yaya, kuma ma da ban yi masa binciken ba ai tunda mukayi auren nake fama da ciwon sanyi. Ke kanki fa sau biyu kina karbo min

magani, duk gidan da naje bana shiga bandaki saboda a zatona a nan nake samo ciwon. Sai faman kame-kame nake ashe shi yake kwasowa ya shafa min. Tsabar idona ya rufe kuma zuciyata babu zargi shi yasa ma ban kawo komai ba don wani lokacin ko gaya masa bana yi saboda kada ransa ya sosu.’

Nan dai ta bata labarin yanda akayi ta gane da kuma kadan daga cikin irin sakonnin da ta ji ta gani. Hajiyayyaye ta bude baki tana tafa hannu da mamaki domin gaba daya basu taba zaton Mukhtar zai aikata wani abu mai kama da wannan ba. Suka yi shiru na dan lokaci, jimawa kadan ta cigaba

‘Kuma fa da nayi masa magana jiya da daddare cewa yayi duk abinda zanyi naje nayi.’

Ta kama haba tana mamaki

‘Subhanallahi! Shi Mukhtar din ne ya fada miki haka?’

Ta jijjiga kai tana share kwalla.

‘Kai jama’ah! To ai shi yasaka dai ake hanaku duba wayar miji domin ita wayar miji kamar albasa take, in dai za ki duba to zakiyi kuka. Kuma da yake baki da wayo sai kika yi masa maganar ai dama kin taro rigima.’

Ta kalleta ta kawar da kai don ta fuskanci Yaya Hajiyayyaye so take ma tace laifin nata ne, bata ma tunanin yanda za ayi ya daina so take kawai tayi mata fadan yi masa bincike.

‘Kenan yanzu shi bashi da laifi, nice nayi laifi da naga abinda yakeyi kuma nayi masa magana?’

Ta kamo hannunta tana kallon fuskarta

‘Ba haka bane tabbas yana da laifi to amma ya zakiyi da shi? Ko babu komai dai kin san shine yake da shugabanci a kanki don haka ma ba zai saurareki ba. Kuma ma idan banda abinki mazan yanzu ai duk haka suke, sai dai kawai kiyi ta hakuri.’

Ta zare hannuwanta duka biyun ta share hawayen da kawo yanzu ta bari yana zuba ba tare da wani shamaki ba

‘Yanzu kenan haka zan zauna ina ji ina gani ya dinga raba mana kwana ni da matan bariki, kuma duk cutar da ya debo ya zo ya shafa min ba yanda na iya.’

‘A’a ba haka bane, ai kema ba zama zakiyi ba. Dagewa za kiyi ki ta addu’a kina sadaka, sannan kuma duk inda kike da gazawa sai kiyi kokari ki gyara. Don wani mijin matar ce take sa ya fara yawo saboda halinta. Ki kara tsafta da kula da jikinki sosai, kuma ki dage da kwalliya. Wajen kwanciyar auren ma kuma ki kara dagewa, duk abinda kike jin yana bukata kiyi masa. Kin san wasu matan basa zagewa su sarrafa miji a wannan lokacin shi yasa za kiga wasu suna bin matan kwararo.’

Ta jijjiga kai cike da damuwa tace

‘Wallahi Yaya ina iya kokarina, duk wani abu da kike tunani ina yi tsabar fitna ce kawai da wulakanci. Kuma ma yanzu mutum sai kace jahili idan matsala ce ba zai yi magana mu gyara ni da shi ba sai yaje ya fada sabon Allah. Kuma ace wai nayi hakuri!’

‘To kinga dai ni yanzu ba hurumina bane nace zan yi masa magana, ki cigaba da hakuri ki dinga addu’a in sha Allahu zai daina. Kuma kin san tunda ya aureki ai yana sonki shi yasa ma bai auri su matan barikin ba, ki kwantar da hankalinki ki cigaba da addu’a ki rungume mijinki.’

Suka yi shiru na dan lokaci. Zuwanta wajen Yaya Hajiyayyaye Bai bata amsoshin tambayoyin da ke kanta ba sai ma kara mata wasu tambayoyin a kan nata. Allah ya sani tana iya kokarinta wajen duk abinda ya shafi aure, bata taba gazawa wajen biya masa bukata ba ko a wanne yanayi take ciki. Idan tana shayarwane kawai wani lokacin dole suke raba daki saboda bata son kwana da yaro da miji a gado daya saboda tarbiyya. Idan ta gama biyan bukatarsa sai ta barshi ta koma dakinta inda ta kwantar da yaran ta karasa kwanan. Kuma ta san yana samun gamsuwa da ita sosai tunda ita din gwanar gyara ce musamman yanzu da ta kara sanin dabarun gyaran. Ta yi ajiyar zuciya ta kawar da kai tana fadin

‘Umm! Allah ya kyauta.’

‘Amin Safiyya, Maza kam yanzu sai addu’a kowanne da irin ta sa matsalar sai dai kawai ka sami mai dan dama-dama. Ki cigaba da hakuri kina lallabawa in sha Allahu zai bari.’

Shigowar yara daga islamiyya ne ya katse musu hirar, da gudu Mujahid da Sulaiman suka fada jikinta da yake sune kanana suna kiran

‘Anti Safiyya mun dawo baki tafi ba.’

Ta taresu da dariya tana fadin

‘Dama jiranku na tsaya yi idan na gaisheku sai na tafi.’

Abdallah, Amina da Fariha da yake sune manya suka tsuguna suna gaisheta. Bayan ta amsa gaisuwarsu ta mike tana fadin

‘Yaya bari na tafi yanzu za ki ji Magriba.’

Tayi sallama da yaran suka fito ita da Safiyyan , suka tsaya a bakin gate Yayan ta dubeta tace

‘Kiyi hakuri Safiyya kin ji ko? Ki guji yin fito-na-fito da shi maza basa son haka sannan kuma basa so kina matarsu ki dinga gaya musu laifinsu. Idan abin ya ci tura dai kya iya neman mahaifiyarsa ki gaya mata cikin hikima idan ta fahimceki sai ki ga ta tsawatar. Amma kada ma ki bari wannan ya zamar miki wani abun damuwa.’

‘To Yaya, nagode.’

Sukayi sallama, har ta kusa fita gate Yaya Hajiyayyaye ta kirawo sunanta. Ta waigo ta dawo tana sauraronta

‘Kada fa ki je kina gayawa wani wannan zancen, don ba abin yadawa bane in ba haka ba sai ki sayowa kanki raini a dinga kallonki banza-banza.'

Tayi ‘yar dariya

‘Babu ma wanda zan gayawa Yaya ballema tunda ga yanda mukayi dake in sha Allahu babu wanda zai ji.’

‘Yauwa akwai wasu kayan gyara da na saya daga Sokoto, gobe in sha Allah za a kawo su. Da na karba zan dibar miki ki kara ki kara dagewa sosai, zai bari in sha Allah.’

Sukayi sallama ta tafi gida zuciyarta a jagule.

Tun da safe da ya sauka a Abuja Fatima ta kirawo shi ta sanar da shi cewa tana da test gobe da safe don haka zata canza ticket dinta sai ta biyo jirgin Talata da karfe sha biyun rana. Hotel din da ya sauka yana da nisa da wajen da ake Taron don dama haka yake yi, in dai zai taho da wata baya kama hotel kusa don yawancin bakin nan kusan suke sauka. Baya so ya sauka a kusa don kada a dinga ganinsa da mata daban-daban, duk da dai matan da yake mu’amala da su basu wuce uku ba ko ma biyu.

Ranar farko ba wasu abubuwa ake yi a conference din ba, sai dai ana bawa kowa dama su karasa registration su karbi kyautarsu wadda ake bawa duk wani wanda ya halarci taron don haka iya abunda yayi kenan ya koma masaukinsa. Sai da zai kwanta sannan ya kirawo Safiyya suka dan taba hira, bayan yayi mata sallama Kuma ya shiga hira ta Whatsapp da ‘yan matansa.

Kanta cike da tambayoyi ta dawo daga gidan Yaya Hajiyayyaye, tana shiga Nana ta makale mata saboda kusan ranar gaba daya basu hadu ba. Dole haka ta hakura ta zauna wajen yaran da Hamida, suna kallon TV suna hira har akayi Isha suka ci abinci ta kwantar da yaran. Sai da ta kulle gidan ta rufe ko ina sannan tayi sallama da Hamida wadda take falo tana kallo, ta shiga daki ta kintsa ta kwanta.

Maganganun da sukayi da Yaya Hajiyayyaye ne suka dinga yi mata yawo a kwakwalwa. Kenan ma laifinta ne da ta ga abinda yake yi, shikenan yanzu babu yanda za ayi da shi haka za ta zuba masa ido yana raba mata kwana da karuwai? Duk wani abu da miji yake bukata a wajen mace tana yi iya kokarinta, amma tayi alkawarin zata cigaba da addu'a da kuma sadaka kamar yanda Yaya Hajiyayyaye tace mata. Haka ta kwana da takaici saboda yanda zuciyarta take tuna mata yana can a rungume da wata 'yar iska. Ko da ya kirawo a waya da daddare sai da tayi kamar bazata dauka ba amman dai haka ta daure ta dauka tayi kamar babu wani abu suka taba hira.

.....

Haka ta hakurkurtar da zuciyarta ta cigaba da rayuwarta, musamman da taga damuwarta tana nema ta shafi mu'amalarta da yaranta. Tana addua sosai saboda tanaso ta dawo da nutsuwarta kafin ya dawo daga Abuja domin bata so ta rasa mijinta.

Shi kuwa Mukhtar tunda Fatima ta isa Abuja ya sake shiriricewa domin kullum idan ya gama hidimar conference din haka zai koma hotel din su kwana suna lalacewarsu.

.....

Ranar alhamis da safe ya kirawo Safiyya a waya bayan sun dan taba hira ta kirawo Nurain da Nana suka karbi wayar suka gaisa da Abbansu sunata yi masa labari. Bayan ta karbi wayar ta sallami yaran ta kara a kunnenta tace

‘Gobe za ka dawo ko?’

Yayi gyaran murya sannan ya bata amsa

‘No, sai jibi. Akwai wani mutum da nake son gani to yace sai Saturday da safe in sha Allah by Azahar na gama sai na biyo jirgin karfe hudu.’

Ta danyi shiru sannan tace

‘Um! Allah ya nuna mana.’’

‘Akwai matsala ne?’

‘A’a babu komai muna nan muna jiranka.’

Yayi dariya, sukayi sallama suka ajiye waya.

Ya juya ya dubi Fatima wadda take kwance a bayansa tana murmushi yace

‘Shikenan kin ji dadi ko? Za mu kara kwana dayan in ya so ranar Asabar sai mu tafi da yamma.’

Ta matso jikinsa tana dariya

‘Ko kai fa Baby na, ai ma tafi a nutse.’

Suka yi shiru na dan lokaci.

‘Um, komai dai sai an tambayi Madam nima dai na kusa na shigo daga ciki.’

Yayi dariya ya lakace mata hanci

‘Kwarai kuwa ga dakinki ga nata.’

‘Ka ga daga wannan session din saura semester daya na gama, itama don ina da spill over ne. Idan aka yi hutu na tafi Zariya sai ka turo a zo ayi gaisuwa ai ko?’

Ta bi fuskarsa da kallo kamar a nan zata karanto amsar

‘Haka za ayi in sha Allah, ko babu komai mu huta da buya da satar hanya.’

Suka yi dariya gaba daya.

Tunda suka gama waya da Abban Nurain damuwarta ta dawo sabuwa, wannan kara kwanan da yayi ya tabbatar mata ba shi kadai ya tafi Abujan ba. Ko da yake dama ai bai boye mata ba da ta tambaya. Ta kasa sukuni gaba daya, sai can wajen shabiyu na rana tayi masa waya ta sanar da shi tana son suje gidan Ummanta ita da yaran. Ba tare da wani musu ba da yake dama bai fiya hanata fita ba yace sai sun dawo. Don haka ko abinci bata iya tsayawa sun ci ba tace su tafi idan sun je gidan Umman sa ci.

Har sun fito Hamida ta tuna mata akwai jakar da ta cika da kwancen kayansu wanda za a kaiwa Umman ta bayar don haka ta koma ta dauko suka tafi da ita.

Suna shiga Umma ta hau hidima da jikokinta, suna ta zuba shagwaba irin yanda suke so. Tuwon shinkafa miyar taushe aka dafa don haka nan da nan aka zuba kowa ya sa hannu ana ci ana hira.

Ana gama cin abinci aka tashi don yin sallar azahar, Umma ta shiga dakinta don yin Sallah nan da nan Safiyya ta bawa Hamida umarnin ta jire mata yaran ta bi bayan Umman. Bayan sun idar da sallah Umma ta shafa addu’arta ta juyo ta dubi Saffiyan tace

‘Tunda kuka zo bakinki yake motsi, Allah ya sa dai lafiya kuke.’

Ta Kalli Umman ta koma ta sunkuyar da kai

‘Lafiya kalau Umma.’

Umman ta kalleta suka hada ido alamar tana dai sauraronta. Ta kau da kanta ta bude baki a hankali tace

‘Abban Nurain ne Umma.’

Da mamaki tace

‘Me ya sami Abban Nurain din?’

Kafin ta fara magana kwalla ta kwace mata, ta share kwallar sannan tace

‘Umma mata yake nema harda wadda take turo masa hotunanta tsirara.’

Ta zaro ido tana tafa hannu

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun! Amma yaron nan ya bani mamaki kuwa, ya za ayi yayi haka gashi kamar mai ilimin addini. Kai jama’ah! Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Suka yi shiru na dan lokaci Safiyya tana cigaba da share hawaye, Umma ta katse shirun tace

‘Anya kuwa Safiyya kin tabbatar, ke wa ya gaya miki? Kada fa ki sa zargin a cikin aurenki ga mijinki da kokari kuma yana nuna miki duk wata kauna da kulawa.'

Ta share kwalla tayi kwafa, kowa yana kyautata masa zato basu San shi babban mai ta’asa bane.

‘Wallahi Umma da idona na gani a wayarsa, kuma da nayi masa magana cewa yayi duk abinda zan yi a kai naje nayi.’

Umma ta rike haba cikin matsananciyar damuwa

‘Ikon Allah! Shi Mukhtar din dai? Kai maza basu da tabbas.’

Suka sake yin shiru na dan lokaci, Umma ta gyara zama tace

‘To ke me ya kaiki ma kika bincika masa waya? Wannan shine dalilin da yasa ake hanaku binciken wayoyinsu tunda yanzu waya ta riga ta zama fitna ga ma’aurata. Shi bincike ma gaba daya a wajen musulmi bashi da alkhairi ka dinga bibiyar mutum har ka ganowa kanka tashin hankali.’

Wannan fadan binciken da ake yi mata shi yake kara bata mata rai, ta hadiye malolon da yake makogoronta da kyar sannan tace

‘Umma ba fa bincike na yi masa ba.’

Ta bata labarin yanda akayi taga sakonnin sannan tace

‘Kuma fa Umma da na gaya masa ce min yayi duk abinda zanyi naje nayi.’

‘To me kike so yace Miki? su maza ai dama basa karbar laifinsu shi yasa da kin sani ma shiru kika yi masa kawai ki bishi da addu’a.’

Ta share hawaye

‘To Umma ni yaya zanyi, haka zan cigaba da zama da shi yana yawon zina?’

‘To ya za kiyi? Ina fatan dai kin san mutuwar aure ba zabi bane ko? Duk mace da kika gani a dakin miji hakuri takeyi da shi, mazan yanzu kuma in dai harkar matace sai dai kawai mu bisu da addu’a. Ke dai ki tabbatar duk wani hakki na aure kin sauke masa Kuma ke ma ki samo dabarun da zaki janye hankalinsa daga kan matan banza.’

Hawaye kawai take sharewa, wajen Umma ne karshen inda zata kawo maganar nan amma gashi ba wata mafita; nema kawai ake a dora mata laifi. Ta zata ma akwai wata dabara tasu ta manya ko kuma Umman zata sa Yaya Habibu yayi masa magana tunda yanzu shine waliyyinsu tunda ba ran Abbansu. Allah sarki Abba ta san da yana raye da tabbas sai ya samar mata mafita, ba zai barta ta cigaba da rayuwa cikin kunci ba.

Ummace ta katse mata tunanin tana fadin

.....

Ku taho muje telegram mu karanta har karshe.

N800 kacal 😍

Send to

7037834664

Opay Digital Services

Sakina Muhammad Yazid

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA HUDU

04

Magana da Ummanta bata kara mata komai ba sai tsananin damuwa, ranar haka ta kwana tana kuka gashi gobe zai dawo. Haka ta bawa kanta hakuri kuma tayi alkawarin zata bi shawarar Ummanta da Yaya Hajiyayyaye; zata kara dagewa da addu’a kuma duk wani abu na gyara da kulawa da miji zata sake mayar da hankali a kai.

Sai la’asar yace mata zai dawo don haka ta san abincin dare zai ci, tun sassafe suka fara aiki ita da Hamida. Suka yi cake mai dadin gaske don ta san yana son snacks irin haka wanda take ajiye masa a dakinsa ya kwana biyu yana ci; suka hada kunun aya sannan tayi tuwon semovita da miyar kubewa danya don shine abincin da yafi so musamman da daddare.

Kafin la’asar sun gyara gidan tsaf sai kamshin turaren wutarta ne yake tashi, ita da yara kowa fes. Sai wajen karfe biyar da rabi ya iso gidan, kaninsa Saifullahi ya kawo shi. Bayan sun gaisa ta kawowa Saifullahi cake da kunun aya sannan suka gaisa, ya dubi cake din yace

‘Maman Nurain ai wannan kayan dadin juye min abuna zakiyi in tafi in dinga ci a hankali kada su kare da wuri.’

Ta yi dare tace

‘Uhm, wato yau tun kafin a fara cin abincin ake santi Allah ya so dai akwai makari a bayan kujerar.’

Shima dariyar yake yi yana fadin

‘To ai abincin naki ne matar Yaya kullum mai dadi kike girkawa babu kama hannun kishiya.’

Ta harareshi tana dariya, ya sa hannu ya toshe bakinsa yana fadin

‘Au ashe an hana ni wannan maganar.’

Ta mike tana masa dariya saboda ta san in dai ta biye masa haka za ayi ta hira ana dariya, ta sami roba ta zuba masa kunun ayar da cake din a leda. Yana karba yayi mata sallama ya fice ita kuma ta wuce daki wajen Abban Nurain.

Yana zaune a gefen gadon ya tokare hannuwansa ta baya yana hutawa ta shiga da sallama tana dauke da cake da kunun aya a tray, ya riga ya bawa su Nurain chocolates din da ya siyo musu don haka sun fice wajen Hamida ta bude musu.

Da fara'a ya amsa sallamarta ta karasa ta ajiye kayan hannunta a kan durowar gefen gado tana dubansa tana murmushi. Haushinsa take ji saboda yanda ya tabbatar mata shi da wata suka tafi Abuja suka kwana biyar suna aikata sabon Allah Amma babu yadda zata yi, dole ta danne zuciyarta ta kara fada murmushinta.

Ta fara zuba masa kunun aya tana yi masa sannu da zuwa.

Da fara'arsa yake amsa mata saboda bai ma zata zai sameta haka da walwala ba saboda yanda suka rabu. Ya karbi kunan ayan daga hannunta ya kai bakinsa yayinda ita kuma ta zagayo ta zauna a gefensa. Saida ya shanye kunun ayan sannan ya dago ya dubeta yace

'Ya na sameku da yaran?'

'Lafiya Alhamdulillah, ya taro da gajiyar hanya?'

Nan suka dan taba hira jimawa kadan suka jiyo kiran sallar magriba don haka ya tashi ya yiwo alwala ya wuce masallaci.

.....

Haka Safiyya ta mayar da komai ba komai ta hakura, kuma a hankali sai taga kamar abun ya wuce. Komai na Abban Nurain ya koma kamar yanda ya saba, dama kuma bai taba fashin kwana a gida ba sai idan yayi tafiya kuma bai fiya yin dare sosai ba a waje.

Karkarin dadewarsa ya kai sha daya na dare, ya kan ce mata yana tare da abokansa su Shamsuddin; wannan bai fiya damunta ba saboda ta san shi da yawan abokai. Yanzu ne ma ya fara damunta tunda zuciyarta ta fara zargin ba wajen abokan yake ba wajen matan banza yake zuwa.

Duk wani abu da ta san zai kara musu kusanci yanzu shi take yi, lallaba shi kawai takeyi. Kuma kawo yanzu ta fara ganin kamar hakan ya sa ya daina kula matan banza.

Tunda ya dawo daga Abuja ta faki idonsa ta haddace pattern din da yake bude wayarsa da shi, don hak duk lokacin da ta faki idonsa ta kan samu dama ta bude wayar ta caje tas. Bata kara ganin messages din Sucre ba wanda da alama gogewa yayi, amma ko cikin contacts dinsa ma da ta duba babu sunan Sucre kuma babu wani sabon suna don haka ta dan sami nutsuwa kwana biyu. Duk lokacin da zata faki idonsa ta bude wayar tasa idan ta duba Whatsapp bata samun wasu hirarrakin na ‘yan mata sai hirarrakinsa da suka shafe shi. Ta gode Allah da ta dauki shawarar Ummanta bata cigaba da fada da mijinta ba don yanzu haka ma ya rabu da yarinyar.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA BIYAR

05

.....Suna fitan ta koma ta zauna, kafin ta gama gyara zamanta wayarta ta fara waka don haka ta mike ta dauko wayar.

Tana kallon screen din wayar ta fara murmushi, kawartace Karimatu Jibril Saminaka. Tare sukayi karatu a KADPOLY, bayan sun gama kuma aure ya dawo da su Kano gaba daya wanda ita Safiyya dama 'yar Kano ce karatun ne ya kaita Kaduna.

Tana murmushi ta kara wayar a kunnenta

‘Kawata ta kaina.’

Kamar nai gaggawa ta bata amsa

‘Um kawata ya weekend? Ki bude Whatsapp na turo miki message, ki duba yanzu don Allah.’

‘Allah kawata, bari nayi sauri ma gaisa a can.’

‘Yauwa.’

Ta ajiye wayar tana dariya ta san yanzu haka wata gulmar ce take son yi mata kuma maigidanta yana kusa, don sun saba haka. Ta dauko katin da aka siyo mata tun safe ta sa a wayar sannan ta sayi data din MTN ta naira dari biyu, nan da nan kuwa ta kunna ta hau Whatsapp.

Mintuna kadan sakonnin suka gama shigowa, a kan idonta sakon kariman ya shigo don haka nan da nan ta bude.

Video ne guda daya sai kuma rubutaccen sako a kasan video din

“Wannan ba Abban Nurain bane?"

Gabanta ya fadi, bugun zuciyarta ya kara sauri yayinda ta zaku sakon video din ya gama sauka. To shi kuwa Abban Nurain me ya faru da shi Karima take tambaya?

Kafin ta bawa kanta amsa videon ya gama sauka ba tare da bata lokaci ba ta bude, tana kalla bugun zuciyarta yana kara gudu hawaye yana bin fuskarta.

Tabbas Abban Nurain ne, yau ne ma wannan don kayan da ya fita dasu ne kuma bai taba saka su ba sai yau din.

A tsaye suke sun kallon juna rike da hannun juna sun ta hira cike da matukar nishadi, ba a dai jin me suke fada saboda da alama daga nesa kadan aka dauki video din kuma a karkace ma wayar take. Ya kamo hannunta ya sumbata yayinda suka cigaba da magana, jimawa kadan kuma ya janyo kwankwasonta ya mannata a jikinsa suka yi murmushi sai kuma ya saketa suka kama hannun juna suka bar wajen.

Ta share hawaye ta sa hannunta na hagu ta dafe kirjinta

‘Innalillahi wa inna ilaihi rajiun.’

Ta fada a fili. Wato Mukhtar gaba abun nashi yake yi tunda yanzu ta kai a kwararo ma yake rungumar ‘yan mata. Ta sake kunna video din ta kara masa girma ta karewa fuskar yarinyar kallo; tabbas wannan itace Sucre. Ashe basu rabu ba goge lamabarta yayi kawai don yaudara?

Shigowar wani sakon na Karima ne ya katse mata tunani, ta dago wayar ta kalla. Hotone guda daya don haka nan da nan ta saukeshi. Suna zaune a kan kafet tare da wasu ‘yan matan gaba daya sun sha kananan kaya, ga cake nan an yanka har ya dauka zai sa mata a baki. Da alama birthday ake yiwa ita Sucre din.

Wani rubutaccen sakon ya shigo

“Safiyya ko ba Mukhtar bane wannan?”

Ta share hawaye, sai yanzu ta tuna ya kamata ta tura amsar sakon don haka ta rubuta ta tura

“Shine Karima, haka ya mayar da kansa.”

Kafin minti biyu wayar Karima ta shigo, kamar ba zata daga ba sai kuma ta canza ra’ayi. Me zata boye mata bayan ta riga ta ga komai, don haka ta amsa wayar ta kara a kunnenta. Kafin tayi magana Karima tace

‘Safiyya wanna karuwar yarinyar da take tare da Mukhtar fa? Na dai san ba kara aure yayi ba don babu mutumin da zai fito da matarsa a haka.’

Ta share hawaye

‘Um Karima ba wani aure wallahi tsabar wulakanci ne da rashin tsoron Allah. Kin san ban taba sanin mutumin nan yana neman mata ba Karima sai kwanaki lokacin da nace miki yayi hatsari a mota; wallahi sai a lokacin na sani kuma wannan yarinyar ce dai.’

Da mamaki ta bata amsa

‘Ikon Allah! Kin ganmu birthday din Jawad muka zo yi a Minjibir park kawai sai ganinsu nayi, Ina jin birthday yake mata. Yanzu haka ma gasu can sai wani iyayi suke babu ko kunya, ko da yake bamu taba haduwa ba nima a hotuna na sanshi.’

A halin yanzu bata cikin yanayin da zata iya wani bayani saboda yanda zuciyarta ta cunkushe, don haka tace

‘Uhm! Ki bari kawai Karima, za muyi waya zuwa gobe in sha Allah za ki ji bayani.’.....

Domin jin yanda take kasancewa, ki turo kudin karatu

N800

7037834664

Opay Digital Services

Sakina Muhammad Yazid

Sai ki turo receipt ta wannan lambar

07037834664

BABI NA BIYAR ya sauka da zafinsa a telegram, BABI NA SHIDA yana tafe in an jima da yamma in Sha Allah.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA SHIDA

06

Ta sake kunna video din tana kallo kamar wadda take neman wani abun a ciki. Wato dama inda za shi kenan ya ce mata daurin aure zai tafi? Wato birthday ma yakewa budurwa? Tun kafin aurensu tana yi masa happy birthday wataran harda ‘yar kyauta amma shi kullum nuna mata yakeyi birthday babu kyau a addini don haka ita in nata yazo sai dai kawai yace mata happy birthday. Tunda sukayi aure ma baya ko tuna ranar haihuwar tata har abun ya daina damunta, amma shine ya kwashi budurwa bayan gari yana mata birthday.

Ta jefer da wayar a kan kujerar ta mike tsaye tare da dora hannunta a ka, ihu take so ta kurma ko zata ji sanyi a ranta amma bata so ta tarawa kanta mutane. Ta koma ta durkusa a gaban kujerar tana share hawaye. Wai dama haka ake auren? Shikenan yanzu ya daina sonta sai matan banza? Shikenan yanzu haka zata kare sauran rayuwarta?

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta fada a fili tana ajiyar zuciya, ta kwantar da kanta a jikin kujerar tare da runtse idanunta, ta cigaba da ambaton Allah don taga alama idan ta cigaba da tunanin nan zuciyarta zata buga gaba daya. Tana nan a haka dabara ta fado mata, ta tashi ta koma kan kujerar ta dauko wayar ta fara laluben Abban Nurain din a WhatsApp.

My love shine sunan da tayi saving lambarsa da shi, ta kalli sunan ta ja tsaki. Ta fara rubuta masa sako

‘My love.’

Sai da aka dauki mintuna kamar uku sannan ya bude sakon, ba wai don yana so ya bude sakonta ba sai don ya san idan bai bude ba yanzu zata kirawo shi. Yana karantawa ya turo mata da amsa

‘Yes matar Mukhtar.’

Ta ja tsaki a fili. Ta budo videon da Karima ta tura mata ta tura masa, minti biyu taga alama ya bude videon. Tayi murmushin takaici ta rufe Whatsapp din, dama so take ta tabbatar ya gani in ya so idan ya dawo ya ji bayanin ta.

Tana shirin mikewa daga wajen ta jiyo shigowar su Rukayya ta dawo da su Nana, tayi sauri ta goge fuskarta ta amsa sallamarsu.

Suna shiga falon nana ta fizge daga hannun Rukayya ta fada jikinta da gudu tana kuka tana fadin

‘Mama kitso ne!’

Ta dauketa ta rungume tana bata hakuri. Jamila ta dubeta tace

‘Anti kema fuskarki kamar kinyi kukan kitson.’

Tayi yake tace

‘Kawata ce mijinta ya rasu yanzu muka gama waya shi yasa kika ganni a birkice.’

Cikin tausayawa tace

‘Allah sarki, Allah ya ji kanshi Anti. Bari na tafi maggi zan siyowa Ummanmu.’

Ta fice ta barta a nan da yaran.

……

Tunda ya bude videon nan da Safiyya ta turo masa ya shiga rudani, ya kalli samarin nan da suke zaune nesa kadan yaga harkarsu sukeyi kawai. Saurayi da budurwar nan ma suna nan makale da juna, ga masu yiwa yaro birthday yanzu ma su rawa sukeyi. Samarin nan da suke zaune kasa kan ciyawa kuma sun tafi daga inda suke lokacin suna tsaye shi da Fatima.

To waye ya dauki wannan video din ya turawa Safiyya? Duka mutanen dake wajen ma babu wanda yayi kama da wanda Safiyya ta sani, to ya akayi ta sami wannan video din? To ko sakawa tayi a dinga binsa?

Ya gaza amsa tambayoyin don haka ya dubi Fatima yace

‘Ya kamata mu tafi ko? Kada magriba tayi mana a hanya.’

Ta kara kwantowa a jikinsa yayinda ya fara wasu waige-waige yana gyara zama

‘Gaskiya ne Baby, ka ga zamu je shopping.’

Nan da nan suka fara hada kayansu suna zubawa a mota, ba tare da bata lokaci ba suka bar wajen suka kamo hanyar Kano.

Motar Mukhtar na tashi Karima ta ja tsaki ta dubi Suwaiba wadda suke tare tace

‘Aikin banza mugu kawai, ya cuci kawata.’

Suwaiba tace

‘Ai kam, da kin sani dai baki gaya mata ba.’

‘Ba wannan tsakaninan da Safiyya dole na gaya mata ko don ta san irin zaman da zata yi da shi. Kana yawo a gari wai kai me miji ashe miji duk ya gama yin tsirara a wajen marasa mutunci. Mtsewww!’

‘Ki bari kawai Ya Karima, Allah ya sauwake.’

Received at 10:43 AMReactions: □ 3, □ 1

Viewed 103 times

Suka cigaba da hidimarsu.

Sai wajen karfe tara na dare sannan Mukhtar ya mayar da Fatima hostel ya kamo hanyar gida, hakan ma don ya kasa natsuwa sosai ne tunda Safiyya ta tura masa video din nan. Ji yake kamar ana binsa ana daukar mata hotunan abinda yakeyi.

Fatima ta so ya mayar da ita Zariya da kansa amma haka ya tsarata ya bata kudin mota a kan sai ya zo Zariyan. Yana tuki yana ta tunani kala-kala; tabbas idan Safiyya ta nemi fitnarshi yau din nan sai ta gane kurenta. Kuma sai ya ji dalilin da yasa ta sa ake binsa, dole sai ya koyawa yarinyar nan hankali don fitnarta ta fara isarsa. Ta sa masa ido daga tayi masa bincike sai kuma ta sa a fara binsa, ai dole ma ta canza hali in ba haka ba wallahi zai ci mutuncinta. Ya gama tanadin duk wani wulakanci da zai yi mata idan ya koma gidan.

A falo ya sameta tana zaune tana kallon tashar Zee World. Da kyar ya kakalo sallama sai wani muzurai yake yana shakar numfashi da kyar, tana kallonsa ya bata dariya. Ta danne ta fadada fara’arta ta amsa sallamarsa tare da yi masa sannu da zuwa. Ya amsa yana ta wasu muzurai, ya wuce dakinsa. Ta tashi tana ‘yar dariya ta wuce kichin ta dauko ruwa kamar yanda ta saba idan ya dawo ta bi shi dakin. Ya riga ya shiga bandaki don haka ta ajiye ruwan a kan durowar gefen gado ta zauna tana jiransa, jimawa kadan ya fito daga bandakin ya wuce ya fara kokarin canza kaya ba tare da ya kalleta ba.

Sai da ta bari ya gama saka kayan sannan ta zuba ruwa a kofi ta tsaya a gabansa ta mika masa tana fadin

‘Sannu da zuwa, ya gajiyar biki?’

Fuskarsa take kallo shi kuma yana ta kokarin kauce hada ido da ita, ya karbi ruwan yana fadin

‘Alhamdulillah.’

Ya wuce ya zauna a gefen gadon ya kurbi ruwan ya ajiye a kan farantin, ta karaso ta zauna a kusa dashi tace

‘Na sa maka abincin dare?’

Ya fara wani waige-waige kamar mara gaskiya, kafin yayi magana tace

‘In kuma kaci kayan dadi a wajen dinner na bar tuwona mayi dumame.’

Yayi sauri yace

‘Eh, ma ci dumamen.’

Gaba daya ma shi ya manta ashe ma ce mata yayi za suje dinner din auren da suka daura da safen. Ta mike tsaye tana fadin

‘Bari naje na shirya na zo na kwanta.’

Kafin ya bata amsa ta fice daga dakin, ya bi kofar da kallo yana mayar da numfashi.

Gaba daya tayi masa kwarjin ya kasa yin fadan da ya shiryo zai yi, ya yi zaton zata fara tsiwa amma sai ya ga tayi kamar bata ga video din ba. To me yake faruwa ne? Ya fi so tayi rigima yanda zai yi mata kaca-kaca ya juya laifin kanta amma gashi ta basar.

Yana nan zaune ta dawo sanye da rigar baccinta tana rike da wayarta. Yana nan zaune a inda ta barshi, bayan ya amsa sallamarta ta karasa ta zauna a kusa da shi tace

‘Ba yanzu za ka kwanta bane Abban Nurain.’

‘Eh, sai an jima kadan.’

‘Kafin nan nayi nisa a bacci.’

Ta zagaya ta kwanta a daya barin gadon daga bayansa, ta warware abun rufa ta rufe kafafunta. Ta gyara kwanciya ta juya masa baya, kwallar da take rikewa ta gangaro, ta ja abun rufar ta faki idonsa ta goge.

Ta riga ta gane duk ranar da yayi irin wannan fitar ba zai kulata ba saboda an riga an biya masa bukatar a waje, a da kafin ta gane abinda yake yi ta zata gajiya ce ta sa idan dai yayi dare bai dawo ba to baya bi ta kanta amma yanzu ta gane.

Yanda taga ya shigo gidan yana muzurai ya sa ta canza shawara, gara tayi kamar bata san an yi ba ta zuba masa ido taga iya gudun ruwansa. Ta riga dai ta gane muzuran da yakeyi duk don kada tayi wani wargi ne, to ta kyaleshi itama ta yarda yau kwanan Sucre ne ba nata ba. Kwalla ta sake gangarowa ta kara gogewa.

Ta jiyo kukan nana ta farka daga bacci tana yi tana kwala kira

‘Mama.’

Kafin ta karasa mikewa Abban Nurain ya juya ya dubeta yace

‘Ga Nana can tana kiranki.’

‘Hmm! Na ji ta, yau rigima take ji Allah ya sa ta barmu muyi bacci.’

Ta sauka daga kan gadon ta dauki zaninta wanda yake ajiye a cikin wardrobe din dakin ta daura a kan rigar bacci ta fice.

Received at 10:43 AMReactions: 1, ❤ 1

Viewed 101 times

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA BAKWAI

07

Ta so kwarai da gaske ace Mukhtar ne zai mayar da ita gida don tana so ya kara gaida Mommy taji daga bakinsa cewa nan da karshen wata zai turo maganar aurensu, amma babu yanda zata yi don ya nuna mata aiki ba zai barshi ba. Tun dare ta hada kayanta, kafin karfe takwas na safe ta bar hostel ta nufi tasha domin hawa motar Zariya. Karfe goma da ‘yan mintuna motarsu ta kama hanyar Zariya, da yake a jikin kofar motar ta zauna hanya kawai take bi da kallo tana murmushi; ta san bazata sake zuwa Kano ba sai a matsayin amaryar Mukhtar.

Duk da ta san da farko Mommy bata so alakarta da Mukhtar ba saboda yana da mata, takan ce ina jiye miki zaman kishi Fatima gara ki auri saurayi kya fi samun natsuwa. Amma da ta dage kuma shima Mukhtar din ya je suka gaisa da Mommyn sai ta yaba da hankalinsa.

Su biyu ne a wajen iyayensu daga wanta Ibrahim sai ita, wanda shekaru takwas ne a tsakaninta da shi. Shekarar da ta wuce akayi auren Yaya Ibrahim don haka Mommy ta sake kwallafa rai a kan lallai tana son Fatiman ma ta fitar da miji.

‘Ku biyu mahaifinku ya mutu ya bar min, yanda muka rabu da shi lafiya haka nake so kema na kaiki dakinki lafiya Fatima. Aurenki shine abu na karshe da zai faranta min rai.’

Haka Mommy take cewa duk lokacin da take maganar auren Fatima.

Ta kauda kanta daga kallon hanya lokacin da ta ji kwalla tana neman fitowa daga idonta sakamakon tunowa da Abbanta da ta yi. Abba yana sonta, yana matukar sonsu gaba dayansu ita da Yaya Ibrahim da Mommy. Ta sa hannu ta dafe kirjinta tana kokarin boye hawayenta saboda kada wadanda suke kusa da ita a motar su gane kuka takeyi. Mutuwa tayi musu yankan kauna, bata fi awa daya da gama waya da Abban ba ya gama yi mata fadan karatu yana cewa

‘Ki mayar da hankali ki gama karatunki kin kinji Fati, Allah yayi miki albarka.’

‘Amin Abba.’

‘To maza ki je kiyi karatunki nima yanzu Kaduna za mu tafi daurin aure, Allah ya bada sa’ar jarrabawa.’

Sukayi sallama ta cigaba da karatunta tunda dama jarrabawa za suyi da karfe uku na yamma. Tana fitowa daga jarrabawa taga labarin rasuwar Abbanta a status din wani Jamil dan wajen amininsa, take ta sumewa su Janan. Da kayar suka riketa ta kwana saboda yamma tayi kuma Mommy tace ta zauna sai gobe za a turo a dauketa.

Ana sallame sallar asuba ta kasa jira don haka ta kirawo Mukhatar ya kaita Zariyan; haka ta rasa jarrabawa biyu wadanda sune na karshe kuma sune suka janyo mata spill over don a lokacin tana ajin karshe ne.

Wannan shine karo na farko da ya gaisa da Yayanta da Kuma Mommy.

Allah dai yasa kada su Mukhtar su ja bikin da nisa don a yanzu kam ta fi Mommy matsuwa da ta zama matar Mukhtar.

Kafin azahar ta isa gida, babu kowa a gidan sai mai aikin Mommy Baba Habi don haka da suka gaisa sai kawai ta shige dakinta. Da yake ta sanar da Mommy dawowarta Baba Habi ta riga ta gyara mata dakin, sai ta haye kan gadonta sannan ta kirawo Mukhatar ta sanar da shi ta isa gida lafiya. Ta kwaso hira yace

‘Zan shiga meeting ne yanzun, idan na fito sai muyi waya.’

Da haka suka yi sallama suka ajiye wayar.

Sai bayan azahar Mommy ta dawo da yake malamace a makarantar ‘yan mata. Fatima ce tayi mata oyoyo ta karbar mata kayan hannunta ta raka ta har dakinta.

Suna shiga Mommy ta cire mayafinta ta ajiye a kan kujera sannan ta wuce ta zauna a gefen gado, ta dubi Fatima da take zaune a kusa da ita tana murmushi tace

‘Fatin Abba, an gama karatun ko?’

‘Na gama Mommy in sha Allah duk da dai spill over din nan sai ta rage min points amma ina sa rai da 2-2 ko mai sanyi ce.’

Tana murmushi ta dafa kafadarta tace

‘Babu komai Allah ya sa albarka, Allah ya nuna mana aurenki kuma.’

Tayi murmushi ta sunkuyar da kai, Mommy tace

‘Ina Mukhtar din?’

Received at 11:16 AMReactions: □ 3, 😁 1

Viewed 93 times

Koda suka gama hirar ma tana ajiye wayar ya ja tsaki ya mayar da wayar mazauninta ya ajiye.

Ta so ta bashi tausayi amma gaskiya ba zai iya aurenta ba, shi ba ya ma sha’awar zama da mace sama da daya. Kuma ko ta kama zai kara auren ma ba zai iya auren Fatima ba. Ya san shine ya bude mata ido don a budurwa ya santa, amma a yanzu ba zai taba amincewa shi kadai take bawa kanta ba duk da bai taba kamata da wani ba. Ba zai iya aurenta ba amma dai yana yi mata addua Allah ya bata miji na gari, don shi yanzu a rayuwarsa ma baya jin zai kara zuwa Zariya.

Ya karya mota ya shigar da ita farfajiyar gidansu bayan da Abbati dan autan gidan ya bude masa gate.

KARSHEN BABI NA BAKWAI

Received at 11:16 AM

4 people reacted with □

Viewed 90 times

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TAKWAS

08

Tunda suka yi waya da Karima take so ta sameshi ta bashi shawara ya kara aure amma bata sami dama ba, ta fi so sai tana cikin walwala shima yana cikin walwalar sannan tazo da maganar domin bata san irin amsar da zai bata ba. Tana so duk amsar da ya bata ta kwantar da kanta ta lallabashi wanda haka ba zai samu ba idan ita da shi basa cikin yanayi na walwala.

Sama da sati daya kenan da tura masa video din shi data yi, tun yana muzurai yana daure mata fuska har ya saki ya dawo yanda ya saba.

Ita kuma ba wai ta hakura bane tana nan tana tara shi ta fatan azo wata gaba da ta dace da zancen.

Tana shirin dora abincin dare wayarta tayi waka, tana dubawa taga Hamida ce. Da murmushinta ta amsa wayar

‘Yaya Safiyya ina wuni.’

Kafin ta bata amsa ta cigaba

‘Yaya na sami admission an bani English Education a BUK.’

‘Kai ma sha Allah, nayi miki murna sosai kuwa. Sai ki dage ki maida hankali ki fita da points mai kyau, Allah ya sa albarka.’

‘Amin Yaya, nagode. Bari na kirawo Yaya Hajiyayyaye.’

Kafin tace wani abu ta katse wayar saboda tsabar doki.

Dariya kawai tayi ta ajiye wayar a kan kujera, ba karamin dadi taji ba da Hamida ta sami damar yin degree. Da ita da Yaya Hajiyayyaye duka diploma ce da su, Yaya Habibu ne kawai me degree. Ita Yaya Hajiyayyaye ko JAMB batayi ba ma SSCE tana fitowa Abbansu ya nema mata diploma a Polytechnic ta Kano. Ita Kuma Safiyyan tayi JAMB har sai biyu ma mma makinta bai kai ba, ta tafi Kaduna gidan Baba Shehu kanin Abbansu kawai sai ya hadata da Sajida yarinyarsa ya samar musu admission a KADPOLY. Don haka a can ta zauna gidan Baba Shehu har ta gama diploma wato ND kuma tayi HND a fannin computer science. A can Kadunan suka hadu da Mukhtar ya je daurin aure ita kuma ta taso daga makaranta.

A da tana da niyyar ta koma tayi degree a nan BUK amma tana gama jarrabawar karshe aka yi bikinsu da Mukhtar, ita kuma bata sake tada zancen ba.

Babu wanda ya hanata haka kawai ta zabarwa kanta hakura da karatun domin tana ganin da ta gayawa Mukhtar din zai barta ta cigaba. Yanzu ma kuma tana ji a ranta idan ta sami dama zata yi masa zancen ko Allah zai sa tana da rabo ta koma tayi degree din.

Sai wajen karfe tara ya dawo lokacin yara sunyi bacci, tana zaune a falo tana kallon wani fim a MBC 2. Tayi masa sannu da zuwa ta karbi ledar hannunsa wadda ya siyo musu burodin safe yayinda shi kuma ya wuce dakin, da kyar ta dauke kanta daga kallon da takeyi ta dauki ruwa ta kai masa dakin.

Ajiyewa tayi ta fito tana kallo tana jera masa abincin dare, tana gamawa ta koma ta zauna ta cigaba da kallon. Tana jiyo fitowarsa ta hakura da kallon film din ta mayar tashar Aljazeera, ta riga ta saba indai yana zaune to ba a kallon fim saboda shi baya son fim daga labarai sai ball ko kuma wrestling. Idan ma ya zauna bata canza ba da kanshi zai dau remote din ya canza yana fadin

‘Ana nan ana ta kallon shirme.’

Don haka ma ta riga ta hakura da kallon TV, da rana ta kunnawa yara da daddare kuma shi yayi nasa kallon.

Yana zama ta tashi ta zuba masa abinci, yana ci suna dan taba hira har ya gama.

Yana kwance a kan gadonsa da waya a hannunsa ta shiga dakin da sallama, bayan ya amsa sallamar tace

‘Baka kwanta ba.’

Ya dubeta yace

‘Sai dai niyya.’

Ta wuce daya gefen gadon ta kwanta tana fuskantarsa, jim kadan ya ajiye wayar ya kalleta yayi murmushi yace

‘Kema ba baccin zakiyi ba ai kallo-kallo kika mayar da ni.’

Tayi dariya ta cigaba da kallon nasa, ya lakace mata hanci yace

‘Gobe zamuje mu kai kudin auren Saifullahi.’

Murmushinta ya karu tace

‘Kai ma sha Allahu, Allah ya sa albarka, Allah ya sa ayi damu. Saura Aminin Hajiya.’

‘Wannan ai da saura, kin san Baba ba zai barshi ya yi aure ba sai ya gama bautar kasa ya sami aiki ya shekara yana yi tukunna.

‘To Allah ya nuna mana ai kamar yau ne.’

Sukayi shiru shi ya cigaba da abinda yakeyi a wayarsa ita kuma tana kwance kawai tana tunani kala-kala. Jimawa kadan tace

‘Habibi.’

Ya kalleta yace

‘Ga ni.’

Tayi dariya tace

‘Nima ga ni.’

Shima dariyar yayi yace

‘Ina sauraronki.’

Ta mika kafarta ta fara sosa masa tafin kafa sannan tace

‘Kaima da auren ka kara kawai.’

Maganar ta shammaceshi matuka har saida ya dan razana. Ya dubeta da tsananin mamaki ya ga hankalinta a kwance yake murmushi ma takeyi, ya jijjiga kai sannan yace

‘Um! Haka nace miki ina bukatar karin wata matar?’

‘A’a, haka dai na gani.’

Ya bata rai sannan yace

‘To baki ga dai-dai ba.’

Tayi shiru kamar baza tace komai ba, jim kadan sai ta daure tace

‘Wannan yarinyar da kayiwa birthday last week ai ko itama da ka aura ku huta.’

A fusace ya ajiye wayar dake hannunsa a kan durowar gado, ya tashi daga kashingidar da yayi ya zauna don haka itama ta mike daga kwance ta zauna tana kallonsa tana mamakin yanda ya fusata daga magana. Hararta yake yi yana magana a fusace

‘Dole ki tsara min rayuwa tunda ke kika haifeni, shi yasa kika tura ana bibiyata saboda ki samu abinda za ki kafa min hujja da shi ko?’

‘Ni ban tura a bibiyeka ba, ina gida aka turo min video din, kuma naga yarinyar itace wadda take turo maka hotunanta tsirara shi yasa nace kuyi aure ku huta da buya kuna sabon Allah.’

Ya kara fusata

‘Shi yasa kika sakani a gaba zakiyi min rashin kunya ko? Kin..’

Ta katse shi a marairaice tana fadin

‘Ba haka bane Abban Nurain, kaida Allah ya bawa damar auren mace hudu idan ka kara daya ai ba zai zama matsala ba. Aure ai shine cikar burin masoya, tunda kuna son juna ku cika burinku mana kuyi aure ku huta.’

‘To tunda ke kika haifeni kiyi min auren dole mana?’

Ya fada a fusace. Ta sunkuyar da kanta sannan ta dago a hankali tace

‘Allah ya baka hakuri, dama gani nayi...'

Da hanzari ya katseta a fusace

‘Bana son jin abinda kika gani ki tashi ki fice min daga daki kafin ranki ya baci.’

Ta kalleshi taga yanda ya sha kuna yana nuna mata kofa, ta sunkuyar da kai ta share kwalla cikin sanyin murya ta fara kokarin mikewa tana fadin

‘Allah ya baka hakuri.’

Ta fice ta barshi a dakin yana huci. Tana shiga dakinta ta turo kofar ta zube a bayan kofar, kafafuwanta sun kasa karasawa da ita kan gadonta.

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Bata taba tsammanin wannan maganar zata bata ran Abban Nurain ba domin ita ta zata son yarinyar nan yakeyi tsakani da Allah, kuma ta zata zai yi farin ciki da ta kawo wannan shawarar amma ya rufe ido yana mata fada. Itama bata so ayi mata kishiya amma da ya dinga bin mata a waje gara ya auro uku su hadu suyi zamansu.

Ta gyara zama a nan bayan kofar ta tankwashe kafa ta ja zanin jikinta ta goge hawaye, tayi ajiyar zuciya. Ta daga hannuwanta tana kai kallonta sama

‘Allah Kai ne Allah, bani da wata dabara Ya Hayyu ya Qayyum Allah Ka kawo min mafita.’

Ta sauke hannuwanta ta share hawaye zuciyarta tana mata kuna saboda takaici. Jimawa kadan ta mike ta yiwa alwala ta zo ta tayarda Sallah, tun tana yi ba tare da ta san me take karantawa a sallar ba har ta fara samun nutsuwa. Kafin ta idar zuciyarta ta dan yi sanyi, tayi addu'ointa sosai, ta tashi ta sa yara a fitsari sannan ta kwanta.

.....

Ko da gari ya waye ma haka ya tashi yana fushi da ita don ko abincin safe bai ci ba duk da ta dafa, haka ya shirya ya fice suka tafi kai kudin auren. Sai dare ya dawo gidan, bayan tayi masa sannu da zuwa ta saka masa abincin dare, ya dai ci abincin amma har a lokacin fushi yakeyi da ita. Sai da suka kwashe wajen kwana biyar a haka, duk yanda ta kai ga kokarin kyautata masa ya ki ya daina fushi da ita. So takeyi ma ta je ta yiwa Hajiya Allah ya sanya alkhairi na kai kudin auren Saifullahi amma ta kasa tambaya saboda yanda yake fama daure fuska yana fizge-fizge.

Sai da aka yi wajen sati daya sannan taga kamar ya fara saukowa tunda yana dan tsayawa suyi hira.

Dawowarsa kenan daga office ya gama cin abincin da ta saka masa ya tashi daga falon ya shige daki ya barta ita kadai a falon, chatting takeyi a WhatsApp don haka bata bishi ba tayi zamanta. Bai dade da shiga ba aka buga gate, ta tashi ta fito ta tsaya daga ciki ba tare da ta bude gate din ba tace

‘Waye?’

Daga wajen aka amsa

‘Musa me wanki ne.’

‘Ana zuwa.’

Ta juyo ta dawo ciki ta wuce daki don ta kirawo Abban Nuraina yazo ya karba, haka ya sanar mata idan yana gidan aka buga kofa indai namiji ne ya fi so ta kirawo shi ya bude.

Babu takalmi a kafarta watakila shi yasa bai ji takun tahowarta ba har ta tura kofar corridor din da dakin yake ciki ta shiga, tana jiyo sautin muryarsa yana waya wanda ko ba’a gaya mata ba ta san da mace yake wayar saboda yanda yake ta kwantar da murya kamar me waka. Da sallama ta shiga dakin da yake kofar dakin a bude take ta jiyo kalmar karshe da yake fada

‘Kada ki damu Baby na yanzu zan zo.’

Ta karasa ciki yayinda shi kuma yayi sallama da wadda yake wayar da ita ya ajiye wayar ya dago yana dubanta ya amsa sallamarta. Tayi kamar bata ji me ya fada a wayar ba tace

‘Musa me wanki yana kiranka a bakin gate.’

Ya mike ya fara kokarin fita

‘Yauwa bari naje wankina ya kawo min.’

Yana wucewa ta juyo ta biyo bayansa ta dawo falon. Danne zuciyarta take tana ambaton Allah don bata so ta nuna masa ta ji wayar da yakeyi, to idan ta nuna masa ta ji ma babu yanda zata yi tunda dai duk alamu sun nuna ba zai iya dainawa ba. Ko wacece kuma Babynsa oho? Kullum addu’a take Allah ya yaye masa amma kullum canza salon kawai yakeyi, ko da yake shi a karan kansa baya so ya daina don haka zai yi wahala ya daina.

Ya shigo da kayan wanki a hannunsa ya wuce daki, Nurain da Nana suka bi shi a baya da gudu. Tana nan zaune ya fito a shirye tsaf yana baza kamshi su Nana suna biye da shi, ya dubeta yace

‘Zan dan je wata unguwa ne daga can kuma zan wuce gidan Hajiya.’

Ta dubeshi da fara’arta

‘A dawo lafiya, don Allah ka gaishe min da hajiya. Muma dai in sha Allahu gobe ma je da yara mu gaida Hajiya.’

‘To Allah ya kaimu goben.’

Ya fice ya barmata kamshin tuararensa wanda babu abinda yake kara mata banda takaici.

Tana ji tana gani ya fice ya tafi wajen wata wadda shi kanshi ya tabbatar ba auren ta zai yi ba.

Haka ta zauna a gidan nan ranta babu dadi tana ta tunanin mafita amma ta rasa.

Sai wajen karfe tara da rabi na dare ya dawo, tana rabarsa ta ji kamshi na daban a jikinsa. Bata san kamshin ba don tabbas ba kamshin turarensa bane kuma ba na Sucre bane don tun tuni ta gane kamshin turaren Sucre. Ya wuceta a falo ya shige daki zai canzo kaya, ta bi bayansa da kallo tace

‘Ikon Allah! An yi sabuwa kenan, Allah ya raba bawa da wahala.’

Haka ta kwana tana tunanin mafita bata samu ba, mafita daya ta rage mata shine ta kai kararsa wajen Hajiya in ya so ko auren ne su saka shi yayi. Amma gaskiya tana matukar jin kunyar Hajiya kuma tana ganin rashin dacewar kai karar da wajen mahaifiyarsa, amma kawo yanzu bata da wani zabi. Ta dai bari zuwa gobe taje wajen Hajiya taga idan zata iya dagewa ta fada mata don tana kyautata zaton Hajiyar zata samar mata da mafita.

KARSHEN BABI NA TAKWAS

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TARA

09

Tunda zai fita office ya bata kudin motar zuwa gidan Hajiya, ya sanar da ita idan ta shirya su tafi in ya dawo daga aiki zai samesu a can sai su dawo tare. Sai da tayi sallar la’asar sannan ta shirya su suka kama hanya.

Suna isa suka tarar da Inna a tsakar gida ita da masu aikin gidan saboda a ranar itace da girki. Inna kishiyar mahaifiyar su Mukhtar ce wadda itace amarya, tana da yara uku; Amina, Maryam da Habiba dukanninsu kuma kannen Mukhtar din ne. Nan ta zauna ita da yaran suka gaisa sosai da Inna sannan ta shige wajen Hajiya ta bar yaran a nan, wadanda tana wucewa suka bita da gudu.

A falo suka sami Hajiya tana zaune tana kallon TV yayinda Bahijja ‘yar danuwanta wadda take riko take ta ‘yan gyare-gyare a wajen.

Nan da nan aka hau hidima da su ita da yaran, Bahijja ta kawo musu ruwa da kuma cin-cin. Basu dade da zama ba Ummahani da Maryam suka dawo daga makaranta; Ummahani itace autar Hajiya da yake mata biyu ne da ita ita kadai ce ta rage batayi aure ba ita kuma Maryam ‘yar wajen Inna ce. Suna ajiye jaka suka dawo wajen Safiyya aka yi ta hira.

Sai can daf da Magriba sannan duk suka fice, ya zama babu kowa a falon sai Hajiya da Safiyya. Ta yi dan gyaran murya tace

‘Ashe kuma an kai kudin Saifullahi.’

Take fara'ar Hajiya ta karu tace

‘I, saifu girma ya zo in sha Allahu.’

‘Allah ya sa albarka, Allah ya sa muna raye kuma Allah ta nuna mana na

‘yan baya.’

‘Amin ya Allah.’

Suka yi shiru na dan lokaci.

Tun bata fadi komai ba ta fara neman birkicewa, da kyar ta tattaro nutsuwarta ta dan yi gyaran murya tana ta faman murza ‘yan yatsu kamar mara gaskiya

‘Umm, Hajiya shima Yayan da aure aka ce ya kara da ya fi.’

Maganar ta zo mata a ba zata, tayi firgigit tana dan zare ido

‘Me kika ce Safiyya, wanne Yayan ne zai kara aure Safiyya?’

Nan da nan ta birkice ta fara nadamar abinda ta fada, duk kunya ta kamata, ta kasa cewa komai saboda yanda Hajiyan ta tsattsareta da ido.

‘Mukhtar din ne shine zai yi auren amma sai yanzu nake ji.’

Ta daure a kunyace tace

‘A’a Hajiya, nice nace dama shima zai kara.’

Mamakin hajiya ya karu sosai, tace

‘Ke Safiyya wace mace kika gani tana cewa miji yayi aure, abinda sai idan babu yanda zaka yi. Ko dai akwai wata matsala ne ki gaya min sai a san abun yi.’

Ta muskuta cike da nadamar fara wannan zancen saboda yanda kunya duk ta lullubeta, da kyar ta lalubi muryarta tace

‘Hajiya dama wata yarinya ce da yake nema,suna tare kullum sai dai suyi ta waya ko kuma su fita tare. Na ce ya aureta mu zauna tare ya kama fada kuma yace ba zai aureta ba, amma kuma har yanzun suna tare. Shine nace ko za kiyi masa magana.’

‘Ikon Allah, Mukhtar din dai?’

Kai kawai ta gyada mata

‘To ai kuwa gara ya aureta idan ba haka meye manufar kana da matarka kuma ka bal-balce a wajen wata, kuma kai da ma ta gidan da kanta tace ka auro waccan.’

Suka yi shiru na dan lokaci. Sosai hajiya ta fahimci inda zancen ya dosa, duk da ta ga kokarin Safiyyan da ta tunkareta da wannan zancen. Sai dai kuma ta ji dadi da ba wani wajen take ba tazo nan wajenta, in sha Allahu zata yiwa tufkar hanci. Ta san tunda Safiyya tayi wannan maganar lallai ta rasa yanda zata yi da Mukhtar din ne domin kuwa shi mutum ne mai saukin kai sosai amma kuma idan yana son yin

wani abu to hanashi sai dai wani ikon na Allah ga kafiyar tsiya. Tayi gyaran Murya tace

‘Kada ki damu Safiyya, barni da shi kinji zai zo ya sameni. Ai musulmi muke ba arna ba dole yayi abinda Allah yace.’

Tayi ajiyar zuciya saboda yanda Hajiyan ta fahimceta ba tare da ta nuna mata wani abu ba.

Nan suka zauna Hajiya tana kara kwantar mata da hankali da bata shawarwari. Ana yin sallar Magriba ya shigo gidan, tana ta rokon Allah kada Hajiya tayi masa magana a gabanta sai taji shiru. Ya gaida Hajiya suka dan yi hirarsu sannan ya dubi Hajiyan yace

‘Bari naje wajen Baba, yanzu zan sauko sai mu tafi.’

Tace

‘Kada ma ka sauko yanzu, Inna ta dora abincin dare da su idan kunci gaba daya kwa tafi.’

‘To Hajiya.’

Ya amsa ya wuce falon sama inda nan ne bangaren Baban nasu.

_

Duk yanda Fatima ta so ta boye damuwarta a kan halin da alakarsu da Mukhtar take ciki ya gagara, tayi wani zuru-zuru ga rama. Da Mommy ta matsa mata da tambaya sai tace zazzabine yake damunta, don haka Mommy da kanta ta kai ta asibiti. Gwajin zazzabin malaria aka yi mata kuma aka samu akwai shi a jinkinta duk da likita yace ba mai yawa bane. Aka bata magungunan harda na karin kuzari, bata son shan magani don haka Mommy ce ta ajiye magungunan a wajenta. Idan lokacin

sha yayi da kanta zata kirawo Fatiman ta sata a gaba ta sha sannan ta kyaleta, don haka tana ji tana gani ta dinga hadiyar magungunan nan har ta shanye.

Ta gaji da kiran wayar Mukhtar baya dauka, kuma baya biyo baya. Ta kirawo abokinshi ma Suraj da yake tana da lamabrsa yace mata abokinsa yana nan lafiya aiyuka ne kawai suka yi masa yawa saboda an bashi deadline din gamawa, amma ya bata tabbacin zai sa yayi mata waya amma shiru har yau. Tun karshen wata take sa ran zuwanshi ko kuma ‘yan aikensa amma gashi yanzu har an shiga sati na biyu a wani watan shiru.

Tana idar da sallar azahar ta fito farfajiyar gidansu ta zauna a kasan bishiyar mangoro da waya a hannunta, Mukhatra din dai take son kira. Tana matukar son Mukhtar har bata jin zata iya rabuwa da shi, gara idan wani abu tayi masa ta bashi hakuri ya zo ayi auren nan a huta. Tun shekaran jiya rabon da ta kirawo shi duk da shekaran jiya ma bai dauka ba, ta rasa haushinsa take ji ko kuwa kewarsa take yi, gashi kullum dare da tunaninsa take kwana don wata ran idan ta tashi da suba sai tayi wankan tsarki sannan tayi sallah. Ta lalubo lambarsa zata kirawo sai kuma ta fasa, ta mike ta nufi cikin gida. A kicin ta sami Baba Habi tana shirin dora abincin dare, bayan ta amsa mata sallama tace

‘Baba Habi don bani aron wayarki na kira wata lamba, wayata taki kawo network.’

Ta nuna mata karamar wayar da take ajiye a kan tagar kicin din tace

‘Gata can ‘yar gidan Hajiya sai dai wayar tawa ina jin babu kati fa.’

Ta karasa ta dauki wayar tana fadin

‘Yanzu zan saka Baba, sai ma na rage miki.’

Ta juya ta fice ta bar Baba Habi tana ta godiya an ce za a saka mata kati.

Inda ta tashi nan ta dawo ta zauna ta tura kati wayar Baba Habi daga wayarta sannan ta kwafe lamabar Mukhtar a wayar Baba Habi. Yau zata gane wayarta ce Mukhtar baya dagawa ko kuma wayar kowa ma baya dagawa.

Kafin ta gama wannan tunanin wayar ta fara ringing take ta rike numfashinta tana fatan kada ya daga don idan ya daga hakan yana nufin itace baya son magana da ita ya daina daga wayarta yau kusan wata daya.

‘Salamu alaikum.’

Fes taji muryarsa daga daya bangaren yana mata sallama. A cikin sanyin murya ta amsa

‘Hm! Wa alaikumussalam.’

Da alamun mamaki a muryarsa yace

‘Fatima.’

‘Mukhtar.’

‘Fatima, Lafiya kike naji ki haka?’

‘Uhm, Lafiya kalau. Na ji ka shiru ne kuma naga baka daga kirana shi yasa na ari waya na kirawoka, Mommy tana ta magana saboda tun last month nace mata za ku zo ayi magana ban san me zance mata ba. Idan ka fasa aurena ne ai sai ka gaya min na nemi wani ko?’

Ta dan tsagaita shi kuma ya sami damar bata amsa cikin kwantar da murya

‘Ba haka bane Fatima kin gane ko? Kin san Hajiya bata so ayiwa Safiyya kishiya har yanzu ban shanyo kanta ba amma in sha Allahu ina sa rai idan Baba ya dawo daga Umra ya sa baki komai zai daidaita. Za mu zo ai kuma na gaya miki yanzu haka kwangilar da na samu ce aiyuka sun min yawa sosai shi yasa ko a waya bakya ji na.’

Tuni hawaye suka wanke mata fuska, ko wanda bai san Mukhtar ba yaji wannan maganar ya san wanda yake fadanta karya yake yi.

Ta cire wayar daga kunnenta ta zubawa madannan wayar ido, babu komai a kanta don ta rasa ma me zata tuna. Ta share hawaye ta danna ta katse kiran, ta saki wayar a kancinyarta tare da tata wayar da take daya hannun ta sa hannuwanta tana share hawayen dake bin fuskarta.

Da kyar ta tattara nutsuwarta ta tashi ta shiga cikin gidan cikin hanzari ta ajiyewa Baba Habi wayarta a kicin din ba tare da ta bari sun hada ido ba ta wuce dakinta.

Tana shiga dakin ta murza mukullin da yake jikin kofar ta ciki ta fada kan gado a rub da ciki. Ta saki kukan da take makalewa gaba daya harda shessheka, saida ta dauki lokaci tana wannan kukan sannan ta dan ji sanyi a ranta ta fara ajiyar zuciya. Ta tashi zaune ta zubo kafafunta kasa, ta saka tafukan hannunta ta rufe fuskarta; Ya za ayi Mukhtar yayi mata haka? Yanzu ba zai aureta ba kenan? Ta cire hannuwan daga fuskarta ta dora a ka, ba zata iya kirga sau nawa suka wuni da shi a hotel yana moreta ba, kenan ya ci bulus? Shi ya fara saninta budurwa kenan ya rabata da budurcinta yanzu duk wanda zai aureta sai dai ya sameta a haka? A yanda Mukhtar ya dinga nuna mata kauna bata taba zaton zai yi mata haka ba. Yanzu me za ta ce da Mommy wadda take jira a zo maganar aurenta? Ta sauke hannuwanta daga kanta, kwakwalwarta tana neman kullewa ta dakatar da tunanin. Ta sa hannuwanta ta dafe kirjinta lokacin da ta tuna cewa Mukhtar yana da hotunanta tsirara babu iyaka.

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta fada a fili lokacin da ta tuna har video dinta ya taba dauka tana tsaye a gaban mudubi a hotel din da ya saba kama musu tana ta rawa tana jijjiga jiki shi kuma yana dariya, gashi har fuskarta ya dauka a lokacin. Ko bayan dawowarta daga Kanon ma ta tura masa wasu hotunan nata Kuma duka harda fuska gashi tsirara;

don dayan a bandaki ta daukeshi tana wanka jikinta duk kumfa. Ta mike tsaye zumbur kamar wadda aka tsikara ta fara kaiwa da kawowa a dakin. Yanzu idan ya fito da hotunan ya nunawa wani fa? Ko kuma suka fito Yaya ko Mommy suka gani. Ta sake dora hannuwanta a ka tana fadin

‘Ka cuceni Mukhtar, ka cuceni? Ni ka mayar karuwa Mukhtar? Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Ta tsuguna a gaban gadon kamar me yin addua irin ta arna, hawaye yaki ya kare a idonta don haka ta gaji da sharewa. Ta juyo tsayuwar mota a tsakar gida wanda ya tabbatar mata Mommy ta dawo, gaba daya ma ta manta Mommy daga wajen aiki tayiwo mata waya ta sanar da ita sun wuce asibiti da Aisha matar Yaya Ibrahim zata haihu.

Kafin ta gama wannan tunanin ta jiyo takun Mommy ta nufo dakin don haka cikin sauri ta haye kan gadon ta kwanta ta kama goge fuskarta da zanin gadon.

Saida ta ji Mommy tana kokawa da hannun kofar sannan ta tuna ashe ta kulle dakin, ta tashi da sauri don ta san Mommy ta tsani jira kuma bata so ta dinga kulle kofar dakin ta karasa ta bude kofar. Da fara’arta ta shige dakin tana neman ture Fatiman tace

‘Kina in …..’

Ta bi fuskarta da kallo tana mamaki

‘A’a! Me ya sameki ne haka Fati kukan me kike yi.’

Ta kakalo murmushi ta kawar da jajayen idanuwanta tace

‘Ba kuka fa nake ba Mommy, kaina ne yake min ciwo.’

Da matukar mamaki tace

‘Ciwon kan ne kikayi kace-kace haka.’

Ta sunkuyar da kai tana kokarin boye kwallar da take shirin fadowa daga idanuwanta. Fitsarin da yake marar Mommy ne ya mintsineta don haka ta dan cije lebe, tun safe rabonta da fitsari gashi ta sha ruwa da yawa. Ta dubi fatiman tace Allah ya sauwake ta juya cikin sauri ta nufi nata dakin.

Tana fita Fatima ta rufe kofar dakin ta jingina da bayan kofar dakin ta daga kai sama tanawa Allah godiya da Mommy ta kyaleta ta tafi. Ta juya ta kalli kofar ta daga hannu sama kamar me addu’a tace

‘Allah ya sa kada ta kirawoni.’

Ta share kwalla a idonta ta koma ta kwanta a kan gadon tana fatan Allah yasa mafarki ne abinda yake faruwa. Bata dade da kwanciya ba akayi kiran sallar la’asar, har aka tayar da sallah a masallacin kusa da su tana kwance ta kasa tashi sai gyangyadi da yake kwasarta.

Tana nan kwance Baba Habi ta kwankwasa mata kofa tana fadin

‘Fatiti kizo inji Hajiya tana dakinta.’

‘To.’

Ta amsa daga ciki. Nan da nan ta mike ta sauko daga kan gadon ta nufi bandaki da niyyar ta fara yin alwala tayi sallah sai kuma ta tuna idan tayi jinkiri da yawa Mommy zata iya biyota har dakin don haka kawai ta fice daga dakin ta nufi dakin Mommy.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA GOMA

10

Tunda Safiyya tayiwa Hajiya maganar Mukhtar saida sati ya zagayo sannan Hajiyan ta sami damar yi masa maganar. Wajen karfe biyar na yamma ya shiga gidan yayi sa’a babu kowa a wajen Hajiyan sai ita kadai don haka ya zauna suna hira. Tayi gyaran murya tace

‘Ni kuwa wace ‘ya ce aka ce kana zuwa zance wajenta?’

Da mamaki ya kalleta don tambayar tata ta shammace shi

‘Hajiya zance kuma? Ni babu wajen wadda nake zuwa.’

‘Ka tuna dai domin kuwa wanda ya gaya min baka isa yayi maka karya ba.’

Ya kalleta suka hada ido, yanda ta tsattsareshi da ido yasan dole ta kawar kai

‘Hajiya nifa babu wata da nake zuwa zance wajenta.’

Tana so ta yarda da zancen bakinsa amma a sanin data yi masa yanayinsa in yana fadan karya daban be, ta jijjiga kai tace

‘To idan ma dai zancen kake zuwa ai ba wani abu zance maka ba, a matsayinka na namiji ai ka kai ka auri mata har hudu don haka idan kaje zance a halin yanzu babu laifi.’

Ya kalleta alamar mamaki don ya zata fada zata yi, har ya fara murmushi tace

‘Sai dai ka sani kasancewarka namiji Allah bai baka dama ka dinga kula ‘yayan mutane kana bata musu lokaci ba, kuma Allah ya sani bamuyi maka wannan tarbiyyar ba. Don Allah duk yarinyar da ka san ba aurenta zakayi ba ka rabu da ita, ka rabu da ita! Idan kuma aure zaka yi to ga mahaifinku can ka sanar dashi sai a hada da na Saifullahi. Ka kare mutuncinta ka kare mana namu mutuncin. Kuma ka duba kannenka mata gasu nan, ka duba ‘yarka Nana. Allah ya sauwake.’

Ta mayar da hankalinta ga kallon talabijin din dake kunne a falo. Yayi tsuru kamar wanda ruwa yaci, tabbas wani ya kawowa Hajiya gulmarsa kuma ya san ba kowa bane sai Safiyya. Ya mike tsaye

‘Bari naje wajen Baba.’

Ba tare da ta kalleshi ba tace

‘Sai ka dawo.’

.....

Suna zaune a falo ita da Nurain da Nana bayan sallar isha’i taji dawowarsa, tayi mamaki saboda bai fiya dawowa da wuri ba sai wajen karfe tara na dare. Nan da

nan ta karasa saka musu kayan baccin da take saka musu suka ruga bakin kofa suna jiranshi, yana shigowa kuwa suka rungumeshi suna

‘Oyoyo Abba.’

Ya dauki Nana wadda ta tare gabansa tana daga masa hannuwa Nurain ya bi shi suka karasa ciki.

Tana kallon fuskarsa ta san da matsala, tayi masa sannu da zuwa ya amsa a ciki ba tare da ya kalleta ba. Ta mike tsaye ta karbi Nana a hannunsa tana cewa

‘Bacci zasuyi.’

Sai da ta goya Nana sannan ta dauki ruwa ta kai masa dakin, ta ajiye a kan durowar gado tace

‘Ga ruwa Abban Nurain, na ajiye maka abincin a falo zan kwantar dasu yanzu zan fito nima.’

Bazata iya cewa ya amsa ko bai amsa ba, ta dai san ko kallonta bai yi ba. Ta ja hannun Nurain suka fice daga dakin tana mamakin abinda tayi masa don a iya saninta lafiya suka rabu da zai fita da safe. Saida ta kwantar da Nana sannan ta fito, kai tsaye ta wuce falo. Tun kafin ta karasa ta hango kayan abincinta a kan kafet yanda ta ajiye kuma baya falon ma, don haka ta koma ta wuce dakinsa.

Ta tura kofa ta shiga da sallamar da bata tabbatar ya amsa ko bai amsa ba, yana zaune a gefen gado yana ta faman shafa waya don haka itama ta karasa ta zauna a kusa dashi tana kallon fuskarsa

‘Habibi baka ci abincinka ba, ko ni kake jira?’

Ya galla mata harara

‘Na koshi.’

Mamakinta ya karu tana bin fuskarsa da kallo yayinda shi kuma yake kuma bata rai yana dauke kai.

‘Um wai me yake faruwa ne Abban Nurain?’

Ya juyo ya sake yi mata wani kallon

‘Me kika je kika gayawa Hajiya?’

Mamakinta ya kara yawa kanta ya shiga duhu

‘Hajiyan Baba? Ai tun last week rabona da gidan hajiya fa, me zan gaya mata kuma?’

Ya fuskanceta sosai kamar mai shirin kure mai karya

‘Wanne munafikin ne yacewa Hajiya ina neman wata yarinya?’

Sai a lokacin ta gane inda ya dosa, ta kawar da kanta tayi dan gajeran murmushi mai kama da yake

‘Iya abinda ta gaya maka shi na gaya mata.’

Ya kalleta a raine yana nuna mata yatsa

‘Ni kike gayawa wannan maganar banzar saboda baki da mutunci ko? Kin gama sa min ido da bibiyata kin ga abinda ya dameki kin koma kina so ki hadani da mahaifiyata ko? To wallahi baki isa ba, kin ji na gaya miki. Ki fita daga idona na rufe in ba haka ba wallahi zaki tafi gidanku ki je kiyi wa wani wannan munfurcin da kika tsira kinji na gaya miki.’

Ta dago idonta da ya riga ya cicciko da hawaye ta dubeshi tace

‘Allah ya baka hakuri.’

Ya ja tsaki ya mike tsaye, tayi sauri itama ta mike ta fice daga dakin tana jiyo tsakinsa.

Tana shiga dakinta ta turo kofar, ta karasa ta zube a bakin gadon saboda tana tsoron fadawa kan gadon ta tashi Nana. Hawayen da take makalewa ya kwace gaba daya, haka ta dauki tsawon lokacin tana zubar da hawaye kirjinta yana zafi. Wannan wacce irin fitna ce? Kenan yanzu babu wanda zai gayawa Mukhtar gaskiya ya dauka? Kenan idan dai tana sonshi haka zata kare rayuwarta ya kulleta a gidansa yana bin matan kwararo shida yake da damar ya auri mata har hudu? Ta dafe kirjinta wanda yake kara yi mata nauyi ta kwantar da kanta a gefen gadon ta lumshe idonta tana fitar da hawaye tana ambaton Allah a zuciyarta a haka har bacci ya kwasheta.

…

Mikewar da Mukhtar yayi dama ficewa zai yi ya bar mata dakin, don haka da yaga ta rigashi fita sai kawai ya ja tsaki ya koma ya zauna a inda ya tashi. Tunda taga sakonnin su da Fatima take masa fitna kala-kala, shi bai ma san yanda akayi ya bar sakonnin fatiman har ta gansu ba. Duk ‘yan matan da yake harka da su baya saving lambarsu a wayarsa, haddacewa kawai yakeyi ko ya rubuta a wani dan littafi da yake ajiyewa a mota. Haka ma sakonninsu, da sun masa message yana gama karantawa yake gogewa. Amma na Fatima da yake suna masa dadin sake karantawa da kuma kallon hotunan lokaci-zuwa lokaci sai ya barsu tunda yaga sun dauki shekaru da Safiyyan baya taba ganewa ba.

Ya ja tsaki a fili ya kwanta a kan gadon kafafunsa suna kasa.

Yanda Safiyya ta kwana cikin damuwa haka ya kwana yana hirarrakin banza tsakanin sabuwar budurwar da yayi wadda yanzu ita yake yayi wato Amra da kuma wata inyamura wato Lindsay; wadda suka hadu a Abuja lokacin da yake taro ta taya shi kwana kafin Fatima ta sameshi a Abujan.

Saida Abban Nurain ya kwana biyar baya yiwa Safiyya magana, baya cin abincinta baya ma zama inda take balle suyi magana. Yayi matukar bata mamaki saboda idan ma hakuri yake so ta bashi to ai tun ranar da yake mata fadan ta bashi hakurin don haka ta yiwa kanta alkawarin bazata bashi hakuri ba; don bata ga laifin ma da ta yi ba. Duk abinda ta sabayi na kula da gida da shi kansa bata fasa ba, sai dai kawai babu kulawa. Abinci kuwa yanda ta dafa ta ajiye masa haka zata kwashe kayanta, bata dai fasa girkawa ba saboda shima bai fasa cefane ba.

Wajen karfe tara da rabi na dare ya shigo gidan, tana kwance a falo ita kadai domin yaran sun yi barci. Wayace a hannunta tana karatun labari a group saboda babu wuta kuma bata tayar da inji ba. Bayan tayi masa sannu da zuwa yace

‘Ke dai kina son zama a duhu, akwai mai a inji bazaki tayar ba kiyi ta fama da sauro.'

Tayi murmushi tana mamakin yanda ta ji maganar tasa kamar ba shine ya fita da safe ba tare da ya kulata ba, tayi dariya tace

‘Na kasa tashi ne wallahi, kwana biyu duk jina nake kamar me zazzabi jikin ba kwari.’

‘To ai sai kije asibiti a dubaki don yanzu haka malaria ce.’

Kafin ta amsa ya koma waje ya tada injin sannan ya shigo gidan, bata falon don haka ya wuce daki. Ta fito daga kicin da ruwa ta kai masa daki tace

‘Na ajiye maka abincin a falo.’

‘Ina zuwa.’

Taji dadi amma tayi mamaki, a ranta tace Abban Nurain mai abin mamaki kenan kai kadai kayi fadanka kuma ka sauko. Ta dawo falon ta zauna tana jiransa.

Jimawa kadan ya fito daga dakin da takardu a hannu sa, ta sauka daga kan kujerar da take zaune ta zuba masa abincin. Bayan ta gama ya janyo kwanon ya mika mata takardun yana fadin

‘Idan an koma hutu da Nurain za a koma gashi nan na siyo form, tunda nan kusa ne idan na kaishi da safe sai ki dauko shi da yamma.’

Ta karba tana ta fara’a

‘Ma Sha Allah, yayi hakan. Allah ya kara rufin asiri bari ya tashi nayi masa albishir.’

Yayi dariya

‘Allah ya sa dai kada ya bada ke yayi mana kukan makaranta.’

‘In sha Allah ba zai yi ba.’

Suka dan taba hira sannan daga baya suka wuce suka kwanta.

.....

Tun wajen sati uku da suka wuce take son ta yi gyare-gyare amma ta gagara, gidan duk yayi yana da kura. Tana so ta goge fankoki, tagogi da irin su karkashin gado da kujera amma yara sun hanata. Ta so Hamida tazo mata kwana biyu amma makaranta kuma gashi BUK ta fi kusa daga gida don haka Umma tace sai dai ta bari Hamidan ta sami hutu tukunna.

Bayan ya fita aiki suna zaune ita da yara Bahijja da Habiba suka kawo musu ziyara, bayan sun gaggaisa ta dubesu tana dariya tace

‘Yau an tuna da mu kenan ‘yan matan kulle.’

Bahijja tayi dariya tace

‘Baba baya gari shiyasa muka sami kafar yawon Juma’ah.'

Nan suka wuni sai bayan la’asar suka fara shirin tafiya, Nurain ne ya dubi Habiba yace

‘Anti Biba gidan Hajiya za ku tafi.’

Ta shafa kansa tace

‘Can zan tafi Nurain, za ka je ne?’

‘Zan je, don Allah ki tafi dani.’

Ta Kalli Safiyya tace

‘Anti gaskiya zan tafi da yarona.’

‘Kinga kuwa da na samu na yi kiba kafin ku dawo, amma ki kira babansu ki gaya masa.’

Take ta dauki wayarta ta kirawo Mukhtar, kuma ya bata umarni ta tafi da su idan ya zo zai dawo dasu. Nana tana ji za a tafi da Nurain itama ta dauki takalminta da gudu ta mikawa Bahijja tan fadin

‘Anti Nima zan je.’

Don haka da suka gama shirinsu suka tafi da yaran gidan Hajiya.

Sai da ya tashi daga aiki sannan ya biya gidan, bayan sun gaisa da hajiya yace mata a shirya su Nurain zai tafi dasu. Ta dubeshi tace

‘Baza su bika ba, na riga na cewa Aminu ya biya ta gidan ya karbo kayansu sai sun kwana biyu za su koma. Haba yara suna son shiga mutane amma kana faman hanasu, itama Safiyyan ta huta da hidimarsu su shiga dangi suga gari.’

‘To Hajiya.’

Haka ya taho ya barsu ba tare da yana so ba. Baya son yaran nan suna yin nisa , duk inda za su in dai ba tare da uwarsu bane to baya farinciki. Tun Safiyyan tana damuwa tana ganin gidansu yake hanata kai yaran har ta gane ba haka bane don ko wajen Hajiyan tace a kaisu sai yace a’a.

Ba karamar murna Safiyya tayi ba da taga ya dawo babu yaran, ko babu komai zata samu ta gama gyare-gyarenta kafin a dawo dasu don tana sane ta sami akwati ta cika musu da kaya da Aminu ya zo karba.

……..

Da yake ranar asabarce ta san yakan kai goma ko sha daya bai fita ba, wataran ma sai yaci abincin rana sannan ya fita. Tun wajen shida na safe ta sulale ta tashi zata fita daga dakin ya riketa yana dariya

‘Ina jinki, ina zaki bayan yaran basa nan bazaki huta ba sai sun dawo kice bacci baya isarki.’

Tayi yar dariya don da ta zata bacci yake

‘Hm! Kwalema zanyi gaba daya gidan zan gyara yau kafin su dawo idan na gama sai na zauna na maida kibata kafin su dawo.’

‘Sarkin aiki.’

‘Um kai da kanka fa kace karkashin gadonka kamar bola ai gara na share na goge ko? Sai a tara wani dattin.’

Ya saketa ta fito tunda ya san tagama hidimarsa.

Tana fitowa ta fara hada abincin safe ta rufe sannan ta fara gyaran gidan. Zuwa karfe tara ta gama gyara falo, tagogin ne kawai bata goge saboda su gaba daya na gidan zata goge a lokaci guda. Ta nufi dakinsa tana sanye da t-shirt da gajeran wando rike da tsintsiya, tana so ta duba idan ya tashi sai ta gaya masa ta sa abincin safe idan ya fito sai ta fara gyara dakin nasa tunda bata sani ba ko zai fita ko ba zai fita ba. Tana shiga corridor din ta jiyoshi a bandaki yana wanka, da alama shower a kunne take. Ta so taji kamar yana waya a bandakin amma zubar ruwa bai bari ta tantance ba , kuma da yake tunda ta karanta sakonnin Sucre ya tsiri shiga bandaki da wayarsa abun bai dameta ba. Ta dawo kicin ta dauki tsintsiyoyinta ta koma dakin.

Sai da ta debi kayan da zai saka da duk abinda yake bukata na shiryawa ta kai dakinta, tana nufin idan ya fito sai yaje can ya shirya saboda kura. Da yake zanin gadon ya riga yayi datti sai bata cireba, ta dai rufe wardrobes. Da yake karkashin gadon ne a ranta ta nan ta fara.

Katifarsa tana da nauyin sanna kuma katakon gadon ma bashi da dadin sha’ani don haka sai dai ta kwanta ta sharo sannan ta zura mopper ta goge duka ta karkashi.

Ta zagaya can ciki ta kwanta tana leka karkashin gadon, ta zura tsintsiyar kwakwa ta fara kokarin sharo kasan gadon. A dai-dai nan ya fito daga wanka yana daure da tawul da waya a kunnensa, hira yakeyi cikin nishadi bai ma kula da tsintsiyarta a gaban mudubi ba balle ya san tana cikin dakin. Ya nufi gaban wardrobe ya tsaya ya bawa gadon baya yana cigaba da wayarsa cikin nishadi

‘Ke matsoraciya ce ai, babu abinda zata yi miki.’

‘Me kike so kiji ne, ai na gaya miki a kanki na fara soyayya kuma tunda kika ga na nace kinsan ta gidan bata kaiki komai ba.’

‘Ai babu yanda zata yi dake, ba naje dake na nuna miki gidan da nake ginawa ba. Ke kika dace da wannan gidan don haka ko zata shiga ma sai bayan kin tare ki daina damuwa da ita. Jiyan ma na gaya miki ba ita ta hanani zuwa ba don bata isa ba, kawai dai ina wajen Baba ne.’

‘Yauwa, ki shirya gani nan zuwa yanzu kuma yau sai lokacin da kika ga dama kika sallameni sannan zan barki.’

‘Minti talatin.’

‘Yauwa Baby sai na zo.’

Tayi gyaran murya daga inda take tsaye rike da tsintsiyar kwakwa bayan da ta mike daga karkashin gadon, firgigit ya juyo yana kallonta don bai yi zaton tana dakin ba. Yanayin fuskarta da kallon da take masa ya tabbatar masa taji abinda ya fada a wayar.

Har ya juya kamar me shirin dauko kaya sai kuma ya juyo a fusace yana mata wani kallo.

‘Me kike yi a nan?’

Da kyar ta hadiye malolon da ya tokare mata makogoro tace

‘Shara.’

Ya watsa mata harara

‘Da kuma labe ko? To ai gashi nan kin ji abinda kike son ji.’

Ya juya ya cigaba da kokarin zaro kaya daga wardrobe din. Ta share kwalla daga idonta ta bude baki da kyar tace

‘Mukhtar yanzu karuwar kake gayawa ni matarka ban kaita komai ba? Ashe ma soyayyar da ka nuna min lokacin kana neman aurena duk karyace tunda yanzu ne ka fara soyayya? Ashe ginin da kake yi nake faman raba dare ina addu’a ka gama mu rabu da gidan haya ashe ba don ni ake yi ba, har an kai karuwa ta gani ni ina nan zaune? Yanzu Mu…'

Ya daga hannunsa yana dakatar da ita

‘Kada ki gaya min maganar banza, sau nawa na gaya miki ki daina bibiyata ki daina yi min labe yanzu ai kin ji abinda kike son ji ko?’

Ta bude baki tana nuna kanta da yatsa

‘Yanzu nice karuwarka ta fi ni komai Mukhtar?’

Ya bita da kallo daga sama zuwa kasa

‘Shi kike son ji ai kuma kin ji ko?'

Tsintsiyar da take hannunta ta subuce ta fara busar da iska mai zafi

‘Allah ya isa Mukhtar, Allah ya saka min….’

Ya daga hannu ya dakatar da ita yana matsowa yana kokarin zagayawa inda take, don haka itama ta fara tahowa suka hadu a gaban mudubi

‘Wallahi idan kika sake kika zageni sai na kwakkwada miki mari juma na daki banza wallahi. Sai dai ki tafi gidanku kije kiyi a can.’

Idonta gaba daya ya rufe saboda hawayen da kuma kunan rai, ta bashi amsa

‘’Kai ai sai ka zageni ko ba komai haka maza na gari sukeyi, shima zagin yana cikin sunnar aure da kuma bin karuwai.’

Ya dunkule hannunsa kamar zai kai naushi sai kuma ya dago daya hannun ya nausa a ciki.Ya ware yatsa ya nuna mata kofa

‘Zo ki fice min daga gida Safiyya, nace zo ki fice min daga gida ba zan dau raini ba.’

Duk maganar da zata fada ba mai dadi bace kuma bata so takai ga zagin nasa don haka ta ja kafa ta fice, dakinta ta shiga ta mako kofar iya karfinta. Ta zauna a kan gadon jagwaf, gaba daya kanta ya kulle zuciyarta tafasa kawai takeyi.

Yanzu ashe duk soyayyar da Mukhtar ya gwada mata a baya karyace? Tana gida tana jin kanta a matar aure ashe duk ya gayawa ‘yan matansa ita din banzace? Wannan wane irin cin fuska da wulakanci ne Mukhatr yake mata? Haka ta zauna hawaye yana zuba a fuskarta ba tare da ta goge ba saboda babu yanda zata yi, babu wanda

zata gayawa taji sanyi a ranta.

Tana fitowa daga dakin shi kuma ya cigaba da shirinsa, tabbas sai ya koyawa Safiyya hankali. Shi bazai kai kararta wajen iyayenta ba amma tabbas zai korata gida taje da kanta ta kai karar kanta, idan sun mata fada tayi hankali ta dawo.

A shirye tsaf ya fito ya turo kofar dakin nata a fusace, ta daga kai ta kalleshi da idonta cike da hawaye. Baya son kukanta amma baya son sa idon da take masa don haka dole ya koya mata hankali.

‘Me kike min a gida? Baki ji nace ki tafi gidanku bane? Ki tashi ki fice min daga gida.’

Take hawayenta ya bushe malolon da ya tokare mata makogoro ya fara neman hanata numfashi, ta kalleshi tsaf suka hada ido sannan tace

‘Idan naje me zan ce musu?’

Ya kalleta a banzace

‘Kice na sakeki saki daya.’

A razane ta dago kai ta dubeshi, abinda ta so fada ba shi ta fada ba saboda yanda ta gani a fuskarsa yana jin dadin yadda sakin ya razan ta, ta bude baki da kyar tace

‘Ka rubuta saboda na basu hujja.’

Yaja tsaki ya juya ya koma dakinsa, jimawa kadan ya dawo ya sameta a zaune a inda ya barta ya mika mata takardar da ke hannunsa

‘Gashi nan, kizo ki fice min daga gida saboda zan rufe gidan na fita.’

Ya juya ya koma falo ya zauna yana jiranta.

Duk wani takaici da take ji ya juye ya koma mamaki, yanzu ashe Mukhtar zai iya sakinta? Shike nan so ya kare? Yanzu me zata je ta cewa Umma? Gashi yace dole sai ta fita balle tace zata zauna tayi idda a gidan. Ta daga hannunta sama tana addu’a

‘Allah Kaine Allah, ka kawo min mafita.’

Ta mike a hankali saboda yanda jiri yake kwasanta, ta karasa kan dadduma ta dauki hijabinta ta saka ta dauko jakarta ta ciro wayarta da take chaji ta hada da chajar ta jefa a jakar. Ta fito falon tana zaune kawai, har ta nufi hanyar fita ta juyo ta dubeshi tace

‘Yaran fa?’

A cikin halin ko in kula ya dubeta yace

‘Ai ba da su kika zo ba ko?’

Ta sunkuyar da kai murya a sanyaye tace

‘Hakane.’

Bata jira me zai ce ba ta juya ta fice daga gidan.

KARSHN BABI NA GOMA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA GOMA SHA DAYA

11

Da kyar ta samu ta share hawayenta ta saita fuskarta saboda bata so ta hadu da wanda ta sani a tambayeta dalilin kukanta, saida ta tsaya a bakin titi sannan ta tuna bata ma da kudin mota don kudin da suke cikin jakartata bazasu kaita gidan Umma ba. Dole haka ta dauki shatar dan sahu a kan sai ya kaita zata shiga ta karbo masa kudin motarsa a gidan.

Tana shiga Umma ta fara tambayarta

‘Lafiya na ganki haka.’

Ta ajiye jakar hannunta tace

‘Kudin mota zaki bani na sallami mai adaidaita-sahu yanzu zan shigo.’

Ta shiga daki ta dauko naira dari biyu ta mika mata, ta juya ta fice, Sabir da yake zaune yana game a waya ya bi bayanta. Jimawa kadan ta dawo Sabir din yana biye da ita. A nan falon inda suka bar Umma nan suka sameta, Safiyyan ta zauna kusa da Umma ta kalleta, itama nata idon yana kanta don haka suka hada ido. Nan take ta saki kuka tare da rufe fuskarta da tafukan hannunta.

A razane Umma take dubanta

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun, Ke Safiyya wai me ya faru ne za ki sani a gaba kina kuka? Ina yaran da babansu?’

Ta share hawayenta tana ajiyar zuciya, ta janyo jakarta ta zaro takarda ta mikawa Umma tare da fadin

‘Ya sakeni.’

Sabir da ke zaune yana saurarensu ya bude baki cikin mamaki tare da rufe bakin da tafin hannunsa yayinda Umman tace

‘Subhanallahi, kin san me kike fada kuwa Safiyya, shi Mukhtar din ne ya sake ki?’

Kafin tabata amsa ta gama bude takardar, nan da nan ta karanta harda tsallaken kalmomi. Ta saki hannunta me rike da takardar a kan cinyarta tana fadin

‘Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun, ke kuwa me kika yi masa?’

‘Wallahi Umma babu abinda nayi masa.’

Nan ta mayar mata da abinda ya faru. Cikin takaici tace

‘Amma kuwa yaron man bai kyauta ba wallahi, wannan ai wulakanci ne.’

Sukayi shiru, Safiyya na ta faman share hawaye. Umman ta dubeta da takaici tace

‘Kema ke ce da shegen taurin kan tsiya, na ce ki fita harkarsa ki rabu da ‘yan matansa. Daga ganin yanda ya aureki ya ajiye ki a gidan ai kin san kin fi duk wata mace da yake tare da ita, yanzu ga abinda kika janyowa kanki. Ko da ya zo ya mayar da ke dai ai kin ragewa igiyar auren kima.’

Ta ja tsaki tare da kauda kai. Suka dauki lokaci shiru kowa da abinda yake tunani, Sabir ya mike yana fadin

‘Umma bari naje na dawo.’

Bata cikin yanayin da zata amsa masa don haka kallonshi kawai tayi ya fice ya barsu. Jimawa kadan shirun ya gundiri Safiyya ta tashi ta nufi dakin Umman, har ta kusan shiga ta tuna indai a dakin Umma zata sauka to akwai alamun zasu kwana Umma tana yi mata fada don haka ta juya ta wuce dakin Hamida wanda shima yana nan cikin falon.

Tana jiyo Umman daga falo ta kirawo Kanin Abbansu wato Alhaji Safiyanu wanda suke kira Baban Hotoro, ta sanar da shi halin da ake ciki sannan ta sanar da Yaya Habibu ma.

Sai bayan sallar la’asar sannan Baban Hotoro ya iso gidan; tun bayan rasuwar mahaifinsu shine wanda yake kula da lamuransu duk da ba wani kudine da shi ba ammma dai shine ubansu. Bayan sun gaisa da Umma ya jajanta mata yasa aka

kirawo Safiyya, ta bashi labarin duk yanda abun ya faru. Ranshi yayai matukar baci duk da shima din yayi mata fadan binciken

‘Tunda ba shi ya aike ki kika yi masa bincike ba ai da abinda kika gani sai ki hadiye a cikinki ke kadai tunda ciki ba don tuwo kawai aka yi shi ba.’

Ta sunkuyar da kai tana share kwalla. Suna nan zaune ya dauko wayarsa ya kirawo Alhaji Kabiru Balarabe wanda wa ne a wajen mahaifin Mukhtar kuma shine madaurin auren Mukhtar din. Bayan sun gaisa ya sanar dashi abinda ya faru, suka jajantawa juna sannan ya gaya masa su basu ma san an yi hakan ba amma in sha Allahu zai yi magana da Mukhtar din.

Sai da ya gama wayar ya dubi Umma wadda take ta faman cika tana battsewa kamar zata doke Safiyyan yace

‘Hajiya Umma hakuri za kiyi tukunna muji daga wajensu, in sha Allahu komai zai daidaita.’

Ya dubi Safiyyan yace

‘Kiyi hakuri Safiyya, shi bawa baya wuce kaddararsa kuma rayuwa gaba dayanta jarrabawa ce. Idan da sauran zama zai zo ku daidaita idan kuma akasin hakan ne to sai mu nemi mafita daga Allah, Allah shine ya san yanda zai yi da bawa kuma in sha Allahu baza ki tozarta ba.’

Har cikin ranta taji dadin wannan maganganu na Baban Hotoro, tun bayan sakin da Mukhtar yayi mata babu wanda ya gaya mata wata kalma mai dadi kamar wannan. Haka Baban Hotoro yake, duk girman rigima a dangi haka zai kwantarwa da kowa hankali kuma cikin hukuncin Allah ba a tozarta. Yayi musu sallama ya tafi bayan ya sanar da Umma idan yaji daga wajen iyayen Mukhtar din zai sanar da ita sannan kuma ya gaya mata ya kirawo Yaya Habibu yace ya sameshi a gida da daddare don su kara tattauna maganar.

Kafin ya tashi sai da ya kirawo Baba shehu; wato kaninsu da ke zama a Kaduna ya sanar da shi suka jajanta. Ya bashi Safiyyan a waya shima ya kara yi mata nasiha ya bata hakuri kuma yace ta cigaba da addu’a.

Tunda yaje office yake tunani kala-kala, yana son Safiyya baya son rabuwa da ita, sai dai baya nadamar sakin nan da yayi mata don yana so taje ta dana zaman gidan da zawarci taji idan da dadi. Yana da tabbacin cewa idan ta dan taba zaman gida in ta dawo zata shiga hankalinta, kuma ya san za a nemeshi a gidansu zai sami damar da zai gayawa Baban Hotoro irin yanda take bibiyarsa kuma tana kokarin yi masa rashin kunya.

Yana zaune a office bayan sallar azahar wayarsa tayi kara, yana dubawa yaga Baba ne. Cikin girmamawa ya daga bayan ya amsa sallamar Baban ya gaisheshi. Baban yace

‘Kazo gida yanzu ina son ganinka.’

Kafin yace wani abu Baban ya ajiye wayar, ya cire wayar daga kunnensa ya dubeta cikin faduwar gaba. Yace

‘Allah yasa dai lafiya.’

Take ya mike ya hada tarkacensa ya fito daga office din, ya sallami masinjansa ya kama hanyar gida yana ta mamakin neman da Baba yake masa yanzu-yanzun nan.

Yana tsayawa a bakin gate din ya danna honk yaji babu wanda ya bude gate din don haka ya gyara parking a waje ya kulle motar ya shiga ciki.

Bai kula da motar Baffa Kabiru a farfajiyar gidan ba saboda tsabar sauri, babu kowa a wajen don haka kai tsaye ya haye saman wajen Baban. Yana shiga falon ya tarar dasu a zaune shi da Baffa Kabiru, nan take gabansa ya fadi, ya tsuguna har kasa ya gaida Baffan sanna ya matsa kusa da kafar Baban yace

‘Baba ga ni.’

Ya dubeshi suka hada ido sannan yace

‘Sai yaushe zaka gaya mana ka saki matarka har ka koreta daga gidanka? Maigida.’

Take gumi ya karyo masa duk da AC din falon a kunne take, bai taba tunanin labarin sakin zai riga shi zuwa gidan ba don shi bari yayi sai ya tashi daga office sai ya sami Hajiya yayi mata bayani gashi har su Baba sun yi masa taron dangi. Shirun ya tsawaita baba yace

‘Kai muke saurare.’

Ya shafo kansa idonsa yana kasa yace

‘Ayi hakuri Abba, daman ina nufin idan na taso daga aiki nazo sai na fada.’

Ya kwalawa Bahijja kira wadda nan da nan ta shigo falon da sallama, ta riga ta gaisheda Baffa Kabiru tun zuwansa don haka ta tsuguna daga nesa kadan tace

‘Ga ni Baba.’

‘Ki kirawo min Hajiya.’

‘To Baba.’

Nan da nan ta fice ta barsu zaune sun yi shiru, jimawa kadan Hajiya ta shigo da sallama ta nemi kujera me zaman mutum daya ta zauna tace

‘Ga ni Baba.’

‘Daman Mukhtar ya gaya miki zai saki matarsa shi yasa ya kawo miki yaransa?’

Ta zare ido tare da dafe kirji tace

‘Subhanallahi! Saki kuma? Ni bai gaya min ba yara su Habiba ne suka je gidan suka taho da su, ya ma zo daukansu nace bazasu tafi ba sai an kwana biyu.’

Baba yace

‘To ya saketa yau kuma saboda tsabar rashin hankali bai yi shawara da mai zuwa masa neman auren ba yayi sakin.’

Baffa Kabiru ya dubeshi yace

‘Wai me tayi maka ka sake ta?'

Da kyar ya hada yawun bakinsa ya nemo muryarsa ya sake shafo kansa sannan yace

‘E dama Baffa bincike take min a waya kuma tana min rashin kunya don yau din nema tayi ta zageni.’

‘Shine kai kuma kayi mata saki nawa?’

‘Daya ne Baffa.’

Hajiya tace

‘Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun, yanzu ka kasa shawara da ni idan da wata matsala Mukhtar? Ai shikenan daga ni har iyayen naka bamu da wani amfani kenan.'

Ya bude baki zaiyi magana Baffa ya dakatar dashi

‘Kayi kuskure Mukhtar, mace idan ka aureta ka sameta tana maka biyayya to rike ta kake yi, idan ka sake ta fita taje ta ga abubuwan dake faruwa a duniyar waje to za ayi dayan biyu; ko taki dawowa gidanka ko kuma idan ta dawo ta canza hali ka kasa gane kanta.’

Baba ya dubeshi yace

‘Ai shikenan, Allah ya sauwake. Tashi ka bani waje.’

Da sauri ya tsahi ya fice yana neman yin tuntube saboda dama kamar a kan kaya yake jinsa. Hajiya ta dubi Baba tace

‘Alhaji ai ce masa zakayi yaje ya dawo da ita yanzun nan ka barshi ya fita, in ba ayi wasa ba yanzu zai gudu tunda bashi da gaskiya.’

Ya jijjiga kai yace

‘Duk lokacin da ya shirya ya dawo da ita idan ya gane mahimmancinta a rayuwarsa, idan aka saka shi ya dawo da ita ba da son ransa ba haka zai saka ta a gaba yayi ta

muzguna mata abun ya kara lalacewa. Kina nan zaune zai zo da zancen aje a dawo masa da ita, za ki ga yanda zamuyi dashi.’

Baffa Kabiru yace

‘Gaskiya ne, duk da ban yarda da zancen bakinsa ba amma dai wani abun sirrine na aure idan tayi wari ma ji.’

Suna nan zaune Baffa Kabiru ya kirawo Baban Hotoro ya sanar dashi abinda sukayi ita da Mukhtar din yarinta ne amma yana ga idan an basu lokaci komai zai yi dai-dai, ya sake basu hakuri sukayi sallama.

……..

Sai da daddare sannan Yaya Habibu yazo gidan, ya sa Safiyya a gaba da nasiha daga karshe yace

‘Ki daina damuwa kinji, ki mayar da hankali kiyi ta ibada komai zai wuce in sha Allah.’

Umma da take zaune bata saka musu baki ba tace

‘Kada ma ta daina damuwar, wa ya janyo mata? In banda shegiyar fitnar tsiya tunda ya zabi ya bi matan banza ki kyaleshi mana ki rungumi yaranki amma s..’

Yaya Habibu ya katseta da murya mai cike da girmamawa

‘Umma, in dai abinda ta fada gaskiya ne bata fa da laifi, mutumin da yake da damar auren mace hudu amma ba zai yi auren ba ya dinga bin yaran mutane yana lalatawa. Ga ya mace nan ta haifa masa idan hakki ya fado a kanta kuma sai muce ita ta barta ta lalace bayan haka ubanta yayiwa yaran wasu. Kumafa Umma Allah cewa yayi ‘ku amfusakum wa ahlikum naara..’ kin ga itama hakki ne a kanta tayi iya

kokarinta taga ta tseratar dashi fushin ubangiji, ba zai yiwu ta zuba masa ido ba. Kuma idan ya dawo din ma za a zauna ayi magana ai mu ba arna bane musulmai ne.’

Hararsa kawai Umma tayi ta kawar da kai, dama ta san za ayi haka.

Jimawa kadan yayi musu sallama ya tafi.

Haka suka kwana a dakinsu na da wanda yanzu ya zama dakin Hamida, suka kwanta kai da kafa a kan gadon dakin tunda dama Babba ne. Haka Safiyya ta kwana tana kuka sai wajen karfe uku na dare ta tashi tayi sallah tayi ta addu’a da karatun kur’ani, kafin asuba zuciyarta ta sami natsuwa hawaye ya daina bin idanunta.

Tun karfe bakwai suka tashi, nan da nan Hamida ta hada musu abinci da yake tuwo ne na daren jiya zasu dumama sai shayi, gaba daya suka zauna a falo suna karyawa harda Sabir da yake sanye da uniform dinshi don shi yana SS3 ne a halin yanzu. Safiyya ta dubi Umma tace

‘Umma ban taho da kayana ba don Allah idan sun dawo daga makaranta Sabir da Hamida suje su debo min kayan sawa.’

Nan da nan Umma ta hade rai

‘Ba za su je ba, ke da kike neman shiri. Idan ma za a debo kayan to ke da kanki za ki datsi lokacin da yake gidan kije in ya so idan kin sameshi kika bashi hakuri ba sai kiyi zamanki ba.’

Ta sunkuyar da kai ba tare da ta ce komai ba; itama tana so ta koma amma a halin yanzu bazata iya zuwa inda yake ba balle har ta bashi hakuri

To me tayi masa ma da zata bashi hakuri? Saboda dai ita bata da gata? Indai sai taje debo kayanta gara tayi ta zama da zani daya idan an gaji da ganinta a bata ko na aro ne.

Sabir ya Kai kwanukansa kicin ya dawo ya goya jakarsa bayan ya karbi kudin makarantarsa yayi musu sallama ya fice makaranta. Yana fita suma duk suka tashi, Hamida ta shiga wanka yayinda Safiyya ta koma daki ta zauna ta kafa tagumi; tana son Mukhtar kuma tana son komawa gidansa amma a halin yanzu zata hakura ta zauna har sai lokacin da ya bukace ta ya zo ya mayar da ita.

Bata dade da zama ba Sabir ya dawo da gudu, Umma na falo tace

‘Ya haka? So kake ka makara ko?’’

‘Calculator dina na manta a wajen Hamida.’

Kafin ta bashi amsa ya fada dakin da gudu ya nufi Safiyya wadda take zaune a gefen gado ya zauna kusa da ita ya kai bakinsa kunnenta yace

‘Zan debo miki kayan Yaya Safiyya, yanzu zan je don na sameshi a gidan.’

Kafin ta bashi amsa ya sake tashi ya fito da gudu ya kama hanya. A gurguje ya tsaya a gidan Mukhtar, ya bude masa dakinta ya shiga ya debo mata kaya kala shida, ya ga underwears dinta a kan gado wadanda ta wanke ya debo su ya hada da kayan ya kalli kan mudubin ya dauko mata turarukanta da Mai, har ya juyo ya koma ya dauko takalmi guda daya wanda ya gani a tsakar dakin. Ya fito ya karbi leda awajen Mukhtar ya zuba kayan a ciki a yayi tafiyarsa. Yana zuwa makaranta ya bawa malamar ajinsu ajiyar kayan sannan ya shige aji.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA DAYA.

May 9

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA SHA BIYU

12

Sai bayan suna sannan Fatima ta koma gida. Tana komawa gidan damuwarta ta dawo; tana son Mukhtar sosai kuma bata taba tsammanin zai yi mata haka ba amma babbar damuwarta itace hotunanta da ta tura masa. Bata sani ba ko yana nan da su kada ya zo yayi amfani da su ya cutar da ita nan gaba. Idan kuma ta tuna ya rabata da budurcinta sai taji kamar ta bar duniya ta huta, yanzu kenan idan tana da rabon aure haka zata jewa mijinta ita ba budurwa ba kuma ba bazawara ba? Ta kasa yafewa kanta yanda ta banzatar da kanta ta wulakanta kanta a wajen Mukhtar, gashi ya kasa yi mata halacci yana wajen matarsa wadda ya aura a cikakkiyar budurwa.

Haka a daddafe har aka kafe musu posting na bautar kasa, da taimakon Yaya Ibrahim ya sa aka mayar da ita nan Zariya. Kwanakin da sukayi a camp suka dan kara debe mata kewa sannan ta hadu da mutane daban daban. Suna fitowa daga camp aka turata koyarwa a makarantar ‘yan mata wadda take nan kusa da gida don haka kullum daga gida take zuwa.

Yaran da take koyarwa su suka zama masu debe mata kewa daga tunane tunane barkatai, suna sakata nishadi watarn kuma su bata tausayi.

Haka ta cigaba da rayuwarta tana kokarin cire Mukhtar daga zuciyarta kuma tana fatan Allah ya fito mata da miji tayi aure kafin ta gama bautar kasa.

_

Kwanci tashi yau satin Safiyya biyu a gida, kullum da daddare sai ta tashi tayi ibada ta roki Allah mafita mafi alkhairi kuma tana addu’a Allah ya bata hakurin zama da Umma zuwa lokacin da mijinta zai mayar da ita.

Iya takurawa Umma tana takura mata. Yanzu kullum itace take dafa abincin safe sabanin da da kullum Hamida kafin ta tafi makaranta sai tayi, amma yanzu ko asabar ce Hamida sai ta kai goma na safe tana bacci amma da sassafe Umma zata tashi Safiyya tayi musu abinci. Ga aikin gida, komai sai ace ita. Duk lokacin da Umma ta sami dama tana gaya mata ta san yanda zatayi ta hilato mijinta ya zo ya mayar da ita dakinta. Babu wanda take jin dadinsa a gidan sai Sabir, Yaya Habibu ba zuwa yake sosai ba kuma ko ma ya zo ba wani zama suke ba kullum yana gaban Umma, Yaya Hajiyayyaye kuwa ra'ayinsu daya da Umma; ta san yanda zata yi kawai ta koma dakinta, ita kuwa Hamida miskila ce ta gaske sai a wuni da ita ba ayi hira ba.

Yau asabarce don haka Yaya Hajiyayyaye tazo gidan ita da yaranta gaba daya za su wuni, tunda suka zo Safiyya take tsaye tana hidima da su, da an bukaci wani abu Umma zata kwala mata kira duk da kasancewar Hamida tana gidan. Ita tayi abinci ta raba aka gama ci aka tara wanke-wanken da ta san ita zata yi shi don Hamida tana zuwa islamiyya, ta rasa da da bata zo ba ya sukeyi da wanke-wanken.

Sallar la’asar ta idar a daki ta mike a kan dadduma ta lumshe idanu, bacci ne yake kokarin dibanta saboda yanda ta gaji. Tana jiyo hayaniyar yaran Yaya Hajiyayyaye daga falo, kamar a mafarki taji Umma tana kiranta. Cikin hanzari ta mike ta fito ta nufi dakin Umma. A zaune Umman take a kan dadduma da alamar itama sallar ta idar yayinda Yaya Hajiyayyaye take zaune a gefen gado, ta shiga da sallama ta zauna a gaban Umma. Kafin ta karasa zama Umma ta dubi Hajiyayyaye tana nuna Safiyyan tace

‘Kin ganta nan babu yanda banyi da ita ba a kan ta kirawo shi a waya ta bashi hakuri yazo ya mayar da ita amma ta ki, ta zabi zawarci a kan ta koma dakinta. So take sai an fara nuna ni a dangi, ta mayar da kanta karamar bazawara.’

Ta sunkuyar da kanta tana fatan kada Allah ya bari idonta ya zubar da hawaye. Ya Hajiyayyaye ta dubeta tace

‘Dole fa ki nemo shi Safiyya, ya zo ya mayar dake dakinki. Ko ni ai na gaya miki mazan yanzu duk haka suke idan dai a kan mata ne sai dai kiyi hakuri da su, kuma tunda shine shugaba ai kinga dole ke zaki bashi hakuri.’

Sukayi shiru suna jira tace wani abu amma itama tayi shiru kanta a kasa, Yaya Hajiyayyaye tace

‘Me yasa bazaki kirawo Mukhtar din ba Safiyya?’

Ta rasa yanda zata yi da su don haka ta yanko karya

‘Baya dauka Yaya Hajiyayyaye, kusan kullum sai na kirawo shi amma baya dauka. Wallahi nima inaso ma koma.’

‘To gaskiya dai ki kara dagewa, ko ta Whatsapp ne kiyi masa magana ku daidaita ko kuma ma in ta kama kije ki sameshi.’

Ta kalleta da mamaki suka hada ido, ta jijjiga kai ta cigaba

‘I mana, mijinki ne fa kuma yana kusantarki aure ya koma don haka in kinje ba laifi kika yi ba. Ko a ‘yan uwansa idan da wanda kike ganin zai muku sulhu ko mahaifiyarsa. Tunda Umma ta ce da kanta ta kirawota tana bata hakuri kuma ta tabbatar mata zai zo ya mayar dake. Kina kallo Umma tana fama da marayun kannenmu duk nauyin gidan yana kan Yaya Habibu sai abinda Umman ta samu ke kuma ki zo ki kara mata nauyi ai da kunya ma ko?'

Ta hadiye malolon da ya tokare mata makogoro ta share kwalla, wadannan maganganun na Yaya Hajiyayyaye sunyi kama da cin fuska amma dole ta

saurarensu tunda bata da yanda zata yi da su. In sha Allahu in dai Mukhtar ya mayar da ita ko barikin karuwai zai mayar da gidan bazata ce masa komai ba, hakuri za tayi ta zauna don gara nashi wulakanci da na mutanen da take gani bata da na biyun su. Cikin takaici Umma take dubanta tana fadin

‘Kin gani ko Hajiyayye, da ka yi magana sai ta sa kuka sai kace wadda aka daka.’

‘Ai ba kuka zakiyi ba, ki lallabo mijinki ki koma gida. Ai ko don yaranki ma kya hakura ki zauna da shi komai mugun halinsu tunda dai yana kula da duk wani hakki naki.’

Ta sake share kwalla tace

‘Zan sake kiransa in sha Allahu.’

‘Gara dai ki dage gaskiya.’

Sai bayan magriba sannan mijin Yaya Hajiyayyaye ya zo ya kwashe su ita da yaran suka tafi.

Sati biyun da Safiyya tayi a gidansu jinta take kamar a kurkuku, gaba daya tayi baki ta rame bata ko son kallon kanta a mudubi. Ga wani ciwon kai da bazata iya tuna tun lokacin da ta fara shi ba. Bata taba zaton saboda tana auren Mukhtar bane Umma take sonta, gaba daya yanzu gani take kamar an canza mata Umma da 'yanuwanta. Ga shi tana kewar Mukhtar da yaranta, ba za su iya gane yanda take tsananin son Mukhtar ba ji take kamar ta mayar masa da kanta. Tun da ta kwana daya a gidan take masa magana ta Whatsapp amma zuwa jiya bai kulata ba, tana gani zai bude sakon ya mayar ya rufe ba tare da ya bata amsa ba. Ta dai yiwa kanta fada a kan ta hakura da yi masa maganar haka, amma har yanzu kokawa take da zuciyarta. Da kyar ta danne zuciyarta ta kwanta baccin dare ba tare da tura masa sako ba, amma tayiwa kanta alkawarin gobe da safe zata shirya taje gidan ta sameshi idan ba zai mayar da ita ba sai dai ya kasheta ya kawo musu gawarta, a haka bacci ya kwasheta.

Haka kawai ta farka tana tsakiyar baccinta, ta tashi zaune ta lalubi wayarta taga karfe biyun dare da minti uku. Sai karfe uku alarm dinta yake kararrawa ta tashi sallar dare don haka ba shi ya tada ita ba, ta sa hannu ta shafa mararta saboda yanda marar take mata ciwo, take ta gane ciwon marar ne ya farkar da ita. Sai da tayi dogon tunani sannan ta gane yanzu haka al'ada zata yi shine dalilin ciwon. Idan tana shayarwa bata al'ada don haka rabonta da jini tun na haihuwar Nana, Kuma da yake bata dade da yaye Nanan ba wannan shine karo na farko da zatayi al'ada.

A lissafinta ma ya kamata ace tayi al'adar tun tuni amma saboda tsabar damuwa da bacin ran da Mukhtar yake dora mata gaba daya ma ta manta da lissafinta, yanzu ma da take jin zai zo tana tunanin wannan ciwon marar yana da alaka da damuwar da take ciki don ciwon da yake mata bai kai haka ba.

Babu wuta don haka ta haska da fitilar wayarta ta sauko daga gadon ta shiga bandaki don ta duba. Jini Bai zo ba sai ciwon kawai don haka ta dauro alwala, tana fitowa ta dauki Panadol a kan mudubin ta Sha sannan ta zauna a kan dadduma ta fara karatun kur'ani don bazata iya tsaiwar Sallah ba.

Nan a kan daddumar ta karasa baccinta har asuba. Hamida da Sabir suka shirya suka fice makaranta yayinda Umma ta koma bacci don bata ma san Safiyyan bata da lafiya ba. Haka ta lallaba ta gyara gidan tsaf ta dora abincin rana. Sai wajen Sha biyu da rabi Umma ta fito ta zauna a falo, daga kicin Safiyyan ta fito ta shigo falon da sallama saboda ta jiyo motsin Umman

'Sannu da fitowa Umma.'

Ba tare da ta kalleta ba ta amsa

'yauwa.'

Jimawa kadan ta sake wucewa ta dubo abinci, bayan ta dawo ne Umma tace

'Me yake damunki ne kike ta wani yatsuna fuska.'

Ta dan tsaya ta juyo

‘marata ce take ciwo Umma, amma na Sha Panadol.’

Ta tsareta da ido na dan lokaci, ta yafito ta tana fadin

‘Zo nan ki zauna.’

Ta karaso ta zauna kusa da Umman a kan kujerar zaman mutum uku. Umma ta dubeta da kyau sannan tace

‘Al’ada zakiyi?’

Ta sunkuyar da kai

‘Eh.’

‘To ina fatan kin san idan kika gama wannan al’adar saura al’ada biyu aurenki ya mutu gaba daya, kin zama bazawara kenan.’

Sai yanzune Safiyya ta tuna da wannan lissafin, take gabanta ya fadi yayinda mararta ta kara kartawa da ciwo. Ta sunkuyar da kai ba tare da ta ce komai ba, Allah ya tsareta da zama bazawara ko jin kalmar bata son yi balle ace ta tabbata a kanta. Umma tace tana nunata

‘Kinga ki mayar da hankali ki nemo mijinki, ki san yanda za kiyi ki sanar dashi kinga al’adarki don yanzu haka shima baya lissafi gara ku san me kuke ciki. Kuma fa ni yanda nake ganinku ma kallon mai ciki nake miki wallahi.'

‘Bani da ciki fa Umma, tunda na yaye Nana ban ma yi al'ada ba. Dama kuma idan ina shayarwa bana al'ada.'

'Hmmm! To Nana ai ta kusa wata uku da yaye, don haka idan ance ciki ne da ke ai babu mamaki. Amma dai bari mu gani zuwa kwana biyu. Sai ki sanar da Mukhtar din don ku san lissafin da kike ciki.'

Haka ta tashi ta bar Umma a nan ta koma daki.Tana shiga daki ta fada kan gado ta sa kuka; yanzu nan gaba idan ta kara al’ada biyu ta zama bazawara? Tana hango wayarta a chaji, da zarar ta gama kafin nan mararta tayi sauki zata tura masa sako ta fara al’ada do ta san shima lissafinsa al'adarta bata dawo ba.

Haka ta dinga dunkulewa a kan gadon nan saboda yanda ciwon mara yake karuwa, jimawa kadan taji ta jike don haka ta shiga bandaki ta wanke jikinta ta sami audugar da Hamida ta rage saura daya ta sa a jikinta. Ta fito daga bandaki tana tunanin inda zata sami kudin sayen pad, domin da ta tambayi Umma kudi a sayo mata Panadol sai da ta gwammace bata tambaya ba saboda yanda Umman ta dinga yi mata gori da tuna mata yanda tana fama da marayun kannenta ta kaso aurenta zata kara mata nauyi madadin ta tambayi mijinta. Ta zauna a gefen gado ta dafe mararta, a hankali kuma ta dunkule ta kwanta tana fitar da hawayen da ta kasa tantance na menene; ciwon mara ko kuwa tunanin inda zata sami kudin pad ko kuma dai bakin cikin yanda Mukhtar yaki ya zo ya mayar da ita.

Karfe uku Sabir ya dawo daga makaranta, kana shigowa gate din gidan kafin ka shiga cikin gidan dakinsa yake. Sai da ya ajiye kayansa sannan ya shiga cikin gidan, ya sami Umma a falo. Bayan ta amsa sallamarsa yace

‘Umma Yaya Safiyya tana daki.’

‘Eh tana ciki’

Yana shiga dakin ya sa hannu a aljihu ya zaro gyadar da ya siyo mata; tunda ta dawo haka yakeyi in dai ya dawo daga makaranta sai ya kawo mata wani abu, gyada, kwakwa, cashew da sauransu.

Yanda ya hangota a tsakiyar gadon a dukule ya san ba lafiya ba. Da sauri ya karasa ya ajiye gyadar a gefen gadon

‘Ya Safiyya baki da lafiya.’

Ta dago kanta ta dubeshi, goshinta ya jike da gumi ga hawaye a idanuwanta da sun riga sun yi jawur da kyar tace

‘Cikina Sabir, ciwo.’

Ta koma ta dunkule tana numfashi da kyar. Cikin hanzari ya fito ya sami Umma a falo

‘Umma Ya Safiyya bata fa da lafiya asibiti ya kamata a tafi.’

Hararsa Umma tayi tace

‘To ubanta, ai ta sha magani kuma ba wani abu bane period pain ne.’

Ya jijjiga kai

‘Ki zo dai ki gani Umma.’

Ta ja tsaki sannan ta mike ta bi bayansa, yanda taga Safiyyan itama ya dan razana ta. Ta karasa ta zauna ta dafa bayanta

‘Safiyya wai dama haka al’adarki take miki ciwo da yawa.’

Tana cije baki tace

‘Na manta Umma, ai tunda na haifi Nana banyi ba, wannan ne na farko.’

Da sauri Sabir ya fice daga dakin ya dawo falo ya dauki wayar Umma ya kirawo Yaya Habibu, ya dauka kafin su gaisa yace

‘Sabir ne Yaya, gara kazo a kai Yaya Safiyya asibiti bata da lafiya sosai kada ta mutu.’

‘Subhanallahi, ka ganni dama ina hanyar gidan yanzu zan karaso ka ce da Hajiyan su shirya.’

Kafin minti goma shabiyar Yaya Habibu ya karaso Umma ta kama Safiyya ta cewa Sabir ya zauna saboda Hamida zata dawo daga makaranta, suka wuce asibiti.

Asibitin Mallam Aminu Kano ya nufa wanda shine ya fi kusa da su, suna isa Yaya Habibu ya wuce da su emergency inda daga nan aka ce tunda matsalar mara ce su wuce bangaren mata.

Da kyar likitan ta samu ma’aikatan jinyar suka mikar masa da ita, ta daure ta amsa tambayoyinta bayan ya lallatse cikin. Take aka turasu scanning wanda a nan kusa dakin yake, suka gama Yaya Habibu ya biya suka karbo takardar suka kawowa likitan.

Likitan tana zaune a kujerarta yayinda Yaya Habibu yake zaune a gaban teburin inda Umma take tsaye a gefen Safiyya wadda take kwance a kan gadon tura mara lafiya da yake dakin likitan. Likitan ta dubi Yaya Habibu tace

‘Yallabai dama an san tana da ciki ko?’

Ya juya ya kalli Umma, wadda tace

‘Ban sani ba gaskiya.’

Ta mayar da dubanta kan Safiyyan ta dunkufa kusa da fuskarta tace

‘Kin san kina da ciki ko Safiyya?’

Ta share gumin Dake fuskarta tace

‘Ban sani ba wallahi, ai na gaya miki idan ina shayarwa bana al’ada kuma kin san idan na sami ciki bana laulayi sai dai kawai naga ciki yana girma. Gaskiya idan cikine sai dai ko kafin na yaye Nana na sameshi tunda kinga yanzu kusan wata uku ko biyu ne da yayeta ban yi al’ada ba don ko yanzun ma na zata al’adan zan yi.’

Wadannan bayanan duk a kunnen likitan don haka ta dubi Yaya Habibu tace

‘To gaskiya ga scanning dinta ciki ne da ita sati goma sha hudu, ya riga ya lalace a ciki shine yasa marar take ciwo zubewa cikin zai yi. Don haka yanzu zamu yi mata allura sannan mu bata magungunan, amma in sha Allahu nan da awa daya idan ta dan huta abinda ke cikinta ya fado sai ku tafi da ita gida don ba wani abu ne da yake daukar lokaci ba.’

Tuni yawun bakin Safiyya ya kafe, ta kawar da kanta daga hararar da Umma take zabga mata wadda idon likita da Yaya Habibu ne suka hanata magana. Yaya Habibu yace

‘To babu damuwa Doctor, a ina za a biya kudin?’

Ta miko masa takardu tana fadin

‘Ka sa mana hannu a wannan sai ka fita nan waje ka kai takardun za su rubuta maka kudin idan ka biya sai ka dawo da takardu da rasit din sai a yi mata.’

Ya mike ya fice, likitan ta kirawo ma’aikatan jinya ta umarcesu da su tura Safiyya dakin wankin ciki, suka turata suka fice Umma na biye da su.

A bakin kofa Umma ta zauna ita da Yaya Habibu suna jira a gama da Safiyya, Yaya Habibu ya dubi Umma yace

‘Kinga ikon Allah ko Umma, aure ya kare ita da Mukhtar sai dai idan ya sake shiga sawun manemanta.’

Umma ta jijjiga kai

‘Babu yanda banyi da yarinyar nan ba ta kirawo shi ta bashi hakuri, da tuni ta koma dakinta amma tayi kunnen uwar shegu dani yanzu gashi ai ta zama bazawara ko?’

Da mamaki ya dubi Umma

‘Umma ai sai hakuri, bata da laifi tunda kinga aure baya hannunta shi ya kamata ya mayar da ita kuma bai yi ba. Allah ya tabbatar musu da alkhairi kawai.’

Kafin tace wani abu ya zaro waya yana fadin

‘Bari na gayawa Baban Hotoro don ya sanar da iyayen Mukhtar din, don ni ba zan sake yi masa waya ba tunda ranar da ya sako ta na kirawo shi bai daga ba buma bai biyo bayana ba.’

A take kuwa ya sanar da Baban Hotoro wanda yace yanzu zai kirawo iyayen Mukhtar din, in yaso da daddare zai zo ya samesu a gidan Umman.

Sai da likita tazo sallamarsu Safiyya ta dubeta tace

‘Likita dama ana haka, ban fara al’ada ba fa tunda nayi yaye amma na sami ciki gashi har wata uku ban sani ba?’

Tayi dariya ta bar rubutun da takeyi ta fuskanci Safiyyan sannan tace

‘Me zai hana? Abun ai ikon Allah ne, bakiga wasu idan suka haihu da zarar jinin haihuwa ya dauke suke samun wani cikin ba? Kuma ai kince wannan shine na uku, Kinga cikin fari shine yake motsi da wuri gashi kuma kince ba kya laulayi. Kuma da yake kin taba haihuwa marar ta bude ba lallai ya daga miki mara da wuri ba, watakila shi yasa baki san dashi ba tunda ma kin saita kwakwalwarki a kan kina jiran al’ada.’

Tayi dariya ta dafa kafadarta tana fadin

‘Kada ki damu, yanda aka wanke miki cikin nan ba lallai ma kiyi al’ada ba zaki ga wani cikin ya shiga.’

Ta sunkuyar da kai, ita kuma likitan ta cigaba da rubutunta ta gama ta sallamesu.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA BIYU

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA SHA UKU

13

Tunda ya shigo gidan ta fito daga falon Hajiya da gudu ta makale a jikinsa, ya sa hannu ya dauketa yana duba fusakarta, yace

‘Nanata ya akayi ne? Ko Yaya ya tsokaneki ne in zane shi?’

Ta kara zumbura bakinta wanda dama a zumbure ta fito da shi, ya kalleta yana shafa bayanta yayi murmushi. Ya san yau muskilancin Khadija ya motsa. Ya karasa falon Hajiya dauke da ita, babu kowa a falon sai Bahijja wadda take zaune tana kallon tashar MBC 4, bayan Bahijjan ta gaisheshi yace

‘Anti Ba yau me kika yiwa ‘yar taki ne take fushi, ko magana ma taki yi.’

Ta harare ta tace

‘Wallahi yau haka ta tashi Yaya, takiyiwa kowa magana wai dole sai an kaita wajen Mamanta abinci ma yau sai da na zare mata ido taci.’

Ya dubi Nanan yace

‘Nanata wajen Mama za ki je?’

Ta kara zumbura baki ta jijjiga masa kai alamar eh.

‘Gobe zan kai ki wajen Mama kin ji. Bahijja ina Hajiya ne?’

‘Tana wajen Baba.’

Ya gyara zama don ya jira ta ta sauko kafin yaje wajen Baban, Bahijja ta mike tana fadin

‘Bari na dubo abinci Yaya, ko akwai abinda za a kawo maka?’

‘A’a babu komai.’

Ta wuce kicin ta barshi da Nana tana ta faman cika tana batsewa. Sati mai zuwa zai je ya dawo da Safiyya don ko shi ma ya gaji da kewarta, duk da ya sami damar yin abinda yake so da ‘yan matansa amma baya jin dadin shiga gidansa ya tarar bata nan. Yana kallon sakonninta a WhatsApp jira yake har sai ta bashi hakuri in ya so sai ya kafa mata sharuddan dawo da ita, smma ya ga bazata fadi abinda yake ranta ba don sallamace kawai sakon da take tura masa. Ya yanke ko ta bashi hakuri ko bata bashi hakuri ba zai je da kanshi ya gayawa Umma bincike takeyi masa, idan Umma tayi musu shari’a sai ya mayar da ita su tafi gida. Ko don su Nana ma ai ya mayar da ita, duk abinda suke so ana musu a nan gidan amma ya san suna kewarta. Ga shi Nurain ya fara zuwa makaranta ya bar Aminu da aikin kaishi har unguwarsu, shi kuma kullum sai ya baro office da rana ya dauko shi ya dawo da shi gidan Hajiya.

Sallamar Hajiya ce ta katse masa tunanin, bayan ya amsa sallamarta ta shiga ta zauna ya gaisheta ta amsa. Ta mikawa Nana hannu tana fadin

‘Taho Nana kawata kinji, zo in baki labari.’

Ya sauketa yana fadin

‘Yau ai na ga kawar taki rigima take ji.’

‘Hmm! Khadija dama ai gidan rigima ce. Kaje Baba yana sama yana kiranka.’

Ya tashi ya fice.

Yana shiga ya tarar da Baban a kan kujera ranshi a matukar bace, ya tsuguna a gabanshi yana mamakin abinda ya bata masa rai haka. Da kyar a ciki ya amsa gaisuwarsu, sukayi shiru na dan lokaci.

‘Mukhtar.’

Baban ya kirawo shi, ya dago da kansa suna hada ido ya koma ya sunkuyar da kai. Baban ya cigaba

‘Ka yi waya da Safiyya ne?’

‘A’a Baba.’

‘Ka mayar da aurenta ne?’

‘A’a Baba amma in sha Allahu ranar Asabar zan je na mayar da ita.’

‘To ka barshi ma don ko ka mayar ma ba zai yiwu ba.’

Zuciyarshi yaji tana neman ta daina harbawa don ya zata mutuwa Safiyya tayi. Take ya fara Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun a zuciyarsa. A firgice yake duban Baba da ayar tambaya a fuskarsa.

‘Ka saketa da ciki kuma cikin ya zube dazu, wanda hakan yake nufi ta gama iddarka idan kana sonta sai dai ka shiga cikin zawarawa ko zata saurareka.’

Ya ji wani abu ya tokare masa zuciya, take yawun bakinsa ya kafe. Ya lashe lebe yace

‘Baba bata da ciki fa.’

Ya harareshi sannan ya yi masa bayani kamar yanda Baban Hotoro yayi musu. Ya goge fuskarsa wadda ta jike da gumi, tabbas ya tuna tana ta ciwon kai a daidai lokacin da yayiwa Fatima birthday wani lokacin kuma tace cikinta ya kumbura. A lokacin yayi tunanin saboda ta dorawa kanta damuwa ne shi ya sa kanta yake yawan ciwo, ya san kuma itama abinda ya hana ta bawa ciwon mahimmanci kenan. Kuma ya san in ta samu ciki bata laulayi ko daya sai dai kawai yawan ciwon kai. Yana Allah-Allah ya tsokaneta yace mata cikine da ita; don ta gaya masa da tayi al’ada zata je tayi tsarin iyali sai Nana ta shiga makaranta zata sake haihuwa; sai ya manta kuma ya zo yayi wannan sakin.

Ya sunkuyar da kai yayi shiru kamar wanda ruwa ya cinye, Baba ne ya katse shirun yace

‘Hakane ko ba haka bane?’

‘Hakane Baba.’

‘To sai ka koma cikin zaurawa Allah ya bawa mai rabo sa’a, idan kuma cikin ‘yan kallo zaka koma sai muyi mata addua Allah ya bata mijin da yafi tsohon mijinta.’

Suka yi shiru kowa da abinda yake tunani. Wai shi Baba yake cewa tsohon mijinta, lallai da ba Baba bane sai ya zagi mutum.

‘Tashi ka bani wuri.’

Ya tashi jikinsa babu kwari ya sauko ya nufi falon Hajiya. Tana zaune tana bawa Nana custard yayinda Bahijja take ta danne-danne a waya. Ko sallama bai iya yi ba ya zube a gaban Hajiya, ta harareshi tace

‘Meye haka kake nema ka fado kan mu?’

Bahijja ta mike ta shige kichin. Ya dubi Hajiya ya goge fuska

‘Wallahi Hajiya ban san tana da ciki ba, jibi Asabar nake cewa zan je da dawo da ita.’

‘To ai yanzu ka sani ko?’

Ya sunkuyar da kai, suka yi shiru. Jimawa kadan Hajiya ta sauke Nana ta mika mata kwanon custard din data shanye tace

‘Jeki ki kaiwa Anti Ba.’

Ta karba ta wuce kichin.

Ta mayar da hankalinta kan Mukhtar wanda yake zaune a gabanta ya sunkuyar da kai kamar mai daukar karatu

‘Damuwar me zaka yi, ka huta da wadda take damunka? Ai sai kawai ka fara sabuwar rayuwa babu mai damuwa da abinda kayi, ka dai cutar ‘yayanka tunda ka rabasu da uwar da ta haifesu bayan kai ba haka mahaifinka yayi maka ba. Allah ya sauwake.’

Kafin yace wani abu ta tashi ta shige daki ta barshi a falon, jimawa kadan shima ya tashi ya fice.

Tun da aka fito da Safiyya daga dakin wankin ciki Yaya Habibu yake faman tambayarta ko wani wajen yana mata ciwo tana cewa a’a, amma kuma yana kallonta ta kasa daina kuka. Kuma yana kallon yanda Hajiya take ta faman harararta tana kwafa, ya san dukansu su biyun mutuwar auren Safiyyan ne yake tada musu hankali musamman ita Safiyyan da yake matukar jin tausayinta. Bayan sun dawo gida ya dade a falon shi da Hajiya yana ta faman bata baki a kan tayi hakuri ta kyale Safiyya ta sami natsuwa. Yana nan a zaune a falon ya kwalawa Safiyyan kira, zuwa lokacin tayi wanka ta canza kaya tana shirin kwantawa don ta huta.

Ta lallabo ta fito ta zauna a kan kujerar da take kusa da kofar dakin, a nutse ya dubeta da kulawa

‘Ki yi hakuri kin ji ko Safiyya, aure rai ne da shi kamar mutum idan kwanansa ya kare babu wanda ya isa ya rikeahi sai ya rabu. Kuma ko wanne bawa yana tare da kaddararsa wadda Allah ya gama rubutawa tun kafin a halicci mutum, don haka ki barwa Allah al’amarinki ki yawaita addu’a. Allah karimi ne kuma Yana sane dake kin ji.’

Kai kawai ta daga masa, ya cigaba

‘Gobe in sha Allahu zan zo da mota sai na dauke ki muje mu debo kayanki, in ya so sai na wuce da su can gidana na rufe M

miki su a daya gareji na zuwa lokacin da za a bukata.’

Yayi musu sallama ita da Hajiya, har ya kama hanya ya dawo Safiyyan tana zaune inda ya barta ya zaro kudi a aljihunsa 'yan naira dari biyar-biyar guda hudu ya mika mata

‘Ungo wannan ko zaki bukaci wani abu kafin na zo goben.’

Ta karba tayi godiya shi kuma ya kama hanya ya wuce. Sai can bayan magriba Sabir ya shigo da ledoji ya sami Umma da Hamida a falo, ya ajiye ledojin a gaban Umma yace

‘Yaya ne da zai tafi ya bani ya ce na siyo kaji guda biyu a dafawa Yaya Safiyya da kuma wannan lemo da ayaban yace na kawo mata.’

‘Ajiye a nan.’

Ya ajiye a gaban Umma ya juya.

Duk da tana jini haka ta tashi cikin dare tayi alwala ta zauna ta kalli gabas, da yake tana da hadda haka tayi tulawar wajen izu guda sannan ta dauki lokaci tana zikiri. Kafin ta tashi daga wannan zaman nauyin da take ji a zuciyarta ya ragu da kaso nai yawa, tayiwa kanta alkawarin daga wannan daren ba zata sake yin kuka a kan Mukhtar ba.

……..

Washegari da wuri Safiyya ta tashi daga bacci kamar yanda ta saba sai dai bata fito ba, da yake ranar babu aiki Hamida sai juyi take a gado. Tana nan zaune a kan teburin gaban Mudubi tana duba wayarta Sabir ya shigo, ta bashi dari biyar kudin da Yaya Habibu ya bata ya siyo mata pad, ya karbo ya fito.

Yana fitowa tsakar gida ya nufi waje Umma da take aiki a kicin tace

‘Ina zaka fita baka ci abinci ba Sabir?’

‘Ya Safiyya zan siyowa pad.’

‘Koma kace ta bayar da kudi ka siyo mana sabulun wanki da Omo, na ga jiya yayanku ya bata kudi.’

Tana jiyo duk abinda Umman take fada daga inda take zaune a dakin don haka kafin ma ya shigo ta dauko dari biyar, yana shiga ta mika masa ya tafi. Bata ji komai ba domin ta san watakila babu kudi ne a hannun Umman sai dai kuma jiya tana kallo Yaya Habibu ya bawa Umman kudin da yawansu zai iya kaiwa naira dubu goma, ta daga kafada ta bar wannan tunanin.

Yanda aka sanwa kowa kazar nan haka itama Safiyya aka saka mata yanka uku; hakarkari da cinyoyi biyu, ta cinye ta lashe romon shike nan tare da shayi da burodin safe kamar yanda kowa yayi.

Sai wajen karfe tara sannan Yaya Habibu ya zo, ba tare da bata lokaci ba ya dauki Safiyya da Sabir suka kama hanyar gidan Mukhtar me akorikura yana binsu a baya.

Basu sanar da shi zuwansu ba don haka babu tsammani ya gansu, yana ta wani faman sunkuyar da kai suka gaisa da Yaya Habibu. Yayi musu iso suka shigo falo, bayan sun zauna Yaya Habibu ya dubeshi yace

‘Kaya muka zo diba na Safiyya.’

Ya gyara zama yace

‘Yaya don Allah kuyi hakuri, wallahi ni kaina ban san yanda akayi ba.’

Ya kalleshi yana jin kamar ya buge shi saboda takaici

‘Babu komai ai ya wuce, na san an sanar da kai cewa cikin da ya bare a jikinta ya kai sati Sha uku don haka kaga daga jiyan ta gama iddarka.’

Ya share gumi ya hadiye malolon da ya tokare masa makogoro. Yana daga zaune ya mike ya nunawa Yaya Habibu hanyar cikin gidan yace

‘Bismillah.’

Ita da Sabir suka mike suka kama hanyar dakin, Yaya Habibu yana daga zaune yace

‘Ki hada kayan sawar sai mu shigo mu balle gadon.’

Suka wuce suka barsu a zaune shi da Mukhtar, wanda so yake yayi magana da Safiyyan amma Yaya Habibu yayi masa kwarjin da yawa ba zai iya ba musamman da yake ya san bai kyauta ba. Basu dade da shiga ba aka bugowa Yaya Habibu waya ya tsahi ya fice yana fadin

‘Ina zuwa.’

Yana fita yayi sauri ya shige dakin. Ta dora akwatinta a kan gado tana ta faman watsa kayan sawarta a ciki, ya karasa ya sha gabanta. Nan Sabir ya fice ya dawo falo ya zauna ya basu waje.

Ta dago ta dubeshi idonta cike da kwallar da take ta kokarin rikewa

‘Safiyya baki gaya min kina da ciki ba, me yasa?’

Tana bude baki zata yi magana kwallar ta kwace ta gangaro kan fuskarta, ta sa bayan hannunta ta share ta dubeshi tace

‘Ni ma ban san ina da ciki ba, ka san bana laulayi kuma bana al’ada idan ina shayarwa. Lokacin da na fara ciwon kai idan nayi magana sai kace na dorawa kaina damuwa, da yake a lokacin bana sa rai da daukar ciki sai na zata damuwar ce tunda ai akwai damuwar ko? Daga baya ma kuma zan iya cewa na manta da kaina kwata-kwata kokari kawai nakeyi na janye hankalinka daga kan matan da ba naka ba, shi yasa ban ma san da cikin ba. Sai dai kai din dama ai haka ka tsara, in ba haka ba me ya kawo saki. Sati na biyu a gida baka mayar da ni ba, ina kallo zan maka magana ta wahtsapp ka bude ka ki kulani ka ga kenan kai ka tsara haka. Allah ya sa haka ne ya fiye mana alkhairi.’

Ya sunkuyar da kai don shima nema yake ya zubar da kwalla, yana son Safiyya; wannan wacce irin jarrabawa ce? Ya bude baki a hankali yace

‘Zan dawo mu mayar da auren mu in sha Allah.’

Duk da kwallar da take fuskarta sai da tayi murmushi irin mai dauke da takaici din nan ta raba ta gefensa ta wuce wardrobe din da yake bayansa don ta debi wasu kayan tana fadin

‘Hmmmmn!’

Har ta kai gaban wardrobe din yana nan tsaye bai juyo ba, ta juyo a kaikaice tace

‘Yaran fa?’

‘Suna wajen Hajiya, za ki iya zuwa ki gansu duk lokacin da kike so ko kuma kiyi min waya sai na kawo miki su.’

‘Toh.’

Ya fice daga dakin saboda yanda hawayenta yake neman saka shi hawaye, ya shige dakinsa ya turo kofar.

Jimawa kadan Sabir ya koma dakin bayan ya ji shigewar Mukhtar, ya tayata suka kwashe kananan kayan tsaf Yaya Habibu kuma ya shigo da mai mota suka balle gadon suka hada da kujerun da kayan kitchen dinta duk suka kwashe. Har suka isa gida tana bayan motar Yaya Habibu tana share hawaye, yana kallonta amma ya rasa kalaman da zai bata hakuri da su don ya san da ciwo. A gida ya ajiyesu ita da Sabir yayi wa Umma bayani sannan ya wuce da kayan.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA UKU.

MATAR MUKHTAR

Written by:

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA GOMA SHA HUDU

14

Sati guda kenan da yin hutun makaranta don haka daga Fatima har Mommy suna gida kullum. A hankali Fatima ta fara samun nutsuwa tana bawa kanta hakuri a kan Mukhtar, domin har tayi blocking din status dinsa saboda kullum ta ganshi a WhatsApp sai hankalinta ya tashi. Satin da ya wuce aka yi birthday dinta, wanda shine na shekaru ashirin da shida. Ji take kamar tafi kowa tsufa gashi ba aure ba dalilinsa, babu ma wanda ya tayata balle ta sa rai. Duk kawayenta sun yi aure Kuma da yawansu sun daina kulata ma saboda ita bata da aure, wadanda basu daina kulata ba ma ita ta janye jikinta saboda gudun fitna. Janan ce kawai suke tare wadda sati biyu da suka wuce akayi bikinta, a Kano akayi don haka Mommy ta

hanata zuwa wanda ta ji dadin hakan don bata son duk wani abu da zai tuna mata da Mukhtar. Kullum sai Janan ta kirawota a waya sun sha hira, don haka take jin kawancensu mai dorewa ne.

So take idan Jami’ar Ahmadu Bello za su koma sabon zango ta koma tayi digiri na biyu (masters) amma bata san yanda Mommy zata dauki abun ba don duk abinda ta nuna tana son yi Mommy sai tace ta bari sai tayi aure. Saboda yanda Mommy take yawan yi mata zancen aure har bata son hira da Mommy yanzu, don in dai sun fara kafin su gama sai Mommy tayi maganar aure.

A falo ta sami Mommy tana zaune da remote din TV a hannunta tana kokarin kunna TV din, ta wuce ta zauna a kusa da Mommy a kan kujerar zaman mutum uku. Ta dubi Mommy tace

‘Sannu da hutawa Mommy.’

Ta ajiye remote din a kusa da ita bayan ta kai tashar Arewa 24 ta amsa da fara'arta

‘Yauwa Fatima.’

Sukayi shiru dukansu suka mayar da hankalinsu ga kallon TV din inda ake nuna wani fim na hausa. Gaba daya hankalin Mommy yana kan TV din yayinda Fatima ta mayar da hankalinta ga wayarta, jimawa kadan ta ajiye wayar ta dan yi gyaran murya tace

‘Mommy.’

Ta juyo ta dubeta, don haka ta cigaba

‘Mommy ina son komawa ABU na fara masters dina shi yasa ma bana kashe alawee don na dan tara sai Yaya ya cika mini.’

Ta sunkuyar da kanta saboda ta kasa gane ma’anar kallon da Mommy takeyi mata mai kama da harara. Mommy tace

‘Kina da hankali kuwa Fatima? Anya kuwa kin san me kikeyi? Wane masters kuma zakiyi babu miji a hannu? Ai yanzu mayar da hankali zakiyi ki fito da miji idan kikayi aure sai ki cigaba da karatun a gidan mijinki idan ya amince.’

Ta karkata kai ta kwantar da murya

‘Mommy wai gani nayi tunda mijin bai zo ba ai sai na fara karatun, watakila ma mijin yana makarantar. Duk lokacin da Allah ya kawoshi sai ayi auren.’

Sai da ta zabga mata harara sannan ta bata amsa

‘Babu wani masters da zaki fara yanzu, ki ma bar wannan zancen sai kin yi aure. Idan kika fara masters maza kara gudunki zasuyi, ko yanzun ma wani wannan degree da kikayi ne zai hanashi kulaki. Kiyi kokari ki fito da miji in ya so daga baya a yi maganar karatun.’

‘To Mommy.’

‘Yauwa.’

Suka yi shiru na dan lokaci, jimawa kadan Fatima ta mike zata koma daki Mommy ta dakatar da ita

‘Fatima.’

Ta dawo ta zauna tana sauraron Mommy.

‘Dubu talatin ne alawee din naki ko?’

‘Eh, ashirin da tara ne Mommy.’

‘To kinga ba kya bukatar kudi da yawa, duk wata ki dinga turo dubu ashirin account dina. Kayan kichin kusan duka na gama saya miki su sai mu fara sayen na daki da falo, kema ki sayawa kanki wani abu.’

Ta kalli Mommy ta sunkuyar da kai

‘To Mommy, daga next month zan fara turowa.’

‘Yauwa. Kuma ki mayar da hankali ki saurari mutane ki samu ki fitar da miji, duk wata dama da kike da ita ta yin ruwan ido yanzu ta kare dole ki hakura ki karbi wanda ya samu.’

‘To Mommy.’

Da taga alamar zancen ya kare ta tashi ta koma daki, tana shiga ta turo kofar ta kwanta a kan gadonta sai hawaye.

Tana son ta koma karatu saboda ta sami cigaba, bata son wannan zaman na jiran mijin da ba’a san ranar zuwansa ba. Kullum sai mommy ta dinga cewa ta fito da miji kamar wadda ta boye shi a jakarta, itama tana son auren kuma tana takaicin kuskuren da ta aikata a baya.

Amma haka zata zauna idan miji bai zo ba ba zata yi komai ba kenan? Sai da ta gama addu’a da shawarar me zatayi da kudin alawee din da take tarawa business ko karatu? Da kanta ta yanke ta fara karatun sannan ta jewa mommy da maganar amma gashi mommy tace kayan aure za a siya da kudin, ko a ina ake aure babu

miji oho? Ta so tace ba haka za ayi da kudin ba amma ta kula kadan Mommy take jira tace bata son aure don haka ta hakura ta amsa kuma ta san dole ta yi yanda Mommyn tace.

Ta juya ta gyara kwanciyarta, ta share hawayenta da zanin gadon; babu wanda ya janyo mata wannan takaicin sai Mukhtar da kuma wautarta, Allah take roka ya kawo mata mafita. In dai masters ne ta hakura, Allah ya sa zuwa karshen shekara ta sami miji don ta kula zamansu da Mommy ya kusa ya fara tsami.

_

Tunda Umma taga Safiyya ta koma Sallah ta saka ta a gaba sai da ta fito aka raba aikin gida da ita, itama Safiyyan hakan yayi mata daidai tunda ta san yanzu kam babu wanda ya san iyakacin zaman. Abu daya ne yake bata haushi yanda duk wani aiki itace zata yi ko da Hamida tana nan, idan ta saka ta aiki sai Umma tace ta kyaleta ita karatu takeyi.

Idan dai kaji Safiyya tana hira a gidan nan to ita da Sabir ne, duk kusancin da suke da shi da Hamida basa doguwar hira domin ita Hamida miskila ce sosai kuma bata fiya hira ba sai ta wuni ba tare da ta cewa kowa komai ba.

Damuwarta ta karu musamman da yake duk abinda take bukata sai ta tambayi Umma, Yaya Habibu yana bata kudi amma a gaban Umma take bata. Yana tafiya Umma zata fara neman dalilin rabata da kudin; kawo a siyo maggi, kawo a siyo sabulu, saka min katin waya ko kuma kawo kudi a siyo mana salad; a haka tsaf sai Umma ta ga babu ko sisi a hannunta. Don haka wani lokacin ma in dai Yaya Habibu ya bata kudi yana fita zata mikawa Umman tace ta ajiye mata, bata sake bi ta kai.

Idan ta tuna yaranta kuma sai tayi kuka; ta san za a rikesu cikin kulawa a inda suke amma itama tana son yaranta, tana kewarsu tana son kasancewa da su. Haka zata yi kukanta ta bawa kanta hakuri. Wani lokacin sai ta yi kamar taje gidan Yaya Hajiyayyaye ta kwana biyu sai kuma ta fasa saboda bata ga fuska ba daga wajen Yayan, gani take kamar ba zata barta ta sake ba. Ko babu komai idan aikatau zata yi gara tayi a nan gidan Umman kawai.

A kwance take a daki bayan sallar la’asar ta jiyo muryar Nurain yana yiwa Umma magana a tsakar gida, da hanzari ta tashi ta matsa bakin tagar dakin ta daga labule ta hango su. Aminu ne ya kawo su bayan ya gaida Umma ya sanar da ita sai da daddare zai zo ya daukesu, yayi mata sallama ya fice.

Ta juyawa tagar baya ta runtse ido tana fuskantar sama tana murmushi tare da yiwa Allah godiya. Yau sati hudu kenan da kwaso kayanta, duk da yace idan tana son ganinsu ta gaya masa zai sa a kawo mata su amma ta kasa kiransa. Duk da tana gayawa kanta zata basu lokaci sosai su saba kafin ta nemesu, ta dafa kirjinta tare da bude idonta a dai-dai lokacin da suka shigo dakin da gudu. Nana ce a gaba tana kiran

‘Mama Mama.’

Da karfi suka fada jikinta suna dariya, saura kadan su kada ita. Ta ja su ta zauna a gefen gado ta dorasu a kan cinyarta tana duban fuskokinsu. Nana ta kalleta ta rungume hannuwanta tana zumbura baki tace

‘Mama kika gudu inata nemanki ashe kina gidan Umma.’

Kafin ta bata amsa Nurain ya cigaba

‘Eh Mama, kinga har Abba ya sani a makaranta Baba Aminu ne yake kaini bakiga jaka ta ba.’

Ta hadasu ta rungume tana kokarin tokare kwallarta

‘Iyye! Sabon dan makaranta.’

Nana ta juyo da fuskarta wajenta tace

‘Mama muma a nan zamu zauna ko?’

Tayi murmushi tace

‘Baba Aminu zai zo ya daukeku in an jima, amma gobe ma zai dawo daku.’

Nurain yace

‘Haka ma Hajiya tace mana. To Mama yaushe zamu koma gidanmu da mu dake?'

Ta kallesu tayi shiru, tamabayoyin nasu suna neman sakata kuka, ta rasa wanda zata amsa. Kallonsu kawai takeyi tana murmushi.

Ummace ta shigo ta samesu tana fadin

‘To Nurain ga karas an siyo maka, ga yalo harda goruba yanzu na sa aka siyo a makota.’

Da gudu suka sauka suka nufi Umma da take tsaye a bakin kofa saboda suna son irin wannan kwadayin kuma sai a nan gidan Umma suke ganinshi.

Haka suka karasa wunin, da daddare Umma tayi tuwon shinkafa da miyar kuka, tare su Nurain suka zauna da mamansu a daki suna ci suna hira. Sai can wajen karfe tara sannan Aminu ya zo daukarsu, Safiyya ta gode Allah saboda lokacin Nana ta yi bacci don haka a hankali ta dauketa ta saka masa ita a mota tana godewa Allah idan ta tashi tayi musu rigimar a can.

Bayan sun tafi Safiyya da Hamida suka dawo suka zauna a falo wajen Umma. Ta dubi Safiyya tace

‘Me yasa Baban nasu bai kawo su ba?’

‘Ban sani ba Umma, nima kawai haka na gansu.’

Sukayi shiru suka mayar da hankalinsu kan TV dake kunne a dakin.

Umma tace

‘Kinga saki daya ne aurenki akwai damar a sake daurawa ku koma, ki bishi a hankali ki samu ki koma wajen ‘yayanki. Duk matar da kika gani a gidan aure hakuri takeyi da miji, ki lallabashi ki koma wajen ‘yayanki ya fi rufin asiri kada ki tsaya wannan miskilancin naki na banza.’

Ta gyada kai tace

‘To Umma.’

Jimawa kadan ta tashi ta shige daki, wucewa tayi ta tsaya a bakin taga ba tare da tana kallon wani abu ba; wato ko a wane hali Umma so kawai takeyi ta mayar da ita gidan Mukhtar. Ita Umma sam har ya zu bata ga laifi sa ba, ina ma laifi ace tunda auren ya mutu Allah ya fito mata da miji na gari. Tabbas ta ji dadin ganin yaranta bazata bari wani tunani ya kwashe mata ‘yar walwalar da ta samu ba don haka ta juya ta koma ta zauna a gefen gado. Ta dauko wayarta da take gefen gadon ta fara duba Whatsapp, tana cikin kallon status ta zo kan status din kawarta Karimatu wadda ta sa hoton Jawad yaronta. Har zata yi mata sako a kai sai kuma ta canza shawara, sun kwana biyu basuyi waya da Karima ba don haka kiranta zata yi su gaisa ta san bata kwanta ba tunda ta ganta online.

Tana kirawa kuwa aka dauka, da hayaniya da murnarsu suka gaisa suka fara hirarsu, Karima tace

‘Kin san tun last week nake son kiranki ban samu time ba nayi miki albishir.’

‘Allah kawata, na me?’

‘Mun dawo Kano, nan kKarkasara. Idan ba na manta ba kusa da unguwarkune ko?’

A sanyaye ta amsa don Karima bata san aurenta ya mutu ba tace

‘Eh kusane amm..’

Kafin ta rufe baki Karima tace

‘Ai kuwa gobe da yamma za ki ganni.’

‘Karima ai ina gidan Umma fa, aurena da Abban Nurain ya mutu.’

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun! Ke kawata? Garin yaya? Kar dai a kan maganar nan?’

Ta amsa cikin firgici.

Tayi murmushi tace

‘Uhm, kusan hakan kenan.’

Ta dan bata labarin yanda abun ya faru yayinda ita kuma ta jajanta mata sosai. Tace

‘Shiyasa nace ki shigo da manya ciki kawata kada kuyi abu daga ke sai shi.’

Ta jijjiga kai

‘ba zaki gane ba kawata.’

‘Allah ya kyauta, Allah ya sa ku daidaita ku koma kawata ko don yara ma.’

‘Uhm, ta wajen ina kuke a Karkasaran zan fito ranar Asabar in sha Allahu sai na biyo mu gaisa mu sha hira.’

‘Um, muna nan dai ta bayan Aminu Kano dai-dai farkon katangar idan kika tsallaka titi. Idan zaki taho kiyi min waya dai sai na karasa miki kwatancen.’

‘To kawata in sha Allahu za ki ji ni.’

Suka yi sallama suka ajiye wayar.

Hirar da sukayi da Karima ta kara debe mata kewa don haka da farin ciki ta kwana.

Tunda aurenta ya mutu bata fita ba amma yanzu tana jin ranar Asabar din in dai ba ummace ta hanata ba zata fita idan taje gidan Baban Hotoro in tana dawowa sai ta tsaya su gaisa da Kariman. Gidan Yaya Habibu ma ta so zuwa amma shi Yaya Habibu matarsa bata son mutane, ko daya bata son taga wani a cikinsu ya rabe shi, don haka ma suke baya-baya. Duk kokarinsa na ganin ta canza ya ci tura don haka Umma tace ya rabu da ita tunda itace uwar yaransa kuma bashi da matsala da ita sai wannan kin mutanen kawai.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA HUDU.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA SHA BIYAR

15

Tun ranar Juma’ah da daddare ta gayawa Umma tana son zuwa ta gaida Baban Hotoro sannan ta biya ta gidan Karima, ta ji dadi sosai da taga Umma batayi wani musu ba kuma da yake jiya da yamma da Yaya Habibu ya zo ya bata dubu biyu, Umma ta karbi dubu daya tana da sauran daya don haka bata bukatar ta tambayi kudin mota.

Ita ta dafa musu abincin safe don haka tana saukewa ta yi maza ta gyara gidan ta wankewa Umma bandaki sanna ta shirya. A falo ta sami Umma tare da Hamida da Sabir suna zaune a falo, Sabir ya dubeta yace

‘Ya Safiyya ina zaki je?’

‘Gidan Baban Hotoro.’

‘Kai ai kuwa nima na dade ban je gidan ba, ko na zo mu tafi?'

Da fara’arta ta amsa shi

‘Eh mana, taso mu je.’

Ta dubi Hamida

‘Ko zaki je kema sai mu jira ki ki shirya mu tafi?’

Ta girgiza kai

‘A’a, ina da test ranar Monday gara nayi karatu wataran naje.’

Umma ta hararetа tace

'Ko baki da test ma daman ba zuwa kike son yi ba, daddawar daka. Ayi mutum shi dai ba zai shiga mutane ba sai kace wata mujiya.'

Sukayi dariya ita kuma Hamida tana ta zumbura baki. Safiyya da Sabir suka yiwa Umma sallama suka kama hanya.

.....

Matan Baban Hotoro biyu da kuma ‘yaya goma sha biyu, biyar na uwar gida wadda ake kira Mama bakwai kuma na amarya wadda ake kira Anti. Matsaikaici gidane me bene hawa daya, wajen Mama ne a kasa yayinda wajen Anti yake a sama shi kuma Baba nasa wajen a kasa yake daga gefe.

Wajen karfe sha daya da rabi suka isa gidan, suna shiga suka sauka a wajen Mama. Yaranta duka sunyi aure don haka babu kowa a wajen sai mai aikinta sai Aisha da Zahra jikokinta na wajen Babbar yarinyarta Afiya da suka zo mata hutun karshen mako. Nan suka zauna suka gaisa suka dan taba hira, suna cikin hirar ne Sabir ya jiyo su Aliyu a farfajiyar gidan don haka shima ya tashi ya fita.

Aliyu da Yasir sune kananan yaran Anti kuma sa’anni ne da Sabir sai dai Yasir ya girme masa da shekara daya da rabi. Da yake yaran Anti mutum biyu kawai aka aurar akwai 'yan mata biyu Saliha da Rukayya wadanda suke karatu a jami’a, don haka ba jimawa Safiyya ta dubi Mama tace

‘Bari naje sama mu gaisa da su Saliha, kafin na sauko Baban ya fito sai na gaisheshi mu wuce.’

‘Au na zata wuni kuka zo mana Safiyya?’

Tayi murmushi

‘A’a Mama, ai in sha Allahu da bikin su Saliha kwana ma zanzo nayi tunda an kusa, yau din akwai inda za mu je shi yasa.’

Ta haye sama wajen su Saliha, sun dan jima suna hira duk da su din ba sa’anninta bane tunda ta basu wajen shekaru hudu amma akwai shakuwa ta zumunci tsakaninsu.

Ta mike tayi musu sallama ta sauko don ta gaida Baba su wuce, tana karasowa cikin falon Mama ta tarar da Auwalu yana zuane suna hira da Mama. Auwalu dan wan mahaifinsu ne wanda a nan wajen Maman ya girma, yana da aure da yara hudu kuma suna zama ne a Jigawa saboda a can yake aiki; ya zo hutun karshen mako ne da yake nan ne gidansu ya zo ya gaida Mama da Baba.

Ta dan zauna suka gaisa da shi tana saka baki a hirar tasu, a haka Baba ya fito ya samesu. Ya zauna a kan kujerar zaman mutum uku su kuma suka koma kan kafet suka kwashi gaisuwa. Ya dubi Safiyya yace

‘Safiyya, ya gidan ya Umma da kannenki?’

‘Lafiya kalau Baba.’

‘To ya naki yaran? Kina dan tuntubarsu ko?’

‘Eh Baba, an kawo su ma sun yi mana wuni.’

‘To ma sha Allahu, in sha Allahu komai zai warware kinji. Ki ci gaba da rayuwarki kina walwala kada ki sa wata damuwa a ranki, Allah yana sane da bawa kuma Allah mai jin kai ne. Allah ya baki mini na gari.’

‘Amin.’

Ta amsa da murya kasa-kasa.

Baba ya juya ya dubi Auwalu wanda fuskarsa ta nuna alamun sun sakashi a duhu yace

‘Ka san aurenta ya mutu, harma ta gama idda.’

Mamakinsa ya kara yawa

‘Subhanallahi, ai ban sani ba. Allah ya sa haka ne ya fi alkhairi.’

Ta amsa da murya kasa-kasa

‘Amin.’

Ta yiwa Baba sallama ya mike ya zaro kudi a aljihunsa naira dubu biyu ya mika mata

‘Ungo wannan ku hau mota, canjin kya sayi wani abun.’

Ta tsuguna tana godiya kafin ta rufe bakinta Auwalu ya zaro naira dubu biyar yana ta wani murmushi ya mika mata yana

‘Ga wannan ma kya kara.’

Ta dan ja baya tace

‘Yaya Auwalu ka b…'

Ya harareta ya dubi Baba

‘Ka gani ko Baba ni bata kawai nayi amma ba zata karbi nawa ba.’

Baba yayi dariya

‘Ai yayanku ne Safiyya, to in bakwa so duk ku bani na sayi goro.’

Ta karba tayi godiya, ta wuce kicin domin tayiwa Mama sallama tana tunanin abinda ya sa Auwalun yake kallonta kamar wani mayunwacin maye; Allah ya sa dai ba cewa zai yi yana sonta ba don bazata aureshi ba, ba don komai ba sai don kawai baya cikin tsarin mazan da take sha’awar aure. Amma shi din ta san mutumin kirki ne kuma yana da dan abun hannunsa.

Bayan ta fito ta sami Sabir a kofar gida da su Aliyu, sai da ya koma ciki yayi sallama da mutanen gidan sannan ya fito suka kama hanya.

Tasi suka hau zuwa court road inda zasu sauka su karasa karkasara gidan Karima kamar yanda tayi mata alkawari. Suna zama a tasi din ta dauko wayarta don kiran

Karima, sai ji tayi ance babu kudi; wanda taci bashi ta kirata jiya ma ashe ya kare. Ta kalli Sabir tace

‘Da kudi a wayarka na kira Karima, za mu dan tsaya a gidanta idan muka gaisa sai mu wuce.’

Ya zaro wayar ya mika mata, tana saka lamabr ta kira, bugu daya Kariman ta dauka

‘Hello, Salamu alaikum.’

‘Wa alaikumussalam, Karima Safiyya ce kin ganmu a tasi mun kusa karasowa AKTH din ta wajen ina za mu sauka in zan zo gidan naki.’

A ka dan yi shiru don haka tace

‘Hello kawata.’

Shiru dai har yanzu, sai dai kamar tana jin alamar numfashin mutum da ‘yan surutan da suke can wajen kamar na TV kadan-kadan. Ta sake cewa

‘Hello.’

Har yanzu shiru, ta cire wayar daga kunnenta tana kalla

‘Ikon Allah inaga dai bata ji na.’

Ta katse kiran ta sake kira nan take, haka wayar tayi ta ringing ba a dauka ba. Har suka zo Aminu Kano ba a dauka ba don haka tacewa direban tasi tunda BUK zai je ya wuce da su sai su sauka a unguwarsu wato kofar fanfo.

Har suka zo gida tana mamaki don kuwa ta tabbatar kariman taji lokacin da tace itace Safiyya, amma sai ta basar da yake ta san halin network. Suna sauka daga tasi bayan ta sallami direba ta zaro kudi a jakarta ta cewa Sabir

‘Ka ga ma har dubu biyu Baba ya bamu mu hau mota.’

‘Ai kuwa mun gode, ki barshi kawai a wajenki kya kashe ba ma sai kin gayawa Umma ba.’

Tayi ‘yar dariya

‘Gara dai na gaya mata kada shi ya gaya mata zancen ya zama wani abu da ban. Ungo dari biyar dai ka siyo min katin dari uku ka siyo na dari biyu idan munje sai mu bata canjin mu gaya mata haka.'

Ya karba ya tsallaka titi don ya siyo musu katin, ta cigaba da tafiya tana tunanin idan ta saka sai ta kirawo Karima da wayarta watakila don bata san lambar Sabir ba shi yasa ta ki dauka kuma taki biyowa.

……

Zuwa yanzu Safiyya ta riga ta saba da zama a dakinsu ita da Hamida idan dai ba wani abu zata yi a tsakar gida ko falo ba. Umma tana yawan zama a falo ko ita kadai ko ita da Hamida da Sabir, itama Safiyyan tana son zama da su sai dai yanzu da Umma ta ga tana walwala zata yi mata gorin aure:

‘da yanzu kema ai kina dakinki cikin sakewa.’

‘duk matar da kika gani a daki hakuri take wanda ke kika kasa.’

‘Allah ya baki miji mai kula dake baki sami natsuwa ba sai da kika kashe auren, ai kinwa kanki.’

‘ki lallabo Abban Nurain ku mayar da aurenku don yanzu ba son auren zawarawa ake ba, shine ya sanka shine kawai zai iya zama dake.’

Wadannan sune kalaman da Umma take yawan gaya mata wadanda suke bata mata rai. Kawo yanzu idan aka ce mata ba Umma ce ta haifeta ba to tabbas ba zata yi musu ba. Don haka kusan kullum tana daki ita kadai kamar wata mai laifi.

A kashingide take a gefen gado ta gama saka katin wayar da Sabir ya siyo mata; a cikin kudin

da Yaya Auwalu ya bata da suka je gidan Baban Hotoro ta bayar ya siyo mata tunda bata nunawa Umma su ba. Ta gama shigar da katin wayar ta sayi data ta yin Whatsapp, nan da nan ta kunna ta fara duba sakonnin. Tana cikin dubawa ta tuna tun wancan satin da suka je gidan Baban Hotoro tace zata kirawo Karima bata kirawota ba, don haka nan da nan ta danna mata kira ta san yanzu zata dauka tunda da wayarta me. Haka wayar tayi ta ringing ba tare da an dauka ba har ta tsinke, sai da ta buga Sau uku sannan ta hakura; watakil Kariman bata kusa da wayar. Ta hakura da kiran ta koma Whatsapp ta cigaba da duba sakonnin groups dinta, wani kira ne ya shigo wayar da wata lamba da bata sani ba, tayi tunanin Karima ce don haka tayi sauri ta dauka.

‘Salam alaikum.’

‘Wa alaikum salam.’

Sai kuma taji muryar namiji, wadda ba tare da bata lokaci ba ta gane Yaya Auwalu ne. Cikin fara’a suka gaisa duk da tana mamakin kiranta da yakeyi tunda bai taba kiranta ba sai dai su gaisa a WhatsApp ko a group dinsu ma family. Tace

‘Banibda wannan lamabar taka ai, shi ya sa da ban gane ba.’

‘Eh, ai ba itace ta Whatsapp din ba.’

‘Allah sarki.’

‘To ya kike Safiyya? Ya kuka je gida rannan?’

‘Lafiya kalau.’

Ta amsa da sanyin murya tana mamakin dalilin da yasa yake kiranta; Allah ya sa dai kada yace yana sonta don ba zata aureshi ba, ko babu komai suna mutunci da matarsa sannan kuma baya cikin irin mazajen da take fatan aure. Ya katse mata tunani daga daya bangaren

‘Kina jina ko Safiyya, wata magana ce dama nake so muyi dake, Allah ya sa dai ki fahimceni mu samu mu fahimci juna.’

‘Um to ina jinka Yaya Auwalu.’

‘Yauwa kin gane ko? Akwai wani waje da nake dan zama idan na shigo Kano can a farm center, da zaki zo ki sameni da sai muyi maganar a nutse.’

Taji wani banbarakwai amma dai ta daure tace

‘Gaskiya Umma bata barina fita zai ma fi sauki muyi maganar ta waya.’

Bata so tace ya zo gidan don kada Umma ta ganshi ta ce sai ta aureshi. Ya katse mata tunani

‘Umm kin gane ko, ai za ki san dabarar da zakiyi wa Umma ki fara fita tunda ni ma din maganar da nazo da ita sai an fitan in dai kin amince.’

‘Ai idan na san menene sai na san abinda zan gaya mata watakila idan taga abun yana da mahimmanci sai ta barni na fito.’

Tana jiyo sautin murmushinsa ta cikin wayar sannan yace

‘Yauwa ‘yar gari. Kin gane ko? Zuwa za ki dinga yi mu amfana da juna, ki dan taya ni hira ni kuma duk wata bukata taki ta kudi nayi miki ita komai yawansu.’

Ta so ta fahimci wani abu amma kuma bata son ta munana zato.

‘Ban gane ba fa Yaya Auwalu.’

‘Kin gane ko? Akwai hotel da nake sauka a nan din, yana can nesa da gari don haka kada ma kiji komai babu wanda zai ganki. Idan na shigo gari sai na kiraki kizo mu dan abun nan ni kuma sai na cika miki jakarki.’

Abin da bata son ta yarda dashi shi yake son ya gaya mata, bugun zuciyarta ya kara sauri domin ba a taba yi mata cin mutunci mai kama da wannan ba. Cikin dacin rai ta bashi amsa tana murmushin takaici

‘Hotel Yaya Auwalu? Zina kenan zan zo muyi? Lall…'

Da hanzari ya katseta

‘Ba haka bane, kada ki zama bagidajiya mana Safiyya. Kina bukatar kudi ni kuma ina bukarki ki zo ki debe min kewa, abu ne fa da za a yi a sirri. Ko baki gane bane?’

Zuciyarta ta gama harzuka har daci take ji a bakinta, yanzu har ta fara kama mazinaciya ne bata sani ba da yake mata wannan maganar.

‘Ni bana bukatar komai daga gareka, abunda kake bukata daga gareni kuma ba zaka samu ba. Ina maka addu’ar Allah ya shiryeka ko don saboda mutuncin iyalanka kuma zan cigaba da rokon Allah ya saka min wannan cin zarafin da kayi min. Allah ya isa ban yafe maka ba don ni ba mazinaciya bace.’

‘Ke S..’

Tayi sauri ta katse wayar, tuni kwalla ta cicciko mata ido ta sa bayan hannunta ta goge. Ta daga wayar ta lalubo lambar da ya kirata da ita tayi blocking, ta lalubo daya lambar ma da yake Whatsapp da ita itama tayi blocking.

Ta jefe wayar kan gado cike da takaici yayinda hawaye ya wanke mata fuska, bata son Hamida ta shigo ta ganta tana kuka don bata san me zata ce ya sakata kukan ba don haka ta tashi ta fada bandaki ta turo kofar.

Tunda take a rayuwarta ba a taba yi mata cin mutunci irin wannan ba; bata taba sanin Yaya Auwalu yana neman mata ba. Ko kuma itace tayi masa arha da yawa yake so ya fara ta kanta tunda ta zama bazawara? Abinda mijinta yayi da wasu matan ya haifar mata da fitna shine itama ake gaiyatarta ta aikata? Ba zata taba yafewa Auwalu wannan wulakanci da yayi mata ba. Ta share hawayenta ta matsa ta kunna fanfo saboda bata so a jiyo motsinta a bandakin. Sai da tayi kuka ya isheta har kanta ya nemi fara ciwo sannan ta wanke fuskarta tayiwo alwala ta fito daga bandakin, ta zauna a kan dadduma ta fara karatun kur’ani; wanda duk lokacin da ta ji tana shirin shiga damuwa shi take yi.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA BIYAR

MATAR MUKHTAR

Written by:

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA SHA SHIDA

16

Yayi kewar Safiyya sosai, musamman idan yaje gidan Hajiya Nana ta sa masa rigima sai ya kaita wajen Mamanta. A hankali yaran suka fara sabawa shima kuma ya saba, kuma da yake babu wanda ya sake yi masa maganar Safiyyan a gidan sai shima ya bar maganar. Yana son Safiyya kuma yana son su dawo suyi zamansu, amma shi jira yake ita ta nemeshi ta bashi hakuri, ya saba a rayuwarsa ‘yan matansa da yake lalata da su suna lallabashi don haka itama Safiyya ya san idan ta gama gwaruwa zata nemeshi; a lokacin ne shi kuma zai samu damar kafa mata sharuddan da ya tanada kafin ya mayar da aurensu.

Don haka ya cigaba da rayuwarsa yana cigaba da ginin gidansa yayinda mafi yawancin lokuta a hotel yake kwana da 'yan matansa wadanda yanzu suka kara yawa. Tun tuni ya rufe shafin Fatima don kawo yanzu ma ko tunawa baya yi da ita kwata-kwata.

.....

Sani Bashir abokinsa ne sosai wanda tare suka yi jami’a gaba daya da su Suraj, sai dai suna gama jami’a shi sani ya sami gurbin karatu a UK yayi tafiyarsa. Tunda ya tafi bai dawo ba yana cigaba da karatunsa a can yana aiki har sai yanzu ya dawo, kuma a dai-dai lokacin ne satin bikinsa ya shigo.

Tunda aka fara hidimar bikin aka nemi amarya Rukayya da ta hada abokan ango da babbar kawarta don shirye shiryen bikin amma tace bata da kawa, don haka sai ta hada su da kanwarta wato Jamila A. K. Tanko. Tunda aka hada Jamila da Mukhtar babban abokin ango su tsara yanda za a yi biki suka dinke, duk da a lokacin Mukhtar bai san me yake so daga gareta ba.

Kyakkyawace kwarai da gaske, ga farar fata, gashinta har gadon baya irin na buzaye saboda mahaifiyarta buzuwa ce. Baya gajiya da kallonta kuma baya gajiya da sauraranta musamman da yake ta iya hira ta daukan hankali ga murya kamar

sarewa. Saura sati biyu bikin suka hadu amma sun sami shakuwa kai kace sun yi watanni da sanin juna. Sau da aka gama biki sannan ya tabbatar mata da soyayyasa, itama da yake bata da wani saurayi a kasa sai ta nuna masa a shirye take tunda ya amince zata cigaba da karatu a gidansa wanda yanzu haka a level 2 take.

Da farko ya so ya rudeta ya samu biyan bukatarsa amma kuma da yaji waye mahaifinta ya san gidansu ba inda zai je yayi wannan wargin ya tashi lafiya bane. Ba wai kudi mahaifinta ya tara ba, amma fitacce ne a garin Kano kasancewar ya rike mukamin Chief Judge na kotun jiha. Da yake kuma Jamilan tayi yanda yake jin ta kai a nuna ta a taro sai kawai ya yanke shawarar aurenta tunda ma Safiyyan bata nemeshi ba.

Ana gama bikin yayarta da Sani su kuma suka cigaba da soyayyarsu.

Basu fi wata daya ba mahaifinta ya nemeshi ya sanar da shi idan aure zai yi ya turo magabatansa, idan kuma ba haka ba ya daina zuwa; inda shi kuma yayi alkawarin turo iyayensa nan da sati mai zuwa.

.....

A falo ya sami Hajiya tana zaune tana cin gyada me gishiri, su Nana suna ta kaiwa da kawowarsu tsakanin wajen Bahijjan wadda a dole suka mayar mata da suna Anti Ba da kuma da wajen Anti Habiba. Bayan ya gaisheta ta amsa da fara’arta, ya gyara zama ba tare da yace komai ba. Ta debi gyadar da take gabanta ta mika masa tana fadin

‘Kaima in sam maka gyadar ko in cinye kayata?.’

Yayai dan murmushi

‘Hajiya ai ledar kawai za ki turo min.’

‘Ba zan baka ba tamu ce ni da yara, in dai kana so ga kwaya goma.’

Ya mika hannu ya karbi wadda ta debo a hannunta, suka yi shiru kowa yana cin gyada. Jimawa kadan yayi gyaran murya yace

‘Hajiya dama akwai yarinyar da nake neman aurenta mahaifinta yace na turo, shine nace zan je na gayawa Baffa Kabiru in ya so sayi maganar da Baba.’

Ta dago ta dubeshi da damuwa a fuskarta tace

‘Aure kuma Mukhtar, ina Safiyya? Yanzu ashe bazaka mayarwa da yaran nan mahaifiyarsu ba in ya so daga baya sai ka kara auren?’

Ya sunkuyar da kai yana shafa keya

‘Hajiya ita din ma wannan mun yi magana da ita zata kula da su sosai in sha Allahu.’

Ta zuba masa ido na dan lokaci yayinda shi kuma ya kasa hada ido da ita, jim kadan tace

‘Hmn! Mukhtar dan wani da uwar wani sai a hankali fa, zaman bai fiya dadi ba duk kokarin mutum amma Allah ya tabbatar da alkhairi. ‘Yar gidan waye ita yarinyar?’

Ya fadada murmushi yana wani juyo da shafar kai

‘’Yar gidan Professor A. K. Tanko ce.’

‘A. K. Tanko mai sharia’a?’

‘Eh, shi Hajiya.’

Ta kada kai

‘To Allah ya tabbatar da alkhairi, ka sami Baffan naka kuyi maganar.’

Yayi mata sallama ya tashi ya fita, tunda Baba baya nana gara yaje yau din nan ya sami Baffa Kabiru don aje ayi magana.

Ba tare da wata matsala ba Baffa Kabiru ya fahimceshi, duk da shi din ma ya tuna masa dawo da Safiyya amma sai ya nuna ba zai yiwu ba. Don haka Juma’ah tana zagayowa aka je akayi tambaya inda ba a taso ba saida aka bayar da kudin aure aka saka ranar biki wata hudu.

Nan da nan ya cigaba da gininsa wanda yakeyi a unguwar zoo road; gida ne matsaikaici me ban sha’awa. Lokacin da ya sayi filin sai da ya kai Safiyya ya nuna mata sannan sukayi shawara a gina gida mai bene don tana sha’awar gidan sama. Daki uku ne a sama da falo da kuma dining area, kasa kuma daki biyu da falo da kichin sai wani karamin daki da yace yara ya yiwa wajen karatu.

.....

Yau Juma’ah don haka ana saukowa daga masallaci ya wuce gidan Suraj don sun yi zai rakashi sabon gidan don ya dubo ma’aikatan. Bayan matar Suraj tayi masa iso ta kawo ruwa sannan ta zauna suka gaisa yayinda Suraj din ya fito daga daki ya dubeshi yace

‘To abokina muje ko?’

Ya mike ya dubi Maman Anwar yana fadin

‘To Madam mu mun tafi zamuje mu duba ma’aikata ne a sabon gidana, kada ki damu har nana zan dawo miki da shi ba zan barshi ya je ko ina ba.’

Tayi dariya tace

‘Da kuwa ka kyauta.’

Ta dubi Suraj tace

‘A dawo lafiya.’

Suka wuce suka kama hanya a motar Mukhtar din.

A hankali suka dinga zaga gidan da yake an gama kusan duka ginin, masu aikin wutar lantarki ne suke saka wayoyi a cikin bango. Suna dubawa suna hirarsu yana kara yiwa Suraj bayanin dakunan, suka zo wajen karamin dakin da yake kasa wanda yayi don karatun yara. Suraj yace

‘Amma dai wannan bai kai daki ba ko? Sai dai ko masu aiki?’

‘A’a, su Nurain na yiwa shi don su samu wajen karatu da wasa.’

‘Yayi kyau, ka yi dabara kuma suma za su ji dadin hakan.’

Suka dan yi shiru suka karasa suka shige kichin yana leka inda suka sako wayoyin, Suraj da yake kusa dashi yana taya shi dubawa yace

‘Wai ya labarin Safiyya kuwa? Ko shikenan Jamila tayi fatali da ragowar son da ake mata?’

‘Ba zaka gane ba mutumi na, ai Safiyya tuni na barwa mai rabo. Da dai ace zan iya hada mata biyu to da na dawo da ita ko da bayan Jamilan ta tare ne amma gaskiya bana sha’awar zama da mace sama da daya.’

‘Allah sarki su Nurain, mutumina kai ko lissafinsu ma baka yi!’

‘Kai! Ai dole nayi lissafinsu. Ai ko itama Jamilan sai da muka yi da ita zata rike min su amana sannan aka fara maganar auren, ai duk matar da ba zata rike min yaran nan ba to ba mata ta bace.’

‘Ba zaka gane ba mutumina, ka ganni ko indai da rai da lafiya duk matar da ta haifarmin yaro ko daya ne ba zan iya rabuwa da ita ba sai dai idan yaron nan ya rasu.’

Ya kyalkyale da dariya ya dafa kafadarsa yace

‘Matsoraci, Hajara dai ta saka ka a kwalba sai yanda tayi.’

Shima dariyar yayi yace

‘Duk abinda zaka fada ka fada, ka gode Allah iyayenka suna tare har ka girma. Ni na zauna da matar uba kuma na san ciwon rashin uwa, makiyina ma bana masa fatan Allah ya jarrabeshi da irin wannan zaman. Kai ka san irin wahalar da muka sha ni da kannenna a hannun Anti. Idan dai ka bata yaran nan to ka sa ido sosai idan ba haka ba a gabanka zata kashesu ta ce maka mutuwa sukayi.’

Maganganun Suraj sun ratsa shi amma basu kai su sa ya duba yiwuwar dawo da Safiyya ba, shi zai so ma yaga idonta idan ta ga zai auri kyakkyawar yarinya kamar Jamila. Haka suka karasa zaga gidan zuwa magriba ya sallami sauran ma’aikatan suka kama hanyar gida.

Sai da Mukhtar ya ajiye Suraj a gida sannan ya kama hanyar gidan Hajiya.

Babu wadda yake gani a halin yanzu sai Jamila, idan ba ganinta yayi a cikin gidansaba ba zai sami natsuwa ba. Ya aminta da tarbiyyarta gata kuma wayayyiya, don haka yana ganin da shi da yaransa za su sami duk wata kulawa daga gareta.

Safiyya ce a zaune a daki a kan dadduma bayan da ta idar da sallar la'asar, daga inda take tana jiyo hirar Umma da Hamida a falo wadda da ace zata zo ta saka baki a hirar da sai Umma ta san abinda zata yi mata fada a kai. Sai yanzu take gane abinda ya sa mata ke hakuri su zauna da miji komai wulakancinsa, bata san ko zuwa tsawon wane lokaci wannan zaman zai zo karshe ba. Kamata yayi ace ta je ta dora abincin dare, amma gajiya tayi mata yawa. Matar da take yiwa Umma wanki bata da lafiya kwana biyu bata zo ba don haka yau dolenta ta wanke kayan Umma ta hada da nata.

Tana nan zaune ta jiyo Umma na cewa Hamida taje ta dora abincin dare; ta tabe baki don ta kwana biyu rabon da ta ga Hamida tana girki kusan tunda ta dawo gidan. Ta dauki wayarta ta duba lokaci, karfe biyar saura minti goma, ta mayar da wayar ta ajiye.

Tana nan tana lissafin tashi ta jiyo sallamar Saliha da Rukayya; yaran Baban Hotoro. Suka zauna a falo suka gaisa da Umma da Hamida, Umma ta tashi ta shige daki ta basu wajen.

Saliha ta dafa cinyar Hamida tace

'Hmm, ga ankon ku ke da Yaya Safiyya, jiya na kama Yaya Habibu yaje gaida Baba na lika masa na ce yanzu ake biya, kin san kafin ya bar gidan sai da naji alert ya biya muku ke da Ya Safiyya har dubu goma ya bamu ni da Rukayya wai mu sai janbaki. Kin san Ya Habibu ba dai kyauta ba.'

Ta karbi ledar da murmushinta tana fadin

‘Kai amma wallahi kin min dai-dai ta wajena, yanzu sai dinki kawai.’

Ta ta shi ta dauki ledar ta bi Umma daki ta nuna mata sannan ta dawo ta kawo musu ruwa suka cigaba da hira. Jimawa kadan Rukayya tace

‘Wai ina Yaya Safiyya ne?’

‘Tana daki.’

Hamida ta fada tana nuna kofar dakinsu, nan take ta mike ta fada dakin tare da sallama.

Ta karasa kan dadduma suka gaisa da Safiyya tana ce mata ya hidimar bikin, nan ta gaya mata labarin ankon da suka zo musu da shi. Suka yi shiru na dan lokaci Rukayyan ta dubi Safiyya tace

‘Ya Safiyya wai baki da lafiya ne? Wallahi naga duk kin rame.’

Tayi dariya tace

‘Lafiya ta kalau, bari ma ki ga yau nice zan dafa mana abincin dare amarya.’

Ta mike suka fito tare da Rukayyan, ta tsaya a falon suka gaisa da Saliha sannan ta wuce kicin kafin ta karasa Hamida tace

'Ya Safiyya na dora a abincin ai.'

Jimawa kadan suka tashi sukayi sallama da Umma da Safiyya suka wuce tare da Hamida wadda zata raka su. Suna Safiyya ta koma daki, gaban mudubi ta wuce ta tsaya ta zubawa fuskarta ido a mudubin; tabbas ta rame. Ta kai hannu ta shafa

kasusuwan wuyanta tana kallonsu yanda suka fito wuyan nata ya kara sirancewa, tayi murmushi wanda yayi dai-dai da kwacewar kwalla a idonta. Ta goge kwallar ta juyawa mudubin baya ta dan zauna gefen mudubin. Ta sake shafa kasusuwan wuyan nata; ba dole ta rame ba, shekara hudu kacal da aure amma ace har auren ya mutu. Tana son mijinta tana son yaranta amma ace yanzu tsakaninta da su sai dai daga nesa, ga shi Umma duka ta tsangwameta kamar ita ta saki kanta. Gaba daya ma rayuwar ta fice mata daga rai, babu abinda yafi kona mata rai irin yanda Umma ta hada kai da Yaya Hajiyayyaye suka juya mata baya. Sune matan da suke cikin rayuwarta wadanda ya kamata ace sune za su bata baki a yanayin da take ciki amma sune suka juya mata baya, lallai dan Adam bashi da tabbas.

Ta yunkura da kyar ta hadiye malolon da ya tokare mata makogoro, hawaye ya gangaro kan fuskarta. Nan da nan ta saka hannu ta goge hawayen tare da mikewa ta fada bandaki don bata son Hamida ta shigo ta ganta tana kuka; duk ranar da Hamidan ta ganta tana kuka to idan ta gama lallashinta tana bata hakuri sai kuma ta gayawa Umma; ita Hamida tana gayawa Umma ne don Umman ta rage damun Safiyya amma ita Umman nan zata saka Safiyyan a gaba da fada da bakaken maganganu tana fadin

‘To wa ya janyo miki, da zaki saka mutane a gaba da kuka? Ko ba Mukhtar din yana nan yana yawo a gari ba? Ki lallabo shi mana ku koma kina abu kamar ba mace ba.’

Ta tsani wadannan kalaman na Umma don haka ma tayi wa kanta alkawarin tunda ta kasa daina kuka to bazata sake yarda a ganta tana yi ba.

……..

Washegari da safe suna zaune a falo gaba dayansu har Umman da yake wasu lokutan Safiyyan tana zama a cikinsu in Allah ya taimaka sai Umma ta barta su taba hirar ba tare da ta gwaleta ba, Hamida ta shiga dakin Umma ta dauko ankon da aka kawo musu jiya. Sai a lokacin Safiyya ta ganshi, leshi ne mai kyau shudi da kwalliyar ruwan kwai, sosai ya burgeta har taji tana sha’awar zuwa bikin. Hamida ta zauna kusa da Umma tace

‘Umma ki kawo deposit na kaiwa Babangida ya dinka min.’

Kafin Umman ta amsa ta dubi Safiyya tace

‘Ya Safiyya kema na hada har da naki a dinki mana.’

Tayi Dan murmushi tace

‘Da kin kyauta kuwa.’

Umma ta dubi Hamidan tace

‘Ina naga kudin biya muku ku biyu? Kin san wajen su Babangida yanzu za kiji sun kirawo dubu goma. Ita dai Safiyyan ta ajiye nata har na sami kudi ke da yake kina cikin ‘yan matan amarya sai na biya miki.’

Hamida tace

‘To shike nan Umma, bari na fito daga wanka yanzu zan je na kai. Allah ya sa ki sami kudi kafin bikin a dinka na Yaya Safiyyan.’

Ba a jima ba suka jiyo sallama Yaya Hajiyayyaye ta zo tare da yaranta, wuni suka zo yi.

Nan aka gaggaisa aka cigaba da hira. Zuwa bayan azahar Hamida ta fito daga wanka ta shirya tana dauke da leshin zata kai dinki, ta dubi Ya Hajiyayyaye tace

‘Dinki zan kai Yaya Hajiyayyaye na ankon bikin su Saliha, da ma kina da kudi ki biyawa Ya Safiyya tunda ni Umma zata biya min.’

Nan take ta bata rai ta kawar da kai

‘Bani da kudi, ita Safiyyan bata da shi ne.’

Hamida ta langabe kai tace

‘Wallahi bata da kudi Yaya Hajiyayyaye, kema kin sani.’

‘To ai kuwa dai nima bani da shi sai dai ko daga baya.’

Ta yi musu sallama ta wuce ta tafi kai dinkin ta.

Haka akayi ta wasa da hankalin Safiyya a kan dinkin, tana son ta tambayi Yaya Habibu amma tana jin kunyarsa saboda shi ya sayi ankon kuma leshin ance dubu goma sha biyu ne. Don haka ta tattara ta hakura, zuwa bikin ma gaba daya ya fice mata daga rai. Sai da ya zama saura kwana biyu a fara bikin sannan Sabir ya gayawa Yaya Habibu bata da kudin dinki, don haka Yaya Habibu da kanshi ya zo gidan ya bata dubu biyar yace ta tafi yanzu ta kai dinkin kafin magriba don lokacin la’asar ta wuce.

Ta saka hijabi ta dauki kayan, akwai wani gida da suke kai dinki tun kafin tayi aure gidan Umman Zee can ta nufa don nan ne kawai take jin zata samu dinkin a kwana biyu.

A tsakar gida ta samesu don haka itama nan ta zauna, suka gaisa da Umman Zee cikin fara’a. Ta bata dinkin tayi mata bayani sannan ta bata kayanta wadanda zata dauki awonta a ciki, ta duba ta gaya mata ta kawo naira dubu uku da dari biyar, sukayi alkawari a kan idan zata zo karba zata zo da kudin. Sukayi sallama ta mike, Umman Zee ta biyota don tayi mata rakiya. Sai da suka zo soro har Safiyyan zata fita sannan cikin murya kasa-kasa Umman Zee tace

‘Umm Safiyya ni kuwa in tambayeki? Wai da gaskene aurenki ya mutu?’

Ta hadiye dan mamakin da yake fuskarta ta ta dubi Umman Zee suka hada ido, ta kara kakkafeta da ido kamar wadda aka kai kotu. Tayi murmushi ta sunkuyar da kai

‘Eh, aurena ya mutu harma na gama idda akwai wani abu ne?’

Ta fada itama tana tsattsare Umman Zee din da ido tana jiran taji mai zata ce. Ta sunkuyar da kai tana sosa keya

‘Uhm, a’a, babu wani abu. Hmm, dama kawai dai tambaya ce da yake kana ta ji a unguwa. Allah ya sa haka ne ya fi alkhairi, Allah ya daidaita tsakaninku.’

‘Amin na gode.’

Ta amsa cikin halin ko in kula, ta juya ta nufi kofa tana fadin

‘Sai na zo din.’

‘To Allah ya mai mu.’

Ta kamo hanya tana tunani kala-kala; yanzu labarin mutuwar aurenta har ya karade unguwar kenan, lallai zancen duniya baya buya. Ta riga ta san Umman Zee da gulma don haka abinda tayi bai dameta ba

Ta kama hanyar komawa gida, tafiya take tana ta sauri saboda magriba ta kusa; saura kadan ta Fadi da tazo gaban wasu maza da suke zama a bakin hanya kafin a karasa gidansu. Da ba dan kada ace ta sa musu ido ba da sai tace gulmarta sukeyi, domin yawancinsu ta san su a nan unguwar.

……..

Sai da aka idar da sallar isha’i sannan ta zubo tuwo, har zata wuce daki taga Hamida da Sabir a falo suna kallon wani fim din Hausa don haka ta nemi waje ta zauna a kan kujera don itama tayi kallon.

Ta cika bakinta da lomar tuwo suka jiyo sallama daga tsakar gida, da yake Umma tana kicin ita ta amsa sallamar. Yaron ya karaso tsakar gidan cikin daga murya yace

‘Wai ana sallama da Safiyya.’

Ta saka lomar da take hannunta a baki don ta zata Hamida ake kira sai kuma ta tuna itace Safiyya, lomar tuwon ta kwace ta wuce ba tare da ta tauna ba. Kafin ta gama gyara zama ta jiyo Umma tana bawa yaron amsa

‘Kace tana zuwa ka ji.’

Ta zaro ido suka hada ido da Sabir ya bushe da dariya yayinda ita kuma ta galla masa harara, Hamida ta kalleshi tayi gyaran murya. Ya mike yana fadin

‘Ya Safiyya bari in je screening kafin ki fito.’

Kafin ta amsa Umma ta shigo falon ta dubi Safiyya tace

‘Shine baki gaya min za kiyi baki ba?’

Ta kalli Umma ta sunkuyar da kai saboda yanda Umman ta tsattsareta da ido

‘Wallahi Umma nima ban san waye ba, ban san da zuwan kowa ba.’

‘To sai ki tashi kije ki gani, bamu sani ba ko za a dace.’

Ta so tace bazata je ba saboda bata san waye ba kuma bata jin ta shirya fadawa soyayyar wani namiji a halin yanzu, amma yanda Umma ta tsattsareta da ido ta san idan tace bazata je ba ta janyowa kanta fada. Don haka jiki a sanyaye ba tare da ta koshi da tuwon ba ta tashi ta kai kwanon kicin ta dawo ta wuce daki. Hijabi kawai ta ziro ta fice don ganin wanda yake nemanta.

Tana fitowa daga gate ta cinkaro da motarsu daf da bakin gate din, tana tsayawa suka fito daga cikin motar. Suka karaso inda ta ja ta tsaya tana kallonsu; bata gane fuskokinsu ba don bata jin ta taba ganinsu, amma tabbas motar itace wadda ta wuce dazu a daf da majalisar nan da take kusa da gidansu.

Bayan ta amsa sallamarsu tayi musu iso cikin farfajiyar gidan, da yake kawai irin kujerun robar nan a wajen sai kawai ta gyara kujerun ta ajiye su daf da kofar shiga tsakar gidan suka zauna gaba dayansu. Bayan sun gaisa suka yi shiru na dan lokaci, daya daga cikinsu wanda ta kula kamar shine dan rakiyar yace

‘Malama Safiyya na san baki san mu ba, ni sunan Bashir wannan kuma abokina ne Sulaiman. Muna zaune dazu muka ga wucewarki shine abokina ya nuna bukatar ya zo ko zai dace shine na rakoshi.’

Tayi murmushi kawai ta sunkuyar da kai; har yanzu jin kanta take kamar matar aure ce ita, ji take kamar wannan hirar da takeyi da su bai dace ba. Sulaiman ya yi gyaran murya yace

‘Baki ce komai ba malama Safiyya.’

Murmushin kawai ta sakeyi don bata san me zata ce masa ba. A haka dai suka dan taba hira wadda yawanci sune suke mata tambayoyi tana basu amsa. Jimawa kadan Sulaiman din yace

‘Bari mu tafi haka kada mu cika ki da suruta, kin barni sai faman zuba nake.’

Bashir din ya mike yayi mata sallama ya dubi Sulaiman din yace

‘Abokina ina jiranka a waje.’

Ya mike shima ya mika mata waya yace

‘Ki sa min lambarki ma gaisa kafin na dawo gobe.’

Ta karba ta saka masa lambar tana fadin

‘Ba gobe za ka dawo ba sai wani satin, rana i ta yau kenan.’

Ya kalleta yana jijjiga kai

‘Haba dai, kullum fa sai na zo unguwar nan hira kinga kuwa ai ya kamata in na zo ko gaisawa ne muyi.’

‘Ka bari dai wani satin.’

Yayi murmushi yace

‘To ai shike nan, yanda kika ce haka za ayi.’

Sukayi sallama ta shige gida shi kuma ya tafi.

Tana shiga gida ta tarar da Umma tana jiranta a falo

‘Umma na dawo.’

Fara’ar da Umman takeyi ne ta bawa Safiyya mamaki domin ta dade bata ga Umma nayi mata murmushi ba, kafin ta gama mamakin Umma tace

‘Yauwa, wane yazo?’

Ta sunkuyar da kai

‘Ban san shi ba Umma, ya ce sunanshi Sulaiman.’

‘To don Allah ki mai da hankali tunda dai shi Abban Nurain din ya ki dawowa, Allah ya tabbatar da alkhairi. A hankali za ki fahimci manufarsa sai ku daidaita.’

Ta yiwa Umma sai da safe ta wuce daki don ta kwanta. A halin yanzu bata shirya wata soyayya ba don bata ma san me take so ba, amma ko don saboda ta rabu da tsangwamar Umma duk wanda ya fito hakura zatayi ta aureshi kawai.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA SHIDA.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA SHA BAKWAI

Tun bikin yana saura kusan wata daya Mukhtar da Jamila suka fara daukan hotuna don shagalin bikinsu, ya riga ya kammala gininsa don haka shirye-shiryen biki kawai ake yi.

___

Kamar yanda ya zamar mata jiki tana zaune a daki ita kadai domin Hamida bata dawo daga makaranta ba kuma lokacin abincin dare bai yi ba balle ta shiga kicin. Wayarta ce a hannunta ta bude Whatsapp tana karatun littafin hausa; ta samu jiya Sabir ya siya mata kati ta sayi datar naira dari. Kiran Maman Ashraf ne ya katse mata karatun; sun kwana biyu basuyi waya ba, ita kadai ce suke magana a cikin makotanta na da tun bayan rabuwarta da Mukhtar, kuma sai ya kasance Ashraf da Nurain tare aka saka su a makaranta kuma ajinsu daya.

Bayan sun gama gaisawa Maman Ashraf tace

‘Ya jikin Nurain kuma?’

Cikin mamaki tace

‘Nurain kuma? Bashi da lafiya? Ai ban san ma bashi da lafiya ba.’

Murya a sanyaye Maman Ashraf din ta amsa

‘Aah baki sani ba? Ai wancan satin ma gaba daya Ashraf yace bai je makaranta ba, gashi wannan satin ma yau Juma’ah har yau bai jeba. Kuma yace Abbanshine ya je ya cewa Anti bashi da lafiya.’

Mamakinta ya karu da taji har an kai sati guda yana kwance amma ba’a gaya mata ba, murya a sanyaye tace

‘Ikon Allah, kuma kinga babu wanda ya gaya min duk da dai suna wajen Hajiya kin san.’

‘Eh mana na zata kin sani shi yasa nake miki jaje.’

‘Yanzu dai da na sani zan je na gani.’

Suka cigaba da hirarsu, a nan ne Maman Ashraf take sanar da ita Mukhtar tashi zai yi saboda mutum daya ne suke hayar gidajen wajensa shi ya gaya musu nan da wata biyu za a saka sabon dan haya.

Suka gama waya suka yi sallama suka ajiye.

Tunda taji Nurain bashi da lafiya ta kasa samun nutsuwa, so take kawai taje ta ganshi. Sama da sati guda ko makaranta baya zuwa amma ko su gaya mata, ciwo idan na ajaline kenan sai dai ta tarar da gawa? Lallai mutan gidansu Mukhtar basu kyauta mata ba. Ta dauki wayarta da take kan cinyarta, ta shiga lalubo lambar Aminu ko Saifullahi domin ta kirawo taji jikin nasa. Har ta samo lambar Saifullahi sai kuma ta sake shawara; gara kawai ta bari zuwa gobe ta je ta duboshi. Sai dai kuma bata da kudin mota kuma ta san in dai tace Umma ta bata sai ta sha gori da mita, bata son ta tambayi Yaya Habibu saboda yana iya bakin kokarinsa sai dai ko nawa ya bata Umma sai ta karbe. Wasu zafafan kwalla suka zubo daga idanunta; Allah ya kawo mata mafita, miji ya saketa ya rabata da yaranta, kullum ta tuno yaran nan sai zuciyarta tayi ciwo amma bata da zabi. Wani lokacin ma ta kan gode Allah da bai korota da yaran ba su zo suga yanda aka mayar da ita mai aiki, gara suyi zamansu a can watakila sa fi walwala.

Sai da daddare sannan take sanar da Umma Nurain bashi da lafiya, suka zauna suna ta jaje itama Umma ta nuna bacin ranta a kan rashin gaya musu. Sai dai Safiyyan ta kasa gayawa Umman cewa tana son zuwa ta duboshi saboda yanda take tsoron bakaken maganganun da Umman take yawan gaya mata. Haka ta tafi ta kwanta cikin matsananciyar damuwa tana neman mafita a wajen Allah.

Washegari ya kama ranar Asabar, suna zaune wajen karfe sha daya na safe sai ga Yaya Habibu. Bayan an gaggaisa ya cewa Umma daurin aure yazo nan kusa shine ya karaso, suka zauna suka cigaba da hira a falon Umman. Jimawa kadan ya dubi Safiyya sannan ya dubi Umma yace

‘Umma wannan yarinyar sai ramewa take kamar ana tsomen shayi da ita, ko Mukhtar din ta sa a ranta haka?'

Umma ta tabe baki tace

‘Wane Mukhtar da ta daina zancensa, damuwa dai tata wadda ita kadai ta sani. Ko kuma don an ce mata Nurain bashi da lafiya ne ban sani ba?’

Ya dubi Umman da mamaki

‘Ah, Nurain bashi da lafiya? Tun yaushe kenan?’

‘Ina jin zai kai sati kusan biyu don an ce mata wancan satin gaba daya bai je makaranta ba ga wannan satin ma haka.’

Ya dubi Safiyyan yace

‘Subhallahi, shine baki gaya min ba? To an je an dubo shi?’

Umma tace

‘Wace dubiya, ai babu wanda ya gaya mana rashin lafiyar ma itama a gari ta tsinta.’

Ya sake duban Safiyyan

‘Ikon Allah, ai sai ku tashi muje yanzu na kaiku a dubo shi. Ai muma danmu ne ko sun kirawo mu ko basu kirawomu ba dole ne muje, je ki shiryo muje.’

Ya dubi Hamida da Sabir da suke zaune yace

‘Kuma ku shirya muje gaba daya ai ba dadewa zamuyi ba.’

Ya sake duban Umma yace

‘Yanzu zamu dawo Umma.’

‘To, kwa gaishe min da shi. Ka saya mishi gugguru a hanya kace masa in jini.’

‘To Umma.’

Suka yiwa Umma sallama suka kama hanya a motar Yaya Habibu.

Saida suka tsaya a hanya Yaya Habibu ya cika musu leda da ayaba da apple, kuma ya sayi gugguru na Naira dari biyar sannan suka wuce.

A bakin gate ya tsayar da motar ya dubi Safiyya yace

‘Ku shiga, minti goma sha biyar na baku ku fito mu tafi. Ku gaishe min da Nurain din da Nana.’

Suka amsa suka shige gidan.

Sosai aka karbesu a wajen Hajiya kamar wasu manyan baki, bayan sun gaisa Hajiya tace

‘Sai da suka gaya miki ko? Cewa nayi su kyaleki idan ya sami lafiya a kawo miki shi kada su daga miki hankali. Yana sama wajen Baba yana ta surutu shi da ‘yaruwar.’

Kafin ta bata amsa kuwa sun shigo da gudu shi da nana kowa da alawa a hannunsa wadda Baba ya basu, nan take suka fada jikinta suna ta murna. Ta dubi Nurain tace

‘Ya jikinka Nuraini?’

‘Na warke harma Baba yace Monday zan je makaranta.’

Nana tayi caraf tace

‘Kuma yayi kukan allura.’

Ya hararetа yace

‘Mama ai kin san allura da zafi ko? To ma na daina kula Baba Aliyu shi yake kaini ana yi min me zafi, don haka nayi fushi dashi.’

Tayi dariya tace

‘Hakuri zakayi ai tunda ka warke, za ka ga shima Baba Aliyun ba zai sake kai ka allura ba.’

Ya jijjiga kai yace

‘Hmm, baki san shi bane Mama.’

‘To ku tashi Baba Sabir ya kaiku waje ku gaisa da Daddy din su Sayyid sai mu tafi.’

Nan da nan kuwa suka mike suka nufi wajen Sabir wanda ya kama hannun su suka fice. Ta tura ledar da suka je da ita gaban Hajiya tace

‘Gashi Umma tace a kawo.’

‘To an gode, Allah ya bar zumunci. Don Allah ki gaishe min da Umman sosai.’

‘In sha Allah.’

Jimawa kadan suka mike ita da Hamida suka yiwa Hajiyan sallama, ta dubi Bahijja wadda itama take zaune a wajen tace

‘Anti Bahijjan taso muje ki dauko ‘yarki don na san yanzu haka tace sai ta bimu.’

Ta mike tana dariya ta bisu suka wuce, suna gaba ita da Hamida yayin da Safiyyan ke biye da su a baya. Sun kusa isa gate din Mukhtar ya turo kofa ya shigo gidan, a takaice Hamida ta gaisheshi suka fice ita da Bahijja.

Yana kai idonsa suka hada ido da Safiyya, suka kasa kawar da ido na dan lokaci. Tayi dan gajeran murmushi ta sunkuyar da kai tace

‘Ina wuni.’

‘Uhm, lafiya kalau ya mutanen gidan?’

‘Lafiya kalau. Ya jikin Nurain? Shi muka zo dubawa daman.’

‘Eh haka Yaya Habibu ya ce min, ya sami lafiya ai.’

‘Allah ya kara lafiya, bari na je suna jirana.’

Ta wuce shima ya wuce ciki, sai da ya waiwayo ya kara kallonta kafin ta fice daga gate din. Duk da hijabin da yake jikinta ya hango yanda ta rame sosai domin idanuwanta ma duk sun nuna. Gashi tayi wani baki da kuraje a fuskarta, ya jijjiga kai kawai. Shi dama ya san zawarci wahalace kawai, haka kawai ta saka masa ido sai da ta sa ya sake ta ai gashi nan ta janyowa kanta. Wa ma zai hadata da Jamila, lallai ya sake tabbatarwa a halin yanzu Jamilan ce ta dace dashi. Gashi bashi da ra’ayin zama da mace sama da daya da sai ya dawo da Safiyyan, yanda yake son Jamila ma baya jin zai iya yi mata kishiya don haka itama Allah ya bata wani mijin ta aura.

.....

Tunda suka zauna a mota Safiyya ta kasa cewa komai, ganin da ta yiwa Mukhtar ya taso mata da kewarsa da take ciki. Kafin su kai gida suka ga Yaya Habibu ya tsaya a Sahad store, gaba daya suka shiga yace Hamida da Sabir kowa ya dauki abu daya ita kuma Safiyya yace ta dauki abubuwan da take bukata.

Tabbas da ace kafin su hadu da Mukhtar ya kawota da sai ta fi jin dadi, amma duk da haka ta samu ta dauki pad guda uku, turare, man shafawa da ribbon da kanshi ya debar mata chocolates guda Huda da yoghurt, ya biya kudin sannan suka wuce gida.

Suna shiga gidan Hamida ta yi sauri ta dora abincin rana don ta san in ta bari Umma cewa zata yi Safiyya ta dora kuma ta kula da yanda Safiyyan ta shiga damuwa.

Ita kuwa Safiyya suna shiga ta wuce daki ki mayafi bata ajiye ba ta fada kan gado. Allah ya sa Mukhtar yana jin yanda take ji. Tayi sauri ta kawar da tunanin don bata son abinda zai saka ta cikin damuwa. Haka ta wuni babu sukuni, ita Umma tana tunanin ko don ta gano yaran ne take kewarsu don haka tayi banza da ita.

Tana idar da sallar isha'i ta kwanta don ko abincin dare bata iya ci ba. Bata fi minti goma da kwanciya ba wayarta ta fara kara, ta sakankance Mukhtar ne don haka da hanzari ta dauka. Tana dubawa taga Sulaiman ne; tayi tsaki ta mayar da wayar ta ajiye a gefen filonta. Ta mayar da idonta ta rufe ta cigaba da tunanin Mukhtar tana fatan bacci ya dauketa. Sai da Sulaiman ya kirawota wajen sau goma bata daga ba don daga karshe ma a silence ta saka wayar ta koma ta rufe idonta. Tana ji Sabir ya shigo dakin ya zo har daf da gadon yana kiranta a hankali amma tayi shiru kamar nai bacci don haka ya fita.

Gaba daya ta manta ta cewa Sulaiman ya zo yau, don haka kiran da yake mata yana tsaye ne a kofar gidansu. Da ya gaji da kira ya turo Sabir kuma haka ya koma yace masa tayi bacci, ya wuce ya barshi a nan. Ranshi yayi matukar baci saboda da safe suka yi waya tace yazo yau shine zata yi masa wulakanci; yana da matarsa don haka ba zai dau wulakanci daga wajen wata bazawara ba musamman da yake jin rufa mata asiri zai yi ya aureta. Ya tuka motarsa yayi gaba da niyyar ba zai sake zuwa wajen Safiyya ba don shi baya juran wulakanci.

Har wajen goman dare da Hamida tayi bacci ita tana kwance tana juyi. A karo na babu adadi ta gyara filonta ta gyara kwanciyarta, ta ji danshi a fuskarta sai da ta kai hannu ta shafi idonta sannan ta tabbatar kuka takeyi. Tun safe take rike hawayen don ta riga tayi alkawarin ta daina kuka a kan Mukhtar amma ta kasa jurewa don haka ta saki hawayen gaba daya. Tana kewar mijinta, da yanzu tana jikinsa tana bacci. Tabbas da ta san yi masa magana zai janyo mata wannan damuwar da bata yi ba, da ta barshi ya cigaba da yawonsa tunda dai duk tsiya da ita zai kwana.

Ta Kai hannu ta dafe zuciyarta wadda take ta bugawa da sauri, Allah ya sa dai Mukhtar ya zo su mayar da aurensu, ko babu komai ta zauna itama da nata 'yayan kuma Umma ta daina jin haushinta. Ta lalubo wayarta ta kunna data dinta wadda ta riga ta kasheta kafin ta kwanta, so take ta duba ko zata ga hoton Mukhtar da yake kan dp dinshi na Whatsapp don tun bayan da tayi barin nan ta goge duka hotunansa daga wayarta. Sai kuma ta tuna ashe tayi blocking dinsa a WhatsApp don haka ta lalubo lambar ta bude blocking din da ta yi masa. Ta gyara kwanciyarta ta mayar da idonta ta rufe.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA BAKWAI.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

18

Zuwa yanzu su Fatima saura ‘yan watanni su gama bautar kasarsu, don haka ta sanar da shugaban makarantar da take aiki a kan zata cigaba da koyarwa kyauta zuwa lokacin da zata sami aiki ko kuma lokacin da Umma zata barta ta fara masters.

Dawowarta kenan daga aiki ta ajiye jakarta a kan mudubin dake dakin, har ta juya ta nufi bandaki ta jiyo karar wayarta daga cikin jakar don haka ta dawo ta dauka. Tana dubawa taga Janan ce don haka da murmushinta ta dauka, tana kara wayar a kunnenta tace

‘Kawata mutanen Minna.’

Itama tayi dariya daga daya bangaren tace

‘Aminiyata kenan, ya Zazzau? Ya Mama?’

‘Lafiya kalau, ya angonki? Ya bakunta kuma? Ko da yake yanzu ai kin saba kin zama Uwargida ko?’

Sukayi dariya gaba daya

‘Ke kika sani tunda dai kin kasa ziyarata.’

‘Kin san dai Mommy bata barina fita wallah, amma zan zo in sha Allah.’

‘Yanzu dai ba wannan ba, ranar Asabar din nan zanzo gida. Adnan yana da daurin aure a KD don haka zai kawo ni idan ya gama sai ya dauko ni mu koma kinji ko.’

Sai da tayi ihu da tsalle sannan tace

‘Allah kawata, kai gaskiya na ji dadi wallahi.’

‘Kamar gaske, ki dai ajiye min abun dadi kuma da sassafe zaki ganni sai na zo nan zan yi breakfast don na tara zafafan labarai duk da ma ina jin haushin ki shegiya.’

‘Allah sarki kawata to ni din kuma me nayi?’

‘Idan na zo kya ji.’

Suka karasa hirarrakinsu suka yi sallama suka ajiye waya.

Ta ji dadi da Janan tace mata zata zo, ita kadai ce kawar da ta rage suke zumunci duk da tayi aure. Ragowar kawayen nasu da sun yi aure suke daina kulata da yake ita kadai ce tayi saura a kawayen nasu batayi aure ba.

A falo ta sami Mommy bayan sallar isha’i tana zaune ta kunna TV tana kallon tashar Aljazeera kuma tana rike da waya, ta nemi guri a kan kujerar zaman mutum uku kusa da Mommy din ta zauna. Bayan sun dan taba hira tace

‘Mommy jibi Janan zata zo?’

‘To Allah ya kaimu, daga Minna din zata zo ina maigidan nata?’

‘Shine ma zai kawota ai, idan ya gama abinda zai yi a Kaduna sai ya dawo ya dauketa su tafi.’

‘Allah sarki, Allah ya nuna mana. Ai gara ta zo tayi miki fada kema ki dage ki fito da miji kina nan zaune muna hada kafada ga kawayenki nan duk suna gidan mazajensu.’

Tayi murmushi ta sunkuyar da kai ba tare da tace komai ba yayinda mommy ta mayar da hankalinta ga kallon TV.

Ta riga ta saba kawo yanzu duk wata dama da Mommy ta samu sai ta yi mata gorin aure, ta gode Allah Mommy tana da seminar ranar Asabar din don haka ta san ba za su hadu da Janan din ba. Domin yanzu duk wata kawa ko ‘yaruwa da take shiri da ita idan Mommy ta ganta sai tace ‘ki yiwa kanwarki fada itama ta fitar da miji’ don haka yanzu bata ma so Mommy ta hadu da kawayenta ko cousins dinta masu aure. Hirarsu ta daina tsawo da Mommy saboda bata son gorin da Mommy take yi mata, itama tana son auren, zaman hakan ya dameta. Gashi ta saba Mukhtar ya mayar da ita kamar matarsa don haka lokaci zuwa lokacin tana jin bukatar kasancewa da namiji; dagewa kawai takeyi tana bawa kanta hakuri saboda bata so ta sake maimaita kuskuren da tayi a baya.

Ta dago ta dubi Mommy tace

‘Bari naje nayi sallar isha’i Mommy.’

Ta wuce ta barta a nan.

Tana shiga dakin ta fada kan gadonta a rub da ciki, hawayen da ta kasa denawa ya kwace mata. A haka bacci ya kwasheta da yake dama ta riga tayi sallar isha’i dinta tun kafin taje wajen Mommy.

Can wajen goma na dare Mommy ta taso daga falo, zata wuce dakinta ta hango fitilar Fatima a kunne don haka ta tura kofa ta shiga dakin. Ta kalleta ta jijjiga kai tana mamakin yanda ta bari bacci ya kwasheta a haka. Ta karasa ta tabata

‘Fatima ki gyara kwanciyar ki kiyi azkar.’

Ta juya daga rub da cikin ta bata amsa cikin magagin bacci

‘Na yi.’

Ta janyo abun rufar ta ta lullube mata kafafu, ta kashe fitilar sannan ta ja mata kofa ta fice.

Tana son Fatima sosai, amma a dai-dai wannan lokacin bata da burin da ya wuce ace Fatima tayi aure. A halin ya zu ma gani take kamar tana kin kula samarin ne da gan-gan saboda wani abu da ta saka a ranta, amma duk da haka tana yi mata addu’a Allah ya bata miji na gari.

……..

Ranar asabar tun asuba Fatima ta shiga kichin, kafin karfe takwas ta gasa cake mai dadi sannan ta hada zobo ta cewa Baba Habi a yi abincin safe da kawarta; wanda ta san kunun gyada za a dama da kosai. Wajen karfe tara da Rabi Janan ta iso, zuwa lokacin Mommy ta jima da fita. Tana tsayawa a gate tayiwa Fatima waya don haka tun daga mota ta tarota, bayan sun gaisa da Adnan suka shigo gidan tayi mata masauki a dakinta.

Sai da ta jere mata abincin safe sannan suka gaisa yayinda Fatima ta bude kwanon kosai ta tura mata tare da zuba mata kunu a kofi sannan ta koma kusa da ita a kan kafet din da yake dakin ta zauna.

Bayan Janan ta kurbe kunun da ta cika baki da shi ta dubi Fatima ta ce

‘Kawata duk kin wani rame sai kace dake Mommy take tsomen shayi.’

Tayi ‘yar gajeriyar dariya tare da kawar da kai

‘Ba zaki gane ba kawata, sai a hankali.’

Bayan ta gama cin abincin Fatima ta kwashe kwanukan ta mayar kicin ta debo cake din da zobo ta ajiye a kan mudubin tace

‘Ga wannan kuma na anjima ne.’

Suka koma kan gado suka baje. Janan ta dubi Fatima tace

‘Kawata kin san kuwa tun yaushe nake nemanki? Na shako gulma kuma bazata yiwu ta waya ba shi yasa na tsaro shi ya kawo ni. Tukunnama wai ni ina mutuminki Mukhtar ne?’

Tayi tsaki ta kawar da kai

‘Hm! Ki bari kawai kawata. Kin san wulakancin da mutumin nan yayi min kuwa? Na zo na gama bazawa zai aiko a saka rana amma kawai sai ya dauke wuta ya daina kulani, ke daga karshe dai blocking dina yayi.’

Ta zaro ido tare da cije lebe

‘Kutumar Uba! Lallai wannan ya cika mara mutunci, yana so yace ya bata miki lokaci a banza kenan? Shi bai barki kin kula mutanen arziki kin sami miji ba shi kuma don ubanshi har ke zai yi blocking?’

Ta kawar da kai ta share kwalla, wannan hirara ta fama mata ciwo. Janan ta sa hannu ta sake share mata kwallar yayinda ita kuma ta cije lebe ta rike hannun Janan din tace

‘Janan ba zaki gane irin cutar da Mukhtar yayi min ba, kin san haka ya mayar da ni kamar matarsa duk lokacin da muka fita hotel muke zuwa ya gama bukatarsa sannan ya dawo da ni a kan alkawarin zai aureni.’

Tuni ta fizge hannunta ta dora a ka tare da bude baki, takaici ya sa itama ta saki kwalla

‘Fatima garin yaya? Ke me yayi miki zafi? Ya za ayi ki amince da shi har haka? Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun.’

Zuwa yanzu gaba dayansu kowa hawaye takeyi. Mamakine ya cika Fatima, kenan su su Janan da sauran kawayensu da take gani suna rungume-rungume da samari su basa bada kansu kenan; iya rungumar suke tsayawa? Ta bude baki cikin rawar murya

‘To ya yi min alkawarin aure kuma naga wadda ba ayiwa alkawarin aure ba ma haka za ki ga saurayin ya tsotseta a mota kuma ki ji sun fita shan ice cream da daddare.’

Ta sauke hannun daga ka ta kama hannun Fatima

‘To ai kawata iya nan ake tsayawa baka bada kai tunda ba karuwanci muka zo yi ba, kai da kake so ko waye ya aureka ka je a cikakkiyar budurwa? Ai dole ma ya guje ki kawata to me zai yiwa doki idan ya aurenki?’

Ta fada jikin Janan ta saki kuka gaba daya Janan tana tayata, sai da sukayi mai isarsu sannan suka bari. Janan tace

‘Bana son saki kuka kawata amma kin san gulmar me na shako nake nemanki?’

Ta jijjiga kai alamar a’a, don haka Janan ta cigaba

‘Ya gaya miki dalilin da yasa bazai aureki ba.’

‘Hmm! Kafin dai ya daina kula ni cewa yake wai Hajiya ce bata yarda a yiwa Safiyya kishiya ba saboda ‘yar kanwarta ce amma zai tsara Hajiyan. Har wayar mu ta karshe da yana borin kunya haka ya gaya min. Sai daga baya na gane duk ni yake rainawa hankali Bai taba niyyar aure na ba.’

‘Tabbas! Bai taba niyyar aurenki ba.’

Ta zaro wayarta daga jaka ta budo wani hoto ta mikawa Fatima, screenshot akayi na hoton don haka da rubutu a kai “New love story”. Tana ganin hoton ta saka hannunta daya ta dafe kirji saboda yanda takeji kamar zuciyarta zata faso kirjinta ta fito; Mukhtar ne da wata farar yarinya kyakkyawa, ya rungumota suna kallon fuskar juna suna murmushi. Daga ganin hotunan ka san pre wedding ne. Ta tuno lokacin birthday dinta da suka je Minjibir park, kwalla ta kara cicciko mata ido. Ta turawa Janan wayarta tana fadin

‘Aure zai yi ko Janan?’

Ta kawar da kai

‘Um, harda ma katin bikin ya saka a status ban san yanda akayi ban sauke katin ba.’

Ta sake dafe kirji tace

‘Allah ya isa na, duk sanda na tuna mutumin nan sai na yi masa Allah ya isa. Shi ya fara sanina a mace kuna shi kadai na sani duk a kan yana cewa zai aure ni, hotunana da yake da su wanda nake tsirara sun isheni takaici. Ya cuceni kawai, gashi har yanzu ba wani labari ban san ma da wanne idon zan kalli mijin da zan aura ba; idan ma ina da rabon auren kenan.’

Janan ta share mata hawaye ta rungumeta, suka dauki lokaci a haka, kamar wadda aka tsikara Janan din tace

‘Ke daina kuka kawata, wallahi bai isa ya ci bulus ba ko da wa yake yawo a garin nan sai munyi maganinsa daga shi har wannan kazar da zai aura.’

Ta kalleta da mamaki, Janan din ta dafa kafadarta

‘Ki zo na kaiki inda za a saka miki dan iska a kwalba, wallahi sai yanda kika yi da shi. Ko uwarshi ba zata fiki iko da shi ba; ki ja shi a kasa in kin ga dama ki aureshi ki sa ya saki waccan idan kuma kin sami wanda ya fishi ki fasa kwalbar kiyi aurenki ai dai kema kin rama.’

Ta kalleta da mamaki

‘Kai kawata!’

Ta hararеta

‘To ki zauna a nan kiyita kuka, ya fafe ki yaje ya auri wata wai shi mai wayo ke kuma ya ci bulus kenan.’

Tayi tunani na dan lokaci ta yi murmushi ta dubi Janan din tace

‘To ya za ayi kawata, don sai yanzu ma da naga aure zai yi na gane ni ya rainawa wayo.’

Ta Mika mata hannu suka tafa

‘Yauwa ‘yar gari, sai ya dawo hannunki kema ki ja banza a kasa.’

Tayi murmushi kawai don ko bazata aureshi zata so ta tarwatsa masa gida kamar yanda ya tarwatsa mata rayuwa. Janan tace

‘Adnan zai je Umra da azumi kuma sai bayan sallah zai dawo don haka da an fara azumi zan tafi gida, bayan Sallah zan koma Minna sai ki san yanda za kiyi ki tsara Mommy, a Minna malamin yake sai kizo muje kawata. Aikinsa kamar yankan wuka ne, ke dai ki tanadi kudi kamar wata dubu dari haka.’

‘Kada ki damu kawata, zan sami kudi ko da a wajen Yaya Ibrahim ma kuma ga ‘yan canjin alwee dina; don ma Umma tana karbewa.’

Nan suka karasa hirarrakinsu har sai wajen sha biyu na rana sannan Adnan ya zo ya dauki Janan, suka yi sallama a kan sai bayan Sallah fatiman zata sameta a Minna suje wajen malam.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA TAKWAS

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA GOMA SHA TARA

19

Bai taba murnar rabuwa da Safiyya ba sai da yaga Jamila a gidansa, tabbas ya godewa Allah da ya rabashi da Safiyya domin da bai rabu da ita ba da yanzu bai auri Jamila ba. Tana da matukar natsuwa bayan kyau da haduwa, gashi kuma tana da ilimin addini. Itama Safiyyan ba baya bace amma a halin yanzu baya ganin kowa sai Jamila. ‘Yan uwanshi duk sun ziyarci gidan amarya yayinda itama amarya taje gidansu ta gaida Hajiya da sauran mutanen gidan.

Tun kafin ya aureta ya riga yayi mata maganar zata rike masa Nana da Nurain kuma ta amince. Duk da a gidansu daga ita sai auta amma bata da matsala da yara, musamman da yake kanana ne kuma yayarta ta nuna mata yadda ta tarbiyyantar dasu haka zasu taso; don haka da shirinsu ta shigo gidan. Sai dai ya sanar da ita sai bayan karamar sallah zai dauko su, saboda yana so ya gama amarcinsa kafin su dawo.

A can gidan ma tun kafin ya fara maganar aure Hajiya take gaya masa ya dawo da matarsa ko kuma yayi aure don ya kwashi yaransa.

Ranar da aka fara azumi bayan an sha ruwa ya dauketa suka je yiwa hajiya barka da shan ruwa. Nan falon Hajiyan ya barta da Bahijja, ta ja su Nana da hira don tana so su dan sake da ita kafin su dawo hannunta.

A falo ya sami Baba suna hira da Anti, amaryar Hajiya, bayan ya gaishesu Anti ta tashi ta basu wajen. Sun dan taba hira a nan Saifullahi da Aminu suka shigo suka samesu duka suka yita hira da Baban, jimawa kadan ya dubi Baba yace

‘Bari naje mu tafi Baba.’

Ya kalleshi

‘Yaushe zaka dauki ‘yayanka?’

‘Bayan sallah in sha Allah Baba.’

‘Ina fatan ka gaya mata zata zauna da su, ko wajen uwarsu zaka mayar da su? Don dai kaga Hajiya yanzu ma lallabawa take kada kafarta ta dameta da ciwo.’

‘Eh na gaya mata Baba, zata zauna min da su.’

‘To Allah ya bada zaman lafiya.’

Ya amsa sannan yayi sallama da su Saifullahi ya fito suka koma gida.

–

Tunda Safiyya take bata taba yin azumin da bata ji dadinsa ba kamar wannan; tana jin dadin ibadarta matuka gashi kullum sai ta raba dare tana sallah don haka wannan yana sa mata nutsuwa ta zuciya. Amma kuma tana shan aiki don kullum a tsaye take wuni, Umma da kanta take kare Hamida idan ta dawo daga makaranta sai tace ta gaji. Zuwa yanzu abun ya daina damunta kuma ya daina bata mamaki don haka hidimarta kawai take yi.

Ta san bata ajiye ko sisi ba don haka bata sa rai da kayan sallah ba, tana kallo dai Umma ta siyawa Hamida leshi da mayafi. Bayan da aka kawo kayan da yake duk suna zaune a falo aka kawo sai Umman ta dubi Safiyya tace

‘To ke kuma idan na kara samun kudi na ga abinda zan iya yi miki na sallar ki sabunta.’

Murmushin kawai tayi tace

‘Allah ya hore.’

Bayan kwana biyu kuma tana ji aka sayi takalmi da jaka na Hamida. Sai da akayi azumi goma sha biyar Yaya Hajiyayyaye ta zo gaisuwar azumi ta kawowa Umma atamfa da takalmi wanda daman duk shekara maigidanta ya saba bawa Umman atamfa. Hamida kuma ta tambayeta kudin dinki tace ta kai zata biya. Ita kuwa Safiyya ko maganarta ba’a yi saboda kada tace ma ayi mata, ita kuwa ta ja bakinta tayi shiru tana harkar gabanta.

Sallah saura kwana goma sha biyu Yaya Habibu yazo da nashi kayan; ya kawowa Umma leshi, Hamida atamfa yayinda ya bawa Safiyya atamfa itama. Da zai tafi kuma yace Sabir ya raka Safiyya da Hamida shagon abokinsa a kantin kwari su zabi takalmi da mayafi. Har ya tashi zai tafi ya kawo naira dubu biyar ya bawa Safiyya yace ta kai dinki, don haka yana fita ta wuce ta kai dinkin ta.

…….

Ta gaji da wannan zaman na jira wanda bata san me take jira ba; kullum kara shiga damuwa takeyi. Sai ta fara kokarin tursasawa kanta walwala sai wani abu ya faru wanda zai sake mayar da ita damuwa; ko kuma Umma ko ‘yanuwanta su gaya mata wata magana da zata mayar da ita damuwa. Wani lokacin har ji take kamar an saka zuciyarta a keji kirjinta yayi kunci, wani lokacin kuma sai ta ji da kyar take numfashi.

Kullum sai tayi sallar dare tayi addu’a amma kuma kullum damuwarta karuwa takeyi; duk da haka kullum tana addu’a Allah ya yaye mata kuma tana sa rai Allah ya amsa.

Ta yanke shawarar bayan sallah islamiyya zata koma, sai dai kuma tana tsoron gayawa Umma kada ta hana; ba wai tana da tabbas din hakan bane amma ta san kadan da aikin Umma tace babu inda zata. Don haka ta kirawo Yaya Habibu ta sanar dashi a kan yayiwa Umman magana; yaji dadi sosai don haka yace ta bari bayan sallah zai siyo form ya zo mata da shi sai ya kaita da kansa.

Ranar Sallah da wuri suka gama aikinsu da yake kowa ya sa hannu, nan da nan kowa ya shirya cikin kwalliyar Sallah. Can bayan azahar tana zaune a daki ta jiyo shigowar Nana da Nurain, Aliyu ne ya kawo su ya gaida Umma a tsakar gida ya sanar da ita bayan magriba zai zo ya daukesu.

‘Umma ina Mamanmu?’

Nurain ya tambaya bayan ya gaida Umma da Hamida dake tsakar gida, Umma tayi dariya tace

‘Ai nice mamanku.’

Shima dariyar yayi ya nufi daki da gudu yana fadin

'Ai na san tana cikin nan.'

A take Nana ta bi bayansa, suna shiga dakin suka fada jikinta da gudu sunata dariya. Ta rungumesu gaba daya itama tana dariyar domin tayi kewarsu sosai. Ta dago su ta shafa kan Nana wanda ya sha ribbons sai dai babu kitso tace

‘Nana kin bari kikayi a yi miki kitso ko?’

Ta noke kai, Nurain yace

‘Eh Mama, kuka takeyi Baba yace a kyaleta.’

Ta shafa kanta

‘Ki dinga tsayawa ana yi miki kitso kinji Nanan Mama, in ba haka ba ba zaki zama yar gayu ba.’

Kafin ta bada amsa Nurain yace

‘Mama Abbanmu yayi wata amarya, sunanta Anti Jamila amma yace Mommy zamu dinga ce mata. Mun je ma gidan wani babban sabon gida ne, Abba yace ni da Nana bayan sallah zamu koma muma mu koma wajenta.’

Nana da take kan cinyarta ta tallafo habarta tana kallon idonta tace

‘Mama kema ai zaki dawo sabon gidan ko?’

Kafin ta amsa Nurain ya dubi fuskar Nanan yace

‘Ke Abbanmu ya saketa ba zata dawo ba, sun rabu.’

Ya dubi Safiyyan yace

‘Ko Mama.’

Ta kalleshi tayi murmushi tana kokarin neman amsar da zata bashi, taga dai babu abinda yayi saura da zata boye tunda su can sun gaya masa don haka ta daga kai alamar eh tace

‘Umm.’

Nana ta kwabe fuska tana duban Safiyyan tace

‘To nima gidan Umma zan dawo na dinga bacci a wajenki kinji Mama.’

Ta shafa kanta tana murmushi, ta rasa amsar da zata bata don haka ta canza hirar ta hanyar tambayar Nana ko Abba ya sakata a makaranta.

Haka suka wuni sunata wasa da surutu a gidan, kafin magriba ta lallaba Nana ta yi mata kitso mai kyau; da yake ta iya kitso sosai kukan tane yasa bata yi mata sai ta bayar a kaita inda bazata ji kukan ba.

Sai bayan magriba Aliyu yazo daukarsu. Yana shiga gidan Nana ta sa kuka ita bazata bishi ba, da kyar da lallashi ya dauketa suka wuce.

Itama Safiyyan haka ta kwana ranta babu dadi, ta rasa binda yake damunta; kishin labarin amaryar da suka zo mata dashi ko kuma kewarsu. Ta ji tausayinsu sosai kuma taji tausayin kanta, a haka bacci ya kwasheta.

_

Tunda Aliyu ya mayar da su Nurain gidan Hajiya ake ta fama da Nana, ta dai hakura ta daina kuka amma ta ki kula kowa; da anyi magana sai tace ita wajen Mamanta zata. Haka dai aka rabu da ita aka cigaba da hada musu kayansu domin babansu ya ce a shiryasu, washegari za su zo da Jamila kuma idan sun zo da su zasu tafi shikenan sun koma gidansu.

Sai bayan la’asar suka iso gidan, bayan an gaggaisa ya bar Jamila wajen Bahijja ya fice. Sun dan taba hira kadan amma da yake ita din ba mai yawan surutu bace haka suka zauna kowa hankalinsa yana kan wayarsa. Sai bayan isha’i ya dawo, nan da nan aka saka kayansu a mota Nurain yana ta murna zai koma sabon gida yayinda Nana take ta fushi; ta ki kula kowa har Abban nata sai dai kawai duk abinda aka ce tayi zata yi. Haka suka kama hanya har gida.

Sai wajen karfe tara suka shiga gidan, gaba dayansu sun riga sun ci abinci don haka nan da nan aka hau shirin bacci.

Ya riga ya sanar da Jamila a dakinta zasu kwana duk da akwai dakinsu a sama amma ya sanar da ita sunyi kankanta a barsu su kwana su kadai; don haka ma babu komai a dakin nasu sai tarkacenta da ta ajiye. A kasa ma suna da daki wanda shi na wasa ne da karatu.

Tsaf ta shiryasu ta saka su sukayi fitsari sannan ta raka su daki ta kwantar dasu a kan gadonta. Ta dubesu tace

‘Kada wanda yayi min fitsarin kwance kun ji ko? Idan za kuyi fitsari ku tasheni.’

Ta dubi Nurain tana nuna masa bandakinta tace

‘Kai Nurain ga bandaki nan ka ji?’

Ya daga kai alamar toh. Ta kwantar da Nana wadda take zaune tana kallonta kawai, ta gyara musu rufa ta tofa musu addua sanna tace

‘To kowa ya rufe ido yayi bacci.’

Take suka rufe ido kamar yanda tace don haka ta tashi ta fice ta bar musu fitila a kunne kuma kofar a bude, ta fito falo ta sami Mukhtar yana kwance rigingine a kan kujera yana kallon Nigerian film. Kai tsaye kan ruwan cikinsa ta kwanta tana fadin

‘Honey na…'

Katseta yayi yana kokarin tureta yana fadin

‘Tashi mana, da yara fa a gidan ba lallai sunyi bacci ba wani zai iya fitowa fa.’

Ta kalleshi da alamar tambaya a idonta, sai kuma ta basar. Ta mike ta koma kan wata kujerar ta zauna tana fadin

‘Ai inaga sunyi bacci ma.’

Suka cigaba da kallon suna hira jefi-jefi; tana fatan Allah yasa kada yaran nan su zamar mata matsala don ta ga sauyi daga wajen Mukhtar yanzu-yanzun nan. A haka har lokacin bacci yayi suka tashi suka shige daki. A hankali ta leka dakin ta hangosu ta cikin gidan sauro suna ta baccinsu, sai kawai ta janyo kofa ta rufe musu ta wuce dakin Mukhtar suka kwanta.

Sun riga sun saba basa kula juna lokacin kwanciyar bacci sai sunyi bacci ya ishesu idan akayi sallar asuba sannan yake nutsuwa da ita, don haka yau din ma baccinsu suka yi. Ana yin assalatu Mukhtar ya shirya bayan ya tasheta ya wuce masallaci don yayi sallah. Kamar yanda ta saba tana idar da sallah ta kara gayar jikinta ta fesa turarukanta sannan ta koma gado ta kwanta, yana dawowa shima ya bi bayanta ya kwanta. Kafin ya gama gyara kwanciyarsa ta juyo ta matso jikinsa tana masa sannu da zuwa. Bayan ya amsa yace

‘Kin dubo yaran naki kuwa.’

Ta gyara kanta da ta kwantar a kan kirjinsa sannan tace

‘Umm, duka bacci sukeyi.’

Ta cigaba da lalubarsa duk da ya rage mata kuzari da ya kawo maganar yara, haka kawai da asubar fari zai wani ce ta duba su kamar wata shanya. Dole shima ya fara biye mata, kafin suyi nisa suka jiyo ihun Nana tana kuka tana kiran Bahijja

‘Anti Ba.’

Ya daga kanta daga jikinsa yace

‘Kin ji Nana can ta tashi.’

Ta dauke wuta na dan lokaci; wannan kuma wace irin musiba ce ace sai yanzune zasu farka su basu san asuba ba kenan. Ta riga ta gama laushi amma haka ta janye jikinta ta dauki zaninta a saman wardrobe ta daura a kan rigar bacci ta fito don zuwa wajensu.

A tsakiyar gadon ta sami Nana tana zaune tana faman rusa kuka, kafin ta karasa kan gadon tace

‘Nana, me ya sameki?’

Ta juyo ta kalleta tana share hawaye tana fadin

‘Na tashi, Anti Ba nake nema ta zuba min shayi.’

Mamaki ya kamata, ta danna wayarta dake hannunta don ganin lokaci taga karfe shida ma bata karasa ba. Ta fara kokarin cire net din tana fadin

‘Nana shayi zaki sha yanzu, ai safiya batayi ba.’

Ta rataye net din a saman gadon ta karaso ta zauna a gefen, kafin ta karasa mika hannunta ta kamo Nanan taji danshi a inda ta ajiye hannunta. Ta dago kai ta dubi Nana tana kokarin hadiye takaicin da ya taso mata

‘Nana fitsari kikayi?’

Tayi narai-narai da ido tana shirin fashewa da kuka, bata son jin kukan don haka ta daga mata hannu tana fadin

‘Ya isa!’

A nan Nurain ya farka, yana mika yana kallon dakin

‘Nurain me ka tashi yi kaima safiya batayi ba fa.’

Ya kalli wajen da yake zaune a kan bargonta da ta ture gefe suka kwanta, ya kalleta ya koma ya sunkuyar da kai kamar mara gaskiya. Cikin yanayi na jin kunya yace

‘Na manta nayi fitsari.’

Ta kalleshi cike da takaici ta kalli wajen da yake zaune, ga fitsarin nan ma yana naso don wannan ma bai wuce ace yanzu yayi shi ba. Takaici ya sake kuleta, wannan wacce irin musiba ce, duka su biyun sun yi mata fitsari a kwance. Ta manta gaba daya Hajiya tace mata ana saka su fitsari bayan sun kwanta; Nurain sau daya ita kuma Nana sau biyu. Ta rufe fuskarta da tafukan hannunta cike da takaici; kenan ba zata dinga bacci ba saboda wadannan yaran; lallai tana da aiki. Ta sa su suka sauka gaba daya, Allah ya so lokacin zafi ne don haka ta wanke musu jiki da ruwan fanfo ta canza musu kaya tana tunanin yanda zata yi da katifar bayan ta yayyafa mata ruwa. Ta kallesu suna zaune a kafet din dake tsakiyar dakin tace

‘Ku kwanta a nan sai an jima zamu tashi.’

Nan da nan Nurain ya kwanta, ita kuwa Nana ta dubeta da murya kasa-kasa tace

‘Shayi zan sha.’

Ta zabga mata harara wadda ta sa Nanan ta sunkuyar da kanta, ta fara kuka a hankali yayi da ita kuma Jamilan take tsaye tana tunanin abun yi. Wajen mijinta take so ta koma su karasa abinda suka fara amma yarinyar nan tana maganar shayi. Ihun Nanan ne ya katse mata tunani, inda ta sa kuka iya karfinta. Ta dubeta cike da takaici

‘Idan baki rufe min baki kin kwanta ba ko na tashi ba zan baki shayin ba.’

Nanan ta fara kokarin hadiye kukanta tana shirin kwanciya Abbanta ya turo kofa ya shigo, ya fara dubansu daya bayan daya

‘Ya hakane, me ke faruwa? Ya na gansu a kasa gadon fa?’

Ta kawar da kai sannan ta bashi amsa

‘Fitsarin kwance sukayi duka su biyun.’

‘Subhanallah, baki farka kin sakasu ba ko? Ai sai ana sakasu cikin dare.’

Tayi murmushin yake tace

‘Ai baka tashe ni ka tuna min ba.’

Ya kalleta shekeke

‘Au nine ma zan dinga tashinki kenan? Ki dai saka alarm a wayarki kawai.’

Ya karasa ya tsuguna gaban Nana yana mata magana

‘Nana kukan me kikeyi.’

Cikin shessheka ta bashi amsa

‘Ssshayi zan sha kuma ka kaini wajen Hajiya da Anti Ba.’

Ya dauketa ya dora a kan cinyarsa ya fara share mata hawaye

‘Kiyi hakuri in an kwana biyu zamu je wajen Hajiya. Nan ma ai akwai shayi, bari Mommy ta hada miki mai dadi ki sha.’

Ya kalli Jamila dake tsaye tana kallonsu yace

‘Ki hada musu shayi.’

A ciki ta amsa ta fice daga dakin jikinta babu kwari; lallai za ayi rigima. Daga farawa yaran har sun isheta, bata san raino ba domin kaninta daya kuma shekara daya ta bashi. Sauran kannen nata da yake ba dakinsu daya ba duk bata san yanda ake rainonsu ba. Wai harda wani hada musu shayi, ita tana sauri ta koma ta biya masa bukata ashe shi yaransa ne a gabansa. Gaskiya da sake!

Ta fito daga kicin da kofunan roba guda biyu a hannuwanta kowanne da shayi rabin kofin, ya riga ya fito dasu falo don haka nan ta samesu ta ajiye musu shayin. Sai da ta ajiye musu shayin tana shirin tashi Nurain ya kalli babansa yace

‘Abba babu burodi?’

Ya dubeta

‘Ki duko masa burodi.’

Haka ya zauna da yaran har gari ya karasa wayewa ko dakin bai koma ba, daga baya ta fito ta koma kichin ta hada musu abincin safe. Bayan ya gama shiryawa zai fita ne ya sameta a dakinta tana zaune a kan kujerar gaban mudubi, ya karasa ya tsuguna a gabanta

‘Jam-jam.’

Ta kalleshi tana wani gajeran murmushi.

‘Ni zan fita. Don Allah ki dinga hakuri da yaran nan kin san yanzu suke kokarin adjusting amma in sha Allah idan suka saba shikenan. Nana tana da rigima amma itama da ta saba shikenan, kiyi hakuri da su.’

Tayi murmushi tana kallonsa tace

‘To kuma me akayi kake wani bani hakuri?’

Yayi dariya

‘Babu komai, kawai dai na san zama da yara sai hakuri.’

Itama dariyar tayi tace

‘To na hakura.’

Ya mike itama ta mike, ta dan matso jikinsa kadan suka hada ido. Ya lakace mata hanci yace

‘Akwai bashi na a kanki, yau da magaribar fari zaki biya bashi.’

Tayi dariya tace

‘Kai dai zaka biya bashi.’

Sai da ya kamo mata katifarta ta fito da ita ta jingine a tsakar gida sannan yayi musu sallama ya fice.

.....

Duk yanda ta dauki zama da yaran nan ya wuce haka, hidimarsu tana isarta. Gashi wani lokacin suyi ta fada suna kawo kara, haka dai take hakuri tana kawar da kai, amma kullum kafin dare sun gajiyar da ita. Shi kansa Mukhtar din sai da yaga alamar hakan a mu’amalarta.

KARSHEN BABI NA GOMA SHA TARA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA ASHIRI

20

Hamida ce a falo tana kallo yayinda Safiyya take kwance a daki, Umma ta shiga makota gaisuwar sallah da yake ranar uku ga sallah ne. Da sallama Sabir ya shigo falon bayan Hamida ta amsa ya zauna a kusa da ita, jimawa kadan yace

‘Ina Yaya Safiyya?’

’Tana daki mana.’

Take ya mike ya shige dakin da sallama, tana kwance a kan gado idonta a rufe amma shi ya san ba bacci takeyi ba. Ya kula da yanda damuwarta take kara yawa tun cikin azumi, duk da ba tare suke kwana ba amm da safe yawanci da ya kalli idonta ya san tayi kuka da daddare. Idan yace ta daina damuwa sai tace ya daina sa ido ita bata da wata damuwa, ya gayawa Hamida amma ya ga ita abun bai dameta sosai ba. Itama Umma da ya gaya mata cewa tayi

“To wa yace maka zawarci yana da dadi, ai dole ta damu, aurenta ne fa ya mutu.”

Ya kula dai babu wanda yake son ya fahimceshi, amma dai yana tsoron ta shiga depression. Shi ma bai san depression din ba sai kwanannan da yake suna SS 3 a makaranta aka shirya musu lakca aka gayyato masana sukayi musu bayani a kan shaye-shaye; a cikin bayanan ne akayi musu bayanin ciwon damuwa da yanda ake gane idan mutum yana cikin damuwa da yanda za a taimaka masa. Shi yasa yake ganin kamar Yaya Safiyya tana cikin damuwa.

Har ya karasa gaban gadon bata bude ido ba kuma bata amsa sallamarsa ba, ya dan doki tafin kafarta yace

‘Ya Safiyya bacci kikeyi?’

Ta bude ido ta tashi daga kwance

‘Idona biyu Sabir, me ka kawo min?’

Ya zauna a gefen gadon inda ta janye kafafunta

‘Yau fa Yaya Habibu zaizo kunyi zancen islamiyyar kuwa?’

Tace

‘Eh, na san in sha Allah yau zai wa Umma magana duk da suna hutun sallah ma.’

Ya zaro katin MTN na naira dari ya dauki wayarta ya fara sakawa, tace

‘Kai Sabir nace ka daina sayamin kati da kudin makarantarka fa.’

Ya gyara zama ya ci gaba da saka katin

‘Haba Ya Safiyya kamar ni babban yaro zaki ce na dogara da kudin makaranta, haba dai ai akwai resources.’

Tayi dariya tana hararsa tace

‘Sannu minister of petroleum resources.’

Ya mika mata wayar yana dariya

‘Kin san wani abu ma Yaya Safiyya, rannan ba muna maganar ki fara sana’a ba kika ce min baki iya komai na siyarwa ba kuma ba kya jin zaki iya koyon wani abu a yanzu.’

Ta daga masa kai alamar eh, ya cigaba

‘To ai kin iya kitso, wanda kika yiwa Nana jiya bakiga yanda yayi kyau ba. Gashi dama su Faridan Yaya Hajiyayyaye ma nan take zube su kiyi musu. Wallahi a sa haraji, kowa yazo ya taho da kudin kitso.’

Tayi dariya

‘Lallai Sabir, ka san kuwa nawa ake biya kudin kitson, hamsin ce fa da dari. Yaushe zan iya wahalar banza?’

Ya gyara zama ya koro bayani

‘Ina laifi Ya Safiyya? A kan yanda yanzu zaki kwana nawa baki da ko sisi gashi wanda Yaya zai baki duk ki bawa Umma ai gara ki fara kitson, a kalla sai ki dinga boyewa ko nima zan dinga ajiye miki.’

Tayi dariya ta kawar da kai

‘Rabani da aikin wahala Sabir.’

Ya marairaice

‘Don Allah Yaya Safiyya ki gwada, da wannan zaman ma ai gara kitson ko ba komai ki sami abun da zai debe miki kewa.’

‘Hmm! To kai wa yace maka maigidan zata yarda.’

‘In dai ke kin yarda ki barni da ita zan tsara miki ita.’

Tayi dariya ta rasa me zata ce masa, bata son gwaleshi saboda yanda ya damu da damuwarta. Amma gani take kitso a matsayin sana’a babu abinda zata samu da shi, kuma ace yanzu shikenan ta zama mai kitso. Ta kalleshi suka hada ido yana jira tace ta amince, ta kawar da kai. Itama bata san ko zata jure ba ko da yake ma ta san unguwar akwai masu kitso don haka ko ma ta fara bazata samu masu zuwa da yawa ba don haka ta kalleshi ta daga kai

‘Toh shikenan duk wanda ya shigo gidan nan yace yana son kitso zan yi masa ya kawo kudi.’

Ya tafa hannu yace

‘Yesss! Kinga nine

sakatarenki, idan mukayi ciniki ya kai dubu uku za muje mu bude account a banki.’

Tayi dariya ta kalleshi da mamaki

‘Wai duk a kan kitson?'

Ya harareta

‘Zauna kina kallo.’

Sai bayan isha’i suna zaune a falo suna cin tuwon dare Sabir din ya dubi Umma yace

‘Umma Yaya Safiyya fa gobe zata fara yin kitso na kudi nine sakatarenta.’

Umma ta yi dariya sannan ta gatsine fuska

‘Kitso kuma? Lallai to ni dai sai da a dinga yi a rumfar kusa da gate saboda bana son gashi a tsakar gidana.’

Safiyya ta kalleshi suka hada ido, ya kalli Umma yace

‘Sami’ina wa ada’ana Hajiya Umma, yanda kika ce haka za ayi.’

Ta dubi Safiyya tace

‘Ina fatan kin san Saratun gidan Hajiya ma tana kitson tun tuni kuma gida daya ne tsakanin mu da su.’

‘Na sani Umma dama nifa ba ma ni na….’

Sabir yayi sauri ya katseta

‘Mun sani Umma kowa rabonshi zai ci.’

Ta tabe baki tana duban Safiyyan

‘Allah ya bada sa’a, ina dai fatan kin san Yayanku yace islamiyya zai sakaki don dazu ce min yayi nan da sati mai zuwa zaki fara zuwa.’

‘Na sani Umma, ya gaya min.’

‘To Allah ya bada sa’a.’

Suka karasa hirarrakinsu suka tafi suka kwanta. Ita dai Safiyyan ta san babu wanda zata cewa tana kitso amma kuma kamar yanda ta fadawa Sabir duk wanda ya shigo gidan da sunan kitso zata yi masa.

_

Tunda aka fara bikin sallah Fatima take ta tunanin karyar da zata yiwa Mommy ta barta taje Niger wajen Janan, gaba daya tunaninta ya kare. Ranar hudu ga Sallah aka yiwa su Mommy waya aka sanar dasu rasuwar kanwar mahaifiyarsu a Kafancan, don haka a take suka fara shiri ita da kanwarta wadda itama take aure a nan Zariyan. Mutuwar ta rudasu sosai suna ta kuka, zuwa dare sun gama shiri a kan gobe da sassafe zasu kama hanya. Haka Fatima ta shirya itama domin da ita za a tafi. Da yake sun tafi da wuri kuma direbansu yana da sauri da wuri suka isa, basu dade da isa ba Babbar yayar su Mommy wadda ake kira Inna Amina itama ta shigo da yaranta daga Abuja. Nan da nan suka hade da su Fatima ana ta hirar yaushe gamo, duk da Fatima ta girmi yaranta mata amma sun shaku sosai. Can bayan la’asar Inna ta hada kan yaranta zata tafi, suka hade baki suka kewaye Mommy akan zasu tafi da Yaya Fatima Abuja. Daga baya Inna ta kalli Fatima tace

‘Taso mu tafi Fati, ko bazaki bar Mommyn ita kadai ba.’

Sukayi dariya gaba daya, Mommy tace

‘Ni a su wa, Allah ya kiyaye hanya.’

Inna ta dubi Fatima tace

‘Ko baki dauko kaya ba ki taso muje tunda next week dole mu tafi Zariyan bikin su Hajja sai ki debo kaya.’

Cikin walwala Fatima ta bi su Inna Abuja domin ta san Inna sai tafi saukin tsarawa ta barta taje Minna, idan taci sa’a ma a bata direba duk da ba zata so hakan ba. Nan sukayi sallama da Mommy suka wuce Abuja.

.....

Sai da ta kwana daya tana hutawa a Abuja sannan sukayi waya da Janan suka tsayar da shawara a kan zasu je ranar Asabar don Adnan ranar Asabar din zai dawo amma da daddare. Tun dare ta sami Inna ta gaya mata akwai kawarta a Minna tayi bari tana so taje ta dubo ta gobe, ba tare da wani kai ruwa rana ba Inna ta amince. Tace

‘To babu damuwa gobe sai kuje da Malam Musa, dama akwai sakon da zan bashi ya kaiwa wata matar abokin Abbansu a Minnan. In ya ajiyeki sai ya kai sakon ya dawo ya daukeki ku dawo; ammafa ba dadewa zai yi ba don haka sai dai kawai ku gaisa ku dawo.’

Da fara’arta ta amsa

‘Babu komai Inna nima dama ba dadewa nake so nayi ba.’

Gari na wayewa Fatima ta shirya, Malam Musa ya kai yaran gidan tahfiz sai su Faisal su uku wadanda dukansu yan jami’a ne. Saida suka fito Faisal din yace zai je shima ya raka Malam Musa don haka gaba daya suka kama hanya. Suna isa Fatima tace Faisal ya fito su shiga su gaisa da kawarta don haka ita da Faisal din suka shiga, bayan sun gaisa yayi musu sallama Janan tace masa za su je nan baya gidan surukanta da Fatima idan sun dawo gidan a rufe suyi waya.

Faisal yana fita Janan ta dubi Fatima tace

‘Haba kawata, kin san kuwa yau Adnan zai dawo; ai saura kadan mu makara.

Ta karkata kai tana fadin

‘Hmm! Kin san Mommy, Allah ne ma ya sa akai wannan rasuwar na samu hanya na gudo Abuja da ban san yanda za ayi ba.’

‘Bari ki gani.’

Da yake a shirye Janan take sai kawai ta dauko mukullin mota da mayafinta suka kama hanya. Suna cikin mota Fatima ta dubeta tace

‘Kawata ince ko dai kusa ne, kada fa su dawo bama nan.’

Ta dafa cinyarta tace

‘Babu wani nisa fa, cikin gari yake shi ba boka bane ai, yanzu zamu isa. Shi yasa ai na cewa Faisal za mu fita don ma kada su kawo wani abu.’

‘Hmmm!’

Sai da suka tsaya a ATM Fatima ta cire duk kudin da yake account dinta wato naira dubu dari sannan suka wuce.

Basu dade suna tafiya ba Janan ta karkata kan motar ta shiga wata unguwa, sun dauki lokaci suna tafiya kafin tayi parking a kofar wani karamin gida. Tabbas a tsakiyar mutane yake don unguwace kamar kowacce, ga mutane nan da kwalliyar sallarsu ana ta harka. Sai da suka shige soro daya sannan suka isa tsakar gidan, wasu mata su biyu wadanda da alama sune matan gidan suka yi musu iso. Daga gani ma sun san Janan; daya cikin matan ta shigar dasu wani daki wanda kofarsa take daf da bakin kofar shiga tsakar gidan. Kana shiga zaka ga kamar falon ba a cikin wannan gidan yake ba saboda yanda aka kawata shi da kujerun masu kyau ga

carpet, ga tv plasma fankokin guda biyu dake saman falon sunata gudu suna karawa kamshin freshener din da yake tashi a falon sanyi.

Kan kafet suka zauna Janan ta janyo filo daga cikin filallukan dake watse a tsakar falon ta tokare hannunta, matar da ta shigo da su ta karasa ta bude firjin dake falon ta dauko ruwan roba kanan guda biyu ta dora a kan farantin da yake kan firjin sannan ta dauki lemon five alive da kuma kofunan tangaran guda biyu duka daga cikin firjin ta hada ta kawo musu. Bayan ta ajiye a gaban su ta zauna suka gaisa cikin girmamawa sannan tace

‘Bari a turo muku Mallam din.’

Ta fice ta kofar da suka shigo. Fatima ta dubi Janan tace

‘Allah dai yasa ya fito da wuri.’

‘Kada ki damu bashi da wasa, yanzu zaki ganshi kuma kin san tun jiya na sanar da shi zuwanmu.’

Sukayi shiru Fatima tana ta karewa falon kallo, ta dubi Janan tace

‘Kalli falon kamar ba a gidan ba, tsakar gidan kaca-kaca amma falon fes kanshinsa ma da ban.’

‘Kin san Malam dai ba boka bane, ilimi ne kawai Allah ya bashi yake bada taimako.’

Ta jijjiga kai kafin tace wani abu ya turo wata kofa da take cikin falon ya shigo da sallama. Bayan sun amsa sallamarsa ya karasa ya zauna a kan kujera mai zaman mutum uku sannan ya fara gaisawa da su. Suna gaisawa Fatima tana kare masa kallo tana mamaki; dan tsurut da shi kuma ba wani babba ba, sai wani cika yake

yana faman kawar da kai tare da zare ido. Ta dubi Janan wadda gaba daya ta nutsu kamar tana gaban sarki. Yayi gyaran murya yana duban Janan yace

‘Itace kika yi min bayaninta?’

Cikin girmamawa Janan tace

‘Eh itace Mallam.’

Ya mayar da dubansa zuwa kan Fatima yana fadin

‘To babu laifi, yanzu za a gama aikinki babu bata lokaci. Za a saka miki ruhinsa a kwalba ko kuma a zobe; idan aka saka miki a kwalba zaki sami waje mai duhu inda ba fuskar gabas ba ki boye kwalbar, matukar baki budeta ba to duk abinda kika fada sai ya aikata; amma fa da kwalba ta fashe aiki ya baci. Idan kuma a zobe aka saka miki to zaki saka zoben a hannunki na hagu ba zaki cire shi ba sai idan da lalura kuma idan kin cire to akwai jaka da zamu baki sai ki mayar ciki amma kada ki bari ya dade ba a hannunki ba. Idan kika rabu da zoben aiki ya baci. Wanne za ayi miki?’

Ta kalli Janan suka hada ido, kafin Janan din tace wani abu Fatima ta dubi Malam tace

‘Zoben dai Malam.’

Yayai gyaran murya yace

‘An gama, tun jiya da ita Janan ta yi min waya aka fara aikinki don haka nan da minti talatin za a gama sai bayani kuma.’

Ya zaro wata takarda da biro a aljihun gaban rigarsa ya mika mata yace

‘Rubuta min sunanshi a nan da sunan mahaifiyarsa da na mahaifinsa.’

Ta karbi takardar ta rubuta sunansa da na mahaifinsa sai kuma ta kasa tuno sunan mahaifiyarsa, sai a hankali kuma sai ta tuna ai yace Nana sunan Hajiya ne da ita kuma sunan Nana Khadija; nan da nan ta rubuta ta mika masa. Ya karba ya tashi ya koma ta kofar da ya shigo. Yana shiga Fatima ta dubi Jana tace

‘Kawata anya kuwa?’

Ta dafa ta tana murmushi

‘Kada fa ki damu wallahi aikin sa kamar yankan wuka, don ma ana bikin sallah ne da wallahi wataran da kyar ake ganinsa bakiga yanda matan manya ke masa zarya ba. Ko nima idan na kasa gane kan Adnan nan nake kawoshi nan da nan zakiga mutum yayi biyayya; zaki sha mamakin aikin Malam.’

Sai da yayi kusan minti talatin sannan ya fito daga dakin dauke da wani bakin faranti da zobe a ai. Yana zama ya mikawa Fatima farantin yace

‘Dauki ki saka a yatsan tsakiyar dake hannun hagunki.’

Ta dauki zoben ta saka kamar yanda yace, tabi yatsan da kallo. Zobe ne kamar na azurfa da wani jan dutse mai kyalli a tsakiyarsa, yayi matukar kama da normal zobe, sai dai kawai yafi zoben azurfa girma. Gyaran muryan Malam yasa ta dago daga duban zoben, yace

‘Matukar kina tare da wannan zoben sai yadda kikayi da rayuwar Mukhtar dan Abdullahi da Hadiza, ko ita Hadizan ba zata iya sakashi ya saba umarninki ba.’

Ta jijjiga kai tana mamakin aikin na Malam, cikin murya kasa-kasa tace

‘To yanzu idan na je gida sai na kirawo shi kenan Malam?’

Ya kyalkyale da dariya har ya so ya bata tsoro saboda sai ta ji dariyar kamar ta fi Malam girma, kamar ba shi yayi dariyar ba. Ta zare ido tana kallonsa, yace

‘Wane Mutum! Babu ruwanki da shi, ki bashi awa ashirin da hudu da kansa zai kawo miki kansa, daga nan kuma sai yanda kika yi da shi. Kada ki kuskura ki neme shi zai zo har inda kike.’

Jijjiga kai kawai takeyi.

Janan tayi gyaran murya tace

‘Mungode Malam, mungode. Allah ya kara daukaka. Yanzu nawa ne kudin aikin?’

‘Naira dubu dari biyu.’

Ya fada tare da tura mata farantin da ta dauki zoben a kai don ta dora kudin.

Fatima da Janan suka kalli juna domin tun suna gidan Janan Fatima ta gaya mata dubu dari ne da ita; shima saida ta hada da kudin da Yaya Ibrahim ya bata don ta sayi kayan sallah dubu talatin da kuma tarin alawee dinta da takeyi. Janan tayi mata alama don haka ta zaro dubu darin dake jakarta ta dora masa a kan farantin, Janan ta tura masa farantin tace

‘Malam ayi mana afuwa da wannan muka zo amma zuwa karshen satin nan zan turo sauran ta account din da ka bani.’

Yayi murmushinsa mai kama da yake

‘Babu laifi Hajiya Janan kina cika alkawari don haka kuje sai na ji ku.’

Sukayi sallama suka fito suka bar Malam a falon, suna fitowa tsakar gidan Janan ta zaro bandir din naira hamsin ta mikawa yaran dake wasa a tsakar gidan wadanda ga dukkan alamun ’yayan malamin ne

‘Ga barka da sallah ko, a siya alawa.’

Suka karba suna ta murna, suka yiwa iyayensu sallama suka wuce.

Suna zama a mota Fatima ta dubi Janan tace

‘Haba kawata, madadin kice yayi ragi. Yanzu ina zan ga naira dubu dari na biya shi, kin san fa aikin da nakeyi voluntary ne babu abinda suke biya kuma wallahi bani da me bani dubu dari a halin yanzu.’

Ta dafa cinyarta tana murmushi

‘Haba mana Fati, ai shi zaizo ya baki dan rainin hankali.’

Ta zaro ido tana dubanta

‘idan fa bai zo ba.’

Tayi dariya ta tada mota tana fadin

‘Shi din banza, ni na baki garanti yanda Malam ya fada in the next 24hours ko wacece ta haifi Mukhtar sai ya kawo miki kansa. Amma kada ki damu idan bai zo ba ni zan biya Malam.’

Ta ja mota yayinda Fatima ta mayar da idonta gaba tana duban hanya tana tunani kala kala, a yanzu dai tafi so suyi sauri su koma kafin su Faisal su dawo.

Ai kuwa basu dade da shiga gidan Janan ba su Faisal din suka dawo, ba tare da bata lokaci ba suka kama hanyar Abuja. Har suka iso Abuja Fatima tana faman kallon zoben nan tana mamakin yanda za ayi yayi aiki; amma dai zata jira zuwa gobe taga ta yanda Mukhtar din zai nemeta.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA DAYA

21

Tunda aka kawo su Nurain bata zauna a gida ba saboda yawon sallah, sai yau. Ta gaji sosai don haka ta kwanta bacci suma su Nana da Nurain ta zare musu ido suka kwanta suna baccin dole. Don haka ko da ya shigo gidan ya leka dakin ya gansu sai kawai ya dawo falon kasa ya zauna a doguwar kujera. Bai jima da kwanciya ba wayarsa ta dauki waka, ya riga ya saita wayarsa bata kara sosai don haka in tana ringing shi kadai yake ji. Ya kalli wayar yayi murmushi saboda jin dadi

‘M. H.’

Shine sunan da ya fito a kan wayar, wato Meena Habu. Haka ta gaya masa sunanta lokacin da suka hadu washegarin sallah don haka yasa M. H. saboda ya badda kama. Yanayinta ya tabbatar masa da cewa ita din a barikinta take amma dai basu taba mu’amala ba, yaune tace masa zasu fita don haka dama kiranta yake jira.

Ta riga ta sanar da shi ba sai ya je daukanta ba ya bata adress zata sameshi, ya san kuma abinda ta kirawo taji kenan. Ya kara wayar a kunnensa yana fadin

‘Hello, ‘yan mata.’

Da murmushi ta amsa har sai da ya jiyo sautin murmushin

‘Uhm, to a ina za mu hadu.’

‘Bristol hotel, ai kin san wajen ko?’

‘Eh.’

‘Room No. 36, sai mun hadu.’

‘Kada fa ka barni in jira please.’

‘Kada ki damu, sai na rigaki zuwa ma don yanzu zan fito kin s……'

Ya karasa a sanyaye sakamakon ji da yayi a jikinsa kamar mutum yana kallonsa.

‘Babu damuwa, thank you.’

Ya fada tare da ajiye wayar ba don ya gama maganar ba. A hankali ya juya ya dubi kofar da ta fito daga corridor; wanda ta nan ake saukowa daga dakin da ya barsu suna bacci; wadda ya bawa baya, tana tsaye a jingine tana kallonsa da alamar tambaya. Yayi sauri ya yake baki

‘Ah kun tashi ne?'

Ta karaso tana goge fuska, ta zauna a kusa da shi

‘Sannu da zuwa.’

‘Yauwa, ke da ‘yayan naki sai bacci kuke ba kwa jin motsi.’

Da kyar ta bude bakinta wanda ya cika da yawu; tara yawun da ya zamar mata jiki tunda ta sami ciki. Wata biyu da cikin amma bata da aiki sai bacci da tofar da yawu, ga baccin nauyi yake shi yasa ma bata jin motsi idan tana yi. Tayi yake tare da mikewa tsaye don taje ta zubar da yawun dake bakinta, tana shigewa bandaki shi kuma ya mike ya shige daki. Ta kuskuro bakinta ta fito daga bandakin ta tarar babu kowa, ta harari wajen da ya zauna sannan ta karasa ta zauna a inda ta tashi.

Tun bata fi sati daya a gidan ba take zarginsa da neman mata, tayi shiru ne saboda bata da hujja; amma sosai take zarginsa. Bata fahimci wani abu ba daga maganar da ta ji yana yi amma dai ta fahimci appointment ya hada kuma da mace, kawai dai zata yi shiru ne don bata da hujja amma dole ta bincika. Ta saka masa ido sosai tana so ta gane pattern din bude wayarsa. Tabbas idan ta kamashi da neman mata za ayi rigima don bazata dau wulakanci ba.

Motsin fitowarsa ne ya katse mata tunani don haka ta dago ta dubeshi, a shirye yake tsaf ya canza kaya kamar mai shirin zuwa zance. Ta tashi ta wuceshi ta zubar da yawun bakinta a bandaki tana fitowa tace

‘Fita kuma zakayi?’

Ya washe baki kamar wani mara gaskiya yana shafa gemu ya bata amsa

‘Eh zamu wajen wani Alhaji ne da Suraj wanda muke so ya bamu wani aiki, dama shi nake jira ya kirani shi yasa na kwanta a nan.’

Da dabara ta bude bakinta da ya riga ya fara cika da yawu tace

‘Uhm, a dawo lafiya.’

‘Allah ya sa.’

Har ya kusa fita ya juya ya dubeta tana zaune a kan kujera yace

‘Kada kiyi abincin dare da ni don zamu zauna gidan Suraj din mu duba wasu takardu idan mun dawo, na san cewa zai yi sai mun ci abinci.’

‘Ok, sai kun dawo.’

Ya fice ya turo mata kofar. Ta yi ‘kwafa tana harara kofar da ya fice saboda takaici. Bai jima da fita ba yara suka tashi daga bacci don haka ta cigaba da hidimarta da su tana tunanin hanyar da zata bullowa Mukhtar.

Sai bayan sallar Magriba sannan dabar ta fado mata, don haka ta dauki wayarta ta shiga daki ta turo kofa. Hajara ta kirawo; matar Suraj. Duk da ba wani shiri sukeyi sosai ba amma dai suna gaisawa, ita Jamilan ce ta kasa sakin jiki da matan abokansa saboda a tunaninta duk kawayen Safiyya ne don haka ma bata shiga cikinsu. Cikin mutunci suka gaisa sannan Jamilan tace

‘Uhm, don Allah maman Anwar Baban Anwar yana kusa.’

‘A’a wallahi, bai dawo ba tunda ya fita wajen karfe biyu na rana. Ina jin dai yana gidan yayansa.’

‘Allah sarki. Don Allah kiyi min wata alfarma mana.’

Da mamaki tace

‘Allah ya bani iko.’

‘Mukhtar ne dama yace min tare zasu fita da Baban Anwar shine nake so na san ko haka ne, ya ma ce min a nan zasuyi dinner . Don Allah idan sun shigo ki sanar da ni ko ta Whatsapp ne.’

Ta riga ta san halin Mukhtar don shi yasa itama take kokarin ta raba shi da Suraj din, don haka tayi murmushi tace

‘Kai gaskiya dai ba a nan zai yi dinner ba don idan zai kawo wani su ci abinci yana sanar dani, amma in sha Allah da sun shigo tare zan gaya miki.’

Sukayi sallama suka ajiye waya.

Ta jefa wayarta kan gado ta ja tsaki, dama ta san karya Mukhtar ya shirya mata amma bari ta Jira kiran Maman Anwar.

Basu fi minti talatin da ajiye waya ba Maman Anwar ta kirawota, bayan ta dauka tace

‘Jamila Baban Anwar din ya dawo yanzu, sai dai bana jin ma sun fita da Mukhtar din don daga gidansu yake.’

‘Ok, babu damuwa nagode sosai Maman Anwar, don Allah kada ki bari su san munyi wannan wayar.’

‘Kada ki damu, in sha Allah babu wanda zai ji.’

Sukayi sallama suka ajiye waya.

Jamila ta jefa tata wayar a kan gado ta ja tsaki

‘Wallahi zaka dawo ka sameni, dan rainin hankali kawai!’

Ta karasa ta zauna jabar a gefen gadon ta zuba fuskarta a tafukan hannunta kawai sai jin danshi tayi. Ta daga ta dubi hawaye da yake kan hannunta tayi kwafa, ta bude bakinta wanda yake cike da yawu tace

‘Ko shekara ba’ayi da auren ba amma zan fara karbar takaicin ka Mukhtar, duk wannan kyan nawa da kake gani har ya zama muni ka koma bariki. Lallai za ayi rigima don wa…..’

‘Mommy na gama.’

Muryar Nana ta katse mata tunanin, kashi ta gama take kira azo ayi mata tsarki. Ta ja tsaki sannan ta mike ta nufi bandakin da yake a falon da ta barsu.

Yanzu haka ma wannan yawon da yake shi ya fitar da uwarasu, ya zo ya hada mata yara ga wani a cikinta shi kuma ya tafi yawo. Kenan yanzu ita ta zama Nanny, aikinta raino kawai, shi kima yayi ta yawo yana fafe matan mutane. Ta sake yin kwafa dai-dai lokacin da ta karasa bandakin.

Sai wajen sha daya da rabi na dare sannan ya dawo gidan, a hankali ya shiga da sanda saboda yana tunanin sunyi bacci ita da yaran, ga mamakinsa tana zaune a falon a kan kujera da take kallon kofar. Da murmushi ya karasa ciki yana sallama, ta riga ta shirya don haka bakinta babu yawo saboda ta saka cingam a bakinta wanda take taunawa.

Bayan ta amsa sallamarsa ya karasa ya zauna a kusa da ita yana kokarin duban fuskarta yana fadin

‘Ah, bakiyi bacci ba har yanzu?’

Murmushin yake tayi ta ce

‘Baka son ganina ido biyu kenan, shi yasa ka jira sai nayi bacci zaka dawo ko?’

‘A’ah, kin ma fi kyan gani idan kina ido biyun ai.’

Ta kawar da kai ba tare da ta ce komai ba, suka yi shiru na dan lokaci. Ya mike ya kulle gidan ya kama hannunta ta tashi tsaye suka shige daki yana fadin

‘Na gaji sosai, bacci nake ji mu je mu kwanta.’

Sai da ya gama shirinsa tsaf zai kwanta yana zaune a gefen gadon tayi gyaran murya tace

‘Wai don Allah yau ina kaje ne?’

Da mamaki ya kalleta

‘Ah, ce miki fa nayi fita zamuyi tare da Suraj kuma gidansa za mu ci abinci.’

Ta tsattsareshi da ido sannan tace

‘To ai ba kwa tare don maman Anwar ta ce min shi kadai ya koma gida tun magriba kuma bai sake fita ba.’

Maganar tata tayi masa ba-zata don bai yi zaton zata bibiye shi ba, da sauri ya kau da fuskarsa tare da shan kunu

‘Oh, ai da yake mun gama da wuri sai na ajiye shi a gida na tsaya majalisa wajen su shamsu, nan muka ci abincin dare ma.’

Ko wanda bai san Mukhtar ba yaji wannan maganar ya san mai fadarta karya yakeyi, ta kawar da kanta sukayi shiru na dan lokaci. Jim kadan ta dubeshi a tsiwace tace

‘Mukhtar.’

Ya juyo suka hada ido tanayi masa wani kallon raini tana tauna cingam din da yake bakinta tace

‘Na san da mace kuka fita, Kai kadai ba tare da Suraj ba. Idan aure kake nema ka sanar dani tun wuri kafin nazo nayi abinda ni da kai za muyi nadama, kuma kayi shi cikin mutunci. Wallahi ba zan yarda da cin amanar aure ba, ina zaune a gidanka na tsare mutuncinka kai kuma kana yawon barbadar da nawa mutuncin. Wallahi sai na tayar muku da hankali da kai da duk yarinyar da kake nema na gaya maka.’

Kafin yace wani abu ta mike ta fice daga dakin ta mako masa kofa.

Nan ta barshi zaune yana mamaki; bai taba tunanin Jamila ta iya tsiwa haka ba ko ta iya ma bai taba tunanin zata iya yi masa ba. Lallai idan bai yi da gaske ba komai ma zata iya aikatawa don yaga tana nema ma ta zageshi. To wa ya gaya mata da mace ya fita? Ko matar Suraj ce ta gaya mata yana da ‘yan mata don ya san bata son ganinsu tare da Suraj?

Haka ya kwanta yayi ta juyi a gado ya kasa bacci saboda tunanin yanda zai bullowa Jamila, sai gefin asuba sannan bacci ya kwasheshi.

Ita kuwa Jamila tana fita ta wuce dakinta ta rufo kofa, ta jingina a bayan kofar da ta rufe tayi kwafa ta share hawaye da ya fara bin fuskarta. Duk da bata tabbatar da abinda take zargi ba amma wannan kame-kamen da yake ya tabbatar mata da zarginta, amma wannan abu ne da bazata dauka ba don tana jin zata iya zuwa gidansu yarinyar ta kora mata warning idan ta dawo shi kuma ta sauke masa rashin mutunci a ka. Ta jijjiga kai ta fada a fili

‘Ba zai yiwu ba wallahi, ba zan dauka ba.’

Ta wuce ta kwanta a kan gadon bayan da ta gyarawa Nana kwanciyarta a kan katifarsu da take tsakar dakin.

Yanda ya kasa bacci haka itama ta kasa baccin tana tunanin mafita,ba zata juri zama da mazinaci ba domin ita ko aure zai kara to tana so ya kai matar wani gidan ba inda take ba saboda gaskiya tana da kishi; balle ace tana nan gidansa yana bin matan banza.

Bata son yanda kullum Nana take tashinsu daga bacci tun shida na safe amma yau taji dadin hakan duk da batayi wani isasshen bacci ba. Nan da nan ta fito da yaran ta shirya musu breakfast; indomie ta dafa sannan ta soya kwai. Suka zauna ita da yaran gaba daya a dining table suka ci suka koshi. Nan ta bar kwanukan a kan table din ta zaunar da su a gaban TV ta kunna musu sannan ta wuce dakinta ta koma bacci.

Kamar yanda ya saba sai wajen takwas da rabi sannan ya fito da shirinsa tsaf na tafiya aiki, abinci kawai zai ci ya wuce. Bayan su Nurain sun gaishe shi ya wuce dining table don yaga alamar abinci kuma Nurain yace masa sun ci abinci su da Mommy. Ya karewa table din kallo bai ga alamar an ajiye masa abinci ba don haka ya wuce kicin inda har tukunya ya buda babu wani abu, ya tabbatar dai bata ajiye masa komai ba.

Ya fito daga kicin din ya wuce dakinta, ya tura kofa a hankali ya shiga da sallama. Tana kwance a kan gado ta bawa kofa baya, bata motsa ba don haka yayi gyaran murya ya kira sunanta. Ta juyo tare da gyara kwanciya ta dubeshi ba tare da tace komai ba, yace

‘Ina abincin nawa zan fita ne fa?’

‘Mtsewww!’

Ta ja tsaki sannan ta cigaba

‘Inda kake zuwa can ai naga suna baka abinci don naga sun baka na dare shi yasa ban girka ba.’

Mamakinsa ya karu, cikin bacin raia yace

‘To yanzu ya kike so ayi, haka zan tafi office banyi breakfast ba kenan?’

Cikin halin ko-in-kula tace

‘Zabi ya rage naka, ni kam ai nayi breakfast yanzu kuma bacci zan yi.’

Cikin bacin rai yace

‘Jamila ba fa na son raini da wulakanci, ni kike gayawa wannan maganar banzan?’

Ta kalleshi a raine tace

‘Uhmmm! Kan ka ake ji.’

Ta juya ta gyara kwanciyarta ta rufe idonta ta barshi nan tsaye.

Ransa yayi matukar baci, wato ma ta mayar da shi mahaukaci. Ya rasa mai zai ce mata don haka yayi kwafa ya fice daga dakin tare da maka mata kofa. Ta gayar kwanciya tayi tsaki tace

‘Ka balla kofar gidan naka sai kaji dadin gyarawa dan rainin hankali.’

Ta juya ta yi kwanciyarta.

Yana fitowa falon ya dauki jakarsa ya fice ya kama hanya, ranshi a bace sosai. Ba wai abincin ne bazai siya yaci ba, wannan ba wani abu bane a wajensa amma wannan wulakanci da tayi masa ya tsaya masa a rai. ‘kanka ake ji’ shine abinda ya fi tsaya masa a rai. Wato ma shi ta mayar mahaukaci kenan? Lallai za ayi rigima don sai ya saita ta. Ba zai dauki raini ba don ba haka ya saba, ko me yayiwa Safiyya sai ta yi masa abinci bata taba fasawa ba.

Cikin hanzari ya kawar da tunanin Safiyya don baya son ya dinga tunata da yawa, amma tabbas sai ya koyawa Jamila hankali.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA DAYA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA BIYU

22

Saboda tsabar bacin rai mantawa yayi bai sayi abinci ba sai bayan ya shiga office, don haka sai da ya zauna sannan ya aika masinjansa ya siyo masa dankali da kwai. Bayan ya kawo ya hada shayi ya zauna a kujerar zaman baki ya fara karyawa, yana cin abinci yana tunani kala-kala.

Haka kawai yaji yana kewar Fatima, yana tuna lokuta da dama da yake tare da ita. Aiki yake amma har azahar ya kasa cire Fatima daga lissafinsa, don haka bayan azahar da ya dawo office din daga masallaci sai ya zauna a kan kujerar zaman mutum biyu da take gefe daya a office din ya zaro wayarsa yana lalubar lambar Fatima domin ya kirawota.

Babu suna ya adana lambar domin tun bayan da Safiyya ta gane lambar ya cire sunan don haka sai da ya dauki lokaci yana tunani sannan ya gano lambar wadda kusan sama da shekara guda kenan rabon da ya kirawota. Har wata 'yar karamar murna yayi da ya gano lambar, wanda shima da kansa ya rasa gane me yasa yake murna don zai yi magana da Fatima.

Sai da ya kirawo layinta kusan sau goma amma wayar bata shiga, duka layikansa biyu yake kiranta da su amma duk ko ringing bata yi take katsewa. Sai da ya nutsu sannan ya gane blocking din layikansa Fatiman tayi; bai taba zaton zata iya blocking dinsa ba, amma sai ya tuna shi ya fara blocking dinta. Har ya hakura da neman nata ya cigaba da aiki sai kuma zuciyarsa ta cigaba da azalzalarsa a kan son jin muryar Fatiman, don haka sai ya mike ya fice daga office din.

Da yake akwai mai sayar da layin MTN a nan bakin gate din office din nasu nan ya tsaya ya sayi sabon layi wanda ya saka a karamar wayarsa wadda dama layi biyu take ci amma shi daya ya sa mata; aka yi masa rajista ya sa kati ya koma office.

Tun kafin ya karasa zama ya danna mata kira yana ta addu’a Allah ya sa ta shiga domin ya fara tunanin ko aure aka yiwa Fatiman.

Bata dade tana ringing ba aka dauki wayar, ta amsa da zazzakar muryarta wadda ta sa ya saki wani murmushi

‘Hello, salam alaikum.’

Sai da ta jiyo sautin murmushinsa a daidai lokacin da ya amsa sallamarta. Tsaf ta gane shi; musamman da yake tun safe take jiran wayarsa tunda Malam ya gaya mata kafin awa ashirin da hudu zai nemeta; amma sai tayi kamar bata san me maganar ba. Bayan sun gaisa yace

‘Fatima.’

Cikin halin ko in kula tace

‘Na’am da wa nake magana?’

Yayi murmushin da har sai da ta jiyo sautinsa sannan yace

‘Fatima baki gane muryata ba? Mukhtar ne fa.’

‘Uhm! Allah sarki. Da yake mun jima bamuyi magana ba kuma bani ma da lambar taka yanzu.’

‘Hakane, to ai kin yi blocking dina a lambobin da kike da su ko da yake ban san ma ko kin yi deleting ba bayan blocking din.’

‘Uhm.’

Suka dan yi shiru, ta fuskanci dai ba zata yi magana ba don haka yace

‘To yanzu ya za ayi Fati? Duk da na san ni mai laifi ne amma ina son ganinki. Kina gidan Mommy ko? In ya so ko gobe ma sai na shigo Zariyan.’

Ta gatsine fuska kamar yana gabanta tace

‘A’a bana nan, ina Abuja gidan Anti.’

‘Ah to ai ta kwana gidan sauki ai ko Abujan sai na shigo, in dai zan ganki ai duk inda kike zuwa zan yi.’

‘Ba ma sai ka zo nan din ba, ka dai jira idan na koma Zariyan na kirawo ka sai ka zo.’

Ya marairaice

‘Haba Fati, kiyi hakuri mana na zo Abujan. Ko da wuri zaki koma gidan?’

‘A’a nima ban sani ba, may be next week may be upper week. Zamu dai yi magana kawai.’

Ta bashi amsa cikin kosawa.

Ya fahimci kosawarta kuma baya son ya gajiyar da ita tunda lallabata yake yi don haka yace

‘To shikenan babu damuwa.’

Sukayi shiru na dan lokaci, jimawa kadan yace

‘Fati.’

Ta amsa a gajarce

‘Um.’

‘Kiyi hakuri ki bude lambobi na da kikayi blocking kinji, kin ga ko ta whatsapp ma dinga hira.’

Ta danyi jinkiri sannan tace

‘To.’

‘Yauwa. Kiyi hakuri kinji, na san ni mai laifi ne shi yasa ma nake so nazo da kaina na bada hakuri.’

Sukayi shiru kamar masu sauraron numfashin juna, jimawa kadan tace

‘Bari na je zan dan taya Anti aiki ne, mayi magana daga baya.’

‘Ok. Please ki bude ni fa, zan miki magana a WhatsApp din yanzu.’

Ta amsa da kyar sannan suka yi sallama suka ajiye wayar.

Yana murmushi ya tashi ya koma kan kujerar jikin tebur din ya zauna domin cigaba da aiki. Shi kansa bai gane dalilin da yasa yake jin dadi ba kawai saboda ya ji muryar Fatima, amma a halin yanzu yana jin zai iya auren Fatima saboda yanda yake so ta kasance a tare da shi kullum; musamman da ya tuno yadda suka rabu da Jamilan yau da safe.

Ita kuwa Fatima suna ajiye waya ta jefa tata wayar kan gadon da take zaune, ta dunkule hannu ta naushi iska sannan ta kyalkyale da dariya sannan ta fada a fili da yake ita kadai ce a dakin

‘Alhamdulillah, ka zo hannu dan rainin hankali za ka gane baka da wayo.’

Tana gama murnar ta dauko wayar ta dannawa Janan kira, nan ta bata labarin abinda ya faru sukayi ta dariya. Ta tsara mata yanda zasuyi Fatiman ta karbi kudi a wajen Mukhtar din idan ya zo Zariyan domin ta cikawa Malam kudin aikinsa. Suka ajiye wayar kowaccensu tana dariya.

……

Duk yanda yake tunanin idan ya share Jamila zata nemi shiri ba haka ce ta kasance ba, domin ita din ma fushi take da shi sosai. Hatta dakinsa na kwana daina shiga tayi balle ta gyara, abu daya dai da zai sa ya raga mata da yaga fushin da take da shi bai sa ta daina kula su Nurain ba duk kuwa da yanda laulayin ciki yake damunta. Don haka gaba daya sai ya mayar da hankalinsa wajen lallashin Fatima saboda yanda zuciyarsa take azal-zalarsa da son ganinta.

Ya samu dai ta bude blocking din da tayi masa don haka suna magana ta Whatsapp, duk da idan yayi mata sako da safe sai ta kai dare bata bude ba; wataran har sai ya kirawota yace ta duba.

A haka har aka kwana shida, ya ma daina shiga gidan sai ya ci ya koshi don ya san ko da abinci Jamila ba zata bashi ba.

Sai ranar kwana na bakwai da ya kira Fatima ta sanar da shi jibi zata koma Zariya don haka suka alkawarin a kan washegarin ranar da ta koma zai je Zariyan.

Baya son Jamila ta zargi wani abu idan ya fara zaryar zuwa Zariya don yana jin akalla duk sati zai dinga zuwa, don haka da kanshi ya hakura ya nemi shiri da ita.

Sosai ya tsarata a kan matar da taji suna waya Director ce a office dinsu kuma shi babu yarinyar da yake nema. Ta ji shi dai amma bata hakura ba don ta yiwa kanta alkawarin sai ta bincike shi sosai domin ko babu komai ta sami natsuwa. Haka suka warware suka koma harkokinsu kamar da.

Saida ya dauki wajen sati biyu yana lallaba Fatima sannan ta ce masa ta dawo kuma zai iya zuwa. Ji yayi kamar ya tafi a ranar da ba don yamma tayi ba, a haka dai ya daure sai washegari da zai kama Juma’ah sai kawai ya hakura da zuwa office ya wuce Zariya.

Tun dare ya sanar da Jamila zai je Zariyan, ya gaya mata akwai wani abokinsu da babansa ya rasu don haka can zai je masa gaisuwa. Bata zargi komai ba ta yi masa ta’aziyya ta sanar da shi ya siyo burodi don ba zata iya tashi ta girka abincin safe ba tunda Nurain yana hutun makaranta.

.....

Sai ranar Juma’ah sannan Fatima ta samu ta tsara Mommy, ta tuna mata dama mahaifiyar Mukhtar ce ta hanashi kara aure saboda Safiyya ‘yar kanwarta ce kuma bata so ayi mata kishiya; kamar yanda ya gaya mata; amma yanzu ta yarda saboda Babanshi yayi magana.

A daki ta sami Mommy din tana shirin tafiya aiki da yake daman ita Fatiman bata zuwa aiki ranar Juma’ah tunda voluntary takeyi ba biyanta ake ba. Bayan ta gama sauraronta ta bata rai tana hararta tace

‘Mai zai dawo yayi? Nifa bana son yaudara. Dama shi kike jira kika ki kula mutane ko?’

Ta sunkuyar da kai

‘Mommy wallah ba haka bane, kuma yanzu ai da gaske yake.’

Suka yi shiru na dan lokaci yayinda Mommy ta zuba mata ido ita kuma ta sunkuyar da kai. Jim kadan Mommy din tace

‘Shike nan, amma idan ya zo ki bashi lambar wayar yayanki ya nemeshi suyi magana ni kuma zan yi magana da Yayan naki kafin nan.’

Sukayi sallama Mommy ta wuce wajen aiki tana ta juya maganar dawowar Mukhtar a ranta. Bata ji dadin dawowar tasa ba don da ace akwai wani mai neman Fatiman ba zata bar Mukhtar ya dawo ba, to amma har yanzu babu wani manemi da yake neman Fatiman ga shi ta kusa shekaru talatin da haihuwa; domin har an fara yarwa Mommy magana a dangi. Don haka tana ganin tunda dai ita Fatiman ta amince gara a bawa Mukhtar din dama ya fito ayi auren.

Sai wajen sha daya saura sannan ya isa Zariya, tun kafin ya tsaya a bakin gate din gidan su Fatima yayi mata waya don ta fito. Sai da ta dauki sama da minti ashirin tana bata masa lokaci sannan ta fito. Tun kafin ta karaso inda yake a cikin motarsa yake ta kallonta yana murmushi; ya ji dadin ganinta kuma tayi matukar yi masa kyau da kwarjini; nan da nan aka tayar da tsohuwar soyayya.

Kafin ta karaso ya mika hannu ya bude mata kofar gaban motar yana ta faman murmushi, ta karaso ta tsaya a daidai inda yake tace

‘Ka fito mu shiga ciki sai mu zauna a falo.’

Bai ga fuskar yin korafi ba don haka ya rufe motar ya fito ya bita a baya, suka shiga har falon baki. Ta nuna masa kan kujerar zaman mutum uku ya zauna ita kuma ta zauna a kujerar zaman mutum daya. Basu dade da zama ba Baba Habi ta shigo ta kawo masa ruwan roba wanda ta dora a faranti tare da kofi guda daya.

Suka dan taba hira ya sake bata hakuri tare da yi mata alkawarin duk lokacin da ta shirya zai turo maganar aure. Suna nan zaune wayarta tayi kara, tana dagawa kafin ta fara magana ta dube shi tace

‘Janan ce.’

Yana murmushi ya amsa

‘Allah sarki, kice ina gaisheta.’

Ta cigaba da magana da Janan din a waya

‘Kai Janan bani fa da kudi, nifa in ban samu ba ma sai na fasa zuwa bikin.’

Ta dan yi shiru tana sauraron abinda Janan din take fada sannan ta cigaba

‘Allah kawata, to ai na gaya miki bani da kudi.’

‘To shikenan ki bari dai mayi maganar daga baya. Mukhtar yana gaisheki.’

Sukayi sallama ta ajiye wayar fuskarta babu walwala. Ya dubeta yace

‘Wani abun zaki saya ne kike ta faman babu kudi?’

Ta kawar da kai cikin damuwa sannan ta bashi amsa

‘Hmm! Wallah bikin wata kawarmu za ayi an kawo anko kuma gaskiya mai tsada ne don a Abuja ma za ayi biki, to ita Janan mijinta ya saya mata ni kuwa ka ga babu wanda na ajiye ai sai dai na hakura.’

Yayi murmushi

‘Haba dai, nawane kudin ankon naki sai na tura miki, tunda kema kin ajiye ni ko?’

Tayi dariya tace

‘Haba dai, 120k ne kawai komai da komai.’

Bai zata kudin zai kai haka ba shi yasa yayi saurin cewa zai yi, to amma tunda ya ce zai yi yana ganin dole yayin musamman da yake tunda ya zo bai ga walwalarta yanda yake so ba.

Ya zaro wayarsa ya fara lalubawa

‘Account dinki na UBA zan tura miki ko?’

Ta fadada murmushinta harda dariya

‘Eh, ai kuwa na gode.’

Ya cigaba da kokarin tura kudin wadanda kudi ne da ya ware saboda haihuwar da Jamila zata yi nan da wata shida, duk da baya son taba kudin amma ya kasa hana kansa haka ya tura mata.

Nan take taji alert, ta dubeshi tana dariya tace

‘Gaskiya na gode sosai, ba zaka gane yanda naji dadi ba.’

Cikin walwala suka karasa hirarsu sai wajen sha biyu da rabi lokacin an fara kiran azhar tace masa

‘Bari naje gida kai kuma ka kama hanya don Mommy tace kada na dade, kuma wallahi idan na dade da yawa Baba Habi gaya mata zata yi.’

Yayi 'yar dariya

‘To ai babu laifi, gara Mommy ta kular min dake.’

Ya mike ta raka shi bakin mota suka yi sallama ya kama hanya yana ta wasiwasi.

Sosai yake son Fatima yanzu kuma aure yake so suyi, amma ya ga kamar ita din bata saki jiki da shi sosai ba. Saboda yana kula da ita, duk yanda ya so ya rike koda hannunta ne bata bashi dama ba domin shi a motar ma yaso suyi zancensu amma taki. Ya so ma yace mata su dan je cikin gari yawo amma bai ga fuskar ba, dole haka ya hakura suka rabu.

Har yazo gida yana tunanin ta inda zai gayawa Jamila zai kara aure, amma ya san dole ya gaya mata don ba zai fasa ba. A yanzu ma yana jin kamar idan an ce ya zabi daya tsakanin Jamila da Fatima to lallai Fatiman zia zaba sai dai duk abinda zai fari ya faru.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA BIYU.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA UKU

23

Tun ana sallacewa Sabir ya fara sanarwa duk wani wanda ya san gidansu akwai mata cewa ana kitso a gidansu, har matan ajinsu sai da ya gayawa duka da dai sun yi candy amma yawancinsu gidajensu na nan kusa da unguwar.

Babu wanda ya zo kitso ko sau daya, ita kuma da yake bata sa a rantaba babu abinda ya dameta. Ta riga dai ta fara zuwa islamiyya tunda ana sallacewa Yaya Habibu ya kaita. Sosai take jin dadin zuwa islamiyyar nan domin ko babu komai yana debe mata kewa da kuma rage damuwa, gashi za a hadu da mata idan babu malami a aji ayi ta hira; duk da dai ita din bata fiya shiga hirarrakin ba amma dai ana yi tana ji.

Ranar Juma’a da safe suke zuwa sai kuma Asabar da Lahadi da yamma, don haka har Allah Allah take Juma’a ta zagayo.

Yau Juma’ah tana dawowa daga islamiyya suka hadu da Sabir a kofar gida ya dawo daga makaranta; inda Yaya Habibu ya saka shi ya koyi computer tunda yanzu yana zaman jiran admission; da fara’arsa ya karaso suka jera yana ta dariya ya dubeta yace

‘Ya Safiyya albishirinki!’

Itama murmushin take tace

‘Goro.’

‘Yau dai na sami kwastoman kitso, in sha Allah da yamma zata zo.’

‘Ummm! Kace yau zamuyi sharholiya da kudin kitso.’

‘Kwarai kuwa don ni naira dari biyar nace mata kudin kitso.’

Ta dube shi tana zare ido

‘Kai Sabir! Allah ya yaye maka son kudi, ina ma laifin dari biyu.’

‘Haka za a dinga biya gaskiya, ba wani ragi. Ai first class kitso ne.’

Har sun kusa shiga tsakar gidan ya janyota baya yana magana kasa-kasa

‘Don Allah dai kada ki bawa Umma kudin, idan an baki ki bani na samo canji sai ki bata dari biyu ki dauki dari uku ki boye. Ko ma dai kawai ki bani na ajiye miki.’

Tayi 'yar dariya tare da yin dage ta doki kansa

‘Allah ya shiryeka jai dai.’

Suka shiga gidan suna ta yiwa juna dariya.

Sai bayan sallar la’asar Sabir ya shigo da ‘yar ajin tasu tare da kannenta su biyu. Ya raka su suka gaida Umma sannan ya kirawo Safiyya. Har tana jin tsoron kada Umma tace bazata yi kitson ba sai ta dafa musu abincin dare sai kuma Umman tace su je rumfar bakin gate suyi kitsonsu. Don haka nan da nan suka fito suka fara kitso.

Daf da magriba suka gama kitson, Babbar ta mike ta zaro kudi naira dubu daya da dari biyar ta mikawa Yaya Safiyya, sukayi mata sallama suka fice. Kafin ta nade tabarmar Sabir ya shigo da yake dama yana waje, da hanzari ya karasa ya karbe kudin daga hannunta yana murmushi. Ya wari naira dari biyar ya bata yana fadin

‘Rike wannan kina shiga ki cewa Umma ga kudin kitson, wannan dubun kuma zan shige na saka miki a jakarki idan sun kai uku sai mu bude account.’

Ta karba da bakinta a bude, kafin tace wani abu ya karbi tabarmar hannunta ya shige gidan ya barta a tsaye tana masa dariya. Bayan ta shigo ta sami Umma tana kwashe ruwa, ta tsuguna daga gefe tace

‘Sannu da aiki Umma, bari na wanko hannu nazo na karasa miki. Kinga kudin kitson.’

Ta karasa tana mika mata dari biyar. Umma ta dan yi murmushi tace

‘Kada ki zo min kichin ba so nake gashi ya shiga miyar ba.’

Ta kalli dari biyar din tana murmushi ta cigaba

‘Babu laifi ma suna biyan kudin kitson, Allah ya sa albarka kuma ya sa an fara a sa’a.’

Har cikin zuciyarta taji dadin addu'arnan tana fara’a tace

‘Amin Umma.’

Ta mike ta shige dakin. Tana shiga ta saka kudin a jakarta ta wanko hannu tare da alwala. Bayan ta idar da sallar Magriba tana kan dadduma tana addu’a da yiwa Allah godiya. Bata taba tunanin kudin kitso zasu sakata farin ciki haka ba, amma dai yanzu wasai take jin zuciyarta musamman da ta san Umma bata san da dubu dayan ba.

Ta dade rabon da ta rike kudi haka nata na kanta wanda take da tabbacin Umma ba zata kwace ba. Lallai ta yarda yanzu kam da kanta zata dinga gayawa mutane tana kitso.

Tun daga wannan kitson kuma bata sake samun masu son kitso ba har aka yi sati biyu. Ranar Asabar suna aji a islamiyya Hajiya Saliha wadda take zaune a teburin da yake gaban na su Safiyya ita da kwayenta suna hira take ta mita; matar da take yiwa yaranta kitso tayi tafiya don haka gashi yau asabar basu samu an yi musu ba, tana tunanin dai ta kaisu saloon. Sai da kyar Safiyya ta bude baki tace

‘Anti Saliha ina yin kitso fa, zan iya zuwa na yi musu in kina so.’

Ta juyo da murmushinta

‘Allah Safiyya? Shine baki taba gaya min ba? To yaushe zaki zo kiyi mana? Wallahi duk yaran babu mai kitso a ka har ni ma.’

‘Ko gobe ma sai na zo idan dai kun shirya.’

‘To Allah ya kai mu, nan wajen masallacin Juma’ah gidan yake. Kina zuwa masallaci idan kika je karshen katangar ki tambayi gidan su Abbale za a nuna miki gidan. Don Allah ki zo da dan wuri.’

Aka cigaba da karatu. Bayan Malam ya fita daga aji Safiyyan tana jin Maman Afaf wadda take kusa da Anti Saliha tana radawa Anti Salihan magana

"Sai fa kin yi a hankali yarinyar nan bazawara ce, kin san zawarawan nan yanzu sai ta fara zawarce miki miji.”

Tana jin Salihan ta bata amsa

“Ke kin fiye kishin banza wallahi, to menene ba shikenan ba.”

Abun ya tsayawa Safiyya a rai amma ta danne, tunda Allah ya sani ita ba wannan ne zai kaita gidan ba. Irin wadannan maganganun zuwa yanzu ta saba jinsu, don haka ma abun ya daina bata haushi.

Haka taje ta yi musu kitson nan su shida; yaran Anti Saliha su hudu, yarinyar makociyarta daya da kuma ita Anti Salihar. Da ta gama anti Salihan ta kirgo kudi naira dubu uku ta bata tana ta godiya.

Tana shiga gida ta boye dubu uku ta nunawa Umma dubu daya, washegari kuwa suka fita ita da Sabir ta bude account a banki don da kanta tace sana’ar kitso ma yanzu ta fara.

_

Kawo yanzu Fatima ta sakawa Mukhtar ka’ida a kan lallai duk Juma’a a Zariya zai wuni, haka zai je gidansu su zauna a falo su sha hira sannan ya taho. Shi da kansa yake tambayarta ta fada masa ranar da za a kawo kudin aure da sa rana amma ta ki, sai dai kawai tace masa akwai shirin da takeyi da kanta zata gaya masa.

A yanzu bata san ko tana son Mukhtar ko bata son sa ba, shi yasa ma ta kasa amincewa ya aiko. Kullum sai tsara Mommy take tana gaya mata zai aiko, ita kuwa

Mommy bata so ta janyo abinda zai rusa maganar auren don haka ta kyale tunda dai nan cikin gidan suke zance kuma Fatiman tace zai turo.

Don haka duk Juma’ar duniya sai ya je Zariya wajen Fatima, ragowar ranakun kuma su wuni suna waya. Ga kashe kudi don duk abinda tace masa tana so to idan zai tafi Juma’a sai ya Kai mata.

.....

Tana sauke abincin safe ta mayar da na rana kamar yanda yanzu take yi tunda cikinta ya girma, idan ta zauna bata yi ba tashin yana mata wahala gashi ta rasa mai aiki mai kwana dole sai mai zuwa da dawowa aka samo mata a unguwar.

Ta zuba na Nurain na makaranta karfe takwas saura Abbanshi ya tafi kaishi makaranta. Bayan ya dawo ya zauna yaci abincin safe wanda ta zuba sannan ya wuce daki.

Tana sauke abincin ranan ta juye musu a flask sannan ta fito falon ta kwanta a kan doguwar kujera yayinda Nana take zaune tana kallon cartoon.

A shirye tsaf ya fito ya samesu, ya dan yi gyaran murya

‘Ni zan wuce, ba lallai na dawo da wuri ba don zan je Zariya.’

Ta yunkura ta tashi zaune ta gyara zama da bakinta wanda yake cike da yawun tace

‘Allah ya kiyaye hanya. Wai ita Zariyan nan yanzu duk Juma’a sai an je ta ne kamar attendance?’

Ya dan yi murmushi

‘Ai na gaya miki wani aikin kwangila na samu a Zariyan shi yasa ranar Juma’a da aiki bashi da yawa sai na tafi na duba wancan. Kada ki damu kwanan nan zan gama ai in sha Allah.’

Cikin halin ki in kula tace

‘Allah ya bada sa’a.’

Yayi mata sallama Nana tayi masa a dawo lafiya ya fice. Yana fita ta sa Nana a daki suka rufe gidan sai bacci; tunda mai aikinta sai sha biyu da rabi take dauko Nurain ta taho da shi sannan ta zo ta fara aikin gidan.

Haka ta kwanta tana ta tunane tunane; wannan zaryar da Mukhtar yake yi Zariya ta isheta, kuma tabbasa sai ta lalubo bakin zaren. Ta riga ta gane yanda yake bude wayarsa don yanzu kusan kullum sai ta bude ta lalube wayar. Bata ga komai ba amma akwai lambobin wayar da ta kwafa domin tana zarginsu, a ciki harda wata lamba da yake kira kullum da safe ranar Juma’a kafin ya fita. Ko yanzun ma kuma akwai kaninta da ta saka ya binciko mata me Mukhtar din yake yi a Zariya duk Juma’a.

Ta kusa haihuwa yanzu domin saura abinda bai fi wata daya ba, don haka bata son ta ja fitna don bata cikin yanayin da zata iya dauka don haka ta bari sai ta haihu don tabbasa tana zargin wata karuwar yayi a Zariya yake raina mata hankali. Ko a Kanon ma Kuma akwai lambar da ta dauka a wayarsa wadda take zargin ta wata karuwarce. Jiran lokaci kawai take da shi da karuwan duk sai ta tayar musu da hankali.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA UKU

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA HUDU

24

Tunda watan haihuwarta ya tsaya take ta gaya masa idan ta haihu event center take so ya kama mata don yin taron suna, ta riga tayi masa lissafin abubuwan da take bukata kama daga abinci, DJ, kudin liki da sauransu. Baya son wannan tsarin nata domin ita Safiyya a gida take yin suna kuma duk abinda ya bayar karba take bata neman kari. Gashi kuma baya son harkar DJ, don haka ma da taga ya dameta da mita tace to taji yayi sauran ita ta biya DJ da kanta.

Kusan kullum sai tayi masa wannan lissafin kuma duk ya amsa zai yi, DJ ne kawai ba zai dauko ba kuma wannan tace zata dauko sai kuma kudin kayanta na fitar suna da ta nemi dubu saba'in ya bata dubu talatin yace ba zai kara ba; haka ta hakura.

Ranar Talata har ya fita aiki ta kirawo shi ta sanar dashi ta fara nakuda, don haka nan da nan ya dawo suka wuce asibiti. Kafin azahar ta haifi yarinyarta mace, da yake ya riga ya sanar musu baya son wankan gida nan da nan yayar mahaifinta wadda suke kira Inna ta iso asibitin inda suka wuce gidan tare.

Ranar da ta haihu da daddare bayan tayi wanka ta shirya ta sameshi a falon sama yana cin abincin dare, yayinda Nana da Nurain suke bacci a gefensa.

Tunda ta shiga yake ta faman kallonta yana murmushi, tana zama yace

'Mai jego, ba kiyi bacci ba? Ai na zata Inna ta hanaki zuwa mu gaisa.'

Tayi dariya

‘Wanka nake lokacin da ka shigo fa.’

‘To ya jikin dai, kalau kuke duk ko?’

‘Alhamdulillah, wanka Inna takewa Baby sai ta gama zan kawo maka ita.’

Sukayi shiru na dan lokaci suna kallon TV, jim kadan tace

‘Maganar suna fa, na sami event center har munyi magana da su. 120k ne kudin zuwa ranar Saturday sai a tura musu duk da yanzun ma suna so a tura deposit.’

Ya dan tsuke fuska

‘Wai yanzu event center din ne 120k, haba ku ko tausayin kudi ba kwa ji?’

Ta karkata kai tana kallonsa

‘To ya za ayi, ai kaga dai mun gama magana don yanzu ma nayi booking wajen.’

Ya jijjiga kai yayi shiru, ita ma shiru din tayi domin in dai a kan taron suna ne zata iya yin komai don babu wanda ya isa ya hanata. Jimawa kadan yace

‘Allah ya sauwake, zuwa Juma’a ko Asabar sai na tura miki kudin.’

Nan da nan ta saki murmushi ta matsa ta dan kwanta a jikinsa

‘Yauwa sahibi ko kai fa.’

Yake kawai yayi ya lakace mata hanci, ta tashi ta fice daga falon. Jimawa kadan ta dawo dauke da Baby ta mika masa ya karba yana murmushi. Ya karewa Baby kallo ya dago ya dubeta yana murmushi yace

‘Ma Sha Allah, fine girl mai kama da babarta.’

Tayi dariya Sannan tace

‘To wanne suna ka saka mata ne?’

Ya zubawa fuskar yarinyar ido yana murmushi, haka kawai zuciyarsa take raya masa ya sa mata Safiyya amma da yake ya san rigimar uwarta sai ya dubeta yace

‘Halimatu Sa’adiyya.’

Tayi murmushi tace

‘Ma sha Allah, Allah ya raya Halima.’

Suka dan taba hira sannan ta tashi ta dawo dakinta yayinda Inna ta hau saman ta dauko mata su Nurain.

…….

Tun ranar laraba ya fara sayayyar abubuwan da za a bukata na taron suna, ya sayi rago ya kawo nan ya daure haka ma abinci, masu lalacewa ne kawai bai saya ba. Ga wani nama kuma da kaji da ya siyo ya kawo gidan yace a gasawa maijego. Duk

wadannan hidimomin a cikin damuwa yake yinsu don tun safe har magriba bai sami Fatima a waya ba, ce masa ake yi wayarta a kashe. Sai yayi kamar ya kirawo Mommy ko yayanta sai kuma ya fasa don da kunya, haka ya wuni ba a hayyacinsa ba saboda yanzu da zarar bai ji muryar Fatima ba sai ya shiga damuwa.

Bayan ya dawo gida da daddare ya gama shirin kwanciya yayi sallama da Jamila ya koma gefen gadonsa ya zauna, wayarsa ya zaro ya kara kiran Fatima a karo na babu iyaka.

Kamar wanda aka tasa daga bacci ya ji wayar tana ringing, kafin wani lokaci aka amsa. Cikin zakuwa ko sallamarta bai amsa ba yace

‘Fatima ina kika shiga ne yau duk kin daga min hankali, tun safe na nemeki a waya na rasa.’

Da damuwa a muryarta tace

‘Hmm! Honey yau abun haushi ne ya sameni, wayar tawa ce ta fada cikin tafasasshen ruwa ta dauke don ko kunnuwa ma taki. Yanzu ma wayar Baba Habi na aro na saka sim dina kuma sai na rasa lambarka don ban haddace ba.’

Yayi ajiyar zuciya

‘Kai! Allah ya kiyaye gaba, amma fa kin daga min hankali Sweetheart.’

Tayi 'yar dariya

‘Nima ba da son raina ba Honey.’

Suka dan taba hira tana tambayar masu jego, ba jimawa tace

‘Bari na mayarwa da Baba Habi wayarta na zo na kwanta.’

Cikin damuwa yace

‘To yanzu ya za ayi kenan na dinga jinki.’

‘Hm! Ka san dai bani da kudi ko? Mommy ma kam yanzu ko saurarona ba zata yi ba, sai dai kawai lokacin da na sami aron waya ka jini.’

Ya sake shiga damuwa don ba zai iya jure rashin jin Fatima ba a yanzu. Yace

‘Ina ga ba haka za ayi ba, nawane kudin wayar sai na turo miki kawai gobe sai ki saya a nan ko?’

‘Ai kuwa da naji dadi Honey, akwai wani dan uwanmu yana sayarwa yanzu zan mishi magana gobe da safe ya kawo min sai na turo maka account din shi ka saka masa kudin.’

‘Ok, to hakan yayi.’

Suka yi sallama suka ajiye waya.

Ya gyara filo ya kwanta. Sai a lokacin sannan ya tuna hidimar haihuwa ce a gabansa kuma ko yanzu ma ya kashe kudi da yawa bai san wayar nawa Fatiman zata kawo ba. Ya san dai ko ta nawa ta kawo dole ya siya shi yasa ma yake fatan ta kawo wadda bata haura dubu hamsin ba.

Haka ya kwanta yana ta faman lissafin kudi saboda yanda hidima take kansa , sai dai da yake bacci barawo ne sai da ya sace shi.

.....

Bai dade da shiga office ba Fatima ta kirawo shi a waya, kai daga jin muryarta ka san tana cikin walwala. Bayan sun gaisa tace

‘Honey ga wayar fa an kawo min, don itace ma na saka sim dina ciki nake kiranka.’

Ya yi murmushi wanda har saida ta jiyo sautinsa a cikin wayar

‘Ah, good. Yanzu dama nake tunaninki ashe ya kawo. To nawa ne kudin?’

Kai tsaye tace

‘Dubu dari da talatin.’

Gumi ya karyo masa don bai zata za ta sayi mai tsada haka ba

‘Har 130k? Wace iri ce ne wayar?’

Ta fuskanci yanda ya canza don haka itama tayi muryar tausayi

‘Umm! iPhone ce. To ko mayar masa za ayi na hakura don gaskiya sai dai na hakura tunda ai ba zan yi ta zama da karamar waya ba ko.’

‘No! Ba wata damuwa fa, ki turo account number din ta whatsapp yanzu zan saka masa. Kin san Jamila ta haihu ne gashi next week suna shi yasa babu kudi sosai.’

‘Au haka ne fa, ka san na manta da ba zan yi maganar wayar ba ma. Don Allah ka turo min hoton Baby.’

‘Ok. Bari na tura masa kudin yanzu idan na tura mayi waya.'

Suka yi sallama ya ajiye waya. Take ya bude Whatsapp wanda yana budewa sakonta ya shigo ta turo da account number. Sunan namiji ne da account din don haka bai kawo wani abu ba, kafin ya gama kwafar account number din wani sakon nata ya shigo

“Honey please 135k zaka tura masa coz yaron shago ne ko don shima ya sami wani abu.”

Yana yatsina fuska ya rubuta amsa ya tura

“Yes my love.”

Haka ya gama lissafinsa ya tura 135k wannan account, sannan ya tura mata rasit. Tana budewa ta kyalkyale da wata dariyar mugunta ta fada a fili kamar mai magana da wani

“Hoo, ai ko zaku tafi tsirara sai ka yi min yanda nake so dan rainin hankali.”

Sannan ta kirawo shi ta yi masa godiya. Ta yiwa wanda ta turawa kudin waya don ya kawo mata waya wadda kudinta 102k ne ya hado mata da canjin kuma ya karbi wayarta wadda babu abinda tayi ya sayar mata.

Haka ya wuni a office yana tufka da warwara domin gobe Juma’a kuma goben ya kamata ya je Zariya amma baya son batawa Fatima rai yace ya fasa, sai faman bitar kalmomin da zai lallasheta da su yake yi saboda yanzu har wani tsoron bacin

ranta yake yi. Idan yace zai je gobe to gaskiya bashi da isassun kudi gara ya bari watakila zuwa Lahadi ya samu.

Ga Jamila kuma da yake ta tunanin yanda zai yi ya gaya mata ba zai iya bata kudin event center ba, domin itama gobene tace za a tura musu kudin.

Sai bayan la’asar ya shirya zai fito daga office ya tafi gida, har ya dauko jakarsa ya tuna gara ya kirawo Fatima ya tsarata tun yanzu don ta san ba zai zo gobe ba. Domin idan ya je gida so yake ya mayar da hankalinsa wajen lallaba Jamila, tunda duk inda yake jin zai sami kudi ya buga amma bai samu ba.

Ba tare da wata damuwa ba Fatima ta yarda yayi zamansa gobe, in ya so kamar yanda ya fada ranar Lahadi ya zo. Don haka abubuwa sun masa sauki, ya nufi gida yana tunanin yanda zai yi da Jamila.

—

Sai da ya gama cin abincin dare sannan ta sameshi a falon sama, yana zaune a kan kujerar zaman mutum uku rike da remote yana kallo. Ta karasa ta zauna a jikinsa tana murmushi

‘Sannu da zuwa.’

Ya amsa yana dubanta

‘Yauwa.’

Ta mika masa 'yar karamar takardar dake hannunta tana fadin

‘Ga account din me event center sai ka tura mata 120k din yau zuwa gobe.’

Ya sa hannu ya karbi takardar yana yake

'Ummm! Kin san ma duk na kashe kudin.’

Tayi gajeran murmushi

‘Ai kuwa dai kai ake jira.’

Ya dan kawar da kai yayinda ya ajiye takardar a gafensa, tayi shiru tana binsa da kallo tana sauraron abinda zai ce. Ya kalleta suka hada ido ya kawar da kansa ya sake bata rai sannan yace

‘Kin gane ko? Gaskiya hakura za ayi da event center din nan, kuyi taron nan a gida don gaskiya yanzu ko dubu ashirin babu a hannuna.’

Nan da nan ta tsuke fuska, ta muskuta ta gyara zama ta yanda zata dinga kallon fuskarsa ta dafe kirji tace

‘Ban gane me kake nufi ba kayi min bayani.’

Cikin yanayin na ko-in-kula yace

‘Kina dai kallon yanda na kashe kudi, tun kafin ki haihu ake abu daya. Dama wasu kudi na sa rai zan samu kuma zuwa yanzu basu shigo ba, wanda zai turo min kudin ma baya kasar.’

Ta sake gyara zama ta galla masa harara, cikin dacin rai tace

‘Amma dai wulakanci ka shirya yi min ko? Ya za ayi don tsabar wulakanci saboda ka nunawa duniya ban isa ba shine zakace baka da kudi. Da can ka san baka da kudin ka sa nayi magana da mutane ana son ayi booking hall sun hana saboda ni kuma yanzu kace baka da kudi.’

Shima ya fara hasala ya dubeta ta gefen ido yace

‘To bani da shi satowa zanyi na baki, shi sunan ce miki akayi idan ba a yi a event center ba an sabi Allah ne?’

Hawaye ya fara bin idonta saboda bacin rai, har wani hayaki take ji yana tasowa daga kirjinta, tace

‘Bana son wulakanci Mukhtar, bana son wulakanci! Ka bani kudin nan na sallami mutane. Na riga na gama gayawa mutane za ayi taro a event center amma kace min ga zance ga magana?’

‘To yanzu ya kike so nayi miki? Na gaya miki bani da kudi. Duk ma wanda kika gayawa ki koma ki gaya musu a nan za ayi, ba shi ke nan ba ai dai an yi suna ko?’

Ta share hawaye tare da zuke majinar da take neman fito mata daga hanci yayinda shi kuma ya mayar da hankali a kan kallon TV din da yake yi. Kallonsa kawai take tana hawaye ta ma rasa me zata ce. Da kyar ta bude baki cikin shesshekar kuka tace

‘Da can me yasa ka sa min rai ka san ba zaka biya min ba, idan kana so ai ko bashi zaka ciyo ka bayar amma don wulakanci kake wannan maganar.’

Da mamaki ya juyo ya kalleta

‘Bashi? Saboda sunan zan ciwo bashi? Lallai baki da hankali.’

Ta dan ja baya da mamaki tace

‘Oh! Bani ma da hankali ashe ko? Da yake nice nayi alkawarin na saba ai dole kace bani da hankali.’

Tayi kwafa ta tashi ta fice daga falon cikin sauri tana tafiya kamar zata kifa. Dakin kasa ta dawo inda a nan take kwana tunda ta haihu, ta fada kan gadon ta rushe da kuka. Bata jima da shiga ba Inna ta shigo da goyon baby a bayanta ta karasa ta taba kafar Jamilan tace

‘Ki tashi ki ci abinci Jamila , ga tuwo can na sauke kije ki kai masa nasa kema na kawo miki ki ci dare yana yi.’

Tana juyowa suka hada ido da Inna ta sake rushewa da Kuka, da hanzari Inna ta matsa ta zauna a kusa da ita ta dafata

‘Subhanallah! Me ya faru kuma wannan kuka haka kamar wadda aka yiwa mutuwa.’

Nan ta gayawa Inna abinda ya faru. Tana rufe bakinta Inna ta dauke hannunta da ta dafata dashi tana mata kallon mamaki tace

‘Au! Yanzu wannan shine dalilin da yasa kike wannan kukan. Naga dai ba sunan aka fasa ba, gidanki ma gashinan ai ya fi event center din kyau.’

Cikin shasshekar kuka tace

‘Inna Wannan ai wulakanci ne yanzu me yake so na gaya mutanen da na cewa za ayi suna a event center?’

‘Sai kice musu an fasa su taho gidanki, idan ba zaki iya ba ki bani ni na gaya musu.’

Haka Inna tayi ta lallabata tana bata hakuri sannan daga baya taci tuwon, amma na Mukhtar cewa tayi bazata kai masa ba. Dole Inna ta tura Nurain ya kai flask din tuwo ya dawo ya dauki na miya sannan ta bashi plate da cokali ya kai.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA HUDU.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA BIYAR

25

Tun daga wannan lokacin Jamila ta daina kula Mukhtar, hasali ma tun ranar alhamis din da ya sanar da ita ba zai biya kudin event center ba har kawo yau ranar Lahadi bai sake ganinta ba. Saboda Inna tana gida ya daina shiga inda take don mafi yawan in lokuta suna tare, ita kuma bata sake nemansa ba.

Tun safe da ya tashi yake shirin tafiya Zariya wajen Fatima, domin a yanda yake ji ba zai iya wuce yau bai je ya ganta ba. Sai da ya gama shiryawa tsaf ya sa kayansa sannan aka kirawo shi daga office, akwai report na wani aiki da office din suka yi ana so ya je yanzu da report din a kai gidan gwamnati.

Babu yanda ya iya don haka ya dauko computer dinsa ya kunna, akwai teburinsa na karatu a falon saman wanda yake daidai kusa da kofar dakinsa. Nan kan teburin ya zauna ya fara aiki don bai ma gama rubuta Report din ba.

Ita kuwa Jamila tana dakinta na sama, zuwa yanzu duk wanda ta gayawa suna ta kirawo su ta sanar da su an fasa don haka babu taro. Ta kudire a ranta ta fasa yin taron tunda yayi mata haka.

A kwance take yayinda baby Halimatu take bacci a gefenta wayarta tayi kara, tana dagawa taga Aminu, wato kanin Mukhtar. Bayan sun gaisa yace

‘Ina falon kasa, megadi yace min kuna nan amma naji gidan shiru shi kuma Yaya na kirawo shi wayarsa busy. Kice masa Baba ne ya aikoni.’

‘Ayya, duka muna sama. Inna ma yanzu ta fita ni da baby ka ganmu bacci muke. Bari na turo maka shi.’

Ta ajiye wayar ya tashi domin ta kirawo shi, ta san dai ba zai wuce dakinsa ba tunda bata ji fitar motarsa ba. Akwai kofa a cikin dakinta wadda zata kaita dakinsa don haka ta nan ta bi, babu kowa a dakin sai dai ta jiyo motsinsa a teburin karatunsa da alama waya yake ko kuma wani abun ya kunna a computer yake saurara.

A hankali ta karasa bakin kofar ta riga ta saita fuskarta a fushi don sakon kawai zata gaya masa ta fita ba wai ta huce bane. Tana matsowa zata tura kofar wadda take a bude kadan ta jiyo maganganunsa a waya yana yi cikin nishadi

“Haba Baby na, ai kin san dole ne nazo na ganki tunda ranar Juma’a ban zo ba. Ba zan iya jure rashin jinki da ganinki ba shi yasa na turo miki kudi kika sayi wayar nan da gaggawawa.”

Ya dan yi shiru yana sauraro

“Eh mana, ai yau dole na zo idan ba so kike zuciyata ta daina aiki ba.”

“Ah ke da kike jira nazo muyi selfie a sabuwar waya?”

Bata san me aka gaya masa ba ya kyalkyale da dariya

“Kina ji ko Baby, bari nayi sauri na gama aikin nan ko na samu na taho, kin san fa Zariya da nisa duk da dai garin masoyi baya nisa.”

Cikin zafin nama ta banko kofar ta shigo ta tsaya a gafen teburin wanda yake manne da jikin bango, hannunta yana kan kwankwasonta tana jijjiga kafa tana masa kallo me cike da masifa.

Yayi wuf ya katse wayar, bai zata zata shigo ta nan a yanzu ba musamman da yake ta kwana biyu rabonta da sashin nasa.

A tsiwace tace

‘Wace 'yar iskar karuwar kake magana da ita? Wato dama ba kudine baka da shi ba kwashewa kayi ka bawa karuwa kawai saboda ta buda maka tsakanin cinyoyinta ko? Shi yasa ka kashe min…'

Ya mike tsaye a fusace ya nunata da wayar da take hannunsa kirar Samsung mai tsadar yace

‘Ke wai me yake damun kanki ne? S…'

A fusace ta fizge wayar hannunsa ta maka ta da bangon da yake bayanta iya karfinta, ya dora hannusa a ka ya bude baki a dai-dai lokacin da wayar wadda ko

batirinta ba a cirewa ta tarwatse tayi dai-dai. Cikin zafin nama ta cakuma kwalar rigarsa tana magana tana huci

‘Ni zaka kawowa bariki har cikin gida? To wallahi baka is….’

Ya fizge hannunta daga wuyansa wanda yayi sanadiyyar zubewar maballan rigarsa a kasa, ya daga hannu ya kwada mata mari . Ta saki kara tare da dafe kuncinta, yayinda Nana wadda take bacci a kan kafet din falon ta farka da kuka a gigice. Nan da nan Nurain wanda ya buya a bayan kujera tunda suka fara fadan ya fito ya rungumeta yana kokarin toshe mata baki.

Mukhtar ya juya da sauri ya nufi su Nana. Iya karfinta ta sa hannu ta fincikoshi har ya doke kujerar da ya tashi

‘Ni zaka bari a tsaye, ka cuceni ka mareni sannan ka barni a tsaye? Wallahi baka isa ba Mukhtar kayi kadan. Mazinaci, macuci algungumi kawai.’

Ya daga hannu zai sake marinta cikin zafin mama ta rage tsawo ta sa karfi ta bangajeshi yayi baya kamar zai fadi, cikin karaji tace

‘Kai ka isa ka sake marina? Wallahi wanda kayi ma ka ci bashi kuma da kai da duk wata karuwa da kake nema sai na mayar daku kalar kwatance a garin nan.’

Ya rasa ma me zai ce mata, da kyar ya samu ya tsaya. Ta juya a fusace zata fice daga dakin sai kuma ta yiwo taku biyu baya ta kaiwa computer dinsa cafka, cikin zafin nama ya tureta gefe ta tafi ta fadi a kusa da kujerar zaman mutum biyu tana huci.

A dai-dai lokacin Aminu ya shigo Nuraini yana biye da shi yana buya a bayansa; wanda Nurain ne yaja Nanan suka fice don su kirawo Inna suna saukowa suka ci karo da Aminu don haka Nurain ya ja shi sama yayinda Nana ta buya a bayan kujera tace ita ba zata koma ba.

Ta taso da hanzari daga inda take zube ta nufo Mukhtar din da sauri, Aminu ya kara hanzari ya riketa domin ya ga lokacin da Mukhtar din ya tureta. Yayi wuf ya cafke hannunta yace

‘Haba Anti yi hakuri mana.’

Sai a lokacin ta gane an shigo wajen, tana hada ido da Aminun kuma ta fisge hannunta ta hada duka hannuwa biyun ta dora a ka ta zube kasa tana faman rusar kuka.

Ya karasa kusa da Mukhtar din yana fadin

‘Yaya lafiya kuwa? Kun firgita yara kuna ta hayaniya. Kayi hakuri mana Yaya.’

Ya kalli Aminun da jajayen idonsa yayi kwafa sannan yace

‘Menene?’

‘Baba ne ya aiko ni na kawo rago, gashi can har maigadi ya daureshi.’

Dama haka Baba yake musu, idan an yi maka haihuwa ko ka sayi rago to shima sai ya bada nashi saboda yana da dabbobi da ake masa kiwo a kauye.

Bai ce komai ba ya wuce Aminun ya tsuguna a gaban wayarsa wadda ta fashe, ya bi wajen da kallon takaici. Aminu ya karaso ya tsaya a kansa ya leka abinda yake dubawa.

‘Subhanallah. Fashewa wayar tayi Yaya.’

Ya mike tsaye ba tare da ya dauki komai a wayar ba ya bi ta gefen Aminun yana fadin

‘Ka cewa Baba nagode, zan zo da daddare.’

Ya tattara computer dinsa da karamar wayarsa ya shige dakin, yana shiga ya sakawa kofar mukulli ya karasa ya kulle wadda ta shigo daga dakin Jamilan ya ajiye computer a kan gado ya zauna ya saka tafukan hannuwansa ya rufe fuskarsa zuciyarsa tana suya. Gaba daya kwakwalwarsa nema take ta daina aiki, kansa ya cunkushe ya ma manta da cewa ana jiransa me ya kai report office za a kaiwa gwamna.

Shi kuwa Aminu yana saukowa Nana ta makale a jikinsa ta sa kuka sai ya kaita wajen hajiya, ya dauketa ya sakata a kafada. A dai-dai nan Inna ta shigo da sallamarta bayan ya gaisheta ya gaya mata daga gidan su Mukhtar yake sako ya kawo. Ta miko hannu zata karbi Nana tana fadin

‘Yaki nan gotai gotai dake Uwar masu gida ake daukanki.’

Ta kara kankameshi, ya dubi Inna yace

‘Rigima take ji wajen Hajiya zan kaisu.’

Yayi mata sallama ya fice da yaran.

Inna Bata hawa dakin Jamila na sama don haka da bata ganta a kasa ba sai ta cigaba da harkonkinta ta san itama idan ta gama abinda takeyi zata sauki.

…

Aminu yana shiga gida ya wuce falon Baba inda yayi sa’a ya tarar da Hajiyan ma a can. Ya mika mata Nana wadda ta riga ta fara bacci, ta rugumeta yayinda ita kuma Nanan ta bude kumburarrun idanuwanta ta kalli fuskar hajiya tace

‘Hajiya.’

‘Na’am kawata, kuka kika yi ko?’

Ta daga kai alamar e sannan tace

‘Bazan koma gun Mommy ba a wajenki zan dinga kwana ko Baba Aminu ya kai ni wajen Mama.’

Hajiya ta kula da baccin da yake fizgar Nanan don haka ta rungumeta tana fadin

‘Shikenan a nan zamuyi zaman mu kawata.’

Baba ya dubi Amin wanda yake zaune a gaba Baban yana ta muzurai yace

‘Ina Jamilan?’

'Tana sama ai inaga dai bacci sukeyi don tun fitarka basu sauko ba.’

Kafin ta rufe bakinta ya shige cikin corridor din da zai kaishi saman. Ta karasa ta zauna a kujerar da take kusa da wadda Aminu ya zauna tana dubansa tace

‘Lafiya dai ko? Na ga kamar da matsala.’

Yayi murmushin yake yace

‘Lafiya kalau in sha Allah. Maganin da ake bawa Nana aka ce a karbo don a cigaba da bata.’

Ta yamutsa fuska ta jingina da bayan kujerar da take kai

‘Ni dai wallahi da ma zaku kyaleta da maganin nan, maganin mura ne kuma ta daina murar yarinyarda kullum hancinta yake a bushe. Tunda na zo gidan nan nace a daina bata ta warke uwar tace min wai haka likita yace a bata na sati biyu don haka dole sai an bata. Murar yaro wallahi ba wani abu bace idan an barta kwana biyu warkewa takeyi gara ma ka bawa yaro zuma kawai. Don Allah ku barta da maganin nan wallahi ba wata mura.’

Cikin yanayi na mamaki Aminu ya jijjiga kai yace

‘In Sha Allah zan gayawa Hajiyan don ita bata ma san na mura bane ta zata na zazzabi ne, na san ita ma bazata bata ba.’

‘Yauwa ko kai fa.’

Kafin suce wani abu suka jiyo amon muryar Mukhtar daga sama ga dukkan alamu fada yakeyi. Suka dan kasa kunne, har yanzu hayaniyarsa suke jiyowa domin da ya hau a kwance ya sameta a kan gadon kuma tunda ya shiga dakin yake tambayarta ina maganin da take bawa Nana tayi masa shiru, duk wannan hayaniyar da yakeyi sau daya ta kalleshi ta koma ta cigaba da kwanciyarta taki ce masa komai.

Da gudu Aminu ya mike ya haye saman yana tsoron kada ya sake kai mata duka, a take Inna tabi bayansa don duk wanda yaji muryar Mukhtar din ya san fada yake.

A tsaye yake a gaban gadon da take kwance, yana jin shigarsu ya juyo ya dube su idanunsa sunyi ja wur ya hada hannuwansa biyu ya shafi kansa da su yana fesar da iska. Inna ta ture Aminu ta karasa cikin dakin ta doki kafar Jamilan ranta a bace tace

‘Wai wane irin iskanci ne wannan ba dake yake magana ba kina kwance kina ji.’

Ta mayar da dubanta ga Mukhtar din tace

‘Me yake faruwa ne?’

‘Magani zata bani wanda take bawa Nana shine nake tambayarta tana jina taki magana.’

Inna ta hararetа

‘Ikon Allah kefa kika ce likitan yace sai an bata na sati biyu, idan ma da wani abun ba sai ki bashi maganin ba in ya so sai ki cigaba da fushin naki tunda ke bakya jin magana.’

Tuni hawaye suka wanke mata fuska saboda takaicin maganar Inna, bata so Inna tayi wannan maganar ba don ba tayi niyyar bada maganin ba. Saboda yanda Nana take hanata bacci shi yasa tun cikinta yana da wata uku da ta kaisu asibiti suna mura aka basu Benelyn taga ya sa Nana bacci don haka tun lokacin kullum da rana sai ta bata don tayi bacci ta barta ta huta.

Muryar Inna ce ta katse mata tunanin

‘Inaga dai tafiya zanyi na bar miki gidan nan Jamila tunda ba mijinki ba nima ban isa nayi magana ki ji ba. Kwana nawa da yin abun nan na baki hakuri, kince kin hakura da sunan amma baki daina wulakanci ba?’

Ta dubi Mukhtar tace

‘Muje Abban Nurain na duba maka maganin ina ga yana kicin ai.’

Ta wuce gaba Mukhtar da Aminu suka bita a baya. Suna fita Jamila ta tashi ta dora hannunta a ka ta fasa kuka me gunji saboda takaici, ji take kamar zuciyarta zata fito ta bakinta. Ya akayi aka san tana bawa Nana magani? Ina yaran ma suke?

Sukuwa su Mukhtar suna shiga kicin Inna ta hau bude durowoyin jikin bango na sama don a nan ne take tunanin zata sami maganin duk da bata da tabbas, ta dai kula kamar daga kicin Jamila take dauko maganin. Sai da ta bude durowa uku, a ta hudun ta samu. Durowar ma gaba daya a cike take da kwalaben magani.

‘Yauwa gashi nan.’

Kafin ta dauko Aminu ya wucesu ya mika hannu ya dauko kwalabe biyu da suke gaba, ya duba yaga Benilyn syrup for children, kwalba daya an sha kamar Rabi dayar kuma sabo ne ko budewa ba ayi ba amma an cire kwalin. Ya zura hannu yana juya ragowar kwalaben wadanda zasu kai kamar guda goma, suma duka na Benilyn din ne sai dai duka babu komai komai a ciki an shanye. Ba tare da yace komai ba ya zaro wayarsa ya dauki hoton durowar ya wuce ta tsakanin Inna da Mukhtar din ya fice ya barsu a nan.

Inna ta bi bayansa da kallo sannan ta juyo ta dubi Mukhtar din tace

‘Wai me yake faruwa ne?’

Ya shafa kansa ya fesar da iska ya kalleta da idanuwansa wadanda suka kara ja da kyar ya nemo muryarsa yace

‘Maganin da yan kwaya suke sha shi take bawa Nana, gashi nan duk wadannan kwalaben a cikin Nana ya kare.’

Ya share kwallar da ta taru a kwarmin idonasa; ya akayi bai gane ba? Yana kallo Nana tana yawan bacci yanzu amma bai kawo komai, idan yacewa Jamila Nana fa da bata bacci sai tace ‘kyaleta aka yi.’

Gaba daya kansa ya cushe , zuciyarsa nema take ta daina aiki, tausayin Nana yake ji yana tunanin tashin hankalin da Baba zai yi masa.

Inna ta katse masa tunani

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun. Wannan wane irin rashin hankali ne?’

Ya raba ta gefenta ya wuce ya nufi corridor din da zata kai shi saman gidan, yana taka matattakala ta daya yaji sallamar Mustafa don haka dole ya dawo ya san daga office ne.

Sai a lokacin ya tuna da report din da ya kamata ya kai office, ya bar computer din da karamar wayar tasa a mota don haka ya san jinsa akayi shiru aka turo Mustafan.

Kafin ya karasa cikin falon Mustafan yace

‘Mutumina ya haka ne DG sai neman ka yake, wayarka a kashe dayar kuma baka dauka?’

Ya sa tafukan hannunsa ya rufe fuskarsa ya ce

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun!’

Mustafa ya karaso ya dafa kafadarsa

‘Lafiya dai, ya naganka duk a firgice.’

Ya kama hannun Mustafan ya sauke daga kafadarsa yana fadin

‘Muje mota, aikin yana can.’

Suka fice suka bar Inna wadda take tsaye a kofar kicin ta kasa motsi saboda tsoron abinda Jamilan ta aikata.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA BIYAR

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA SHIDA

Suna fita Inna ta wuce sama wajen Jamila, tana nan a kwance a inda suka barta tana faman share hawaye. Ta karasa ta zauna a gefen gadon dai-dai inda kafar Jamilan take ta dubeta duba na takaici tace

‘Don Allah Jamila wacce irin barna kika aikata haka? Hauka kike so ki saka yarinyar ko kuwa so kike ki mayar da ita ‘yar maye?’

Ta tashi zaune ta dora hannu a ka

‘Ni wallahi Inna ban sani ba, ki na kallon dai yanda yarinyar nan take da sa mutum wahala. Kuma likita ne ya basu maganin, da naga in ta sha tana yin bacci shine na cigaba da bata.’

Takaicin Inna ya karu

‘Ikon Allah! Yanzu ke har kina da bakin magana? To gara ma na gaya miki tun wuri yaro duka ko wanne da irin wahalarsa sai dai idan ba zaki haifa ba. Kika kasa cewa ubansu ya dauke yaransa amma?’

‘Inna wallahi na gaya masa sai dai kawai yace na yi hakuri, to ya zan yi?’

‘Ai kin yi yanda yayi miki dadi a rai. Bari na jira ya zo naga matakin da zai dauka don ba lallai ya iya zama dake ba. In ya so sai mu wuce na mika ki hannun iyayenki kya yi musu bayani.’

Ta kara rushewa da kuka yayinda Inna ta fito ta barta a dakin. Kanta sai sarawa kawai yakeyi gashi ta kasa daina hawaye, ya hanata suna ya turawa budurwa kudin taron kuma yanzu ga wannan maganar ta fito.

Haka tayi ta kwance har sai da Baby Halima ta gaji da kwanciya ta sa kuka sannan ta tashi ta dauki baby.

.....

Inda Aminu ya bar Baba da Hajiya a nan ya samesu. Yana shiga ya karasa ya mikawa Baba kwalaben maganin, itama Hajiya ta matso don ta gani. Bude baki Baba yayi yabi kwalaben da kallo yana fadin

‘Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun.’

Aminu ya zaro wayarsa ya budo hoton da ya dauka ya mikawa Baba yana fadin

‘Ka ga durowar da take ajiye maganin Baba, wadannan kwalaben duk na benilyn din ne. Allah ne kawai ya san tun yaushe take bawa Nana wannan maganin mayen.’

Tuni hawaye suka wanke fuskar Hajiya yayinda Baba ya dubi Aminun yace

‘Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun, ai yanzu dole a nema mata taimako.’

Hajiya tace

‘Yarinyar nan bata yi mana adalci ba, da ita da Mukhtar din da sun sani sun dawo min da yaran gaba daya.’

A nan baba ya dauki wayarsa ya kirawo Dr. Jibrin wanda da ne a wajen kanin Baban kuma likitan yara ne a asibitin Murtala. A take ya ce zai iso gidan nan da minti talatin.

Yana isowa bayan yaji bayanin Baba yace babu wani abu tunda shekarunta hudu kawai, amma dai sai kunyi hakuri da ita saboda zata yi rigima da yawa. Kuma yace a dinga yawan bata ruwa ana bata abubuwa masu zaki wadanda zasu sa ta sami karfi a jikinta. Sannan yace akwai allura da zai yi mata ta kwana uku, kullum da

daddare zai dinga zuwa yana yi mata. Ya kwantar musu da hankali ya nuna musu ba wani abu bane tunda an gane da wuri.

Haka Hajiya daga baya sai da ta saka aka samo ruwan zamzam wanda kullum take tofa mata fatiha kafa bakwai tana bata tana sha.

.....

Bayan sun fito da Mustafa haka ya dan jirashi ya karasa aikin ya tura computer din Mustafan, yayi masa bayanin idan ya koma office din ya gaya musu an samu accident ne a gidansa. Mustafan ya dubeshi yace

‘Amman dai kada ka koma gidan yanzu don kar kuyi bataciyya, gara a bi abun a hankali. Gara ma kawai ka wuce gidan Baba, nima da na kai takardun nan zan zo na sameka please, just calm down small.’

‘Kada ka damu abokina, ai dole na wuce can din don dole naje na bawa Baba da Hajiya hakuri.’

Haka suka yi sallama Mustafa ya tura motarsa ya tafi ya bar Mukhtar din a cikin tasa motar da dama a waje ya ajiyeta lokacin da suka dawo karbar magani.

Kansa ya kulle, ya shiga matsananciyar damuwa. To yanzu ma ina za shi? Gidansa dai baya son shiga don yana ji kamar idan ya shiga komai zai iya faruwa tsakaninsa da Jamila. Baya son kuma yaje gidan Baba don bai san ma da don idon da zai kalli Baban ba, ya san ma Baba ba zai saurareshi ba a halin ya zu.

Da ya rasa mafita sai kawai ya kifa kansa a kan steering din motar ya rufe idanuwansa. Bai san tsawon lokacin da ya dauka a haka ba, har sai da ya gaji ya daga kansa ya lalubi karamar wayarsa ya duba lokaci.

Karfe uku da minti goma ya gani, da mamaki yace

‘Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun!’

Nan take ya tuna baiyi sallar azahar ba, kafin ya yanke shawara kuma cikinsa ya bada kugi alamar yunwa yake ji.

Baya son kula kowa a cikin gidan don haka sai kawai ya tayar da mota ya zagaya bayan layinsu wani restaurant ya sayi abinci ya ci. Kafin ya gama uku da Rabi ta gota don haka masallacin layinsu ya dawo yayi sallar azahar ya jira aka yi la’asar sannan ya fito da niyyar tafiya gida.

Tun kafin a sallame sallar la’asar ya tuna Fatima tana can tana jiransa a Zariya ko waya bai samu yayi mata ba. Yana idar da Sallah ya sake duba lokaci karfe hudu da minti biyar; ya jijjiga kai don ya san babu yanda za ayi ya tafi Zariya yanzu. Gashi wayar ma da yayi saving lambarta Jamila ta fasa, duk lambobin da suke kan karamar wayarsa babu suna yayi saving.

Da kyar ya lalubo lambar Fatima ya kirawo ta, tana dauka tace

‘Ka bar ni da zulumi, Allah ya sa dai ba accident kayi ba don tun dazu ma nake kiran layinka a kashe.’

A hankali yake magana yace

‘Ban ma taho ba, ina gida matsala aka samu Nana ta gamu da minor accident. Gashi an sace wayar tawa garin na kaita asibiti, sai yanzu na sami kaina.’

Ta yatsina fuska tace

‘Allah sarki, Allah ya sauwake.’

Suka dan taba hira har zasuyi sallama yace

‘Gobe in sha Allah da wuri zan fito zaki ganni.’

‘Allah ya kai mu. Allah ya sa dai ba gidan jiya za a koma ba!’

Ya jijjiga kai cikin damuwa, baya son damuwar Fatima don yanzu in ya bata mata rai sai kawai ya ji zuciyarsa tayi kunci. Kwana biyun nan da bai je ya ganta ba ji yake kamar a wuta yake kwana. Yace

‘Haba Baby, kema kin san ba za ayi haka ba. Da kin barni ma ai da yanzu kina gida na ko?’

‘To babu damuwa, goben mayi magana.’

Sukayi sallama, ya ajiye waya ya sake kifa kansa a kan sitiyari. Mintuna kadan ya tuna a bakin masallaci yake don haka ya san yanzu za a fara tambayarsa ko lafiya. Don haka ya kunna motar ya nufi gidan.

A falon kasa ya sami Inna da goyon baby a bayanta, sallama kawai yayi mata ya wuce ya nufi hawa sama ba tare da ya ce mata komai ba. Ta riga ta san ransa a bace yake don haka itama din ta kyaleshi.

Yana shiga dakinsa ya fada wanka, bayan ya fito ya tsaya a gaban wardrobe domin ya dauki kayan sawa. Ya zaro kayan a hankali, kafin ya ajiye kayan a kan gadon ya tuna ai harda kayan su Nurain Baba yace a kai kuma ba’a kai ba. Don haka yana saka kayansa ya wuce daki Jamila.

Kofar a bude take don haka ya tura kofar ya shiga ba tare da sallama ba. Tana nan kwance a gefen gadon kamar mara lafiya, bai ko kalli inda take ba ya wuce ya nufi

wardrobe. Akwai akwatinsu wanda suka zo dashi daga gidan Hajiya shi ya sauke a saman wardrobe din ya kwashe duka kayansu, ya tura akwatin ya fice.

Yana ficewa ta gyara kwanciya ta kara fashewa da kuka; saboda yanda ta ji babu dadi da ta gane ya kwashe yaransa.

Yana fita ya wuce gidansu, abinda ya zata shine ya faru. Domin yana shiga tun kafin ma ya hau saman Baba Baban ya aiko a kirawo shi. Tun kafin ya tsuguna a gaban Baban ya fara fada, sosai ya kare masa fada yace

‘Ka kori uwarsu kuma ka kasa kula da amanarsu, kana cikin gidan amma sama da wata shida ana bawa yarinyar kayan maye wai baka sani ba saboda sakarci.’

Yana gama fadan kuma yace ya tashi ya fice masa daga gida. Haka ya fito ya kama tuki yana tafiya kamar ba zai je ba, domin maganganun baba sun sa shima ya fara zargin kansa.

Bai taba jin takaicin rabuwa da Safiyya ba sai yau, lallai ya san da tana nan da haka bata faru ba.

Haka har ya isa gidan ya shige dakinsa ya kwanta domin yanzu idan ba kwanciyar na bai san me zai yi ba. Duk wani abu da zai debe masa kewa a kan wayarsa ne kuma ga shi Jamila ta fasa wayar, a halin yanzu ma kuma bashi da kudin da zai sake sayen wata wayar sai dai ko zuwa ayi albashi sai ya sayi wata Yar matsakaiciya kafin ya sami kudin.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA SHIDA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA ASHIRIN DA BAKWAI

27

Zuwa yanzu kitso ya kankama sosai a wajen Safiyya, domin yanzu kusan duk sati sai ta sami masu son kitso; ko su zo ko taje tayi musu.

Tunda ta bude account sai ya zama da zarar ta gama kitso take ware dan wani abu ta bawa Umma sannan ta dauki na kashewa ta bawa Sabir sauran ya kai mata banki. Duk lokacin da ya kai mata kudi idan taga alert sai ta ji kamar ta shide saboda dadi. Ranar da kudin nan suka kai dubu ashirin Allah ne kadai ya san dadin da ta ji.

Washegarin ranar kuwa ta saka Sabir a gaba ya rakata kasuwar Sabon Gari ta siyo hair dryer da kayan wankin kai; saboda ta riga ta yanke shawara duk inda take kitso musamman da yake ana kiranta ne don yara to zata gaya musu har wankin kan yaran zata dinga yi sai mutum ya biya kudi. Sai ta mayar da shi kitso da wankin Kai N800, kitso kawai Kuma N400, na manya kuma N500. Haka ta cigaba da sana’arta tana tara kudin ta.

Sosai Umma ta rage duk wasu abubuwa da take yi mata, duk da har yanzu tana yawan yi mata maganar aure. Tana nuna mata ba zata zauna mata a gida ta ki aure ba saboda tana samun kudi. Haka dai ta cigaba da lallaba Umma don a zauna lafiya, domin a halin yanzu bata da wani manemi ma a kasa.

Mazan ma gaba daya tsoronsu takeyi; tun farkon da ta fara kitso sau biyu tana haduwa da masu sonta.

Kowannensu kamar mutumin kirki amma duka suna zuwa suka nuna mata ba aure zasuyi ba lalata ce ta kawo su, shi dayan ma har bayani yayi mata wai tunda ta taba aure ba wani abu bane don babu wanda zai gane. Haka ta sallamesu duka kuma ta yiwa kanta alkawarin ba zata sake kula wani namiji ba.

Shi kuwa Mukhtar a yanzu ma ji take ko ya dawo ba zata saurare shi ba. Damuwarta daya yaranta wadanda har yanzu duk lokacin da ta tuna su sai tayi kuka, ana kawo su wajenta lokaci zuwa lokaci tunda yanzu gashi an gaya mata sun koma wajen Hajiya. Tana da damar zuwa ta gansu amma tayi wa kanta alkawarin ba zata sake zuwa gidan ba don kada ma su zata ko zawarcin Mukhtar takeyi.

……..

Ita da Sabir, da Hamida ne kawai a gidan don Umma ta tafi biki gidan kawarta. Suna nan zaune suka ji sallama, nan yaran suka shigo da gudu. Yaran Yaya Habibu ne kananan wato Ummi da Halifa wadanda amaryarsa ta haifa masa tare da uwarsu Anti Farida; Yaya Habibu matansa biyu Anti Salma Uwargida mai yara biyar sai kuma ita Anti Farida wadda dai-dai lokacin auren Safiyya ya aureta. Uwargida Anti Salam bata da son mutane kuma bata so a rabi mijinta don haka dole danginsa suke baya-baya da shi babu mai son zuwa gidansa, ita ma kuma sai yayi da gaske take shiga danginsa, don ko yaranta bata bari su je yanda ya kamata. Sai da ya auro Anti Farida wadda ita kuma mace ce mai son mutane sannan danginsa suka fara sakewa a gidansa. Ko yanzu ma ita da yaran zuwa suka yi su gaida Hajiya da yake Alhamis ce babu islamiyya, kuma kamar yanda ta saba sai da ta rikowa Hajiya sabulu da turare; tunda tana koyarwa a makarantar kudi da albashinta take wannan hidimar.

Suna shiga suka zauna wajen su Safiyya aka hau hira. Daga baya kuma Safiyya ta yi musu kitso ita da Ummi. Suna cikin hira Anti Farida tace

‘Ni Safiyya ki dauko kwalinki na diploma mana, ko yayanki ai sai ya samo miki aiki ko da a private school ne. Albashin dai babu yawa tunda kinga nima dubu goma sha tara suke bani inda nake koyarwa amma Ina laifi.’

Hamida tace

‘Kuma wallahi hakane Yaya Safiyya, ga unguwar nan da makarnatun kala kala.’

Safiyyan ta dubi Anti Farida tace

‘To matar Yaya ki wuce min gaba, Allah ya sa Umma ta bari don kin ga yanzu ma gani take kamar kudin kitson nan ne yake hana ni aure.’

‘Bari na sami Yayan naki shi zance yayiwa Umman magana, ai aure nufin Allah ne idan bai zo ba kuma a haka ake so mutum ya kare yana rabe-rabe.’

Haka suka karasa hirarrakinsu sai wajen magriba da Umman ta dawo su Farida sukayi sallama suka kama hanya.

Sai da Farida tayi magana sannan ma Safiyya ta tuna da cewa tayi diploma, a da kuma gani take HND bai kai ya samar mata aiki ba tunda tana kallon yanda masu degree ma aikin yake musu wahala. Amma kuma yanzu tabbas ta san za ta iya samun aiki a private school don haka da Yaya ya zo zata yi masa magana.

Washe garin ranar kuwa Yaya Habibu ya zo gidan da safe kafin ya tafi office, bayan ya gaisa da Umma shi da kanshi ya fara maganar aikin. Sai da ya gama Umma ta dubeshi rai a bace tace

‘Habibu wai me yasa kai baka son yarinyar nan tayi aure ne? Duk abinda zai sa ba za a kulata ba shi kake nuna mata. Kai da kanka ka san idan mace ta tara kudi mazan ma tsoronta sukeyi haka zata zauna ba zata yi auren ba?’

Yayi murmushi

‘Umma ba haka bane, kin ga zaman haka shima babu dadi sai ki ganta kullum cikin damuwa. Amma yanzu kinga tanata walwalarta, kuma auren ma in sha Allah yana nan tafe Umma.’

Ya kwalawa Safiyyan kira, kafin ta fito Umma ta tashi ta shige dakin. Sai da ya karbi takardun Safiyyan sannan ya gaya mata lallai ta dinga lallaba Umma sannan ya tafi.

Sati biyu da karbar takardun ya samo mata aikin kuwa, makarantar ma a kasa take zuwa daga gida. Nan da nan suka bata koyar da yara ‘yan primary 1 zuwa 3 computer science Kuma aka saka ta class teacher din primary 2.

Albashin dai ba wani mai yawa bane, dubu goma sha bakwai ne amma duk da haka ba karamin dadi ta ji ba. Ko babu komai ita kanta ta san tana cikin walwala gashi kasusuwan nan na wuyanta da ido zuru-zuru duk sun koma sannan kuma duk abinda take so yanzu tana iya siya; don ma tana yi a hankali don kada Umma ta zata wasu kudi take samu da yawa. Saboda ita Umma har yanzu ta dai rage tsangwamar tane saboda ko babu komai duk abinda ta nema zata saya mata, gashi duk Juma’a sai ta siyowa Umman kaza ko tsire duk su ci tare da su Sabir.

Amma wani lokacin har tausayi Umman take bata yanda taga tana so tayi aure. Gashi wani lokacin sai taga kamar Yaya hajiyayye tana kara zugata, don tana yawan cewa

‘Shi wannan yawon na kitso ai gara kiyi aure ki huta da shi.’

Haka dai Safiyya ta cigaba da gudanar da rayuwarta.

Tunda Mukhtar ya kwashe yaransa daga wajen Jamila sai kuma ya daina shiga harkarta, suka zama kowa rayuwarsa yake yi. Ita kuma Jamilan tana so ta kulashi amma tana tsoro saboda ta san itace mai laifi, kuma gashi sai wasu muzurai kawai yake mata da sun hadu, don haka itama sai ta ja jikinta.

Ranar da ta cika sati uku da haihuwa Inna ta hada kayanta, ta yiwa Jamila sallama Mukhtar ya dauketa domin ya kaita gida. Tana kallonsu ta san halin da suke ciki don haka har ya isa kofar gidanta babu abinda take masa sai bashi hakuri da kuma nasiha. Ya sauketa yayi mata goma ta arziki suka rabu kowa yana godiya.

Kwana biyu da tafiyar Inna Jamila duk ta shiga damuwa, daga ita sai Baby domin shi ko bi ta kansu baya yi.

Tana jinsa zai shigo haka kuma tana jinsa zai fita, yanda ta ajiye masa abincin a falonsa haka take gajiya ta dauke. Don haka yau ta yi niyyar dole ya saurareta, ta yarda tayi babban laifi amma ai ya kamata ayi mata afuwa ba don halinta ba.

Kamar yanda ya saba sai wajen goma na dare ya dawo, tana jin motsinsa har ya gama abinda yakeyi ya fito falon sama ya zauna ya kunna TV.

Sai da ta tattaro duk wata nutsuwa da take da ita, kayan bacci ne a jikinta amma sai ta dauki hijabi ta saka domin ta kula ko tsirara zata je ba zai saurareta ba gashi kuma bata yi arba’in ba.

Tun ranar da sukayi fada ya riga ya sakawa kofar dakinta wadda take shiga nashi dakin mukulli don haka sai da ta fito daga dakinta ta shiga ta falo.

Ko kallonta bai yi ba balle ya amsa sallamarta. Haka dai ta karasa ta zube a gabansa ta mika masa takarda da biro wanda ta shigo da shi, a fusace ya dubeta yace

‘Meye haka kuma? Ko Sabon hauka kika fara ko kuma kema shaye-shayen kika fara?'

Nan take hawaye ya fara bin idanuwanta, ta zube hannuwanta wanda suke rike da takardar a kan cinyarta ta bude baki cikin shessheka tace

‘Saki zaka rubuta min na tafi gidanmu.’

‘Mtsewwww!’

Yaja dogom tsaki sannan ya cigaba

‘An ki a sake ki din kin ji, ba zan sake ki ba sai ki je ki sake wani sabon hauka ko zaki dace.’

Cikin shassheka ta bashi amsa

‘Don Allah Mukhtar ka sake ni in tafi. Ya zanyi? Na san nayi laifi kuma nayi kuskure amma ko sauraro na ma baka yi balle na samu damar baka hakuri, wajen sati uku ana abu daya. Ya kake so nayi don Allah?’

A fusace yake kallonta

‘Oh, ashe ma kin san kin yi ba dai-dai ba kuma har kina da bakin bada hakuri? Ai na zata bakiyiwa kowa laifi ba.’

Ta dan matsa kusa dashi ta dafa cinyarsa da hannunta tana fitar da hawaye

‘Don Allah kayi hakuri, don Allah! Wallahi ba zan sake ba , kayi hakuri.’

Tsaki kawai yayi ya kawar da kai, da ta fuskanci kamar ba zai ce komai ba ta cigaba cikin sanyin murya

‘Don Allah kayi hakuri, ai Allah nace wanda shima muna masa laifi Kuma muna fatan ya yafe.’

Ta fuskanci ya fara saukowa don haka ta kara matsawa ta dan kwanta a kafadarsa, jimawa kadan tace

‘In sha Allah ba zan sake ba, duk wani abu ma da zai saka ka damuwa nayi maka alkawarin ba zan sake ba.’

Tabe baki yayi kawai ya kawar da kai, ta mayar da kanta ta kwantar a kafadarsa. Jimawa kadan yace

‘Ni in tambayeki ma.’

Ta dago ta dubi fuskarsa sannan ya cigaba

‘Nana kawai kike bawa benilyn din ko tare kuke sha ?’

Mamaki ya cikata, sai yanzu ta gane kallon da yake mata tunda abun ya faru . Ta dafe kirji cikin rawar murya tace

‘Haba Mukhtar! Ina shaye-shaye amma baka tana sani ba? Wallahi babu abinda nake sha, itama Nanan matsala aka samu kuma likita ne ya rubuta mata wannan maganin da farko katin ma yana wajenka zaka iya dubawa. In sha Allah kuma ba zan sake irin haka ba.’

Ta karasa tana sunkuyar da kai. Jijjiga kai kawai yayi yace

‘Hmnn?’

Jinta kawai yayi amma shi ya san sai ya sake saka mata ido sosai, domin daga baya ya fara tunanin ko ita ma tana shan benilyn din musamman saboda yanda ta zo tayi masa wannan haukan har ta fasa masa waya. Kuma ya san dole ya saka mata ido kada taje ta bawa Halima wani abun da zai mayar da ita ‘yar kwaya.

Haka a hankali har ya hakura suka sake, sai dai tana kula da yanda yake wani kaffa-kaffa da ita ya ki sakewa.

Babu yanda bata yi da shi ya dawo da su Nana ba amma ya ki. Daga karshe ma ce mata yayi ba zai kuma bata rikon dan da bata haifa ba, ko wanda ta haifa din ma kuma idan yaga babu hali zai kwashe yaransa don haka ta zama cikin shiri. Don haka ta hakura ta daina maganar su Nanan.

Tana son taje gidan ta bawa su Hajiya hakuri amma ta kasa, ga bukuwa a gidan an saka rana ta kasa zuwa murna. An kawo kayan auren Habiba Yar kishiyar Hajiya sannan kuma itama Bahijja Aminu ne zai aureta don haka aka hada aka sa rana daya. Kaf dangi kowa ya je ganin lefe ita kuwa ta kasa zuwa saboda kunya.

.....

Yau Juma'ah ce don haka tunda taga yana shirin tafiya office ta fara shiga damuwa, tana so ta tambayeshi Zariya zai je amma tana tsoron abinda zai ce mata don har yanzu lallabawa take yi. Bayan ya gama cin abincinsa yayi mata sallama ya fice.

Yana fita ta kirawo kaninta tace

'Don Allah ka bi min Mukhtar ko ka sa a bi min shi kawai ku gani hanyar Zariya yayi ko wani wajen ya nufa?'

Ta ajiye wayar ta zauna tana ta faman kumbura saboda takaici. Domin tun tuni kanin nata ya gaya mata abinda yake zuwa yi a Zariya da ta saka shi ya bincike shi, hatta adireshin gidan su Fatiman sai da ya gaya mata da inda Fatiman take aiki. Lokaci kawai take jira amma tabbas ba zata dauki wannan wulakancin ba.

Sai can an jima tana ta hidimarta ya kirawo ta, tana dagawa yace

'Gaskiya Maman Baby mutumin nan Zariya ya tafi, don ya tsaya a office bai fi minti goma ba ya fito ya kama hanya don wanda na sa ya bishi sai da ya raka shi har suka wuce Naibawa sannan nace ya dawo.'

'To shike nan na gode, za ka ji alert in sha Allah.'

‘Yauwa Hajiyata, ni da abokai na muna godiya.’

Sukayi sallama ta jefa wayar kan kujera ta ja tsaki. Ta cije lebe saboda takaici a yayinda hawaye da take kokarin ta danne suka kwace; yanzu haka zata zauna yana raba musu kwana da wata karuwa a Zariya, tana da yakinin kuma wannan yarinyar ya bawa kudin da zai kama mata event center taje ta sayi waya. Tabbas dole ta dauki mataki, yanzu dai tana lallabawa abubuwa su dawo dai-dai don ta kula yana mata kallon mahaukaciya.

Tana nan da lambobin wayar ‘yan matan nasa da ta dauka a tsohuwar wayarsa tun kafin ta fasa kuma yanzu ma da ta sami dama zata duba sabuwar wayar ta sake hado wasu don ta san da saura. Tana jira ne shi ya gama nasa haukan tunda shi bai yadda ma yana yi ba, a lokacin ne zata bi 'yan matan nasa daya bayan daya ta kora musu jawabin; domin a yanzu tana jin tabbas zata iya bin yarinya har dakin uwarta ta kora mata jawabi idan bata daina bi mata miji ba.

Ta share hawaye ta cigaba da hidimarta, tana yi tana kwafa saboda takaici.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA BAKWAI.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA ASHIRIN DA TAKWAS

A zaune take ta fito daga wanka a gaban mudubi tana shiryawa. Zuwan Mukhtar take jira don shi ya saka ma take shiryawa da wuri. Kwana biyu takurawa kanta kawai takeyi tana sauraronsa, gaba daya ya gama fice mata daga rai.

Ta bar shafa man da takeyi ta kalli zoben da yake hannunta, ta juya zoben a yatsanta. Kwana biyu ji take kamar zoben yayi mata nauyi a hannunta.

Tabbas a da tana son Mukhtar, amma yanzu kam ya fice mata daga rai. Ta kasa tuna irin rayuwar da zata yi idan ta zama matar Mukhtar.

Bata son gori ko daya, kuma tabbas ta san idan ta auri Mukhtar wata rana zai goranta mata, ko kuma ma yayi mata wulakanci.

Ta sake kallon zoben; to yanzu kenan ko bayan ta zama matarsa idan ta cire zoben nan komai zai iya faruwa kenan. Ta jijjiga kai tana so ta daina wannan tunanin.

Ta mike ta karasa gaban wardrobe ta zaro kayan da zata saka.

Mommy bata nan ta tafi Umra tare da Yaya Ibrahim don haka daga ita sai Baba Habi a gidan. Sai jibi zasu dawo, don haka ne ma ta sanar da Mukhtar ya zo ya kaita Abuja gidan Mami inda daga can idan aka dauko Mommy daga airport sai su dawo tare.

Tana son Mommy ta dawo domin tayi kewarta, amma tana fargabar dawowarnan saboda Mommy ta gaya mata da sun dawo zata sa Yaya Ibrahim ya nemi Mukhtar a fara maganar aurensu; domin ita Mommy so take kafin karshen shekara ayi bikin Fatima.

Kafin ta gama shiryawa har Mukhtar ya karaso, haka ta karasa ta fito suka kama hanya. Shi kanshi Mukhtar din sai da ya fahimci wani abu yana damunta saboda yanda bata da walwala sosai, amma haka ya kyaleta saboda shi kanshi yana zaton kewar Mommy take yi.

Kullum lallabata yake yi a kan ta bari ya fito ayi aurensu amma ta ki, yanzu ma da tace ya bari ita da kanta zata yi masa maganar sai ya zama tsoron ma tada zancen yake yi. Gaba daya ya kare a hanyar Zariya, ga kudin mai ga wahala gashi kullum sai ta gaya masa abinda take so ya taho mata da shi daga Kano wanda wata ran sai ta bukaci abun sama da dubu goma; kuma dole ya kawo.

Haka har suka isa Abuja suna yi suna hira wadda yawanci shine yake hirar. Yana sauketa ya kamo hanyar Kano.

.....

Ta kasa gane murna zata yi ko fargaba, a haka dai ta tashi ta shirya suka tafi airport don su dauko su Mommy.

Inda ake tarbar passenger nan suka zauna ita da Faisal dan wajen Mami, wanda shi ya kaisu airport din. Suna kallo jirgin ya sauka, aka gama abinda za ayi fasinjoji suka fara fitowa. Tana hango su Mommy ta mike ta karasa bakin kofar da zasu shigo tana ta faman murmushi.

Suna shigowa ta rungume Mommy, bayan ta saki Mommy ta dan rage tsawo tace

‘Ya Ibrahim sannu da zuwa.’

Da fara’a ya amsa sannan suka gaisa.

Mutumin da yake binsu a baya wanda yake tafe tare da wani yaro mai kimanin shekaru tara ya danyi gyran murya sakamakon tare masa hanya da Ibrahim yayi. Don haka suka matsa daga hanya.

Ta ja Mommy suka zauna a wajen da ake jira yayinda shi kuma Ibrahim ya ja Faisal suka tafi don su dauko musu kayansu. Bayan sun dauko kayan suka nufi su Fatiman, har sun kusa isa wajensu wannan mutumin da yayi masa gyaran murya don ya matsa masa ya dan sha gabansa tare da yi masa sallama yana mika masa

hannu. Suka tsaya shi da Faisal din duka suka gaisa da mutumin da alamar mamaki a fuskar Ibrahim.

Mutumin wanda yake ta fara’a yace

‘Sunana Ahmad Muhammad Auyo, Ina aiki a Federal Inland Revenue Services dake nan Abuja.’

Ya juya ya nuna masa yaron da da ya gansu tare yana fadin

‘Wancan yaronane Hafiz.’

Mamakin Ibrahim ya karu don Bai fahimci dalilin wannan bayanin ba, kafin ya gama tunanin Ahmad ya cigaba

‘Amm, dama ina so ne idan ba kayiwa kanwarka miji ba ka dan bani dama ko Allah zai sa nine mijin nata don ina sonta.’

Ibrahim yayi 'yar dariya yace

‘Wai Fatima?’

‘Ma sha Allah, sunanta Fatima ko? Waccan mai abayar wadda take zaune kusa da Mommynta don naji tace Mommy.’

‘Hakane, to babu damuwa. Mu karasa sai ku gaisa.’

‘No, ka kyale Fatima amma muje na gaida Mommy. In ya so sai ka bani lambarka kayi min kwatancen inda kuke gobe sai na zo na kawo kaina.’

Ya danyi murmushi

‘To babu laifi.’

Nan sukayi musayar lambar waya kuma yayi masa kwatancen gidansu a Zariya. Suka karasa ya tsuguna har kasa ya gaida Mommy yayinda ita kuma Fatima ta dan rusuna ta gaisheshi domin ta zata abokin Ibrahim ne.

Sukayi sallama suka kama hanya.

Sosai Ibrahim ya ji dadin haduwar da sukayi da Ahmad. Shi dama tuntuni yake fama da Mommy a kan a sallami Mukhtar amma Mommy taki yarda saboda tana ganin kamar idan aka bari Mukhtar ya subuce ba lallai Fatima ta sami wani mijin ba, don haka tace masa tunda dai Fatiman ce ta kawoshi kada ma ya tada wata magana kawai ya bari ayi auren.

Don haka kafin su koma Zariya ya sa an yi masa bincike a kan Ahmad din kuma an tabbatar masa da cewa Ahamad mutumin Auyo ne kuma matarsa uwar wannan yaron nasa Hafiz ta rasu tun Hafiz din yana shekaru hudu da haihuwa.

Ta zo haihuwar kanin Hafiz Allah ya karbi rayuwarsu ita da abinda yake cikinta, kuma tun wannan lokacin Ahmad din bai sake aure ba. Kuma ba’a sameshi da wani mugun hali ba, don haka Ibrahim ya sake jin dadi don duk yanda za ayi sai ya raba Fatima da Mukhtar ya aura mata Ahmad.

Shatar mota suka dauka daga Abuja har Zariya, aka sauke su a gidan Mommy. Suna sauka Ibrahim ya dauko mukullin motarsa wadda ya bari a nan, Fatima tayi masa rakiya wajen mota. Kafin ya shiga motar ya juyo ya dubi Fatiman yace

‘Gobe za kiyi bako sai ki shirya.’

Ta dan zare ido

‘Eye, bako kuma?’

Ya bata rai yana hararta

‘Eh, bako. Saura in ji wani labari.’

Ta sunkuyar da kai, ya ja motarshi ya barta a nan.

Ta shiga gida tana zumbura baki tana addu’a Allah ya sa ba tallanta Yaya Ibrahim yaje yayi wa wani ba don ita bata so mutum ya zo ya raina ta.

.....

Mutuwar mahaifiyar Hafiz ta gigita Ahmad sosai; suna ta shirin tarbar baby din da zata haifa wanda an riga an yi scanning an sanar da su namiji ne. Katsam ciki yana wata takwas ta kama nakuda, suna zuwa asibiti aka ce aiki za ayi a cire yaron saboda akwai matsala. Ya saka hannu a duk wasu takardu ya tafi siyo allurai da magungunan da aka bukata yana dawowa aka sanar da shi ta rasu ita da abinda yake cikinta.

Haka suka koma gida akayi mata sutura. Tun wannan lokacin har kawo yanzu shekaru biyar kenan bai sake aure ba kuma bai sake marmarin soyayya da wata mace ba. Mahaifiyarsa da danginsa duk sunyi fada sun gaji, an yi masa tayin ‘yan mata sau ba iyaka amma duk ya ki kulasu.

Don haka kawo yanzu addua kawai ake masa, shima kuma da kansa addua yake wa kansa. Wannan tafiyar ma da suka je Umra sai da yayi dawafi ya roki Allah ya bashi mace ta gari wadda zata zauna da shi da Hafiz cikin amana. Ya gaji da zaman Hafiz din a Auyo wajen babarsa, so yake ya dawo da shi Abuja amma ya san hakan ba zai samu ba dole sai yayi aure.

Tun suna saukowa daga jirgi ya hango Fatima tana tsaye a inda take jiran mommy; da yake glass ne ya rabasu da inda jirgin ya sauka. Haka kawai ya ji ta burgeshi sai dai bai kawo komai ba. Yana shigowa ciki kuma ya ganta da su Mommy ya ji ta kara burgeshi, take ya ji in dai zata aureshi to zai iya aure yanzu. Har zai fito daga wajen sai kuma ya ga gara dai ya koma ya karbi lambar ta, don haka ya sami waje yace da Hafiz ya zauna zai je ya dawo. Shine ya dawo ya tare Ibrahim suka yi magana.

Tun safe suka kamo hanyar Zariya domin daga nan Auyo zasu wuce ya kai Hafiz gida. Ya tsaya a gidan abokinsa nan Zariya ya ajiye Hafiz sannan ya karasa gidan su Fatiman shi kadai.

Ibrahim ya kirawo don haka shine ya kirawota ya sanar da ita zuwan bakonta, ya riga ya gama yiwa Mommy bayani don haka ba tare da bata lokaci ba Fatiman ta fito wajen Ahmad.

Tunda ya hango fitowarta daga gidan ya fito daga motarsa ya mayar ya rufe ya jingina da motar, ya kafa mata ido yana ta wani murmushi. Ya saka ta jin kunya sosai don haka da kyar ta daure ta karasa. Bayan sun gaisa tayi masa iso cikin gida, suka zauna a falo. Da kanta ta tashi ta kawo masa ruwa da lemon; domin da ko ruwan bata yi niyyar bashi ba. Amma yanda ta ganshi ya zarta tunaninta, ba wai kyau yayi da yawa ba amma yayi kwarjini kuma ga kamala duk ya cika mata ido.

Ta ajiye masa ruwa da lemon ta zauna suka dan taba hira, kafin wani lokaci an kulla soyayya mai karfi.

…….

Tuni abubuwa suka dawo dai-dai tsakanin Jamila da Mukhtar, duk da har yanzu tana sane da yanda ya sa mata ido. Ita din ma nata idon yana kansa, domin tana sane da yanda har yanzu duk Juma’a sai ya je Zariya sannan kuma tana zargin ‘yan matan nasa sun kara yawa domin yanzu harda wata wadda take tunanin sunanta Felicia duk da yayi saving sunan da Felix ne. Ga kuma wata wadda take tunanin kamar irin sugar mommies din nan ce, domin ita idan suna waya har wani rusunawa yakeyi kamar wata uwarsa.

Duk wannan abun in yana falo aka kirawoshi daki yake komawa amma haka take bin bayansa ta labe a kofa shi yasa ta san halin da yake ciki. Duk ta kwafe lambobinsu, lambar sugar Mommy din ne kawai bata samu ta kwafa ba saboda ya canza pattern din bude wayarsa wanda har yanzu take kokarin ta gane.

A halin yanzu wadda take Zariya itace ta tsaya mata a rai domin ta gaji da wannan abun, ko me zata ce masa sai ya je Zariya ranar Juma'a. Har karyar rashin lafiya tayi masa ranar wata Juma'a amma haka ya yi mata wayo ya wuce ya tafi Zariya.

Yau Alhamis don haka ta san gobe zai ce zai je Zariya, ta gaji da wannan abun hakurinta ya kare musamman a kan wannan yarinyar don haka dole yau ta dauki matakin da ya dace.

Tun safe da ya tafi office take bitar abubuwan da zata fada, bata sami dama ba har sai bayan la'asar. Ta kwantar da Halimatu wadda ta riga tayi bacci sannan ta sallami mai aikinta wadda dama zuwa da dawowa takeyi; ta rufe gidan ta dawo falo ta zauna. Ta dauko takardar da ta kwafi lambobin ta kwafe lamabar da take tunanin itace ta Fatiman. Bata jima tana ringing ba aka dauka, ta danyi jinkiri magana don haka daga daya bangaren aka ce

'Hello, Salam alaikum.'

Duk da natsuwar da ta ji a muryar ta rage mata karsashin yin masifa amma cike da isa ta amsa

'Wa alaikumussalam.'

Ta numfasa sannan tace

'Fatima nake nema.'

‘Nice Fatima, sai dai ban ganeki ba saboda bani da wannan lambar.’

So take ta fara ruwan asharan da bakaken maganganun amma bakinta yaki bawa zuciyarta hadin kai, gashi kuma natsuwar da take muryar Fatiman tana nema ta sa mata natsuwa itama. Ta bada amsa cikin isa tana batsewa

‘Ba zaki gane ni ba domin dama baki sanni ba, Sunana Jamila, kuma nice matar Mukhtar. Na san yanzu kin gane ni.’

Fatima taji wani banbarakwai, ta tashi daga kashingidar da tayi ta zauna ta zuba kafafunta gefen gadon da take, ta danyi gyaran murya cikin karfin hali tace

‘Allah sarki, kwarai na ganeki. Ya gida? Ya Halimatu da su Nurain?’

Cikin isa ta amsa tana ta wani gatsine fuka kamar wadda take a gaban Fatiman

‘Ba shi na kirawo ki muyi ba. Kiranki nayi na baki shawara kuma na gargadeki, Ina so ki rabu da mijina. Duk wani iskanci da kike yi ina sane dashi, ki rabu da mijina ki nemi naki tun kafin dare yayi miki don bana son nayi abinda ke da shi za kuyi nadama. Na gaji da raini da wulakanci.’

Sai da ta numfasa sannan Fatima tace

‘Allah sarki, ai mun bar iskancin ma tun tuni. Sai dai shi mijin naki bani na kirawoshi ba shi yake kawo min kansa don haka ya rage naki ki hanashi zuwa inda nake….’

‘Au h…'

Jamilan ta fara magana zata katseta don haka itama Fatima ta dan daga murya ta katseta ta cigaba

‘Yanda na saurareki kema hakuri zakiyi ki saurare ni. Ni dinma zan baki shawara, mijinki serial mazinaci kuma bana jin zai iya dainawa sai dai ko in ya kasa don ko ke bana jin zaki iya hanashi. Ni din kuma ba zan auri mijinki ba, kema da Allah ya jarrabeki da zama dashi ina fatan Allah ya kawo miki mafita.

Nayi miki alkawari daga yau ba zaki kara ji mijinki ya zo Zariya wajen na ba; sai dai da yake ni kaina na jima ina zargin in yazo wajena akwai wadda yake zuwa wajenta nan cikin Zariya ko Kaduna to watakila ki ji ya cigaba da zuwa, amma ni nayi miki alkawarin daga yau ba zaki kara jin mijinki yana zancena ba.’

Ta dan tsagaita ko Jamilan zata ce wani abu, taji shiru sai numfashi kawai take ji don haka ta cigaba

‘Na barki lafiya. Ki Shafa min kan Halimatu; Allah ya rayata yayi mata albarka.’

Ta katse wayar ta ajiye.

Ta jefa wayar kan gadon ta mike ta nufi tagar dakin, ta daga labulen tana hango waje sai dai ba ganin abinda yake wajen takeyi ba tunani kala-kala a ranta. Dama ta gaji da dakon soyayyar Mukhtar kuma ta gaji da dakon zoben da yake hannunta, tunda suka daidaita da Ahmad take son rabuwa da Mukhtar din sai dai da tayi niyyar ta wanke shi a karo na karshe.

Jamila ta bata tausayi sosai, tabbas ta san ba zata iya zama matar Mukhtar ba. Ahmad zata aura, sai dai abu daya take tsoro yanda zatayi idan ya gane ita din ba ta kai budurcinta ba tunda ya san bata taba aure ba.

Amma tana nan tana addu’a kuma tana da yakinin Allah zai amsa mata rokonta, domin zaman aure take so tayi mai tsabta da aminci.

Ta dago hannunta ta kalli zoben da Mallam ya bata, ta gaji da zoben sosai. Kuma dama Mallam ya gaya mata duk lokacin da ta cire wannan zoben soyayya ta kare. A

hankali ta zare zoben daga yatsanta, ta zubawa zoben ido tana kallonsa. To yanzu ya zatayi ma da zoben?

Tana nan a tsaye da zoben a hannunta dabara ta fado mata, don haka ta saka hijabinta ta fice daga dakin. Ta lallaba ta leka dakin Mommy ta hangota tana kwance a kan gado don haka cikin sanda ta fice ta nufi boys quarters inda dakin Baba Habi yake. Tana shiga taga dakin a rufe don haka ta san Baba Habi bata nana, nan da nan ta shiga bandakin wajen wanda yake da masai irin na kasa din nan. Ta jefa zoben a ciki ta tari ruwa cikin bokiti a famfon bandakin ta kora. Tayi sauri ta fito ta kamo hanyar cikin gidan.

Haka kawai taji zuciyarta ta washe, ta manta rabon da ta jita a cikin irin wannan walwalar domin har ji take kamar ta rage nauyi. Tana shiga daki ta ta turo kofa ta jingina da bayan kofar, ta daga kanta ta dafe kirjinta ta bude baki a hankali tace

‘Alhamdulillah.’

Haka kawai kuma sai taji hawaye yana bin fuskarta, ta saka hannu ta goge tana murmushi. Ta karasa gefen gadon ta zauna; tuba ma ya kamata tayi domin ta san wannan abun da tayi sabon Allah ne, don haka dole ta tuba kuma tayi addua Allah ya tabbatar da aurensu da Ahmad kuma ya sa musu albarka a ciki.

Ta kwanta rigingine a kan gadon zuciyarta cike da farin ciki.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA TAKWAS.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA ASHIRIN DA TARA

29

Fatima tana tsinke kiran Jamila ta saki tata wayar wadda ta fada kan cinyarta, ta hada tafukan hannunta ta rufe fuskarta. Tana cire hannun sai hawaye, ta maida hannun ta dafe kirjinta wanda yake mata suya a halin yanzu. Ta kasa daina jin muryar Fatima tana maimaita mata abinda ta gaya mata

‘Mijinki serial mazinaci ne, ba zai daina ba…'

Ba wai maganar ce ta bata mata rai ba, amma ashe yanzu abinda Mukhtar yake yi ta kai har ‘yan matan nasa sun sani?

To kenan shi yanzu a duniya babu wanda zai gaya masa gaskiya?

Ta gayawa yayarta yana neman mata, ta gayawa kanwar babarsu har dama maman nasu ta gayawa amma kowa cewa yake tayi hakuri. Yanzu kenan haka zata nade hannu ta cigaba da kallonsa yana yanda yake so? Ya kwana da karuwai ya kwana da ita gata nan kullum cikin shan magani take saboda bata rabuwa da ciwon sanyi.

Gaba daya tunaninta ya kare, ta ma rasa me zata yi. Duk da haka dai ta ji dadi da Fatima tace ta yi alkawarin ta rabu dashi, kuma tana ji a jikinta kamar ba karya Fatiman tayi mata ba don haka sai ta danji sanyi a ranta.

A wannan zaman da tayi niyya tayi bayan ta kirawo Fatima ta kirawo Felicia, amma Fatima ta kwance mata lissafi don ta zata za ta sami dama tayi rashin mutunci. Don haka ta bari sai wani lokacin sai ta kirawo Felicia. Yanzu dai zata zuba ido taga ko za a cigaba da zuwa Zariya, kuma zata saka a bibiyeshi aga inda yake zuwa.

…..

Har gari ya waye ranar Juma’a zuciyarta babu dadi, shi kansa Mukhtar din ya kula da haka. Yana sane ya share ta domin baya so ko daya ya nuna ya san tana da damuwa, domin yana tunani ko taga wani abune a wayarsa. Tun dare da ya kula da damuwarta yake faman duba wayar ko ya bar wani abu amma bai ga komai ba, don haka ya kyaleta.

A cikin walwala da nishadi yake, shima bai san dalili ba haka kawai yake jin ranshi fes don haka baya son ta gusar masa da farin cikinsa.

Nan da nan ya shirya yaci abincinsa na safe sannan ya yi mata sallama zai fita. Har ya kai bakin kofa sai kuma ya dan dawo ya dubeta tana tsaye a kusa da dining table da goyon halimatu

‘Ki ajiye min abincin rana, zan dawo da azahar.’

Ta kalleshi da mamaki

‘Ah yau ba zaka Zariya ba?’

‘Eh, office kawai zan je.’

‘Uhm! An gama kwangilar Zariyan kenan?’

Ya dan tsuke fuska ya kama hanyar fita yana bata amsa

‘Eh, tun last week.’

Ya fice kafin ya amsa a dawo lafiyarta.

Ta ja tsaki ta murguda baki kamar yana kallonta tace

‘An dai fadi ba nauyi, ba a jin tsoron Allah sai tsoron karuwa.’

……..

Tare suka gama cin abincin safe a falon Umma da yake Sabir da Hamida ma suna da lecture din safe. Safiyya ta dauki kofin shayin ta ta kurbe, ta daga kai ta kalli agogon bango wanda ya nuna karfe bakwai da minti goma. Ta mike tana fadin

‘Bari nayi sauri na karasa shiryawa don na shiga kafin a fara tarar makara.’

Hamida ta mike da nata kwanukan a hannu tace

‘Kawo na wuce da kwanukan kichin.’

Sabir ma ya mike da hanzari ya dora nashi kwanukan kan wanda suke hannunta yana fadin

‘Yauwa yarinyar kirki, hada da wannan ma.’

Ta watasa mishi harara ta take masa yatsun kafa tana fadin

‘Dan rainin hankali, waye sa’anka a nan me bakin baya.’

Ya wuce da gudu ya bar musu falon Safiyya tana bata hakuri.

Doguwar riga ta saka ta atamfa mai dogon hannu don haka ta dauki mayafinta matsakaici ta nade kanta da shi sannan ta tsaya a gaban mudubi tana kara goge fuska. Sabir ne ya shigo dakin da sallama

‘Ya Safiyya kin shirya na baki lift a legedisbenz dita?’

Ta kyalkyale da dariya ta fara shafa lip gloss tana fadin

‘A silifas dinka dai.’

Ya dan bata rai

‘Haba Ya Safiyya, idan kika fada a gaban 'yan mata ai sai su raina ni.’

Ta kyalkyale da dariya ta dauko Jakarta ta wuceshi tana fadin

‘To muje.’

Ya biyo bayanta suka fito yana fadin

‘Kin ganki kuwa Ya Safiyya, koyarwarnan ta karbeki fa. Wallahi kin yi fes dake kamar Ya Safiyya, sai yanzu kika rabu da matar Mukhtar kika dawo ‘yar gayunki kamar da.’

Suka yiwa Umma sallama Hamida ma ta fito suka kama hanya tare, idan suka je makarantar da take koyarwa sai ta shige ciki sunkuma su hau mota a nan.

Ko Sabir bai fada ba ta san ta koma Safiyyan da ta sani da. Ta yi fes da ita gashi wannan aikin ya sa ta kara sakewa kuma ga sutura yanzu duk gayunta ya dawo, duk wata ga albashinta ga kudin kitso wanda Sabir yake tattala mata. Ita kadai ta yiwa kanta murmushi a dai dai lokacin da take sa hannu a littafin signing na malamai.

Bata da aji da safe don haka bayan tayi kiran suna a ajinta sai ta koma ofishin malamai mata ta zauna ta fara sa hannu a litattafan ‘yan aji daya da suka yi homework.

Ta zo kan littafin Muhammad Abdurrahman Anas, yaro ne dan shekara shida. Kullum in ta basu aikin aji tsaf yake aikinsa, amma idan aikin gidane to bazai yi ba. Kuma duk sauran malamai haka suke fama da shi domin su sun riga sun ce dakiki ne shi tunda su ko aikin ajin suka bayar baya yi, har malamar ajinsu ta shaida.

Bayan ta gama saka hannun ta dauki littafin Muhammad ta wuce wajen shugabar makarantar ta sake yi mata bayanin ya kamata a kirawo mahaifiyar yaron nan don shi ba dakiki bane, tana ganin dai akwai wata matsala ne ko daga gidan.

Shugabar makarantar ta dubeta tace

‘Safiyya nifa ba zan kuma kiran matar nana ba, sai an aika mata sako sau biyar kafin tazo sau daya. Ta shigo tana wani yauki tana neman ta zagi mutane ita a dole ga mai ilimi. Shi kuma uban kullum aka kira shi yana Abuja, basu fa da lokacin yaran nan. Amma ki rubuta wasika ki basu su kaiwa iyayen, in ya so idan ta zo ke sai ki ganta don ni kam kar ta zo min nan.’

Tayi murmushi

‘Hakan ma yayi Hajiya, in sha Allah yanda muka yi zaki ji.’

Ta fito ta koma office.

Sai da aka tashi sannan ta saka masa wasikar a jaka, tace masa idan ya je gida ya bawa mommy ko Daddy.

.....

Washegari da wuri ta shiga makaranta domin bata san lokacin da uwar Muhammad zata zo ba, amma ga mamakinta sai wajen takwas saura Muhammad din ya shigo. Yayansa wanda yake primary 5 shine ya rakoshi ajin, bayan sun gaisheta yayan Muhammad yace

‘Anty Mommy tana Abuja amma daddynmu yace na gaya miki zai zo in an tashi.’

Duk da bata son abinda zai tsayar da ita idan an tashi haka ta hakura ta dan yi jinkiri, tana da masu yin kitso da yake yau Alhamis. Tana zaune tana nadamar aika wannan sakon mutumin ya shigo ajin inda suke zaune ita da Muhammad da wasu yaran, Yayan Muhammad yana biye dashi tare da Yayarsu wadda ita a secondary take JSS 1.

Cikin girmamawa suka gaisa, ya zauna akujerar da take gaban teburin da take kai. Cikin nutsuwa ta koro bayani bayan ta gama nuna masa duka litattafan Muhammad din, ta rufe da

‘Muhammad yana da kokari fa, kawai dai baya yin aiki ne. Kuma ina ga yana bukatar kulawa ne kawai, shi yasa na so ace mahaifiyarsa ce ta zo domin itace yafi dacewa tayi wannan aiki.’

Yayi shiru na dan lokaci, jim kadan yace

‘To Anti ki taimaka min mana ki dinga yi masa lesson after school, in ya so ko nawa kikace ni sai na biya.’

‘Gaskiya ba ni da lokaci, sai dai a malamai zan duba maka zuwa gobe. In an samu zan rubuta maka note na bawa Muhammad din.’

Nan ya bata lambar waya yace ta kirawo shi idan an samu. Sukayi sallama kowa ya kama hanya.

……..

Duk yanda Alhaji Abdurrahman Anas ya so ya cire Safiyya daga ransa abun yaci tura, da farko yana tunani bai kamata ya yi soyayya da malamar yaronsa amma daga baya dole ya hakura tunda shi aurenta yake son yi. Sai dai bai sani ba ko tana da aure ko bata da aure.

Yana da matarsa daya Barrister Amina Bala Rogo wadda take aiki da ma'aikata shari'a ta tarayya inda take aiki a kotun su dake Kano. Wannan aikin nata bata hada shi da komai ba, domin shi mijin nata ma yana tunanin idan aka ce ta zaba tsakanin aikinta da aure to tabbas zata zabi aikin nan. Yaransu hudu, biyu maza biyu mata. Kuma gaba dayansu bata da lokacinsu, masu aikinta guda biyu sune komai nasu.

Mafi yawancin lokuta idan ta fita sai karfe biyar take dawowa, wani lokacin kuma idan suna da case sai ta kai dare.

Shi kuwa Abdurrahman tun kafin ya aureta yake aikin civil defense kuma ba'a taba kai shi Kano ba, domin a halin yanzu ma Abuja yake aiki sai dai idan ya zo hutu.

Da kyar ya kyar ya daure ya koma Abuja, yana fatan Safiyya ta kirawo shi domin shi bai karbi lambarta ba. Sai dai kafin ya tafi Abuja ya saka ayi masa bincike a kanta don baya son ya zo yayi aure a sami matsala a rusa masa gida.

Kafin karshen satin an sanar da shi duka abinda yake son sani game da Safiyya. Sai dai har zuwa lokacin bata kirawo shi ba saboda kusan duk malaman makarantar suna da wani aikin ko yaran da sukewa lesson in an tashi. Don haka ta kyale kawai ta cigaba da iya kokarinta wajen ganin ta taimakawa Muhammad din.

Ranar Juma'a jirgin karfe bakwai na safe ya biyo sai Kano, daga airport da direba ya daukeshi kai tsaye suka wuce office din Yaya Habibu. Bayan ya gabatar da kansa a wajen Yaya Habibu wanda yake ta mamakin wannan ziyarar yayi gyaran murya yace

'Na san kana mamaki, wato akwai Safiyya kanwarka kamar yanda na sami bayani. Yarona dalibinta ne a makaranta don a nan ma na santa, to gaskiya ina son na

shiga neman aurenta ne shi yasa naga ya kamata na nemi izininka domin ba wai zamu tsaya wasa bane. In dai har ta amince nan da wata shida ma ana iya daura auren.’

Nan da nan fara’ar Yaya Habibu ta karu yace

‘Ah, ma sha Allah. Wannan ai ba zai zama matsala ba in dai ta amince.’

Suka dan taba hira, ya sanar da Yaya Habibu ranar Lahadi zai zo bayan la’asar. A nan yayi masa kwatancen gidan sannan sukayi sallama.

Yana tashi daga office ya wuce gidan Umma, sai da ya gama hirarsa zai tafi yaja Safiyya suka fice daga gidan. Suna zuwa bakin gate yace

‘Akwai wani mutum Alhaji Abdurrahman Anas, yayi min magana a kan zai zo neman aurenki.’

Nan da nan idonta ya kawo kwalla ta sunkuyar da kai, ya cigaba

‘Ba fa wani abu bane, ba dole za ayi miki ba shi yasa ma ban yi magana a gaban Umma ba. Idan ya zo ki dan bashi dama idan kun fahimci juna shikenan, idan kuma da matsala ki sanar dani sai a hakura. Amma dai so far na dan samu bayanai daga wadanda suka san shi sosai mutumin kirki ne, sai dai kawai wajen aikinsa da zan sa a bincika saboda kada a sake.’

Cikin rawar murya tace

‘To Yaya.’

‘Yauwa, ki natsu kiyi tunani a hankali kuma ki bashi dama. In sha Allahu zai zama alkhairi. Ranar Lahadi zai zo in sha Allah don haka sai ki zama cikin shiri.’

Sukayi sallama ta shiga gida tana tunani kala-kala domin ita har kawo yanzu tsoron maza takeyi, musamman 'yan kwana kin nan da har samari ma tare ta suke a hanya zasu tsarata; abinda take gani kamar rashin kunya.

Yau ranar Lahadi ce don haka bai fita ba, a daki ya zauna yana ta aiki a computer. Yana dawowa daga sallar azahar ya zauna a falon don yaci abincin rana. Nan suka zauna suna ci tare, tana yi tana bawa Halimatu wadda ta kai wata shida yanzu.

Ko rabin abincin basu ci ba aka kirawo shi a waya, yana kallon screen din wayar ya saki murmushi. Ya dubeta yace

‘Cigaba ina zuwa.'

Ya tsallake abincin ya wuce daki da wayar a hannunsa wadda har ya amsa ya fara magana cikin girmamawa.

Ta bi bayansa da harara tare da jan dogon tsaki. Tana da yakinin matar da ta saba kiransa ce kwannan nan, ba yarinya bace don ji tayi yana kiranta Hajiya kuma yana girmamata sosai. Tayi kwafa ta rike Halimatu wadda take kokarin rarrafawa ta bishi.

Yanzu dai ya tabbata Mukhtar sugar mommies ya fara bi. Sai jiya ta samu ta gane pattern din da yake bude wayarsa don haka duk yanda za ayi yau zuwa gobe zata sato lambar matar nan ta kora mata jawabi; an girma ana bin mijin yara.

Motsin fitowarshi ne ya karkato da hankalinta, ya fito dauke da mukullin mota da kuma computers guda biyu sababbi a kwali wadanda dama ya gaya mata ya sayar da su jira yake a zo a karba. Ya dubeta yace

‘Bari na kai wadannan, idan na dawo na kara abincin.’

A ciki ta amsa

‘A dawo lafiya.’

Ya sa kai ya fice.

Sai yanzu ta game ya Raina mata hankali don yanzu haka karuwa aka sayawa computer ita tana gida bata da ita. Tabbas za ayi balai kuma har shima zai ji daga gareta amma sai ta kirawo matar nan ta kora mata jawabi dole; don in ta kama zata iya zuwa duk inda matar nana take ta sameta tayi mata rashin mutunci.

KARSHEN BABI NA ASHIRIN DA TARA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN

30

Tana zaune a kan dadduma ta idar da sallar la'asar Yaya Habibu ya kirawota, bayan sun gaisa yace

‘Bakonki ya zo, yana waje. Amma nace ya turo yaro ya kirawoki domin Umma ta sani.’

Tana ajiye wayar kuwa ta ji sallamar yaro, Umma tana kicin don haka ita ta amsa. Tana jin yaron ya gayawa Umma sakon, nan take kuwa tace

‘Je kace tana zuwa.’

Domin ita Umma duk wanda yazo neman Safiyya in dai ta ji labari to dole Safiyyan ta fita, tunda ita so take kawai Safiyya tayi aure. Musamman a ‘yan kwanakin nan da an riga an saka ranar auren Hamida; yanzu haka saura wata biyu.

Nan da nan ta leko daki ta daga labulen ta dubi Safiyyan

‘Ana sallama dake, taso kije ki gani.’

‘To Umma gani nan zuwa.’

Tana mikewa ta kalli kanta a mudubi; hijabinta babu abinda yayi kuma fuskarta ma kalau take don haka ta fito sanye da hijabinta ta wuce waje.

Tana fitowa ta dan karewa bakin gate din kallo, mota daya ta gani da alama mai motar shine a jingine a jikin motar. Daga shi bata ga alamar kowa ba sai masu wucewa, don haka ta karasa wajen da yake.

Tana kusantar wajen tayi sallama, ya juyo tare da amsa sallamarta fuskarsa da fara’a. Da mamaki ta bude baki

‘Ah! Baban Muhammad.’

Tana fada tana waige waige ko zata ga ainahin wanda yake sallama da ita, sai kuma ta tuna ai Yaya Habibu Abdurrahman Anas yace mata; don haka a sanyaye ta dube shi. Ita yake kallo yana murmushi don haka tana dubansa suka hada ido, ta sunkuyar da kanta cikin sauri. Yayi 'yar dariya yace

‘Nine nake nemanki Anti ba wani bane.’

Ta danyi yake tace

‘Bismillah mu karasa daga ciki.’

Ya bi bayanta suka karasa farfajiyar gidan inda ta janyo kujerun roba guda biyu ta saka musu, ta nuna masa daya tace Bismillah. Bayan ya zauna itama ta zauna.

Suka sake gaisawa sannan kuma suka danyi shiru na dan lokaci, da ya ga dai ba zata ce komai ba shi sai ya fara magana inda ya gabatar mata da kansa a matsayin Assistant Commander General na Civil defence a headquarters dinsu dake Abuja, kuma yana da mata daya da yara hudu wadanda ta sansu don dalibanta ne. Har ya gama bata ce komai ba, sai da shima yayi shiru yana kallonta.

A hankali ta dago kai ta dubeshi, da yake ita yake kallo suka sake hada ido, nan da nan ta mayar da nata idon kasa ta sunkuyar da kai. Yayi murmushi; yana mamaki kunyarta kamar wata budurwa, shi ya zata mata sun daina kunya domin ya dade bai ga mace mai kunya kamar Safiyya ba.

Ta danyi gyaran murya cikin damuwa tace

‘Don Allah kayi hakuri Baban Muhammad, ka ga makaranta bata yarda malama ta kulla Alaka irin wannan da mahaifin dalibinta ba; da na tura wasikar ma mahaifiyarsa nace ta zo shine kai kazo. Ai sai a zata dama don haka nace ka zo, kuma ka ga headmistress ba zata ji dadi ba don ko ita ma mahaifiyarsa tace na kirawo. Za ka sa mata su kwashe yaransu daga makarantar mu.’

Yayi murmushi

‘To ai a lokacin mahaifiyarsa bata nan, shi yasa ni nazo; kuma ina zuwa kika sace zuciyata kin ga ai dole na biyo ki nima na sace taki zuciyar ko?’

Ta dago ta kalleshi ta sake sunkuyar da kai, shi da gaske yake wannan maganar kamar wani yaro; gashi a haka gani take kamar ma zai girmi Yaya Habibu.

‘Uhm! Don Allah dai kayi hakuri.’

Yayi dariya yace

‘Gaskiya ba zan hakura ba.’

Ta kalleshi ya daga mata kai, a ranta tace na shiga uku. Muryarshi ce ta katse mata tunani

‘Kada ki damu, headmistress itace ta bani cikakken bayani a kanki kuma ta hada ni da Yayanki tace na je wajensa na nemi aurenki, kin ga da izininta kenan na zo ko? So ki kwantar da hankalinki.’

Ta yi matukar mamaki jin wannan zancen amma dai haka ta daure suka dan kara hira, wajen karfe biyar ya dubeta yace

‘Bari na tafi na barki ki huta ko? Gobe karfe takwas na safe zan koma Abuja so may be zan biyo na ganki kafin ki tafi aiki.’

Ta kalleshi da mamaki

‘Da sassafe ne fa.’

Dariya kawai yayi mata sukayi sallama ya wuce ya tafi bayan ya karbi lambar wayarta ya bata tashi.

Haka ta kwana tana tunanin mutumin nan, tana fatan Allah ya sa dai kada ya janyo mata matsala a wajen aiki. Bashi da wani laifi kuma tabbas ya kai a so shi, sai dai tana jin cewa a yanzu ta sami daidaito a rayuwarta bata so ya zo ya haifar mata da matsala. Tana jin tsoron zama da kishiya balle ace mara imani ce, ita auren ma gaba daya tsoronsa take; kaje ka zauna da mutum da zuciya daya kana masa biyayya kai ka hakura da abinda kake so amma shi yana maka wulakanci a karshe ka tashi babu wata riba. Amma dai zatayi istikhara ko don saboda bata so ta watsawa Yaya Habibu kasa a ido.

.....

Karfe bakwai da minti goma suka fito daga gate din gidansu ita da Sabir da Hamida zasu tafi makaranta. Yana tsaye a jikin mota ya rungume hannuwansa. Bude baki kawai tayi tana kallonsa shima ya bita da kallo yana murmushinsa wanda yake sata murmushi, ta sunkuyar da kai ta dubi Hamida tace ku dan jirani ina zuwa. Tana zuwa kusa dashi tace

‘Sai da ka zo Baban Muhammad? Ina kwana.’

Taji shiru bai amsa ba, ta dago ta kalleshi ashe hararta yakeyi ta kyalkyale da dariya yace

‘Idan kika kuma ce min Baban Muhammad sai na lakace wannan dogon hancin naki ya koma irin nawa, inama dai laifin saurayin Safiyya? Ai ban yi tsufa ba ko?'

Ta kyalkyale da dariya tace

‘Babbar magana. Bari naje mu karasa makaranta kada mu makara.’

‘Hakane kam, tunda na ganki nima yanzu sai na kama hanya.’

Sukayi sallama ya ja motarsa ya wuce, ya so ya karasa da ita makarantar amma ya san ba zata taba yarda ba don haka kawai ya hakura.

Tana dawowa Sabir ya fara

‘Ya Safiyya senator ne bazawarin naki?’

Ta harareshi

‘Kaine ai bazawarin.’

Yayi dariya

‘To abinki da ba saurayi ba, don Allah idan senator ne ki hadani da shi a bani kwangila.’

Hamida tace

‘Kai dai Allah ya shiryeka baki abun magana.’

Haka har suka karasa makarantar su Safiyya suna ta raha.

Duk kokarin da Jamila tayi a kan ta samo lambar sugar Mommy din Mukhtar a wayarsa abun ya ci tura, sai da aka dauki wajen sati biyu. Ta samu ta kwafo lamabar amma dai bata kirawo ba saboda ta ga abun ya dan yi sauki, gaba daya

harkar matan ma kwana biyu da sauki tunda yana yawan dawowa da la’asar kuma baya sake fita sai da safe. Don haka ta dan saurara tana fatan Allah ya sa sun rabu.

A shirye ya fito da Shirin office bayan ya gama cin abincin safe, ya zauna a falo yana wasa da Halimatu wadda take ta kokarin mikewa tsaye a jikin abun koyon tafiya tana ta gwaranci yana yi mata dariya. Ita kuma Jamila tana kicin tana ayyukanta.

Ba a jin ringing din wayarsa don haka bata jiyo lokacin da wayarsa tayi kara ba, sai dai tana jiyoshi ya amsa wayar. Ko bata sani ba ta san wannan sugar Mommy din ce saboda yanda yake magana, ta matso kusa da kofar kicin din don ta kara jiyo abinda yake fada duk da yanda yake magana kasa-kasa.

‘Eh, ai na san wajen.’

‘Ok. Yanzu zan iso nan da minti talatin.’

‘Ok.’

Tayi sauri ta koma can cikin kichin din data ji ya mike tsaye, ya kwalo mata kira daga falon yace

‘Zo ki dauki Halimatu, fita zanyi.’

Bai saurari amsar da ta bayar ba ya shige daki.

Jimawa kadan ya fito a shirye da jakarsa ta computer, ta riga ta dauke Halimatu ta koma kichin don haka yana daga falo yace mata

‘Ni na fita.’

‘A dawo lafiya.’

Ta bashi amsa daga kichin din, ya sa kai ya fice.

Har azahar tana ta faman share kwalla saboda takaicin Mukhtar, daurewa kawai takeyi saboda a tunaninta suna tare. Don haka ta bari sai wajen karfe uku zata kirawo matar tayi mata wulakancin da ba a taba yi mata ba a rayuwarta.

.....

Yana fitowa daga office dinsa zai karasa masallaci suyi sallar la’asar ya ci karo da Suraj a bakin kofa, sukayi musabiha suka gaisa. Mukhtar yace

‘Kayi sallah ne mutumina.’

‘A’a nima fitowa ta kenan ina hanya akayi kira muje in mun idar sai mu zauna.’

Suka rankaya suka tafi masallacin gaba daya. Bayan an idar da sallah suka dawo office din Mukhtar suka zauna suka hirarrakinsu.

Suraj yace

‘Kawai sai naga alert mutumina.’

Mukhtar ya kau da kai

‘Haba abokina 10k ce fa ba yawa, ai data kawai nace ka saka.’

‘Ina godiya mutumina, ai ganina computer biyu ai ba yawa. Ni na ma zata fa da yawa zata siya shi yasa na hadaku wallahi.’

Yayai dariya yace

‘Wa ya gaya maka? Ai kwannan nan ma alert din dubu dari zaka ji mutumina. Ka san bayan ta sayi computers din nan guda biyu yau da safe ta kirawo ni, tace na sameta a makarantarta. Ina zuwa ta nuna min sabon computer lab da suka gina tace na bata estimate na kudin da zasu hada computers guda arba’in kowacce da teburinta da kayan aikinta tsaf.’

Ya mika masa hannu suka tafa

‘Kai amma na maka murna, dama ai na gaya maka bata wasa da kudi tunda senator yana turowa kuma kasan makarantar tata ta yaran masu kudi ce sosai.’

‘Ai dagaske kuwa mutumina. Ka san ina zama a office nayi lissafi na tura mata, tana gani ta kirawo ni. Yanzu haka tace zuwa magriba zata sa a turo min 60% na kudin kayan idan aka kawo sai ta kara 20% sauran kuma idan aka hada computers din aka kunna sai tayi balancing. Ai ina tunanin da kaina zan je China na yo order kayan nan don akwai samuwa sosai Alhamdulillah.’

‘To ma sha Allah abokina, ai ka riketa idan dai kayi mata aiki mai kyau zata hadaka da mutanen kirki sosai.’

Suna cikin hirarsu ya dauki wayarsa yana dan dubawa, ya budo Whatsapp yace

‘Ka ganta ma voice message ta turo min yanzu haka ma an saka kudin’

‘Ai Prof akwai harkar arziki.’

Take ya kunna voice note din wanda yana fara magana kuma ta rubuta masa lambar waya ta turo a kasa ta sa

“with this number.”

Suna fara jin sakon Mukhtar ya saki wayar ya bude baki yayinda shi kuma Suraj ya zaro ido tare da dora hannu a ka suka cigaba da sauraro kamar haka …

“Wai me kike fadane haka, kin san kuwa da wa kike magana?”

Muryar Professor Hajara Bala Gombe ce take wannan tambayar, kafin ta numfasa kuma wata muryar ta shigo wadda ba Mukhtar ba hatta Suraj ma ya gane muryar Jamila ce ta cigaba

“Na sani, da ke nake magana Babbar karuwa mai bin mazan yara. Ko bai gaya miki yana da mata bane Mukhtar din. Kullum cikin waya kike da mijina to wallahi duk karuwancinki na fi ki hauka, idan baki rabu da mijina ba sai na tona miki asiri kuma na nuna miki ke karamar 'yar iska ce wallahi. Matukar baki ji kunyar budewa mijina tsakanin cinyoyinki ba nima ba zan ji kunyar tona miki asiri ba. Ki rabu da mijina idan kina son zaman lafiya, ki rabu da mijina idan kina son zaman lafiya! Idan ba haka ba kuma zaki gane ni yarinya ce 'yar wannan zamani tsohuwar banza kawai! Mtsewwww.”

A nan voice note din ya kare

.

A take kira ya shigo wayar wanda yana ganin lambar ya san ta prof ce duk da bai yi saving ba, ya kalli Suraj wanda shima yayi tsamo-tsami kamar shine yayi laifin , Suraj din yayi masa alamar ya dauka don haka hannunsa na rawa ya amsa wayar ya sa a loud speaker. Kafin yayi magana tace

‘Mukhtar ka san ni ka san ina da aure kuma ka san waye mijina ko? Me ka gayawa matarka a kaina take kirana karuwa tana yi min cin mutuncin da kaf tsawon rayuwata ba a taba yi min irinsa ba?’

Bakinsa yana rawa yace

‘Wallahi ban taba maganarki da ita ba Prof, wallahi babu abinda na gaya mata. Don Allah kiyi hakuri bari na zo yanzu, wallahi bani na…'

‘Kada ka zo inda nake, bana son ganinka.’

Ta tsinke kiran ta barshi yana ta faman hada gumi duk da AC din da take kunne a dakin.

‘Innaa lillahi wa inna ilaihi rajiun!’

Ya dubi Suraj wanda yake kallonsa kawai yace

‘Suraj yarinyar nana zata kashe ni, zata sa a daureni a garin nan. Tunda na aureta ban huta ba, fitna daga ta gama wannan ana murna tayi hankali sai kuma ta sake wadda ta fi ta da. Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun! Yanzu ya zanyi da Prof, ni na yafe kwangilar ma amma don Allah tayi hakuri.’

Suraj ya jijjiga kai yace

‘Allah ya sauwake, ina ga bari naje na sameta duk da ni din ma a kunyace zan je tunda ni na hadata da kai kuyi business.’

Ya mike ya kama hannun Suraj wanda ke kan teburin

‘Don Allah kayi hakuri Suraj, ko dai tasowa zan yi muje?’

‘Tunda tce kada ka zo to ka barshi kawai, za kaji yanda mukayi.’

Suraj din yayi masa sallama ya fice yana jan kafa saboda takaici.

Ya koma ya zauna a kan kujerar kamar wanda aka tunkuda, ya dafe kansa wanda yake sarawa da karfi kamar zai fashe yana fitar da gumi ko ta ina. Ya rufe jajayen idanuwansa ya kifa kai a kan teburin yana fitar da iska mai zafi.

KARSHEN BABI NA TALATIN

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA DAYA

31

Nan ya zauna da kansa kife a kan tebur har mutane suka fara fita daga office din, don haka masinjansa ya tura kofar ya shiga da sallama, sallamarsa ce ta sa Mukhtar din ya dago kai.

‘Yallabai lafiya dai ko? Na ga baka fito ba.’

Ya dan mutssike ido

‘Bacci ne ya dan kwasheni, yanzu zan fito.’

Nan da nan ya tashi ya hada kayansa ya fice daga office din, a lokacin ana ta kiraye-kirayen sallar Magriba.

Har ya kama hanyar gida ya tuna a yanda zuciyarsa take tafasa zai iya jiwa Jamila ciwo, sannan gashi Baba ya ce masa kada ya sake ya kara taba ta da sunan duka, don haka sai ya karkata motar ya nufi Bristol Hotel. Yana shiga ya kama daki; wanka ya fara yi don ya rage zafin da kirjinsa yake yi. Nan yayi sallar Magriba, ya yi order din abinci ya ci ya koshi sannan ya haye gado ya kwanta. Nan da nan bacci ya kwasheshi, bai farka ba sai sha biyu saura, yana farkawa yayi sallar isha'i ya dauko mukullin motarsa ya kama hanyar gida.

Tana zaune a falo zuciyarta sai suya take saboda takaici, tun wajen goman dare take kiransa ya ki ya dauka. Babu wanda take zargi sai karuwarsa da ta kirawo dazu; tabbasa itace ta rike Mukhtar don tayi mata wulakanci kuma ita ta hanshi daukan wayar. Don haka ta ci alwashi duk inda matar nan take gobe zata sa a nemo mata ita don taje ta sameta. Tana zaune tana jiran taga ta inda zai shigo gidan, wajen sha biyu da kwata ta ji motsinsa maigadi ya bude masa get.

Bata ji sallamarsa ba don haka itama bata amsa ba, tana zaune a kan kujera tana jijjiga kafa tana yi masa kallon raini mai cike da alamomin tambaya kala-kala.

Yana shigowa falon ya sa mukulli ya rufe kofar, ya nufo inda take zaune yana goye da jakar computer dinsa, a hannunsa kuma yana rike da shafin wata mujalla. Kafin ya karaso ta mike tsaye

'Wannan wane irin sabon wulakanci ne Mukhtar, sha biyun dare kake shigowa gidan matarka ta sunna kana can wajen matan banza don tsabar wulakanci.'

Kallon takaici kawai yake mata yana jijjiga kai, ya mika mata shafin mujallar da yake hannunsa wanda rubutu ne akayi a kan rayuwar Prof Hajara sai hotonta a tsakiyar shafin daga kasa kuma ga wani hoton nata ita da mijinta Senator Aliyu A. Minjibir.

Ta karba a wulakance, ya nuna hoton senator yace

‘Wannan matar kika kirawo kika ce mata karuwa, ga mijinta sune masu rike da kasar. Suraj ne ya hadani da ita ta sayi computers guda biyu wadanda na san kin gansu, bayan nan kuma tayi order din wasu computers din guda 40 zata zuba a makarantarta Alheri Model Academy, na san kin san makarantar. Duk zagin da kika yi mata tayi recording yana nan na turo miki ta Whatsapp. Ta janye kwangilar computers din da ta bani guda arba’in nayi asarar ribar sama da naira miliyan daya, abinda kika yi mata kuma ban sani ba ko ta hakura ko bata hakura ba amma dai na bata hakuri kuma na gaya mata ba ni na saka ki ba don haka duk wani hukunci da zata dauka a kanki zata dauka. Ai kema babanki mai shari’a ne ne ko? To ki gaya masa abinda kika yi ku zama cikin shiri.’

Ya ja kafarsa da kyar ya wuce ya nufi hawa benen da zai kaishi dakinsa , ya barta a nan tsaye da takardar a hannunta da bakinta a bude.

Ta koma ta zauna a kan kujerar kamar an tura ta, ta dora hannu a ka. Ta sake kallon shafin da ke kan cinyarta; yanzu matar senator ta zaga, Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun! Tabbas ta san Abbanta mai shari’a ne amma na jihar Kano, kuma ma yayi retire. Wannan zancen ma idan Abban ya ji ai ta shiga uku, ba ita ba ko Ummanta ma ba zai kyale ba.

Yanda ya kwanta ya kasa bacci itama haka ta kwanta. Saura kadan ta turawa kaninta lambar matar ya nemo mata inda take Allah ya takaita mata wahala ta kirawo shi wayarsa a kashe; tabbas da ta shiga Babbar matsala. Haka ta kwana tana fatan Allah yasa matar nan ta hakura.

Received at Sakina

Gaba daya gidan ya kacame ana ta shirin biki, Bahijja wadda ‘yar kanwar Hajiya ce Hajiyan take riko ita Aminu zai aura, ita kuma Habiba wadda suke kira Biba 'yar wajen kishiyar Hajiya nata mijin da ban ba dan uwa bane. Gaba dayansu Baba ne zai aura da su don haka ya saka rana lokaci daya. Saura sati biyu bikin don haka Biba da Bahijja sai rabon kati suke.

Biba ce ta leko dakin Hajiya bayan ta gaida Hajiya ta kwalawa Bahijja dake daki kira

‘Anti Ba kin shirya mu tafi?’

Ta fito daga dakin a shirye da jaka a hannu, ta zauna a kusa da Hajiya ta langabe kai tace

‘Hajiya don Allah mu kaiwa Anti Safiyya?’

Biba tace

‘E wallahi Hajiya.’

Hajiya ta bisu da kallon mamaki tace

‘Yanzu har sai an rokeni a kaiwa Safiyya kati, ai ko baku kai mata ba ma ni zan baku na Ummanta ku kai tunda na bikin Saifullahi ma ku na aika kuka kai.’

‘Yauwa Hajiya.’

Suka amsa gaba daya. Hajiya tace

‘Ku hada da na manya ku bawa Ummanta, ga cingam can a kan mudubina Bahijja ki dauko ku hada.’

Har sun fita Hajiya ta sake kiransu tace

‘Wancan leshin da kika ce kawarki ta fasa siya ki dauka na siya a kaiwa Safiyya ace in ji ni don itama ta saka anko.’

Nan da nan da murnarsu suka dauka suka wuce.

Hajiya ta bi bayansa da murmushi tana fatan Allah ya sa Safiyyan ta zo bikin su hadu da Mukhtar, don ita a yanzu babu abinda take so kamar taga Mukhtar ya dawo da Safiyya. Ko ba don yaran ba shi kansa kullum ganinsa take bashi da nutsuwa, gani take kamar zaman lalura kawai yake da Jamila.

Da yake Aminu ne ya kaisu haka suka hadu suka saka Safiyya a gaba sai da tayi musu alkawarin zata zo launching din; wanda biki ne da gaba daya 'yan gidan suke haduwa. Don har dinki ma Aminu yace ta kawo su kai mata tace su barshi zata kai.

Haka Umma ta saka ta a gaba a kan lallai sai ta cika alkawi domin itama idan dai kalau take; da yake yanzu tana fama da ciwon gwiwa; tana son ta jewa Hajiya don bata je na Saifullahi ba lokacin tana jin zafin sakin da aka yiwa Safiyya.

Tun bayan da ya bata wannan shafin mujallar bai sake shiga harkarta ba, haka yayi banza da ita. Tana ta addua kada a zo nemanta kuma tana jin Allah ya amsa don gashi yau kwana biyar shiru.

Abu daya ne yake damunta yanda Mukhtar ya daina shiga harkarta kuma ya daina fita daga gidan, don ko aiki ma tun ranar da ya shigo sha biyun dare bai sake zuwa ba.

Yana kulle a dakinsa, idan lokacin abinci yayi sai dai taga ya fita ya shigo da abinci a leda ya wuce dakin, in ya gama ya fito da su ya sa a shara. Kwanansa biyar a haka yau, abun ya isheta kada ma taje matar sawa tayi aka koreshi daga aiki daga dan wannan abun.

Don haka yau tayi niyyar idan ya fito karbar abincin sa a waje ta tare shi sai ya gaya mata abinda yake ciki.

Tana sallah ya fito ya karbo abincin rana don haka tana idarwa ta zauna tana jiransa ya sauko zubar da ledojin.

Jimawa kadan ya sauko ya kai sharar waje ya dawo.

Sai da ya zo tsakiyar falon sannan ta mike ta sha gabansa, ya kalleta ba tare da ya ce komai ba don haka tace

‘Mukhtar don girman Allah ka zauna muyi magana.’

Ba tare da yace komai ba ya matsa ya zauna akan kujera ya zuba mata ido, ta biyo bayansa itama ta zauna. Suka hada ido ta sunkuyar da kai, ta sa hannu ta share kwallar da ta taru a gefen idonta tace

‘Don Allah ko ma me nayi kayi hakuri, idan ma so kake naje na bawa matar nan hakuri to ni ka kaini inda take.’

Ya kawar da kai kamar ba zai yi magana ba, jimawa kadan kuma yace

‘Ni kam tace bata son ta sake gani na, ke kuma idan tana son ganinki ta san yanda za ayi ta sameki ke dai kawai ki zama cikin shiri.’

Ta sunkuyar da kai ta goge hawaye, jim kadan yace

‘Idan babu wani abun kuma zan wuce daki.’

Ta kai hannu ta dafa cinyarsa

‘To don Allah ka daina zaman daki, ina girka abinci kuma sai ka dinga siyowa? Naga har aiki ma ka daina zuwa, ko hutu aka yi?’

Ya tabe baki

‘Ai na hakura, shi yasa na zauna a dakin, aikin ma na hakura dashi resignation letter zan rubuta na bayar sai na dawo na zauna a gida. Kinga idan kina kallona kina kula dani babu wadda zan kula balle ki dinga bin matan mutane kina zagi. Yan kudin da suka yi min saura da abincin dake gidan idan suka kare na san ko a gidanku ba zaki kasa karbo mana tallafi ba ko?’

Ta sake fashewa da kuka, ta sauka daga kan kujerar ta durkusa a kafarsa tana rusa kuka

‘Don Allah kayi hakuri, ai nace ba zan kuma ba, wallahi kuma da gaske nake.’

‘Mtseewww!’

Ya mike ya kewayeta ya koma dakin.

Haka ya cigaba da shareta, sai dai kawai yana fita yamma yaje gidan Baba.

Ana ta Shirin biki don haka ya san dole za a nemeshi.

Ko da yaje gidan ma sai da Baban ya tambayeshi ko lafiya ya kwana biyu bai zo ba, haka ya shirga karya yace aikine yayi masa yawa gashi kuma yayi zazzabi.

Saura kwana uku bikin ya kawo mata kati tunda dama ya riga yayi mata anko kuma ta riga ta dinka. Bayan ya bata katin tace

‘Ma Sha Allah, Allah ya sanya alkhairi.’

‘Amin. Duk wanda ba zaki je ba sai ki tanadi uzirin da zaki bawa Hajiya don na gaya musu ke da Halimatu lafiyarku kalau.’

Ya wuce ya barta a wajen.

Ko lafiya kalau ake zaune ita din ba mace ce mai son shiga mutane ba, kuma bata fiya kula mutane ba. Tunda ya dauke su Nana bata je gidan ba, domin ko yawon arba’in bata je ba saboda kunyar abinda ta aikata. Ko Hajiya rabonta da ganin Halimatu tun tana kwana biyu da haihuwa, har saida ta iya zama ta fara cin abinci sannan yake daukanta ya tafi da ita idan zai je da yamma.

……..

Kamu aka fara yi ranar Alhamis, bayan ya dawo daga aiki yaci abinci ya shirya zai fice. A shirye ta sauko dauke da Halimatu tace

‘Mun shirya, bari mu fito ka kai mu wajen kamun.’

A gida suke yin kamunsu don haka gidan Hajiya ya wuce dasu. Gidan ya cika makil da dangi, yanda ta zata za a ki kulata ba haka bane domin duk an gaggaisa. Hajiya ma tana ta haba-haba da su tana nunawa dangi amaryar Mukhtar da Halimatu. Dama duk mutan gidan basu saba hira da ita ba saboda ita din ba mai hira sosai bace, don haka dai ta nemi waje a falon Anti ta zauna. Sai bayan isha’i ya daukota suka dawo gida.

Washegari ranar Juma'a itace ranar launching wanda ake yi a event center. Babban waje ne aka kama wanda aka cikashi da kujeru ga kwalliya sai kyalli wajen yakeyi. Yanda ‘yan mata sukayi ankon shudin leshi haka 'yan mazan gidan suka sha farar shadda, wajen zaman mata da ban da inda maza suka zauna.

Kusa da matar Saifullahi Jamila ta zauna inda suke tare da wasu ‘yayan wan Baba.

Sai bayan Amare da angwaye sun shigo sannan ‘yan mazan gidan suka shigo. Daga inda su Jamila suka zauna tana hangen Mukhtar, duk da bata jin zai kula ‘yan mata a bikin gidansu amma dai ta san maza suna da dabara kala-kala ta yanda zasu sami lambar ‘yan mata don haka duk abinda ake yi hankalinta yana kansa.

Har ya kau da kai ya tuna kamar Safiyya fa ya gani a cikin mutanen da suke shigowa, ba tare da bata lokaci ba ya sake kallon wajen. Ya kasa dauke idonsa daga kanta, tare suka shigo wajen ita da Hamida.

Siket ne ta dinka da leshin six-pieces da riga fitted, ga mayafinta Mai ruwan gwal ya sha duwatsu sai kyalli yake, takalmin da ta saka ya dan kara mata tsawo ga 'yar karamar jakarta wadda ta rike a hannunta da yasha agog da zobba masu kyau. Babu make-up a fuskarta don dama ita bata saba yin makeup din ba, amma ta gyara fuskar fes, tayi haske ga fatarta har wani kyalli take.

Teburin da yake zaune yana daga gefe a cikin hall din, a hankali suke tafiya suna waige-waige kamar masu neman wani. Da gudu Nana ta bullo daga cikin mutane ta fada jikin Safiyya. Tayi murmushin da shi kansa sai da ya saka shi murmushi; yayi kewar Safiyya shi kanshi bai san me ya hanashi komawa su mayar da aurensu ba amma in sha Allah yana ganin yanzu lokaci yayi.

Received at Sakina

Idonsa yana kanta. Nana ta ja hannunsu ita da Hamida suka shiga cikin hall din. Da wuri Hamida ta zauna da ta sami teburi a wajen ‘yan mata. Ita kuwa Safiyya ko ta zauna sai wasu ‘yan uwan nasa su hangota a daga mata hannu ta tashi taje su gaisa. Haka ta karasa teburin su Anti da kannen Hajiya ta zube har kasa ta gaishe su.

Sai yanzu ya gane ba wai kansa kawai ya cuta da ya rabu da Safiyya ba harda danginsa, yanda suke haba-haba da ita bai taba ganin suna yi da Jamila ba; duk da ita Jamila a dabi’arta dama ba mace ce mai son shiga mutane ba kuma bata kai Safiyya fara’a ba.

Sai da ya san yanda yayi ya kirawo Nurain ya rada masa idan Mama zata tafi ya zo ya gaya masa.

Can wajen karfe bakwai da rabi suka mike ita da Hamida, sukayi sallama da amare sannan suka dawo Safiyyan ta tsuguna tayiwa su Anti sallama. Suka kamo hanyar fita tana rike da Nana yayinda su Na’ima 'yan gidan su Bahijja suka mike don yi musu rakiya.

Suka fito suna hira har suka fito bakin kofar hall din, Safiyya ta mikawa Na’ima hannun Nana tace

‘Ga ‘yarki nan Anti Na’ima ku koma mu mu wuce.’

A daidai nan Mukhtar ya fito yana rike da hannun Nurain wanda yayi wa Safiyya sallama ya koma da su Na’ima, suka wuce suna yiwa Mukhtar dariya.

Kafin ya gama tsayawa gaban Safiyya Hamida ta bar wajen saboda takaici. Ita kuwa Safiyya da murmushinta suka gaisa, bayan sun gaisa yace

‘Kina nan Safiyya? Kin buya?’

Tayi murmushi

‘Yanzu da dalili yazo ai na fito. Ya aiki ya family? Na ga Halimatu ta zama budurwa, Allah ya raya mana.’

‘Amin ya Allah, bari na samo yaro sai a kaiku gida.’

‘Ah, ai Sabir ne ya kawo mu a motar Yaya Habibu gashi can ma ni suke jira.’

Ta fada tana nuna masa inda Sabir din yake.

Ya dan taka mata, kafin su karasa motar sukayi sallama ya koma ciki ita kuma ta shiga mota.

Tana zama a motar Sabir ya fara mita

‘Yaya Safiyya don Allah ki daina yiwa mutumin nan dariya, Haba mana. Idan Baban Muhammad ya gani ai ba zai ji dadi ba.’

Kafin ta bashi amsa Hamida tace

‘Eh wallahi Yaya Safiyya, dan rainin hankali kawai. Sai wani faman yagewa mutane baki yake babu kyan gani.’

Tace

‘Ikon Allah, shikenan kuma ba fada sai na hau gaba da mutum?’

Sabir yace

‘Ki dai daina kulashi Yaya Safiyya, wannan yawan fara’ar taki dole ma ki koyi shan kunu.’

Ta kyalkyale da dariya, ya ja mota suka fice daga wajen. Suna tsayawa a danja almajira ta taso tana masa bara, ya mikawa Hamida hannu yace

‘Hamee bani Murtala in yi sadaka Allah ya raba mu da mugun ji da mugun gani kin ji.’

Ya saka mishi nera hamsin Safiyya na masa dariya, ya mika sadakar suka wuce gida.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA DAYA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA BIYU

32

Duk wani motsin Mukhtar a wajen bikin nan Jamila tana kallonsa, tana kallon yanda ya dinga bin duk wani motsi na Safiyya da ido haka kuma tana kallon lokacin da ya ja Nurain suka bi bayan Safiyya. Don haka ranta ya gama baci kafin a tashi daga wannan taron. Bata sani ba itama Safiyyan nemanta yakeyi ko kuwa dawo da ita zai yi. Ko ma dai menene dole ta kora masa jawabi domin ko dawo da Safiyyan zai yi bazata yarda ta zauna da ita a wannan gidan ba sai dai ya nemi wani gidan ya ajiyeta a can.

Sai wajen tara da rabi na dare aka tashi daga taron, kafin ma ya fito Jamila tana jiransa a bakin mota tana dauke da Halimatu. Sai da kannen Hajiya suka fito su hudu suka shiga bayan motar sannan ita ta shiga gaba suka kama hanya.

Har suka isa kofar gidan Hajiya bata ce komai ba, shi kadai yake hirarsa da ‘yanuwansa. Bayan sun sauka daga motar tayi musu sai da safe ya juya motar suka kama hanyar gida.

Yanda yake ta faman walwala yana yiwa Halimatu wasa shine abinda ya kara bata haushi, ta manta rabon da taganshi cikin walwala haka. Tun da ta kirawo matar nan

rabon da ya kulata, ko Halimatu ma bai fiye yi mata wasa sosai ba. Amma gashi yanzu daga yaga tsohuwar matarsa ya fara walwala harda wasa.

Yanda ta maka masa kofar motar bayan ta sauka ya isa ya sa ya fahimci akwai matsala, amma da yake hankalinsa baya wajen bai ma san tana yi ba.

Sai da ta samu Halimatu tayi bacci sannan ta wuce dakinsa. Yana zaune a gefen gado yana ta faman latsa waya ta shiga, tana shiga ta zauna a kan kujerar zaman mutum daya da take dakin. Bata ce masa komai ba, shima kuma da yake batayi sallama ba ta shiga bai ce mata komai ba kawai ya cigaba da abinda yake yi.

Sai da ta numfasa tace

‘Mukhtar.’

Ya dago ya kalleta.

Cikin izgili tace

‘Meye na ga kana ta wani bin Safiyya a wajen biki, naga dai yanzu babu aurenka a kanta ko?’

Yayi ‘yar dariya

‘Kwarai babu aure amma ina fatan kin san ina da damar na sake aurota ko? Ina kuma fatan kin san itace uwar ‘yayana don haka kin ga dole na bita ko?’

‘Ni da ba uwar ‘yaya ba! Ina fatan dai idan ka sake aurotan ba nan zaka ajiye min ita ba don babu matar da zan zauna da ita a wannan gidan, kuma Allah ya sa kada a bige da aure a shiga lalacewa kuma.'

Ta fada tana mikewa don ta fice ta bar masa dakin.

Nan take ya hade fuska ya mike ya sha gabanta yana nuna ta da yatsa yace

‘Kada ki sake ki taba mutuncin Safiyya idan kina son zaman lafiya kin ji na gaya miki, kuma in na kawota gidan nan kina iya ficewa tunda dama ban taba rufe miki kofa na hanaki fita ba.’

‘mtsewwww!’

Ta ja tsaki, ta juya ta fice ta bar masa dakin.

Ya koma ya zauna a kan gadon; ya za ayi ma ya hada Safiyya da Jamila a gida daya, ai ba zai ma yiwu ba. Yanda Safiyya take girmamashi tana kula dashi ba zai hada ta da Jamila ba ta ga yanda ake wa miji wulakanci itama ta koya. Dole ma ya nemi gida ya siya a nesa da wannan unguwar, ko babu komai ya sami inda zai dinga nutsuwa tayi ta fitnarta ita kadai.

Ya dauki lokaci yana kokarin samun Safiyyan a WhatsApp amma ya gagara, sai daga baya ya gane tayi blocking dinsa. Har ya dauki layinsa wanda bata sani ba zai kirata sai kuma ya fasa, gara ya bari kawai tunda in sha Allahu jibi Lahadi idan aka gama biki zai je ya sameta a gidansu.

……..

Tunda gari ya waye yake Allah-Allah dare yayi domin yaje ya sami Safiyya, yanda ya ganta ya san ba zata bashi matsala ba in sha Allahu. Dama ya san Safiyya bata da fushi da yawa.

Yana idar da sallar la’asar kuma ya canza shawara; yasan yanzu haka tana da zawarawanta da suke zuwa zance da daddare don haka gara ya je bayan sallar la’asar ya sameta a nutse.

Nan da nan ya dauki mota ya fice, ya cewa Jamila ya tafi gidan Hajiya. Gidan Hajiyan ya fara tsayawa don haka sai wajen biyar sannan ya wuce gidansu Safiyya.

.....

Kamar yanda ya sabarwa kansa in dai zai wuce Abuja yana tsayawa yayiwa Safiyya sallama, kuma shi dama baya zuwa zance da daddare. Ya gaya mata in dai yana gari toh baya son fita da daddare ya fi son ya zauna a gidansa tunda yana dadewa bai hadu da yaransa ba, wannan shine lokacin hirarsu.

Jirgin karfe takwas na dare zai bi don haka yana idar da sallar la’asar ya sa direbanshi ya tukoshi suka taho wajen Safiyya; don in ya gama ya koma gida kafin dare yayi maman Muhammad ta kaishi airport ita da yara.

Inda suka saba zama nan suka zauna, sai da biyar ta gota sannan yace mata zai tafi, don haka ta mike domin ta rakashi bakin get kamar yanda ta saba.

Shine ya fara fitowa ta karamin gate din tana biye da shi suna ta hirarrakinsu cikin fara'a. A dai-dai wannan lokacin kuma Mukhtar ya karyo kwanar gidan, idonsa a kan get din. Ko ba a gaya masa ba ya san Safiyya ce waccan dan fes yake hangosu, ya sauka daga kan titi ya tsaya a gefen hanya yana mamaki don duk wanda ya hangesu ya san soyayya suke yi.

Tana sanye da abaya ta yane kanta da karamin mayafi mai ruwan omo sai kallon mutumin take tana masa murmushi; irin murmushin da bai taba zaton Safiyya zata iya yiwa wani ba idan ba shi ba.

Safiyya ta dubi Baban Muhammad tace

‘Toh mijin barrister sai yaushe kenan za a sake zagayo mu?'

Ya kyalkyale da dariya yace

‘Ni ‘da su! Yau kuma mijin barrister na koma?'

‘To ai dolene ace da mijin iya Baba.’

‘Shikenan kuma za a kashe ni da Hausa.’

Itama tayi dariyar.

Suka jero tare suka nufo dalleliyar motar da take ajiye daga gefe wadda direban yake zaune a kan booth din baya.

Kafin su karaso direban ya sauka ya zagaya ya tsaya a gaban Baban Muhammad ya sara irin yanda sojoji sukeyi, ya mika hannu ya bude masa kofa. Yayi sallama da Safiyya ya shiga mota. Ba a ja motar ba har saida Safiyyan ta shiga gida ta rufe get din.

Tana rufe get din ya kifa kansa a kan sitiyari motar, ji yake kamar wani abu ya tokare masa zuciya. Bai taba sanin yana da kishi haka ba sai yanzu, domin ko da Safiyya tana budurwa bai taba ganinta da wani ba. A yanayin da yake ciki ba zai iya tunkararta a haka ba don haka ya gwammace ya tafi ya sake dawowa wata ranar.

Don haka ya karya kan motarsa ya juya ya nufi gida. Duk da bai ga fuskar mutumin sosai ba amma ya san ba wani girmansa yayi ba a shekaru,sai dai ko ya nuna masa kudi don ya ga ma kamar soja ne. Kuma da alama Safiyyan tana sonshi; lallai akwai aiki.

……..

Tunda Fatima suka daidaita da Ahmad sai kuma ta shiga fargaba da adduar Allah ya sa kada ya gane ita din ba budurwa bace. Duk sati sai ya zo daga Abuja, duk dangin su Fatima an san shi domin bai fi sati hudu da fara zuwa ba ya sa Ibrahim ya hadashi da dan rakiya suka je ya gaida ‘yan uwan mahaifinsu dake nan Zariyan.

Nan da nan ta manta da maganar Mukhtar domin sosai take son Ahmad. Kuma da yake duk wani bincike da za ayi an gama yi gaba daya an yi na’am da shi.

Yau Asabar, tun safe take shirin tarbarsa; duk da baya yarda yaci abinci a gidan toh takan yi masa wani snack wanda ko bai ci ba sai ta juye masa a container ya tafi da shi. Yau din ma cake tayi masa ga kuma kunun aya mai sanyi.

Sai wajen sha daya ya karaso, suka zauna a falon da suka saba zama. Sun dan taba hira kadan ya dubeta ya cika bakinshi da cake yana shafa ciki yace

‘Kina bani kayan dadi da yawa fa, zaki sa tumbin kudina ya kara tsini.’

Ta kyalkyale da dariya

‘Babu komai kudin ma sai su karu.’

Jimawa kadan yace

‘Zamu je Dubai next week daga office, zamu je wani conference daga nan kuma zamu yi wani short course. Sai bayan sati hudu zamu dawo. Amma na gayawa Ibrahim kafin na tafi za a kawo kudin aure in ya so da na dawo sai a fara shirin biki.’

Ta dago ta kalleshi suka hada ido sai kuma ta sunkuyar da kai. Yace

‘Ko baki shirya bane tayi Daria

‘In dai ka shirya nima na shirya.’

‘Yauwa, ranar Laraba za a kawo don ranar Alhamis zamu wuce.’

Suka karasa hirarrakinsu yayi mata sallama a kan sai ya dawo zasu hadu.

.....

Kamar yanda ya gaya mata kuwa ranar Laraba iyayen Ahmad suka zo da kudin aurenta, gidan kanin Babanta wanda shine waliyyinsu a nan aka karba duk da Ibrahim ma yana wajen.

Cikin karamci da mutunci akayi aka gama, suka bayar da kudin aure naira dubu dari biyu. Da kyar suka karbi tukwicin da aka basu suna cewa

‘Su ai an gama yi musu tukwici tunda aka basu Fatima.’

Suka tafi a kan da ya dawo za su kawo kayan aure a sa rana.

Haka suka rabu ana son barka.

.....

Tunda Yaya Ibrahim ya dawo da kudin auren Fatima ya kuma ya tabbatar mata za a sa rana da zarar Ahmad ya dawo ta sake shiga damuwa. Duk wani abu da akeyi na shirya amarya ta san Mommy zata yi mata sai dai ta san Mommy bata san ta rabu da budurcinta ba don haka shirin budurwa zata yi mata.

Sai a lokacin ta kara nadamar sakarwa Mukhtar kanta, gashi ko ba a gaya mata ba ta san tana dauke da ciwon sanyi don lokaci zuwa lokaci tana ganin alamomin a jikinta.

Ko ba zata nemi na gyaran ba ta san ko a boye dole ta nemi maganin da zai rabata da wannan sanyi, domin idan taje da shi ya zama wanda ake iya dauka ne ta sawa Ahmad bata yi masa adalci ba.

Nan da nan ta sake shiga damuwa. Sai bayan kwana biyu dabara ta fado mata; makarantar da take koyarwa akwai wata malama maman Haidar; wadda bata fi shekarunta ba duk da ita tana da aure, don haka ta yanke ita zata tambaya tunda suna shiri sosai.

Ranar Juma’a tana shiga makaranta ta ja Maman Haidar, bayan tayi mata bayanin abinda take so ta dubeta tace

‘Ke kuma me ya hada ki da maganin sanyi?’

‘Uhm, kin san zaman hostel nayi, kuma nan da ‘yan watanni za a yi bikina. Kin san duk wanda yake shiga bandakin nan na hostel baya rabuwa da cututtuka.’

‘Hakane kawata, ai kuwa da gaskiyarki. Zan kuma hadaki da wadda zata baki maganin sanyin dan gaske don in dai kin yi amfani dashi yadda tace to babu ke ba sanyi in sha Allah don na gwada maganinta kuma na ga aikinsa.’

Ta yagi takarda ta rubuta mata lambar waya 07039080978, 09077591726. Ta mika mata takardar tana fadin

‘Farida Abdallah kenan, tana nan a Kaduna. Ki kirawota duk wani bayani zata yi miki muma kina tura mata kudi zata aiko miki da kayanki har nan Zazzau.’

Ta karba tayi mata godiya.

Kasa daurewa tayi taje gida don haka ana yin break ta kirawo ta. Kafin a tashi sun gama ciniki ta tura kudi. Don haka kafin magriba sakonta ya iso wanda tace a kirawo Maman Haidar ta karbar mata.

.....

Bata fi kwana biyar da fara amfani da kayan Farida ba taji sauyi a jikinta don haka ta kara dagewa. Na gyara kuma ta bari a kan sai ta gama da na sanyin sai ta nemi na matsi wanda zai matseta tsam.

.....

Duk yanda Mukhtar yake jin ganin Safiyya zai yi masa sauki abun ya ci tura, ya koma ranar litinin da yamma aka ce masa bata nan wanda kitso taje wani gida a hotoro daga nan kuma ta tsaya a gidan Baban hotoro har sai dare ta dawo.

Har ciki ya shiga ya gaida Umma, suka gaisa itama tana haba-haba. Bayan ya tafi Hamida take fadan yanda Umman ta sakar masa fuska, Umma tace

‘Yarinta ke damunki, ai kuma baku isa kuyi fada dashi ba tunda dai shine uban ‘yayanku Nana da Nurain. Kuma ko don kuyi musu kara ai kwa girmamashi ko da baya auren Safiyya.’

Ranar Talata ma haka ya koma, nan kuma tun kafin ya karasa kofar gidan ya hango wata dalleliyar mota a bakin gate, wadda saurayin Hamida ne wanda zai aureta ya zo da ita.

Duk da ba itace motar da yaga bazawarin Safiyya a ciki ba amma sai ya dauka shi ya zo da ita, don haka nan da nan ranshi yayi matukar baci. Ya karya kan motar ya koma zuciyarsa tana ta turiri.

Gaba daya a cikin damuwa ya kare satin, yana tsananin son ganin Safiyya gashi tayi blocking layinsa ko ya kirata bata shiga. baya jin zai iya barinta wani ya aureta a halin yanzu; Safiyya tashi ce shi kadai in sha Allahu.

Sai ranar Juma’ah bayan ya dawo daga masallaci, yana tsaye a mota a bakin gate kafin ya shiga gidan ya dauki karamar wayarsa ya kirawota da layinsa wanda yake jin batayi blocking ba. Ai kuwa yana kira ta shiga, sai da ta kusa tsinkewa sannan ta daga. Tana yin sallama ya saki murmushi saboda jin dadi, bayan sun gaisa yace

‘Safiyya ina kika shiga ne nake ta nemanki, tun ranar Lahadi sai yanzu na sameki.’

Tayi ‘yar dariya

‘Ni din wai? Ina nan a gida watakila baka nemeni bane.’

‘Hmm! To yanzu ya za ayi Safee? Ina son ganinki.’

‘Ai gani ko? Ina sauraronka? Ya yaran dai?’

‘Suna nan lafiya kalau, ai kin gansu ranar Juma’ah ko?’

‘Eh haka ne kam.’

‘To yanzu yaushe zan zo?’

‘Au wai ta wayar ma haka bai isa ba? Inaga ai zaka iya zuwa duk lokacin da ka shirya.’

‘A’a, ki dai gaya min ranar da idan na zo zan sameki ko? Don maganar da nake son mu tattauna da ke mai mahimmanci ce sosai.’

‘Ok, to kazo gobe.’

‘Karfe nawa?’

Cikin kosawa da mamaki tace

‘Daga bayan azhar har dare ina nan.’

Har sun yi sallama yace

‘Safiyya.’

‘Na’am.’

‘Zunubin da nayi kika yi blocking din main layina na tuba please ki bude ni.’

Tayi dariya

‘To in sha Allah.’

Sukayi sallama suka ajiye waya yana ce mata sai goben.

Ta ajiye wayar a gefenta tana dariya a ranta tace; ko menene ake nemana oho. Bata yi tunanin zai zo yace yana sonta ba ko daya don yanda taga ya banzatar da

ita bayan rabuwarsu ta zata ya gama da ita. Duk da dai da suka hadu a wajen biki ta kula da wata rawar jiki da yake. Ko ma dai menene tana jiranshi ya zo taji.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA BIYU.

Talla:

Idan kina son maganin sanyi Mai kyau da inganci ki nemi Farida Abdallah, tana Kaduna Kuma tana aikawa ko Ina. 07039080978, 09077591726.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA UKU

33

Tun safe yake shirin zuwa wajen Safiyya yana bitar kalaman da zai tsarata da su, la’asar tana yi ya shirya ya kama hanya. Yana tsayawa a kofar gidan ya gwada kiranta inda ya samu har yanzu bata bude layinsa da ta toshe ba, yayi murmushi ya dauki karamar wayar ya kirawota. Kafin su gaisa ya ce mata yana kofar gida amma yana so ya shigo ya gaida Umma, Sabir baya nan don haka Hamida aka tura tana ta faman zumbura baki ta shigo da shi. Bayan ya gaida Umman ya koma waje, Safiyya ta fito ta bi bayansa.

Tana zama ya dubeta yace

‘Kin ki ki bude layina da kika yi blocking, yanzu ma sai da na kira shiru.’

‘La! Ka san mantawa nayi, bari na shiga gidan don wayar tana ciki.’

Yayi murmushi sannan suka gaisa, suka dan yi jim tana sauraronsa, ya dan yi gyaran murya yace

‘Safiyya, ya kwana biyu?’

Da murmushi ta amsa, murmushin da yake kara masa karsashi yana ganin kamar Safiyya tasa ce shi kadai

‘Alhamdulillah.’

Suka sake yin shiru na dan lokaci, jim kadan yace

‘Abubuwa da dama sun faru Safiyya, wanda na san nine mai laifi shi ya sa ma na zo na baki hakuri kuma na nemi yafiyarki.’

Ta dan kau da kai sannan ta dube shi

‘Ni dama ban rike da komai ba, idan kuma da hakkina a ciki ma tun tuni na yafe. Allah ya yafe mana baki daya amma ni in dai nice komai ya wuce.’

Sosai ya ji dadin maganganunta musamman da yake har yanzu cikin fara’a take zancen. Jimawa kadan kuma yace

‘Alhamdulillah, nagode. Kinga kenan ba zamu sami wata matsala ba wajen mayarda aurenmu ko?’

Ta kalleshi da mamaki a fuskarta, ta yi ‘yar gajeriyar dariya

‘Wane aure Kuma? Wanda aka gama tun shekaru uku ko fiye? Ai ina ga mun gama aure ni da kai ko?’

A take yanayinsa ya canza, da muryar lallashi yace

‘Kada kice haka Safiyya, idan baki manta ba tun a lokacin na gaya miki zan dawo mu mayar da aurenmu ko? Ai k...'

‘Ikon Allah, to da ni din ka zata riga ce da ka rataye wadda kake da damar ka dauka ka mayar a lokacin da ka ga dama?’

Ya kalleta na dan lokaci ya jijjiga kai

‘Me yayi zafi haka? Ai kin fi karfin haka a wajena. Na san na yi kuskure kuma ban kyauta ba, shi yasa ma na fara da baki hakuri. Inaga kamar ni nafi dacewa dake kamar yanda ke kika fi dacewa da ni, ko don yara ai kya tausaya mana.’

‘Mukhtar kenan, kai ma ka kasa tausayawa yaran balle ni da dama tun kafin nayi aire na san duka binda zan haifa na ubane, haihuwarce kawai tawa?’

‘Kada ki ce haka Safee, don Allah ki yarda ki dawo dakinki. Duk ma wani abu da nake yake sosa miki rai na bari kuma nayi miki alkawarin ba zan sake ba. Kum.....’

Ya fara bata haushi don haka ta daga masa hannu tace

‘Bari kaji Mukhtar, in dai aure ne da ni kai in sha Allahu ya kare. Wato lokacin da ka koroni kace na fice maka gida tabbas na shiga damuwa ba kadan ba, don ban taba zaton zan iya rayuwa babu kai ba. Kusan shekara daya zuwa biyu bayan ka sakeni tabbas da ka dawo a shirye nake da na koma gidanka ko da kuwa nice zan baka sadaki. Amma a halin yanzu na gane soyayya ta fi zuciyarka yalwa haka kuma duniya ta fi gidanka fadi, ba zan taba iya sake aurenka ba Mukhtar. Allah ya tsari gatari da saran shuri!’

Ya bude baki zai katseta ta daga mishi hannu ta cigaba

‘Kayi aurenka ma Alhamdulillah, don haka inaga baka ma bukata ta a rayuwarka tunda ma ka ga kai din ba ka cikin mazan da zasu iya hada mata biyu. Ba sai mun batawa junanmu lokaci ba Mukhtar, ba zan taba sake aurenka ba don haka mu bar wannan maganar. Dole yara sun hada mu ba zan yanke hulda da kai ba, amma don Allah mu cigaba da ganin mutuncin juna kawai ya isa.’

Tayi shiru yayinda shima yayi shiru yana binta da kallo. Ya sa hannu ya Shafa kansa, gaba daya ta goge masa haddar kalaman da ya shiryo don ya tsarata da su. Ya jijjiga kai yace

‘Haba Safiyya! Baki ma saurareni kin ji da me na zo ba kika yanke wannan hukunci.’

Sai da tayi dariya sannan tace

‘Uhm, duk wata kalma da kazo da ita na san ta na ji ta bazata yi tasiri a kaina ba. Kada mu batawa junanmu lokaci, mu bar wannan zancen kawai.’

Binta kawai yake da kallo ya rasa me zai ce mata.

Jimawa kadan tace

‘Bari na koma gida yanzu zaka ji kiran magriba.’

‘Hakane.’

Kafin ya mike ta mike, sannan ya tashi da kyar kamar wanda aka yiwa duka yana faman binta da kallo.

‘Ka gaida yaran da su Hajiya.’

Ta fada tana shirin juyawa ta shige gida.

‘Safiyya.’

Ya kirawo sunanta, ta juyo suka tsaya suna fuskantar juna sannan yace

‘Kada ki zata wannan maganganun da kika gaya min zasu sa na rabu dake, in sha Allah baki da miji sai ni daga nan har Aljannah. Don haka zan dawo kuma zan yi duk abinda zan yi naga na mayar dake dakinki.’

Tayi murmushi kawai ta jijjiga kai

‘Sai an jima.’

Kafin yace wani abu ta wuce cikin gida.

Ya bi bayanta da kallo yana mamaki, shi bai ma taba sanin Safiyya zata iya tsayawa ta karanta masa magana kamar haka ba. Lallai Safiyyan ta canza, canjin kuma ya

burgeshi; dole ma ya san yanda zai yi ya tsaro Safiyya domin ita din tashi ce shi kadai.

.....

Tana shiga gida ta sami Umma ita kadai a falo, bayan ta amsa sallamarta har zata wuce daki Umman tace

‘Zo nan Safiyya.’

Ta dawo ta zauna a kasa gaban Umman. Sai da ta dan kare mata kallo sannan tace

‘Neman me yake miki Abban Nurain din?’

Ta kau da kai sannan tace

‘Uhm! Wai so yake ya sake aurena.’

‘To kinga idan gidan nashi zaki koma sai ki gayawa yayanki ya nemi Baban Muhammad a dakatar dashi.’

A firgice ta kalli Umma kamar wadda aka tsikara da allura

‘Umma ba zan sake aurensa ba, ko da Baban Muhammad ya fasa aurena ba zan sake auren Mukhtar ba. Allah ya kiyaye.’

Umma ta kama Haba tana mamaki

‘Me yayi zafi haka, ko yaran ai kwa duba. Kina dai jin yadda matar tasa tayiwa Nana.’

‘Hmm! Umma shima bai duba su ba lokacin da ya koro ni, in sha Allah babu abinda zai samesu.’

‘Ai shikenan Allah ya zaba muku abinda yafi alkhairi gaba dayanaku.’

Ta amsa da Amin sannan ta mike ta shiga daki domin yin sallar Magriba wadda an riga an fara kira.

Bayan ta idar da sallar Magriba nan ta zauna a kan daddumar tana tunani kala-kala; ko babu maza a duniya ba zata sake auren Mukhtar ba, duka wani so da take masa ya kare ba zata sake iya zama da shi ba. Tabbas wani lokacin tana jin kamar ta koma don yaranta, tana shiga damuwa idan ta tuna dasu musamman bayan da taji labarin dalilin dawowarsu gidan Hajiya. Tana tunanin tarbiyyarsu, duk da tana yi musu addu’a amma wataran tana jin kamar ta koma don ta cigaba da kula da su.

Sai dai idan tayi tunanin akwai yiwuwar ta kare ragowar rayuwarta a cikin kunci kuma ga cututtuka da zai yi ta kwasowa yana saka mata, sannan kuma ga yanda abinda yakeyi da yaran mutane zai iya tasiri a kan nata yaran da yanda idan sun girma zasu shiga damuwa idan suka gane halin mahaifinsu sai taga gara ta hakura da shi. Su biyun kuma tana musu addu’a kuma duk lokacin da ta sami dama in sha Allah zata dawo dasu wajenta. Kai ba zata iya sake komawa gidan Mukhtar ba.

Ta daga hannunta sama ta yi addua a fili

‘Ya Allah, Ya Hayyu Ya Kayyum kada ka jarrabeni da sake auren Mukhtar ko wani mazinacin Ya Allah.’

Ta tuno alwashin da yaci a kan dole ya san yanda zai yi ya mayar da ita dakinsa, ta san dai baya bin malamai amma mutumin da yake zina bata jin akwai abinda zai gagareshi aikatawa.

Akwai adduar da Malam ya basu a islamiyya ta kariya daga sihiri da kuma ta karya sihirin, duk da bata rubuta ba amma in sha Allah gobe idan taje islamiyya zata tambayo Malam don dolene ta dauki matakin kare kanta.

Duk da ya shiga damuwa saboda yanda Safiyya taki amincewa da shi haka ya daure ya cigaba da shirinsa na zuwa conference dinsu na ICAN wanda wannan karon a Lagos za a yi shi. Kwana biyar ake gama conference din amma wannan karon kwana goma yake son yi don ya huta, saboda ‘yan kwanakin nan damuwa tayi masa yawa kansa ya cushe.

Ya riga ya gama shiryawa da Felicia wdda dama ita a Lagos din take, ya hadu da ne a Abuja kuma tun daga lokacin ya zama in dai zata zo Kano shi zai sauketa tunda shima tana biya masa tasa bukatar.

Ya biya kudin registration dinsa dana hotel duk ya gama biya saboda saura kwana hudu taron.

Yana zaune a falonsa kan teburinsa na karatu yana aiki a computer, aiyuka ne da yake son ya gama ya bari a office saboda kar a nema baya nan.

Ta kofar da take shigowa daga dakinsa ta shigo falon, bayan ya amsa sallamarta ta wuceshi ta zauna. Ta dauki remote ta dan kara volume din TV sanna ta dubeshi tace

‘Aiki ya ki ya kare to a barwa gobe mana.’

Yayi dariya yana kallon computer din yace

‘Ba zaki gane ba, so nake na tattara aiyukan nan kada a nemeni. Au ashe fa ban gaya miki ba, ranar Lahadi mai zuwa zamu tafi conference Lagos.’

‘Lallai, ka ma manta da ni, last year ai cewa kayi da ni zaka je wannan conference din kuma ni a shirye nake.’

Ya kyale computer ya taso ya dawo inda take ya zauna.

‘To ke yanzu ina zaki je wani taro Lagos, ya zakiyi da Halimatu?’

‘Wace Halimatu, yarinyar da ko yanzu na yaye ta bani da matsala. Duk wani abinci fa da naci tana ci kaga kuwa zan iya barinta wajen Inna ko Ummanmu, kwana dai biyar.’

‘Ba zaki yaye ta ba yanzu, don mugunta? Ina ma laifi ki bari tayi shekara daya da rabi. Kawai ki bari next year in baki da ciki ko goyo sai muje.’

‘To ai ni ba ce maka nayi zan yayeta ba, kwana biyar ne fa kawai ina dawowa zata cigaba da shan nononta ai ana haka, in ya so idan ta karasa shekara daya da rabin sai a yayeta.’

‘Babu wannan zancen, bana son fitna. Kiyi zamanki kawai in Allah ya kaimu lokacin da baki da ciki ko goyo sai muje, kuma ma ni ba kwana biyar zan yi ba kwana goma zan yi don akwai abinda nake son yi a Lagos din idan an gama yaron.’

Nan da nan ta kara tsuke fuska , tabbas ta san akwai abinda ya shirya, babu mamaki ma da wata zai tafi, amma ko ma menene zata bincika don wannan tafiyar sai dai ya zabi daya ko ya tafi da ita ko ya fasa zuwa.

‘Um!’

Ta bashi amsa ta koma tayi shiru ta cigaba da kallon TV, jimawa kadan kuma ta fice daga falon ta barshi a nan.

Ya bi bayanta da kallo yana jijjiga kai, bazai tafi da ita ba ko me zata yi duk da ma ya ga ta hakura ba tare da wata fitna ba.

Haka ta kwana a dakinsa kamar babu wani abu da ya faru, don haka ma ya kara sakankancewa ta hakura. Sai da suba bayan ya shiga wanka sannan ta sami dama ta lalube masa waya, bata sami komai ba a WhatsApp amma ta samu a telegram da email dinsa. Kuma da yake ita har password dinsa na banking app ta sani saida ta duba, taga ya turawa Felicia kudi naira dubu ashirin da biyar sannan kuma ya tura mata adress din hotel din da ya kama ta email. Sai da ta tura rasit din da email din wayarta sannan ta mayar masa da wayarsa ta ajiye ta fice daga dakin.

Haka tayi ta kaiwa da kawowa a dakin tana tunanin ta inda zata bullo masa; ya za ayi tana matarsa ba zai je da ita ba amma har yayi booking karuwar da zai kwana da ita; tabbas ba zata yarda da wannan wulakancin ba.

Har ya dawo daga masallaci bata fito daga daki ba don haka ya koma ya kwanta, sai wajen bakwai da rabi ya fito a shirye, har zuwa lokacin bata sauko ba. Da yake ya riga ya siyo burodi tun dare don haka sai kawai ya hada shayi ya karya. Bayan ya gama cin abincin sai ya wuce dakinta inda ya tura kofar a hankali ya leka, tana zaune a kan kujera tana bawa Halimatu nono.

Ya karasa ciki

‘Ni zan fita, lafiya kalau Halimatun take ko?’

‘Lafiyarta kalau, a dawo lafiya.’

Ya fice ya barta yana tunanin abinda ya bata mata rai tunda ya san kalau suka kwana.

Sai dab da la’asar ya dawo kuma har lokacin tana nan tana ta faman bata rai, don haka ma bai nemi abincin rana ba musamman da yake ya ci abinci a office.

Yana zaune a falon ta shigo ranta a bace, ko sallam bata yi masa ba ta nemi waje ta zauna kusa dashi. Bai kalleta ba saboda ya fuskanci da rigima ta shigo. Sai da ta dauki dan lokaci a zaune tana ta faman muzurai sannan tace

‘Mukhtar.’

Ya daure fuska sannan ya amsa

‘Na’am.’

‘Don Allah sai yaushe ne kai a rayuwarka zaka daina neman matan banza ne?’

Tambayar ta shammaceshi kuma ta rikita shi, sai da ya dan yi kokawa da nutsuwarsa ya daure fuska sannan yace

‘wannan wane irin cin fuska ne da rashin mutunci Jamila? Ni kike wa wannan tambayar?’

Tas take bin kwayar idonsa da kallo don haka sai shine ya gaji ya dauke idonsa daga cikin nata, ta dan kawar da kai

‘Mtsewww! To ai dole na tambayeka. Kace bazaka je dani Lagos ba amma kayi appointment da Felicia, bayan ka tura mata adireshin hotel din da zaku hadu har dubu ashirin da biyar ka tura mata. To su kuma kudin dama haka kake biyanta ta bude maka tsakanin cinyoyinta ko kuma na gyara ne ka bata domin kafi jin dadinta?’

Da hanzari ya mike tsaye yana nuna ta da yatsa

‘Na gaya miki bana son irin wannan ko Jamila, shikenan babu wata mace da zan yi appointment da ita sai idan nemanta nakeyi? Kwanan nan kika zagi matar mutane kika janyo min asarar miliyoyin kudi amma baki daddara ba ko?’

Itama ta mike tsaye tace

‘Wallahi karya kakeyi Mukhtar, babu wata alaka tsakaninka da wannan Felicia din face alakar zina, kuma wallahi sai nayi maganinku da kai da ita.’

Ya daga hannu zai mareta yana fadin

‘Nine nake miki karyar?’

Cikin zafin nama ta goce ya mari iska

‘Ai na gaya maka ba zaka sake dukana ba, kuma idan har ka sake ka sake dukana sai na mayar da kai kalar tausayi a garin nan. Kai yanzu ko kunya baka ji matan banza kowacce kaje ka kwabe mata wando babu kunya babu tsoron Allah. Haka zan zauna ina kallonka kayi ta kwaso cuta kana shafa min, ga yara nan na fara da mace; wace irin tarbiyya kake son nuna musu da kake haka?’

‘Ba zan tafi dake Lagos din ba kuma abinda nayi niyya bazan fasa ba, duk abinda kike jin zakiyi a kai kije kiyi.’

Ya sa hannu ya tureta gefe ya wuceta ya shige dakinsa ya mako kofar.

Ta zube a nan a kan gwiwoyinta tana faman kuka, zuciyarta sai tafasa take. Shikenan yanzu babu yanda zatayi da mutumin nan, tana kallo haka zai dinga bin

matan banza ya dangwalawa wannan ya dangwalawa wannan kuma ya dawo ya juye a kanta sai kace wata masai.

Da kyar ta mike ta koma dakinta. Tana shiga ta turo kofar ta tsaya a bayan kofar tana faman fitar da hawaye. Ta dubi Halimatu wadda take bacci, tausayinta ya kara cika mata zuciya. Ta wuce cikin dakin ta sauke akwati daga wardrobe dinta ta hau diban kayansu ita da Halimatu tana zubawa a ciki.

Ba zata iya wannan zaman ba, kullum sai an yi rigima mutum yayi kamar ya daina sai ya koma ruwa; kuma idan tayi magana sai ya juya abun ya zama kamar itace mai laifi. Gaskiya bazata iya ba. Ta rufe akwatin ta goya Halimatu sannan ta janyo akwatin ta kulle dakin ta fice daga gidan.

KARSHE BABI NA TALATKN DA UKKU

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA HUDU

34

Tun kafin a fara hidimar bikin Hamida Safiyya ta ware naira dubu hamsin a irin kudaden da take tarawa, ta bawa Umma tace ayiwa Hamidan wani abu. Tunda aka fara bikin ake ta shawara da ita, ita kanta abun har mamaki yake bata.

Lokacin da aka kawo kudin auren Hamidan babu wanda ya bi ta kanta, garama lokacin da aka kawo lefen saboda a lokacin ta fara kitso don ta bada dubu takwas a hada ayi snacks. Amma yanzu taga sai wani shawara Umma takeyi da ita, har Yaya Hajiyayyen ma duk sun canza. Yanzu sosai suke kulata.

Ta gode Allah ta fahimci ashe a duniya mutane suna daukanka yanda ka dauki kanka ne; domin lokacin da ta dorawa kanta damuwa ta banzatar da kanta suma hakan suka yi mata.

Haka aka gama biki aka kai Hamida gidanta da yake unguwar Janbulo.

Kamar yanda Ahmad yayi mata alkawarin yana dawowa daga Dubai ‘yan uwansa suka kawo kayan auren Fatima. A can gidan Baffansu a nan aka karbi kayan, wadanda mata ne suka kawo.

Yaya Ibrahim ne ya bayarda naira dubu dari tukuici sannan kuma ya bayarda naira dubu dari biyu aka shiryawa baki abinci da kayan snacks.

Cikin mutunci aka karbi kayan, suka dora naira dubu dari kudin dinki, aka rabu kowa na son barka. Aka saka ranar aure sati takwas.

Tun kafin a kawo wa Mommy kayan auren nan ‘yan mata a ‘yan uwan Fatima suka dinga turo mata da hotunan kayan auren nan. Akwati tara ne, daya me hudu a saiti daya kuma me biyar, ko wanne cike da kaya domin sutura sai da aka kirga kala dari cif ga tarin mayafai, abaya da sauransu.

Bayan an sallami baki kuma aka zuba akwatuna a mota aka taho gidan su Fatima. Tana daki ta jiyo shigowar mutane, take ta jiyo shewar su Badriyya, Zam-zam da Shukra sun nufo dakinta.

Suna shiga dakin sukayi kanta gaba daya, Zamzam tace

‘Kai Fati, soyayya tayi. Kinga kayanki kuwa? Gaskiya kin more.’

Murmushi kawai take tana binsu da kallo, Badriyya wadda suke kira Badr; wadda kuma sa’anni suke da Fatima kuma kusan cikin damuwa daya suke ta rashin yin aure har kawo yanzu; ta karaso ta rike hannuwan Fatiman

‘Sis Allah ya nufa jirginki zai tashi, saura nawa jirgin.’

Ta fada jikin Badr nan take su duka biyun suka rushe da kuka; ita Badr tana murna kuma tana tunanin yaushe nata auren zai zo itama ta huta da masu damunta wai taki aure, yayinda ita kuma Fatima take zullumin yanda ya ciko kayan nan idan ya gane bata kai masa budurcinta ba ya zatayi da shi? Sai da sukayi mai isarsu Zamzam da Shukra suna kansu suna ta faman iyayi sannan suka saki juna suka hau hira ana shirin biki.

Sai da kowa ya tafi sannan Fatima ta fito suka saka kayan a gaba ita da Mommy suna ta dubawa. Bayan sun gama Mommy ta kalli Fatima ta dafa kafadarta tana murmushi tace

‘Ashe zan ga aurenki Fatima.’

Ta sunkuyar da kai cikin jin kunya.

‘Allah ya ji kan Daddy, ina ma yana nan yaga Fatinsa ta zama matar aure. Wannan mutumin Allah ya sa ya rike min ke amana kema Allah ya baki ikon rike masa gidansa da amanar aurensa Fati.’

Kasa amsawa tayi sai hawaye, ta rungume Mommy sukayi ta yi.

……..

Tunda aka kawo kayan auren nan Mommy ta shiga gyara Fatima, ‘yayan wasu ma a dangi ita take gyarasu balle kuma tata.

Tunda aka fara maganar aure tsakanin Fatiman da Ahmad take ta wata rama don haka Mommy ta saka aka hada mata hadadden garin sabaya wanda zai sa ta murja ta cicciko ko ta ina. Kayan gyara kala-kala ta tanada sai dai tace da Fatiman ta shanye sabaya na sati biyu sai a fara sauran.

Ita kuma Fatima hankalinta a tsahe yake saboda abinda zai matseta take nema ba abinda zai kara mata ni’ima ba tukunna. Sunyi magana da Janan sai dai shawarar Janan batayi mata ba, domin cewa tayi ta turo kudi zata je mata wajen Malam ayi mata aiki babu yanda za ayi ya gane.

Bata son harkar Malam saboda wancan zuwan ma da tayi gani take kamar har yanzu Allah bai yafe mata ba duk da kullum ta tuno dai ta sake tuba ya za ayi kuma ace ta koma; ashe ba tayi hankali ba kenan. Don haka dole ta tsara Janan akan ta sami wani ma za ayi mata aikin don su rabu lafiya.

Maman Haidar ta nema amma ce mata tayi kayan gyara kawai take so, saboda na Mommy sun fara bata mata ciki don tana da ulcer. Nan take Maman Haidar ta bata lambar Maman Ilham (08034375920) tace mata

‘A Kano take, ki nemeta zata baki masu inganci don ko kaza ta dafa miki ta amare lafiya lau zaki ci babu wani tashin hankali kuma kayanta akwai aiki.’

Don haka ba tare da bata lokaci ba ta nemi Maman Ilham inda tace mata kayan matsi tafi damuwa da su saboda ta taba amfani da wani magani na infection wanda kwaya ce ake tusawa, kuma ita bata san ‘yan mata basa cusawa ba sai da ta cushe shi gaba daya. Nan da nan maman Ilham ta hada mata su kowanne da bayaninsa aka aika mata. Gidan Maman Haidar nan ta ajiye, sai an tashi daga makaranta sai su wuce taje taci.

Wanda ake sakawa kuma su a dakinta ta boye.

Haka suka cigaba da shiri, duk abinda Mommy ta bata sai ta wuce da shi dakinta ta zuba a toilet tayi flushing, ta kawo kofi tace ta shanye.

Mukhtar bai san Jamila bata gidan ba sai bayan magriba, bayan ya gama caje gidan ya tambayi maigadi ko ya ga fitarta inda ya tabbatar masa ta fita da akwati da goyon Halimatu.

Da ba don Hajiya da Baba ba da tabbas zai barta ta dana zaman gidan, amma ya san Baba ba zai masa a hankali ba idan ya sami labari. Sannan kuma ga yanda sukayi da Safiyya, daga ya barta ta dana zaman gida abubuwa suka dinga faruwa har auren ya kare ba tare da ya shirya ba, gashi nan yanzu ta ki sauraronsa.

Don haka ya dauki waya ya kirawo Yayanta Abdallah; wanda shine Babba a duk gidan kuma ba uwarsu daya da Jamila ba tunda shi uwarsa itace uwargida tafi kowa yara a gidan ita kuma uwar Jamila itace ta uku kuma su Jamila su hudu kawai ta haifa.

Bayan sun gaisa yake sanar dashi Jamila ta tafi gida, Abdallah yace

‘Eh na ganta ai yanzu na fito daga gidan na zata ma ganin gida taje.’

Yayi gyaran murya

‘Mun dai dan sami matsalane shine ta fice ban ma sani ba sai yanzu da na dawo.’

‘Ikon Allah, to me yake faruwa ne?’

‘Wallahi fitna ce kawai. Bani da ikon nayi waya ko message da wata mace kawai sai tace wai neman mata nakeyi, kuma ta san bayan aikin office ina sayar da computers.’

Nan ya bashi labarin abinda ya faru da Professor, sannan ya cigaba

‘Yanzu ma kuma Lagos zan je conference wai sai na je da ita. Na gaya mata tana shayarwa ba zani da ita ba shine take tayi min bincike. To akwai wata mata marketing manager ce ta wani shagon computer da suke Lagos din wanda nake son idan zan sai computers dai-dai kawai na dinga siya a can don ya dan fi riba, to sai taga nayi appointment da matar nan cewa idan na zo Lagos zamu hadu shikenan fa take ta fada. Shine ina fita ta taho gida.’

Abdallah yace

‘Ikon Allah, to so take ka daina business din kenan ka zauna a gidan kayi mata raino? Mtseww! Rabu da shirmensu na mata, zamuyi magana da Abba in sha Allahu da kaina zan dawo maka da ita ai ta sam Abba ba zai dau wannan shirmen ba. Goben nan zan dawo maka da ita.’

‘A’a zan zo ma da kaina, na dai kirawo ka ne don ka san me yake faruwa. Inaga a barta a gidan in sha Allahu idan na dawo daga Lagos din sai na zo na daukesu.’

‘To shikenan babu damuwa, zan yi mata fada in sha Allah, kuma na san Ummanta ma ba zata barta haka ba. Allah ya bada sa’a sai ka dawo din.’

Sukayi sallama.

Jimawa kadan ya sake daukan wayar ya kirawo Safiyya, har ta gama ringing ba a dauka ba. Tun ranar da yaje gidansu bata sake daukan wayarsa, kuma dama daya layin nasa bata budeshi ba balle yayi mata sako ta Whatsapp. Itama Hamida da yake tun tuni yana da lambarta Sau uku yana kira bata dauka.

Ya ajiye wayar cikin damuwa, babu yanda za ayi ya tafi Lagos bai yi magana da Safiyya ba kuma baya son yaje gidansu idan bata bashi izini ba don baya son ya sake ganinta da mutumin nan idan ba hawan jini yake nemarwa kansa ba.

Duk wata dabar da zai yi ta kare don haka yaga gara yaje ya sami Yaya Habibu a office, watakila idan suka fahimci juna komai ya zo da sauki.

Haka ya rufe gidan ya kwana shi kadai, gari na wayewa Juma’ah, ya shirya ya nufi office. Sai wajen goma sannan ya bar abinda yakeyi ya kama hanyar office din Yaya Habibu.

Duk da yayi mamakin ganinsa amma cikin sakin fuska ya karbeshi suka gaisa, bayan ya gama kame-kamensa yace

‘Dama naje wajen Safiyya ne mun yi magana ina son dawo da aurenmu, duk da dai bamu wani fahimci juna ba amma dai naga ya kamata na sanar da kai don in dai ta amince ba wani lokaci za a dauka ba. Kuma kaima ina baka hakuri a kan abubuwan da suka faru, in sha Allahu wata matsala irin wannan ba zata sake dawowa ba.’

Habibu ya kalleshi ya dan tabe baki

‘Allah sarki, to babu laifi idan dai ita Safiyyan ta amince na san zata yi min maganar ai, in ya so daga nan sai a san abun yi.’

Haka ya hakura yayi sallama da Yaya Habibu ya tafi ba don ya so ba, ya ga kamar Habibun bai gamsu da zantukansa ba amma dai ko babu komai ya sanar da su don in sha Allahu Safiyya tasa ce.

Idan ya dawo daga Lagos ma gidan Baban Hotoro zai je don shima ya san ya dawo sannan ya gayawa Baba, watakila idan ya shiga maganar sa fi sauraronsa.

A zaune take a daki ta idar da sallar la’asar wayarta tayi kara, ta mika hannu ta dauka tayi murmushi bayan taga Yaya Habibu ne yake kiran. Bayan sun gaisa yace

‘Wai meye kuma yanzu tsakaninki da Mukhtar?'

Tayi mamaki saboda bata gaya masa ya zo ba duk da dai ta san zai iya yiwuwa sunyi maganar da Umma.

‘Yaya ba komai fa, ya dai zo nan yace yana son ya maida aurena kuma na gaya masa bazan taba sake aurensa ba yayi hakuri.’

‘Kin tabbatar kin gaya masa haka?’

‘Wallahi Yaya na gaya masa kuma tun daga lokacin ma ban sake daga wayarsa ba. Ba zan aureshi ba Yaya kada ma ka saurareshi.’

‘Yauwa, abinda nake son ji kenan. Shi kuma A A (Abdurrahman Anas) fa? Za ki aureshi don in yazo na san da wacce zan tarbeshi.’

Ta dan yi jim sannan tace

‘Zan aureshi Yaya.’

Sukayi sallama suka ajiye wayar.

.....

Ranar Alhamis ya diro birnin Kano yana sauka daga airport ya karbi mukullin motarsa a hannun direbansa ya sallameshi. Ya shiga mota ya kama hanyar office din Yaya Habibu. Bayan sun gaisa ya sanar da shi gobe Juma’a yake so a kawo kayan auren Safiyya. Yana so zasu hada kudin aure, kayan lefe da kayan sa rana a kai gaba daya kuma a sa wata uku.

Sosai Yaya Habibu ya ji dadi kuma ya gaya masa hakan yayi, sai dai akwai gidan Baban hotoro da yake son yaje ya gaisheshi. Yace

‘Kwarai kuwa kayi min maganar. To ai in babu abinda kakeyi ko yanzu sai muje.’

Don haka tare suka fice suka hau motar AA suka nufi gidan Baban hotoro.

Sosai Baban hotoro yayi murna kuma ya ji dadi, duk da tun tuni Habibu ya kai masa labarin AA din har shima yayi nasa binciken. Sukayi masa sallama suka kama hanya.

Sai da suka rabu da Habibu sannan ya dauki waya ya kirawota, bayan sun gaisa yace

‘Kin kusan zama matar A A fa, nan da sati goma sha biyu.’

Ta kyalkyale da dariya tace

‘Shike nan ma an hutar da mutane ka riga ka saka mana rana.’

‘Zaki sha mamaki. Yanzun nan muka fito daga gidan Baban hotoro kuma ya riga ya bani aurenki gobe za a kawo kayan aurenki.’

Tayi shiru na dan lokaci, sannan tace murya a sanyaye

‘Allah da gaske?’

‘Ina miki wasa ne? Ko kin fasa auren ne?’

Tayi murmushin da har saida ya jiyo sautinsa ta wayar

‘Ni na isa? Babu fashi sai dai in kai ka fasa.’

‘Yauwa matar AA kanwar barrister.’

Haka suka gama wayar yana ta tsokanarta.

Sai da daddare Yaya Habibu ya shigo yake gaya musu zancen kai kayan don har ya bawa Baban hotorom dubu dari tukuicin masu kawo kaya kuma ya aika an kai lemo da ruwa wanda za a basu.

Bayan ya gama zancen ne Umma tace

‘Shikenan dai ba zaka barta ta koma wajen ‘yayanta ba ko?’

Yace

‘Haba Umma, shekarun Safiyya nawa? Da kuruciyarta fa balle ace taje tayi zaman ‘yayanta. Kina kallon mutumin nan yayi aurensa ma sai da ya gama more amaryar sannan zai dawo yace ta koma. Haba Umma, yaje can ya karanta.’

‘Ai shike nan, Allah ya sa haka ne yafi alkhairi.'

Tana jiyosu daga daki ta amsa a zuciyarta

‘Amin.’

.....

Yanda ya alkawarta haka akayi, iyayensa maza sune suka kawo kayan auren Safiyya. Yaya Habibu yana zaune aka karba a falon Baban Hotoro.

Kudin aure naira dubu dari, akwati daya na sa rana sannan akwati shida na lefe, ga kuma buhunan abinci, kayan lalle da su tabarma da ake hadawa duka kamar na budurwa. Sannan suka bayar da dubu dari kudin dinki.

Bakin suna fita mata suka shigo aka hau bubbudawa, Sabir yana tsakiyar kayan yana yiwa Safiyya video don ya san sai a kai sati ba a kai kayan gidansu ba. Haka sukeyi duk kayan wanda aka karba sai dangin ubansu sun gama gani a gidan Baban hotoro sannan sai a kai gidansu amarya.

Tsakanin atamfa, leshi, material da shadda sai da aka kirga kala sittin da biyar kuma duka manya ne. Ga kuma akwatin abaya itama kala goma sha biyu masu kyau dinkin Dubai tare da kayan bacci. Takalma da jaka komai ya ji ga kayan sarkoki, mata sai guda sukeyi ana ta son barka domin kaya sun yi kamar na budurwa.

Nan aka ture kayan gefe a falon Baban Hotoro aka rufe su da Leda, idan aka gama gani sai a kaiwa Umma gida.

Baban hotoro da kansa ya kirawo Umma ya sanar da ita an saka ranar auren Safiyya sati goma sha biyu, maganar kayan daki da hidimar biki kuma zai tattauna da iyayenta maza abinda suka yanke zata ji.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA HUDU

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA TALATIN DA BIYAR

35

Lokacin da Jamila ta isa gidansu Ummanta bata nan, babu kowa a dakin Umman sai Tani me yiwa Umman nata aiki tare da Sultan dan waje yayarta wanda aka kawoshi yaye wajen Umman. Bayan ta ajiye jakarta ta dauki Halimatu suka shiga cikin gidan inda ta gaggaisa da sauran matan gidan, ta wuce wajen Abbansu da yake shima yana nan ta gaisheshi.

Duk wanda ya gansu ita da Halimatu ya zata ganin gida kawai tazo, bayan ta gaisa da mutanen gidan ta mikawa Tani Halimatu ta shiga dakin Umman ta kwanta.

Sai can kusan magriba Umman ta dawo, tunda taga Jamilan ta san da akwai matsala ta dai ji ta ne lokacin da ta ce zuwa kawai tayi ta kwana biyu saboda yayi tafiya.

Sai da dare yayi suka zo kwanciya Umman ta gama shafa’i da witri tana kan daddumar yayin da Jamilan take zaune a gafen gadon inda Sultan da Halimatu suke bacci, ta dubi Umman tace

‘Umma.’

‘Na’am.’

‘Umma ni dai don Allah ki gayawa Abba ya yiwa Mukhtar magana, ya daina neman mata idan kuma ba zai daina ba gaskiya ni dai na gaji da zama da shi.’

Umma ta dan yi shiru tana duban fuskar Jamilan kamar mai karanta wani abu, tace

‘Baki daina yi masa binciken ba kenan?’

Nan da nan ta fara hawaye, ta dubi Umman tace

‘Umma nifa ba haka kawai na fara yi masa bincike ba saida ya sa min zargi a zuciyarta. Kuma wallahi Umma neman mata yake, har Zariya ya dinga zuwa wajen wata karuwa da kyar na samu Allah ya rabasu. Harda kuma kafirai fa yake nema Umma.’

‘To yanzu ya kike so nayi miki? Ba a taba yin matar da ta binciki wayar miji ta zauna lafiya ba, an gaya muku ku bari kun ki. Yanzu ya kike so nayi miki kin je kin ganowa kanki abinda zai hanaki zaman lafiya.’

Ta share hawaye ta kawar da kai, ta rasa me yasa duk lokacin da ta yi maganar Mukhtar yana zina sai a kauda kai daga laifin zinar a dinga yi mata fadan bincike, ta hadiye malolon da ya tokare mata makogoro tace

‘Umma ashe yanzu idan wani bangare na jikinka yana ciwo sai ace ka kau da kanka kada ka kalli ciwon. To ai ko ka kawar da kanka ciwon yana nan kuma zai cigaba da cin jikinka ko ka nemi magani ko ya kasheka idan kuma kana da nisan kwana ka sha wahala. Umma tunda fa na auri mutumin nan nake fama da ciwon sanyi, da ya warke sai ya dawo. Yanzu idan kanjamau ya dauko ya saka min wa zaiyi jinyata?’

Suka yi shiru na dan lokaci, ba a jin komai sai shesshekar Jamila. Umman tace

‘Na fahimce ki, amma dai hakurin zakiyi tunda haka zamani ya zo da shi. Ni dai ba huruminane na yiwa Mukhtar din fada ba amma in sha Allah zan yiwa Abban naki magana yanzu idan na shiga wajen nasa.'

Ta tashi ta baro Jamila a daki ta dawo falonta, ta zauna a kan kujera ta kunna TV kamar me yin kallo. Wannan lamari na mijin Jamila yana damunta, ta fahimci abinda Jamila take fada sai dai ta san Abbansu ba zai saurareta ba, tunda ita kanta Jamilan ta yarda tana yi masa bincike. Sai da ta Jira wajen karfe tara da rabi sannan ta nufi wajen Abban, domin a lokacin ne yake zama afalonsa kuma ko ba kece da girki ba kina da damar ya saurareki.

Tun kafin ta yi masa zancen Jamilan yace

‘Me ya hada Jamila da mijinta ta taho gida?’

Ta kalleshi da mamaki

‘Au ashe ta gaya maka.’

‘A’a shi mijin nata ya kirawo yayansu yayi masa bayanin ai. Ban dawo da wuri ba shi yasa na kyaleta sai da safe.’

Don haka itama Umma tayi masa sallama ta dawo dakinta tunda ba itace da kwana ba.

Ko da gari ya waye ma kafin Jamila ta tashi Abban ya fice ya tafi gona. Can wajen azahar kuma Inna ta shigo gidan; domin dama ta saba zuwa gidan tayi weekend tunda ‘yayanta duka sunyi aure kuma mijinta ya dade da rasuwa. Ita din ma da ta ga Jamilan bata kawo wani abun ba don ta zata ganin gida suka zo.

Sai la’asar Abba ya dawo, karfe biyar na yamma Yaya Abdallah ya shigo gidan. A falo ya sami Abba suna hira da Inna, bayan ya gaidasu ya zauna ya mayarwa Abban yadda sukayi da Mukhtar din. Duk abun nan a gaban Inna akayi domin ita din Yayar Abban ce kuma yawancin abubuwa ko ba ayi a gabanta sun san Abban sai ya gaya mata.

Bayan sun gama sauraron Yaya Abdallah Inna ta dubi Abban tace

‘Au dama Jamilan yaji kenan tayo? Kai wannan yarinya bata kyautawa, ta samu wannan yaron yana ta dawainiya da ita amma tayi ta tijara salo-salo. Da naje mata wanka ma fa haka ta dinga fitna irin wadda ma ni ban taba gani ba, don sai da ta sa ya kwashe yaransa na tsohuwar matarsa ya mayar gun mahaifiyarsa; wanda in da wani mijin nema sai ya korota a lokacin amma shine wai yanzu tana da kafar yaji?’

Abba ya tashi zaune daga kashingidar da yayi

‘To ai Yaya baki gaya min duk wannan abubuwan ba kuma shima Mukhtar din bai fada ba.’

‘Ai kafin na baro gidan sun shirya kuma na sakasu a gaba dukansu nayi musu nasiha, sai naga kamar ta ji fadan da nayi mata shi ya sa ko uwarta ban gayawa ba tunda abun ya wuce. To ashe bata ji maganata ba.’

A nan Abban ya dauki waya ya kirawo Umman Jamila, yace yana falonsa su zo ita da Jamila.

Tunda Jamila ta shiga falon ta ga Inna kuma taga irin kallon da Innan take mata jikinta yayi sanyi, don haka da Ummanta ta zauna a kan kujera sai ta zauna ta takure a kusa da kafar Ummanta.

Tun bayan sunan Halimatun take sa ran taji kira daga wajen Abba amma taji shiru, tana ta murna Inna ta rufa mata asiri. Domin ko dauke su Nana ma da yayi bata gayawa Ummanta dalili ba don ita kanta tana jin kunyar abinda tayi. Ta dai bawa Umman labarin yanda yaki ya kama mata event center ya kwashe kudin ya sayawa budurwa waya.

Sai da suka zauna suka nutsu Abban ya dubi Umman Jamila yace yana nuna Jamilan

‘Me tace miki ya hadata da mijinta ta taho min gida?’

Zuciyar Umma a jagule saboda ganin wannan taron dangin da aka shiryawa Jamilan. Cikin sanyin murya tace

‘To ita dai tace yana neman mata don ko nima nayi mata fadan zargi babu kyau yana lalata aure amma tace ba zargi take ba ta tabbatar.’

Abba ya kalli Abdallah wanda nan take ya mayarwa da Umman abinda Mukhtar din ya gaya masa, Abban ya dubi Jamilan yace

‘Ko karya yayi mikine? Ita matar sanatan da kika kira karuwa itama nemanta yakeyi?’

Cikin rawar murya tace

‘Abba ai wannan ban sani ba amma…'

Ya katseta yace

‘Ohhh!.....kin jita ko?’

Yana duban Ummanta, ya dubi Jamilan ya cigaba

‘Ke kin san girma kazafin zina a shari’a kuwa? Kin san duk wannan maganar da kike idan aka kai kotun a karshe ke za ayiwa bulala ko? Kuma ma a ina kika taba kamashi yana zina?’

Inna tace

‘Wayace dai fitnarta, tunda da kanshi ya gaya min bai isa ya ajiye wayarsa ba sai ta bincike tas. Duk inda taga sako daga mace ko wata lamba da bata sani ba ta kirawo shi to sai tijara. Don kafin sunan Halimatu ma da taji yana waya da mace a kan ya saya mata wayace ni ko computer wallahi fizge wayar tayi a hannunsa ta buga wayar nan da bango wayar nan ta tarwatse sai sabuwa ya siya.’

Abba ya dubi Jamilan da takaici; wadda kawo yanzu hawaye ya gama wanke mata fuska saboda bata da kalaman da zata kwaci kanta, domin duk abubuwan da Inna take fada ta aikata amma ta san ba za a bata dama ta kare kanta ba; yace

‘Wai ko kina hauka ne Jamila? Haka ake zaman auren. Shikenan don yana aurenki ba zai yi hulda da kowacce mace ba? Kin san kuma yana kasuwancinsa?’

Abdallah yace

‘So take idan mata sun zo siyan computers yace musu matarsa ta hana maza kawai yake siyarwa.’

Abba ya cigaba

‘To ai kuwa ba zai yiwu ba, ki ma gayawa kanki gaskiya. Ga iyayenki nan ki tambayesu, koda yake kema da wayonki kina ganin yanda mata har nan suke zuwa kuma iyayenki su bamu waje mu tattauna saboda yanayin aikina. Baki taba jin wadda ta yi wata fitna ba muma babu wadda ta bincika min waya har na gama aiki lafiya. Wayar mutum kuma ai sirrinshi ce don me zaki bincika masa waya har kina kafa hujja da binciken da kika yi?’

Ya danyi shiru, Inna tace

‘Kwarai kuwa, yiwa miji bincike shine silar duk wata matsala idan kuma baki daina ba zaki shiga cikin matsala sosai kuwa.’

Haka dai aka karewa Jamila fada babu ma wanda ya saurareta balle tayi bayani, daga karshe Abba yace idan Mukhtar din ya zo daukanta yana son ganinsa, ita kuma ya gaya mata ta zama cikin shiri idan mijinta ya zo zasu tafi kuma kada ya sake jin wata magana idan ba haka ba ranta zai baci.

Haka ta fito daga falon tana share hawaye, suna komawa dakin Umma tace

‘Ki daina kukan haka, kuma kinga ai da baki bincika masa waya ba da kina nan hankalinki a kwance amma kika je kika ganowa kanki abinda zai hanaki zaman lafiya.’

Ta share hawayenta ta dubi Umman

‘Umma, yanzu ashe idan mutum yaji ciwo a yatsan kafarsa sai ace ya daina kallon ciwon? Kawai ya rabu da ciwon ba sai ya je asibiti ba ba sai ya sha magani ba ai in bai ga ciwon ba ba zai ji komai ba. Kin san kuwa mutum yana nan zaune ciwon man zaiyi ta cin jikinsa karshe ya ja a yanke kafar ko ma a rasa rai. Wannan fa shine kwatankwacin abinda kuke so nayi. Mijina wani jigo ne a rayuwarta, yana aikata zina ana cewa wai na kauda kaina. A lahira ina son mu shiga Aljannah ni da shi, idan ya mutu yana zina akwai yiwuwar ba zai shiga Aljannah, ba a duniya kuma ya saka ni cikin kunci bayan cututtuka da yake debowa yana shafa min daga wajen matan banza. Meye laifina idan nayi magana Umma? Amma tunda haka kuke so in sha Allahu ba zan sake maganaba, sai dai ki gayawa Abba idan bai saka min cutar da zata kasheni ba to tabbas depression zai kasheni.’

Ta share hawayenta ta kama hannun Umman ta cigaba

‘Kiyi min addua Umma, kada Allah ya jarrabi yarana da irin wannan fitnar. Kinga na fara da mace, ki dinga yi min addu’a Allah ya katangeta idan kuma maza Allah ya bani ma to Allah ya hanasu daukan dabi’ar mahaifinsu.’

Ta mike ta shige daki ta bar Umma zaune a falo.

Tana tausayin ‘yar tata, tabbas ta san abubuwan da take fada gaskiyane ta yarda Mukhtar din yana neman mata amma bata da yanda zatayi a kai musamman bayan wannan zantuka da Inna da Abdallah suka kawo, wadanda kuma Jamilan bata musa ba.

Duk yanda yake tunanin idan yaje Lagos zai huta ya sami nutsuwa ba haka ya kasance ba. Gaba daya ma ya kasa jin dadin taron, dare biyu ne kawai suka kwana da Felicia a dare na uku ya sallameta don baya cikin yanayin da zai iya yi mata wani abu. Haka aka karasa taron nan da shi a daddafe, ana gama taron ranar Alhamis ya biyo jirgin Juma’a da safe ya dawo Kano ba tare da ya kara kwanakin da yayi niyya ba.

Karfe goma na safe jirginsu ya sauka a Kano, daga nan ya dauki shatar tasi zuwa gida. Kayansa kawai ya ajiye ya wuce gidansu, a can ya zauna har lokacin masallaci.

Tare da Baba suka je masallaci suka dawo, ko da suka dawo a falon Hajiya ya zauna inda ya sameta tana cin abinci. Yana zama hajiya ta saka aka kawo masa abinci, yana cikin cin abincin bayan ya hadiye lomar da take bakinsa yace

‘Hajiya.’

Ta ajiye kofin da ta sha ruwa tace

‘Na’am.’

‘Hajiya na je gidansu Safiyya fa.’

‘To ma sha Allahu, wani abun ya faru ne a gidan nasu.’

‘A’a. Na dai je ne don mu sake aure da ita.’

Nan da nan fara’arta ta karu, ta harareshi tace

‘Da kaji wuya ko? To Allah ya sa dai bata sami wani bazawarin ba.’

‘To bata dai amsa min ba amma dama na san zai dan dauki lokaci tunda ranta a bace yake. Shima Yayanta na sameshi a office na sanar dashi, yanzu kuma in na tashi zan je gidan Baban Hotoro tunda shine waliyyinta.’

‘Ka dai ji kunya wallahi, shekaru kusan uku baka tashi maida auren ba sai yanzu. Allah ya saka su saurareka ita da iyayen nata.’

‘In sha Allah zasu saurareni Hajiya, ke dai ki cigaba da addu’a.’

‘Hmm! Ka dai ji kunya. Kuma ka gayawa Baba?’

‘A’a. Bari nayi sai mun gama dadaitawa tukunna kin san in ya ga dama yanzu zai bata min rai, kwanaki fa cewa yayi Allah ya bata mijin da ya fini.’

‘Hm! Ka kaisu idan kaya ne!’

Nan ya zauna har akayi sallar la’asar, yana fitowa daga masallaci ya shiga motarsa ya kama hanya. Safiyyan yake son gani amma gara ya fara zuwa gidan Baban Hotoro ya shigar da gaisuwarsa in ya so idan ya gama sai ya tsaya gidansu Safiyyan; duk da bata san da zuwansa ba tunda ta daina daukan wayarsa.

Cikin nishadi yake tukinsa har Hotoro, ba tare da wata matsala ba aka yi masa iso falon Baban Hotoro inda ya sameshi a zaune yana hutawa. Bayan sun gaisa suka dan yi shiru, shi Baban Hotoro yana sauraron Mukhtar yaji abinda ya kawo shi yayinda shi kuma Mukhtar din yake tunanin ta inda zai fara.

Ya danyi gyaran murya yace

‘Dama Baba zuwa nayi na sanar da kai na sami Safiyya munyi magana a kan zamu mayar da aurenmu; duk da dai bata amsa min ba amma in sha Allahu ina sa ran zata amsa. Kuma dama ina so nazo na baka hakuri a kan abubuwan da suka faru, kuskure ne kuma in sha Allahu ba za a sake samun hakan ba.’

Baban Hotoro ya gyara zama yana masa kallon mamaki, yace

‘Ikon Allah, Safiyya dai tawa?’

‘Eh ita Baba.’

Ya bashi amsa shima yana mamakin tambayar.

Baban Hotoro yayi gyaran murya yace

‘Toh ai Safiyya wancan satin aka kawo kudin aurenta.’

Ya nuna jikin bango inda aka ajiye kayan lefen Safiyyan ya cigaba

‘Kaga kayan aurenta can gaba daya komai an kawo an sa rana sati sha biyu, kaga yau saura sati goma sha daya kenan. Kuma in dai ba na gamu da makuwa ba to ba kaine kankawo kayan ba.’

Ya daga idonsa ya kalli kayan, ya sunkuyar da kai domin ya kasa hada ido da Baban Hotoro. Kokari yake ya hadiye malolon da ya tokare masa makogoro ya nemo harshensa amma ya kasa. A take gumi ya rufe shi, ya cire hularsa ya ajiye, ya sake kallon kayan ya dubi Baba yace

‘Uhmm, ai ban sani ba da yake nima na dan yi tafiya yau na dawo.’

‘To ai kuwa an gama maganar Safiyya wannan yaron da ya kawo kaya in sha Allah shi zan aurawa ita idan lokaci yayi. Don haka sai dai nace kayi hakuri a halin yanzu ka rabu da Safiyya tunda kaga musulmi muke kuma addininmu ya hana neman aure cikin nema.’

Ya mayar da hularsa ya bude baki da kyar yace

‘Uhm, Nagode.’

Yayiwa Baba sallama ya fice, Baban ya bi bayansa da kallo bayan ya fice yace

‘Kaga mutum kamar dan wasan kwaikwayo, shekara uku kana yawonka a gari baka mayar da auren ba sai yanzu rana tsaka kazo wai ayi hakuri.’

Nan takeya dauki waya ya kirawo Safiyyan, bayan sun gaisa ya tambayeta me ke tsakaninta da Mukhtar. Bayan ta gama yi masa bayani yace

‘Kina jina ko, kinga wannan mutumin Abdurrahman da ya kawo miki kayan aure? To matukar da ni da ke muna numfashin in sha Allahu babu abinda zai hana na daura miki aure da shi idan ranar tayi, don haka ki fita batun Mukhtar. Kada naji kada na gani ace min kina sauraronsa kin ji na gaya miki.’

‘To Baba, dama na gaya masa ai.’

‘In banda ma rashin kunya sai yanzu ya tuna damu ya san ya kamata ya zo ya bamu hakuri, to mun bashi auren bamu ji dadi ba don haka ba zamu sake ba. Itama Umman naki zan zo na sameta.’

Sukayi sallama suka ajiye waya.

Saida ya dauki lokaci a mota yana kokarin dawo da nutsuwarsa kafin ya tuka motar ya bar kofar gidan Baban Hotoro.

A halin yanzu ba zai iya zuwa wajen Safiyya ba don haka ya karkata motar ya nufi gida, gashi da niyyarsa idan ya gama gidansu Jamila zai wuce ya daukota amma yanzu babu abinda zai iya don haka kawai ya wuce gida.

Bai taba tunanin akwai wanda zai yi masa shigar sauri haka ba, daga tafiya Lagos na kwana biyar har an kawo kayan aure harda sa rana. Yanzu wani ne zai auri Safee?

Ya dafe kansa da yake neman tsagewa saboda ciwo; gaskiya ba zai bari wani aure Safiyya ba, duka yanda za ayi ya janyo ra’ayinta ta aureshi zai yi kafin sati goma sha dayan nan.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA BIYAR.

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA SHIDA

36

Har dare yayi bai ji ya dawo cikin nutsuwarsa ba don haka haka ya hakura ya kwanta ba tare da ya dauko Jamilan ba. Sai da gari ya waye bayan la’asar sannan ya tafi ya daukota.

Saida Abbanta ya sa su a gaba ya dauki lokaci yana yi musu nasiha, ya nunawa Mukhtar din ya daina yin abinda zai kawo zargin tsakaninsa da matarsa.

Sukayi sallama suka kamo hanyar. Har suka iso gida Jamila batace dashi komai ba, sai dai shi da Halimatu yake ta wasa tana masa gwaranci. Suna shiga gidan kafin ya hau saman ya sauko har ta fara kokarin gyara gidan, don haka yana saukowa ya dauki Halimatu yayi mata sallama ya nufi gidan Hajiya da Halimatun.

Tunda ya shiga gidan Hajiya take tambayarsa ya taga yayi zuru-zuru, yace mata babu komai. Sai da ya sameta ita kadai sannan yayi mata bayani har an sawa Safiyya ranar aure, ta dubeshi tace

‘Ikon Allah, kayi wasa gashi gar wani zai shiga tsakaninka da ita. Allah ya sa haka ne yafi alkhairi.’

Yayi shiru, jimawa kadan yace

‘Hajiya da ma ki sa baki, ai ko ba don ni ba ta dawo don yaran ta ko? Watakila idan kikayi mata magana ko kuma Ummanta za su saurareki.’

‘Saboda me zan yi mata magana Mukhtar, kana tausayin yaran ne kai? Ai baka tausayinsu. Babu wanda zan yiwa magana kada ma ka sake min wannan maganar. Idan ita da kanta ta amince shikenan ina murna, amma yadda kayi saki ba tare da ka shawarceni ba haka ma zaka koma ka tsarota kai kadai.'

Nan ta ta shi ta fice ta barshi a falon yana cin abinci.

Haka ya fita ba tare da ya sami abinda yake so ba, don shi ya zata Hajiya zata yarda ta sa baki.

.....

Kamar yanda Jamila tace zata kawar da kai daga abubuwan da Mukhtar yake yi hakan tayi, don tunda ta dawo gidan bata wani shiga harkarsa ba. Sai dai hakan baiyi masa dadi ba. Duk wani abu na hakkin aure tana yi masa kuma tana kwana a dakinsa, amma ta rage hira da shi sosai kuma duk wata kulawa ta musamman ta ja baya. Ya dai kyale haka ne saboda yanzu hankalinshi yana kan fafutukar yanda za ayi Safiyya ta dawo, don haka ya bawa Jamilan lokaci yana jira ya san zata dawo normal.

Duk wata hanya da zai bi yaga Safiyya ta gagara gashi yana lissafe da bikinta yanzu saura sati tara. Ya kasa hakura da ita don shi sai yanzu ma ya san yana sonta.

Daga aiki ya dawo ya ci abinci ya dan koma daki ya kwanta, har bacci ya fara daukarsa ya tashi kamar wanda aka tsikari. Ba zai iya hakura da Safiyya ba gara yaje gidan nasu ya gani, watakila zata saurareshi. Don haka ya tashi ya shirya ya fito.

A falo ya sami Jamila tana kallon TV yayinda Halimatu ke wasanta a falon.

‘Na fita.’

Cikin halin ko in kula irin wanda take masa tunda ta dawo gidan tace

‘A dawo lafiya.’

Ya amsa ya nufi kofa, har ya kusan fita ya dawo, ta bishi da kallo ya tsaya a kusa da kujerar da take K

kai yace

‘Wajen Safiyya zan je, na gaya miki zan mayar da aurenta.’

'Allah ya bada sa’a.’

Ya kula da yanda take amsa masa don haka ya sa kai ya fice.

Tun kafin ya isa gidan yake mata waya amma bata dauka ba kamar yanda ta saba. Ba karamin dadi yaji ba da ya hango Sabir a kofar gidan ko ba komai ya sami mai kirawo masa ita.

Yana tsayawa da mota ya ga Sabir din bai taso ba don haka sai ya fito daga motar ya nufi Sabir din wanda yake zaune a kan benci shi da abokinsa. Ya mika musu hannu suka gaisa ya dubi Sabir din yace

‘Sabir Safiyya fa, tana nan?’

‘No, bata nan ta fita tun dazu.’

‘Ikon Allah, gashi ina tayi mata waya bata dauka ba.’

‘Eh, inaga tana busy ne.’

Yayi shiru, jim kadan yace

‘Umma fa? Tana nan na gaisheta.’

‘Itama bata nan.’

Ya sake yin shiru na dan lokaci, sannan yace

‘Kuma ba yanzu Safiyyan zata dawo ba?’

‘Eh gaskiya ina jin sai dare.’

So yake ya tambayi inda taje don yaji ko zai iya binta, amma ya kula da yanda Sabir din yake ta faman cin magani don haka sai kawai ya karbi lambar wayar Sabir din yana tunanin idan ya kirawota ta ki dagawa sai ya kirawo Sabir din ya hadasu. Yayi masa sallama ya kama hanya.

……

Sai da ya kwana biyu yana kiran Sabir amma shima ya ki dagawa, shi kuma so yake yayi magana da ita don ya tsara kalaman da yake jin zasu lausasa zuciyarta.

Don haka kafin ya shiga office sai da ya sayi sabon layin GLO, yayi rijista ya sa isasshen kati. Yana zama a office ya rufe kofa ya dannawa Safiyya kira da sabon layin.

Bata je makaranta ba saboda Umma tana zazzabi don haka ta dauki hutun kwana biyu don ta zauna da Umman.

Tana zaune a falo yayinda Umman take bacci a dakinta kiran ya shigo, da yake iyayen dalibanta sun saba kiranta idan da wata matsala tana ganin lambar sai ta zata irin haka ne. Da sallama ta amsa wayar, sai dai yana amsa sallamar ta gane wanene don haka ta mike ta koma dakinsu.

Bayan sun gaisa yace

‘Safiyya kika ce ba zamu yanke hulda ba amma na fi sati biyu ina kiranki ba kya dagawa.’

Cikin halin ko in kula tace

‘Watakila lokacin da kake kira bana kusa. Ya yaran ya su Hajiya?’

‘Lafiya kalau Alhamdulillah.’

Suka dan yi jim, sannan ya cigaba

‘Safiyya shine baki gaya min an sa miki ranar aure ba?’

‘Oh, ai bamu hadu ba tun lokacin amma ai yanzu gashi kaji.’

‘Uhm hakane. Yanzu Safee wani zaki aura ba ni ba ina nan da raina da lafiyata.’

Tayi wata ‘yar dariya sannan tace

‘Naga dai nima da raina da lafiyata ina nan kayi aurenka gashi nan kana morewa, nice bai kamata nayi haka ba saboda ni ban san dadin auren ba ko kuwa?’

‘Hakane. To amma yanzu Safiyya kina ganin akwai matar da zan aura ta kula da su Nurain sama dake, ko ba zaki aureni saboda ni ba ai ya kamata ki duba yaran nan ko? Ko yanzu ma da suke wajen Hajiya ke kin san ba Hajiya suke bukata ba ke suke bukata saboda ke ce uwarsu. Kina ganin yanda Jamilan ta yiwa Nana. Don Allah Safiyya ki dawo wajen yaranki, ko ba zaki dawo don ni ba ki duba su mana.'

Maganar ta daki zuciyarta kuma itama abinda yake mata ciwo kenan; rabuwa da yaranta. Idan akwai abinda zai iya mayar da ita gidan Mukhtar din to yaran ne; don lokacin ma da ta ji Jamila tana bawa Nana maganin tari saida tace zata dauko Nana ko kuma ta rokeshi ya mayar da ita, Saida Sabir da Yaya Habibu suka sakata a gaba sannan ta hakura. Cikin sanyin murya tace

‘Mukhtar, don Allah lokacin da zaka sakeni duk ba kayi wannan tunanin ba? Ka sakeni ka koroni? Ko ka manta da nace maka yara fa ce min kayi ai ba da su na zo ba ko? Shekarun nan uku Allah ne yake kular min da su ba wani mutum ba kuma na san Allah baya bacci. Amma ka makara, kuma kamar yanda na gaya maka ba zan sake aurenka ba in Sha Allah. Ka cigaba da kula da yaranka kamar yanda kakeyi bayan ka koroni, nima zan cigaba da yi musu addu’a kamar yanda na dinga yi a lokacin da ko kallo ban isheka ba.’

Ta tsinke wayar a take ta danna masa block.

Ta jefa wayar kan gado, hawayen da taketa rikewa suka kwace.

Tana son yaranta kuma zata so ace tana tare dasu, amma ya zata yi? Tana son A A so ba kadan ba sai dai kuma a halin yanzu duk duniya wanda take so bayan Nurain da Nana ne. Anya kuwa zata iya daurewa wannan damar ta wuceta? Anya kuwa ta yiwa Nana da Nurain adalci idan ta auri wani taje can ta haifi wasu yaran? Anya kuwa zata iya yafewa kanta idan tarbiyyar su Nana ta shiga wani hali saboda rashinta?

Cikin kuka ta bude baki tace

‘Inna lillahi wa Inna ilaihi rajiun!’

Ta saka tafukan hannunta ta rufe fuskarta, ta dauki lokaci a haka tana zubar da hawaye. Ta cire hannuwanta ta daga su sama tana addu’a

‘Allah kaine Allah, Allah ka zaba mana abinda ya fi alkhairi garemu dani da su baki daya.’

KARSHEN BABI NA TALATIN DA SHIDA

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA BAKWAI

37

Tunda Mukhtar ya daukota daga gida suka dawo ta fara neman aiki, tunda an ce ta zauna tayi ta hakuri to ta yarda zata zauna amma dole ta nemi abun yi. Ta san Abbansu zai iya samo mata aiki amma a yanda yanzu aka kawo masa wadannan laifukan nata bata jin zai saurareta, don haka ta bi ta hannun kawarta wadda yayanrta commissioner ce.

Satinta uku da komawa gidan offer ta fito don haka ta tambayeshi zata je gidan kawartata.

Sai da daddare bayan ya gama cin abincin dare yana zaune a falo ta sameshi, bayan ta zauna ta mika masa takardar tana fadin

‘Na sami aiki fa.’

Ya karba yana mamaki

‘Aiki kuma, ai ban san kina neman aikin ba.’

‘To gashi nan dai, kasan da yake minister for women affairs Yayar Nur ce ina kai mata takardu gashi har na samu.’

Da fara’arsa yace

‘Ma sha Allah, Allah ya sa a fara a sa’a.’

Yaji dadi domin shi kansa yana ganin aikin zai sa ta rage saka masa ido, tunda dama shi bashi da ra’ayin hana matarsa aiki; su biyun duka su suka zabi kada suyi aiki.

Sati yana zagayowa ranar litinin ta fara zuwa aiki.

……..

Duk wani shiri na bikin Fatima da Ahmad an gama. Ahmad da kansa ya dauki Ibrahim suka tafi Abuja don ya nuna masa gidan da za a kai Fatima. Gida ne mai daki uku, ya riga ya gyara master bedroom da kuma dakin Hafiz ya saka furniture

da komai, saura dakin Fatiman kawai. Falo kuma ya gyara dining area ga kayan kallo sababbi duk a kwalinsu da za a saka ga carpets, a kichin kuma akwai sabbin cooker da fridge masu kyau. Ya gaya wa Ibrahim duk abinda ya siya ba sai an kuma saya ba domin wannan din ma ita ya siyowa.

Duk wani gyara da Fatima take bukata tayi shi, domin ita kanta ta ji sauyi a jikinta gaba daya. Bata da kawaye don haka ta yanke ba zatayi wani event ba bayan kamu wanda za ayi a gidansu da daurin aure. Janan ce kawai kawarta ta amana sai dai bazata sami zuwa bikin ba saboda ta kusa haihuwa, kuma so takeyi ta ja baya da Janan saboda yanda ita Janan duk wata matsala sai tace a tafi wajen malami.

Nan da nan aka shiga hidimar biki. Naira dubu dari Ahmad ya bayar a matsayin sadakin Fatima, bayan an gama daurin aure aka dauki amarya aka wuce auyo yayinda mutum uku suka wuce Abuja don su karasa kafi su gyara gidan amarya.

Can ma a Auyo biki aka yi sosai, saida suka kwana biyu sannan suka wuce Kano tare da ‘yan rakiyar amarya suka hau jirgi sai Abuja. Kwana daya ‘yan rakiyar amarya suka yi a gidan suka kama hanya. Mutanen Auyo sune na karshen tafiya sai kanwar mahaifin Fatima wadda itama a Kano take. Tare da Fatiman suka tafi ya kaisu airport don tafiya Kano, inda daga nan mutanen Auyo zasu hau mota su karasa Auyo.

Tun da sukayi sallama da kanwar mahaifinta a airport Fatima take matse kwalla, tun Ahmad yana mata dariya har ya fara lallashi saboda kukan ya fara yawa. Haka suka dawo gida daga shi sai ita, da zarar ta kalleshi sai ta kara fashewa da kuka. Abinda takewa kuka daban yayinda shi kuma yake tunanin irin kukan nan ne na amare; tana ta addu’a Allah ya sa kada ta kunyata Mommy.

Haka ya dinga lallabata yana lallashinta har dare yayi.

Saboda tsabar tsoro Fatima har rawa jikinta yakeyi kamar mai zazzabi, a hankali ya lallabata suka kwanta. Duk yanda ta kai ga so ta ki sallama masa kasawa tayi, haka ta hakura ta bada kai bori ya hau.

...

A hankali yake busa mata iska a kunnenta, ta bude idonta a hankali ta dan noke wuya. Yayi dariya sannan ya sumbaci gefen wuyanta, ya sa hannu ya juyo da ita ta kwanta a rigingine ta yanda fuskarsa take kallon tata fuskar ba tare da zuba mata nauyinsa ba.

Suna hada ido tayi kasa da idonta a kunyace, yayi dariya yace

‘Sarkin tsoro tashi gari ya waye.’

Tayi murmushi ta rufe fuskar da tafukan hannunta, ya sa hannu ya dauke hannuwan nata yana fadin

‘Cire hannun zakiyi naga idon matsoraciya.’

Ta zumburo baki tana kokarin hadiye dariyar da ta taso mata tare da rufe idonta.

Haka suka wuni ranar yana mata dariya, suka bude sabon babi na soyayya domin bata taba sanin Ahmad ya iya soyayya ba sai yanzu.

Kuma ko ba a gaya mata ba ta san Allah ya amsa rokonta, don haka ta godewa Allah da bata gayawa Ahmad rayuwarta ta baya ba.

___

Tun bayan da tayi blocking din Mukhtar a waya bata kara ji daga gareshi ba, sai dai kawai tana cikin damuwa. Ta kasa cire yaran daga zuciyarta, musamman Nana.

Yaya Hajiyayye ce ta kawo musu ziyara yau, ita kadai ce ta zo domin yara suna islamiyya. Suna zaune da ita Umma da Safiyyan a falo , lissafi sukeyi saboda Baban Hotoro ya ce suyi lissafin kudin kayan daki shi da ‘yanuwansu zasu bayar don a sayawa Safiyyan. Bayan sun gama lissafi duka Yaya Hajiyayye ta rubuta ta ninke ta saka a jaka ta cewa Umma

‘Ina fita daga nan zan je na kaiwa Baban Hotoro, idan na bawa Yaya Habibu ba zai kai ba cewa zai yi su barshi. Kuma haka sukeyi, shi yasa ma Baban yace a kawo tunda ma ko nawa suka bayar karba za ayi.’

Jimawa kadan ta dubi Safiyyan sannan ta dubi Umman tace

‘Umma ita wannan menene yake damunta naga duk tayi zuru-zuru sai kace auren fari.’

Safiyyan tayi dariya, Umma tace

‘To wallahi kin ganta dai, nayi tambayar duniya tace babu komai. Sai kace mai gudawa sai karewa takeyi kullum.’

Safiyyan tace

‘Umma wallahi babu fa wata matsala, kawai dai yanayi ne.’

‘Uhm, ma ji idan tayi wari.’

Umma ta fada tare da mikewa ta barsu a falon. Hajiyayye ta dawo kusa da Safiyyan tace

‘Idan wani abun ne ai gara ki fada don Allah,ba sai an je an kuma auren da na sani ba.’

‘Wallahi Ya Hajiyayye babu komai.’

‘Ai shikenan.’

Sukayi shiru na dan lokaci, jim kadan Safiyyan tace

‘Ya Hajiyayye yanzu kuma sai na je nayi aure na haifi wasu yaran na manta da su Nurain?’

Hajiyayye tayi murmushi tace

‘Yauwa, ni dama na san da akwai abinda kika saka a ranki kike wannan ramar kamar kudin guziri.’

Ta sunkuyar da kanta ta fara nadamar gaya mata abinda yake damunta. Yaya Hajiyayyen ta cigaba

‘Babu inda uwa ta taba mantawa da yaranta duk duniya, kuma ba za a fara a kanki ba; ke mace ko dan shege ta haifa yana ranta balle ke da kika haifi yaranki cikin amincin Allah. Amma ai ba ke kika zabi hakan ba, haka ubansu ya zaba tunda shi ke rike da aure. Kuma tsari ne na ubangiji. Za kiyi aure ki haihu amma su Nana suna nan tare dake , ko bai kawo miki su ba za a daukosu a kawo miki su kuma addu'arki tana tare da su. Bana son ki sawa kanki wannan damuwar don ba zaki koma gidan Mukhtar ba don naji Sabir yace ya fara zuwa nemanki. Kuma dai kin san me Baban Hotoro yace ko? Muddin yana numfashi A.A ne mijinki. Ki kwantar da hankalinki kamar yanda shi ma ya sakeki ya kwantar da hankali har ya sami natsuwar auren wata. Don Allah ki natsu kafin sati biyar din nan kin ji?’

Ta dago ta kalleta tace

‘In Sha Allahu Yaya.’

‘Yauwa. Ke ba matar Mukhtar bace kuma kin fi karfin zama matar Mukhtar in Sha Allahu.’

Haka Yaya Hajiyayye ta dauki lokaci tana nuna mata ta cire damuwa daga rantata dan mayar da jikinta kafin bikin ya karaso.

Daga baya tayi musu sallama ta tafi.

…….

Maganganun Yaya Hajiyayye sun samar mata da nutsuwa don haka gadan-gadan ta shiga gyaran jikinta. Maganin sanyi ta fara neman bayan ta gama kuma ta shiga aikin gyara. Cikin sati biyu ta kara kyau ta murje duk da har yanzu da ‘yar ramar.

Saura sati uku biki A.A ya zo da kanshi ya dauki Yaya Habibu wanda sun riga sun zama kamar abokai ya kaishi don ya gano gidan da za a saka Safiyya. Flat ne guda biyu a cikin gidan sai dai flat din barrister ya fi girma, na Safiyya shine a karshen gidan kuma daki uku ne da falo. Kusan duka dakunan ya zuba furniture sababbi don wasu ma ba’a bude ba.

Yacewa Habibu ya duba abinda babu kawai shi za a kawo.

Bayan Yaya Habibu ya tafi Kuma da kansa ya dauki hotunan gidan da kayan ya turawa Safiyyan. Don haka kudin da su Baban Hotoro suka hada mata na kayan daki Yaya Habibu ya karbi account number dinta ya tura mata yace idan ta tare ta ja jari.

Zuwa yanzu abu daya ne yake bata tsoro, yanda zata zauna da barrister. A iya labaran da ta samu mace ce mai ilimi kuma ga gayu don wasu ma suna makin abinda AA zai yi da wata mace bayan Barrister. Don haka Safiyya ta zage ta gyara jikinta, ta yi order din hadaddun turarukan wuta da Humra special order a wajen Xee Yaxeed me turaren wuta (08123164559) sannan Kuma tayi order kayan kamshin girki na Jolly Flavors daga wajen Innar su Amal; domin kamar yanda ta fada ba za a fita ilimin boko ba kuma a fita kula da miji da kuma kamshi mai dadi ba.

Sunyi maganar aiki da shi yace ta cigaba da aikinta direba zai dinga kawota, amma idan an kwana biyu zai tafi da ita Abuja sai ya samo mata wani aikin a can ko kuma ta bude saloon tunda ya ga tana son harkar gyaran gashi.

.....

Yau saura sati uku a daura auren Safiyya da A A. Ko daya Barrister bata bashi matsala ba, ta dai gaya masa bata son ya dinga yi mata maganar matarsa kuma idan ta tare ita ba ruwanta da wata amarya. Ya yarda da hakan duk da bai ji dadi ba don shi zai so yaga iyalansa ko ba sa shiri to kada su zama ba ruwan kowa da kowa.

Haka ya hakura ya kyaleta tunda dai bata bashi wata babbar matsala ba.

Ita kuwa a nata bangaren gani takeyi Safiyyan ba ‘yar kowa bace kuma ba wani ilimi ne da ita ba don haka ba zata bata lokaci ta a kanta ba, ta san dai bata isa ta kwace mata miji ba tunda yana sonta itama tana sonsa. A tunaninta Safiyya bata ma kai ayi kishi da ita ba, shi kanshi auren nasu ma gaba daya gani takeyi ba zai yi wani tasiri ba.

Ajjiye wayarta kenan ta gama booking din lalle wanda za ayi mata ranar kamu; domin A.A yace mata ‘yan uwanshi suna yin kamu don haka za su suyi mata kamu kamar na budurwa. Kafin ta tashi daga wajen ta jiyo hayaniyar Nurain da Nana a tsakar gida, tana jinsu suka gaida Umma sannan suka kwaso da gudu. A tare suka fada jikinta har sai da suka kwantar da ita a kan gadon da take zaune.

Ta daga su ta tashi tana dariya, ta lakacewa Nurain hanci tana fadin

‘Kai har yanzu baka girma ba ko? Kun hadu da kanwarka kuna nema ku kadani.’

Suka sa dariya.

Bayan sun gaisa Nana ta gaya mata sakon su Hajiya da suka ce a gaisheta Nurain yace

‘Mama jibi Saturday za ayi speech and prize giving day a makarantarmu, don Allah Mama ki zo. Kin san me? An yi musabaka na zo na biyu, nazo 1st position a class kuma nine best student in Maths. Duk ranar za ayi ta kirana ana bani gift kawai, don Allah Mama ki zo har party zamuyi ni da friends dina in an gama kuma ma..’

Safiyya ta katseshi tana murmushi

‘Ka dinga jan numfashi idan kana zance mana Nurain.’

Ya rufe ido ya ja numfashi sannan ya bude idon yace

‘To Mama na ja numfashi. Zaki zo?’

‘Zanzo Nurain, ai na ji dadi sosai ka burgeni. Zanzo na ga gift dinka kuma nayiwa Anti da Ustaz godiya da suka iya koya maka karatu.’

‘Yauwa Mama, za muyi selfie ma da wayarki.’

Tayi dariya ta juya wajen Nana wadda ta sha kunu

‘Nanata ke kuma me za a baki?’

Ta kara zumburo baki sannan ta bada amsa

‘Mama 5th fa na zo amma Uncle bai ce za a bani komai ba kamar wata dakikiya, na iya karatu, na iya hadda kuma har handwriting ma na iya da drawing amma ni ba za a bani komai ba wai.’

Ta rungumota tana murmushi

‘Kai-kai-kai! Gaskiya Uncle bai san kokarinki ba, amma zanzo in bashi labari. Kuma ni da kaina zanzo miki da gift wanda ya fi na kowa kyau.'

Nan da nan ta fara dariya, shi kuma Nurain ya sa rigima shima dole sai Mama ta bashi wani gift din. Sai da suka gama musu da rigimarsu sannan Nurain ya rufe baki yace.

‘Au Mama Baba Saifu ne ya kawo mu kuma yace kada mu dade yana waje.'

Nan ta tashi ta saka su a gaba ta fito dasu, suka gaisa da Saifullahi sannan ta saka su a mota. Sai da suka rufe kofar motar Nurain ya leko yace

‘Mama kada fa ki manta, jibi ne karfe goma na safe kuma ku taho da kowa Hajiya, Baba Sabir, Anti Hamee harda Anti Hajiyayye ma da kowa na gidanta.'

Tayi dariya tace

‘Inaga ma dai Nurain duka mutan garin zan gayyato muzo.'

Sukayi mata sallama suka wuce suna dariya.

Gari na wayewa ta shirya ta tafi Sahad stores dake kan titin Zoo road domin ta cika alkawarin da ta yiwa Nana. Tana cikin zagayawa wajen kayan wasa A. A ya kirawota, bayan sun gaisa yace

‘Kina ina ne naji hayaniya, na zata an yi sallama da islamiyya.’

Tayi dariya

‘An yi sallama da islamiyya ranka ya dade , na dan zo shopping ne.’

Nan ta bashi labarin alkawarin da tayiwa yara, don haka sukayi sallama ya barta ta cigaba da sayayyarta.

…….

Karfe bakwai da rabi kira ya shigo wayarta lokacin tana kwance a gefen gado tana ta dube-dube a wayarta. Tana kalla taga Hajiya tayi murmushi don ta san Nurain ne tana dagawa kuwa taji muryarsa. Ko gaisheta bai yi ba yace

‘Mama yau ne fa, ai baki manta ba ko?’

Tayi dariya

‘Ban manta ba sarkin zumudi.’

‘Mama menene zumudi?'

‘Idan na zo zan gaya maka kaji, ka bani Hajiya na gaisheta.’

‘Ta shiga wanka ai.’

Nan sukayi sallama tana yi masa dariya.

Karfe goma da rabi suka kama hanya ita da Sabir.

Inda yaran suka zauna da ban da inda iyayen yaran suke, don haka cikin yara ta hango Nurain din yana ta faman daga mata hannu yana dariya. Itama ta daga masa hannu.

Tun kafin ta karasa wajen zaman iyayen yara ya hangota, ta kara kyau sai wani sheki take tana walwala. Wajen zaman mata daban da na maza don haka ya taso daga inda yake zaune ya nufo su.

Tun daga nesa yake ta faman yi mata murmushi don haka itama ta mayar masa da murmushin, yayinda shi kuma Sabir ya kara tsuke fuska yace

‘Don Allah Yaya Safiyya ki hada bakinki, sai ki dinga wani yagewa mutumin nan baki anyhow.’

Ta sa kafa ta taka masa yatsa, ya dan ja baya. Tayi masa dariya tace

‘Uban ‘yayanka ne dai ko kana so ko baka so.’

Ya karaso ya mikawa Sabir hannu suka gaisa, yayinda Sabir din yayi sauri ya bar wajen ya wuce wajen zaman maza ya zauna yana hangosu.

Suka jero suna karasowa wajen. Bayan sun gaisa tayi masa murnar samun nasarar Nurain, bayan ya amsa yace

‘Sai a nan zan iya ganinki Safiyya, wato yanzu ni kike gudu ko?’

Da mamaki ta kalleshi tace

‘Ka je gidan Umma bana nan ne?’

‘Ni na isa nazo bayan kin ki ki bude layika in nemi izinin zuwan. Ina wayarki?’

‘Tana wajen Sabir.’

Yayi yake kawai domin da so yayi ya karbi wayar ya cire lambarsa daga blocking din da ta yi masa.

Suka karaso wajen zaman iyayen, ta karasa wajen mata ta zauna yayinda ya koma inda ya taso ya zauna bayan da ya sanar da ita idan an tashi yana son ganinta.

Malamai daban daban suka gabatar da bayanai bayan nan kuma yara suka fara rawa abun sha’awa ana ta kallo ana tafi.

Kamar da gefen ido ta hango A A yana shigowa filin makarantar, ta juyo ta kalli wajen sosai tabbas AA ne da wasu ledoji guda biyu a hannunsa masu kyau. Yana ta dube-dube kamar yana neman wani, ta san babu yaransa a makarantar don haka ta sa rai ita yake nema. Ta mike tsaye domin taje taji me yazo yi domin a jiya da sukayi waya ce mata yayi yana Abuja.

Tana mikewa Mukhtar ya mike don ya zata wani abu take nema. Daga tsakiyar mata ta tashi ba tare da kalli inda yake ba ta bi ta daya gefen ta nufi hanyar gate. Don haka ya kai dubansa inda ta nufa, inda ya ci karo da fuskar AA yana ta murmushi a daidai lokacin da ya hango Safiyyan. Nan take ya tsuke fuska zuciyarsa ta fara kuna; sau daya ya taba ganin mutumin nan amma ya ganeshi, baya son ganinsa saboda shine wanda yake shirin shiga tsakaninsa da Safiyya. Tabbas da za a bashi dama ya kashe mutum daya a duniya ba tare da da wani sakamakon ba to zai kashe mutumin nan. Ya koma ya zauna yana huci saboda takaici, ya kasa daina

kallonsu duk da yanda kallon nasu yake kara masa zafi a zuciyarsa. Ba zai taba bari wannan mutumin ya aure masa Safiyya ba sai inda karfi sa ya kare.

Suka tsaya suna fuskantar juna, kuma da yake filin makarantar duka bashi da girma sosai tas yake hangosu.

Ta dubi AA tana murmushi tace

‘Mijin Barrister, sai gaka a Kano.’

Yayi dariya yace

‘Kanwar Barrister. Na biyo dare na dawo don naji electrician yana so yayi min shiririta a dakin amaryata.’

Sukayi dariya gaba daya.

Suna nan tsaye suna ta yiwa juna murmushi wanda Mukhtar yake ganin kamar da gayya sukeyi Nurain ya sheka da gudu ya tafi wajensu. Ya rage tsawo ya gaida AA, kafin ya amsa dubeta yace

‘Mama kada fa ki tafi an kusa fara kiranmu.’

Ta shafa kansa tace

‘Ba tafiya zanyi ba Nurain, ina nan.’

AA ya mika masa hannu suka sake gaisawa yayinda Safiyya ta gabatar masa da A A din. Ya dan rage tsawo ya dawo dai-dai da Nurain ya mika masa babbar ledar da take hannunsa yace

‘Wannan naka ne saboda Mama tace min kaci musabaka na siyo maka, wannan kuma na Nana Khadija ne.’

Ya leka ledar yana dariya ya dubeshi yace

‘Nagode sosai, next term ma 1st position zan dauka a musabakar.’

‘Da kayau mutumina, Allah ya kaimu.’

‘Nagode. Mama ki rike min na koma kada a fara kira.’

Ya fada yana mika mata ledar, tana karba ya zura da gudu ya koma inda ya fito. Suka nufi gate ita da AA tayi masa rakiya, kafin su karasa gate din tayi masa sallama ta koma ciki. Tunda ta koma ya sunkuyar da kai yana kokarin hadiye malolon da ya tokare masa zuciya.

Bayan ta zauna ta duba ledodin; digital Qur’an ya kawo wa Nurain yayinda ya kawowa Nana chocolate, ta hada ta ajiye musu.

Aka cigaba da taro har azahar sannan aka gama. Suka gaggaisa da malamai da mutane. Duk yanda Sabir yake son ya raba Safiyya da Mukhtar shi Mukhtar din yaki ya bar kusa da ita, don haka a jere suka nufo gate yayinda Sabir yake binsu a baya. Gashi wayar Safiyyan tana hannunsa balle yayi mata waya.

Suna fitowa daga gate taga motar AA, hadaddiyar marsandi ce ta zamani baka kirin sai sheki takeyi. Ta kalli motar tana mamaki, direban da yake tsaye bayan motar ya karaso gabanta ya sara kamar wata soja, yace

‘Ranki ya dade ke nake jira, yallabai yace a kaiki duk inda zaki je.’

Mamaki ya bayyana a fuskarta tace

‘Shi kuma a me ya tafi?’

‘Tito ne yazo ya daukeshi.’

Ya sake sarawa yace

‘Idan kin gama ina nan ranki ya dade.’

Kafin ta amsa ya koma jikin motar ya tsaya.

Tana juyowa Mukhtar yace mata

‘sai an jima.’

Kafin ta amsa ya bar wajen, don haka ta wuce wajen motar AA. direban ya bude mata kofar baya yayinda Sabir ya shiga gaba yaja mota suka wuce.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA BAKWAI

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA TALATIN DA TAKWAS

38

Allah ne ya kaishi gida lafiya ba don yana tuki a hankali ba, ji yake kamar zuciyarsa zata fito ta bakinsa saboda kunar da takeyi.

Ya za ayi yana ji yana ga wannan mutumin ya aure masa Safiyya? Ba zai yiwu ba.

Da kyar ya amsa sannu da zuwan da Jamila take masa ya wuce daki, ya rufo kofa. Ta ja tsaki ta ci gaba da abinda takeyi.

Sai da ya sakawa kofar mukulli sannan ya zauna akan gadon kamar wanda aka tura, ya sa tafukan hannunsa ya rufe fuskarsa yana jin hucin numfashinsa a hannunsa wanda yayi dai-dai da sarawar da kansa yake yi; idan dai bai bata a lissafin da Baban Hotoro ya gaya masa ba yau saura sati biyu kenan a daura auren Safiyya.

‘Inna lillahi wa inna ilaihi rajiun.’

Ya fada a fili tare da mikewa tsaye, ya fara kaiwa da kawowa a dakin; wai me ya farune ya bari har Safiyya ta subuce masa haka? Gashi kawo yanzu ya tatabbatar duk wani abu da ake samu na nutsuwa a aure zai samesu ne kadai idan Safiyya ce matarsa.

Ya koma ya zauna a gefen gadon a daidai lokacin da dabara ta fado masa; tabbas Safiyya tana kaunar yaranta, idan akwai abinda yake mata ciwo a rabuwarsu bai wuce yanda ya rabata da yaran ba. Don haka zai aika mata Nurain ne ya tsaro masa ita; musamman ma da yake Nurain din yana yawan maganarta, yana so su dawo gidansu kamar yanda yake da. Don haka wannan shine damarsa ta karshe a

tsakanin sati biyun nan ya rikita musu ita, in ya so in an taru ranar daurin auren a daura da shi.

Nan da nan ya mike ya dauki mukullin motarsa ya fito, babu kowa a falon don haka ya fice kai tsaye. Saida ya tsaya a makarantar almajiran dake can cikin unguwarsu ya bawa malamin sadakar naira dubu goma yace a yi masa addu’a a kan bukata da ta taso masa sannan ya wuce gidan Hajiya.

Ranar litinin da safe Safiyya tana daki tana wankewa Umma bandaki ta jiyo Umman a tsakar gida ita da Nurain. Ta tsame hannunta daga ruwan ta fito don ta gani da idonta, tunda shekaranjiya suka rabu a wajen taro basuce mata za su zo ba.

Tana fitowa ta samesu Nurain yana yiwa Umma bayani

‘Abba ne yace Baba Aminu ya kawo mu muyi huta, idan mun yi kwana biyar a zo a daukemu.’

Nan da nan aka shiga murna ana ta hidima. Umma tana kula da yanda jikin Safiyyan yayi sanyi take ta wani faman zare ido tunda su Nurain suka shigo, shi yasa ma tayi zargin akwai abinda ubansu ya shirya ya kawosu a dai-dai wannan lokacin; domin tunda ya saketa ba a taba kawosu su kwana ba sai yau.

Haka dai ta kyalesu aka cigaba da hidimar gidan.

Suna dakin Umma inda Nana take bacci kan gado yayin da Umma da Nurain suke sallar la’asar, suna sallame sallar ya fice da gudu kamar wanda damam a kan kaya yake sallar. Dakin Safiyya ya shige inda ya sameta tana azkar a kan dadduma, ya karasa ya zauna a gabanta yana kallonta. Bayan ta gama azkar din ta dubeshi tace

‘Ya dai? Nana tayi bacci ta barka ko?’

Yayi dariya bai ce komai ba. Sukayi shiru na dan lokaci, jim kadan yace

‘Mama.’

Ta kalleshi ba tare da ta amsa ba, ta dade rabon taga Nurain ya shiga damuwa kamar yanda fuskarshi ta nuna yanzu. Cikin yanayi na kulawa tace

‘Na’am Yaya Nurain.’

Yayi murmushin yake

‘Mama don Allah kada ki auri mutumin nan da ya bani qur’an, ki dawo gidanmu kinga abbanma sabon gida zai siya mana.’

Ta kasa bashi amsa saboda yanda jikinta yayi sanyi, ta faki idonsa ta goge kwallar da ta taru a gefen idonta. Ya cigaba

‘Kinga shi da yaransa a gidansa kuma su mamansu tana nan, Kinga Halimatu ma Mommynta tana nan amma ni da Nana bamu da Mommy. Zamu fi jin dadi idan kika zo muka koma sabon gidan da Abba zai siya mana.’

Da kyar ta hadiye hawayen da ya taso mata ta lalubi muryarta tace

‘To ai kuna gidan Hajiya kuma na san Hajiya tana kula daku sosai ga baba, Anti ga su Baba Aminu ma duk suna kula daku.’

Ya sake langabe kai kamar zai yi kuka

‘Mama ai kowa ya fi son Mamansa, kema kinga ai kin fi son ummanki. Muma muna so muyi bacci tare dake, kiyi mana abinci idan bamu da lafiya ki bamu magani. Yanzu kinga idan kika tafi gidan mutumin nan su yaran gidan suna da Mama guda biyu kenan mu kuma bamu da kowa sai Hajiya, ko Mama?’

‘Ba haka bane Nurain, ni mamanku ce har abada, kuma duk inda naje za a kawo ku kuma nima zan dinga zuwa ina dubaku.’

‘Dan Allah dai ki dawo gidanmu Mama, muma mu zama muna da Mamanmu.’

Tayi shiru yayinda shima yayi shiru yana tunani; duk abubuwan da suke faruwa bai fahimcesu sosai ba saboda karanci shekaru, amma dai ya san babu abinda yake so a halin yanzu fiye da gidansu ya koma kamar da; da Abbansu da Mama. Ya kalleta tayi shiru kawai tana kallon bango yace

‘Mama zaki dawo muje mu fara gyara gidan?’

Tayi murmushin yake tace

‘Sai nayi tunani Nurain.’

Suka sake yin shiru na tsawon lokaci, jimawa kadan yace

‘Mama kinyi tunanin?’

Tayi dariya tace

‘Ak ba yanzu ba sai an kwana biyu.’

Sallamar Umma ce ta katsesu, ta daga labulen tacewa Safiyya

‘Kin san Hajiya Suwaiba tana jiranki kije ki karbo dinkunanki tunda yau kika ce mata.’

‘Uhm, Umma inaga idan Sabir ya dawo ya karbo min kawai.’

‘Ai kuwa tashi zakiyi ki tafi tunda tace kije da kanki don ki gwada a tabbatar sunyi kafin ki taho da su, kuma kin san Inna Hajara tana nemanki baki je ba tunda hanyar ne idan kika karbo kayan sai ki tsaya a gidanta in ya so shi Sabir din sai ya zo ya daukeki tunda na san idan Inna ta sa ki a gaba sai ku kai isha bata sallameki ba.’

Inna Hajara kanwar mahaifinsu Safiyya ce wadda itace auta a gidan, macece mai ilimin addini da dattako don haka duk yarinyar da za a aurar a dangi sai taje and mata lecture ta musamman. Shi yasa da aka kai goron biki tace a turo mata Safiyyan ma.

‘Umma ai ko daga baya ma n…'

Umma ta katseta kafin ta karasa

‘Safiyya tashi zakiyi ki tafi, in dai yara ne da aka kawo ai tare zaku kwana ko? Kije ki dawo suna nan.’

Yanda Umma take magana ta san bata da wata mafita don haka ta mike ta fara shiryawa yayinda Umma tasa Nurain a gaba suka fice daga dakin.

Bayan ta yiwa Umma sallama ta fice Umman tabi bayanta da kallo tana mamaki; lallai shi yasa hausawa suka ce mai ‘da wawa. Saura kwana goma sha daya a daura auren amma an turo yaro zai jagula mata lissafi to ba zai yiwu ba.

Zuwa yanzu itama Umman haushin Mukhtar din take ji; shekara uku yarinyar tana jiransa Bai dawo da ita ba sai yanzu da ta sami miji mai kaunarta sannan zai dinga kawo mata fitna. Babu yanda za ayi a yanzu ta bari Safiyya ta sake auren Mukhtar sai dai duk abinda za ayi ayi, yaran ma zata san yanda zatayi da su bazasu daga mata hankali ba.

……..

Safiyyan bata dade da fita ba Yaya Hajiyayye da Hamida suka shigo, kasuwa sukaje suka karaso sayayyar bikin daga can suka wuto nan don su kawo wa Umma kayan. Bayan sun gaisa Hamida take tambayarta yaushe aka kawo su Nurain; nan Hajiyan ta basu labarin abinda yake faruwa. Yaya Hajiyayye ta fara fada tana cewa

‘Umma in ba ayi da gaske ba a kan yarinyar nan fa so take ta dawwama a matar Mukhtar, ni kuma wallahi ya fice min a rai mara kunya. Kai da aka bata lokaci ana jira sai yanzu zaka dawo.’

Hamida tace

‘Ba dai yara bane, yanzu zan yi maganinsu. Ba zasu sake ganinta ba sai ta zama matar AA.’

Ta kwalawa Nurain kira wanda suke tsakar gida suna wasa tare da Sajida ‘yar autar Yaya Hajiyayye wadda sa’ar Nurain din ce. Gaba daya suka shigo dakin da gudu suka fada kan Hamida suna dariya. Yaya Hajiyayye tace

‘Kai kuyi a hankali kada ku lotse mana hancin jariri.’

Suka kyalkyale da dariya, Hamida ta dubi yaran tace

‘Duk ku shirya gidana zamu tafi, gobe muje park na shop rite, jibi kuma na kaiku gidan zoo sai mu dawo daku ko?’

Nan da nan suka sa ihu, Sajida ta dubi Mamanta tace

‘Mommy nima fa binsu zan yi.’

‘To ki tafi na aiko muku da kayanki.’

A take Hamida ta yiwa maigidanta waya wanda ba tare da bata lokaci ba ya zo ya kwashesu ita da yaran suka tafi gidan bayan ta gayawa Umma ba zasu dawo ba idan Aminun yazo yaje gidanta ya daukesu.

Sai bayan magriba sannan Safiyya ta shigo gidan dauke da kayan dinkinta niki-niki. Can gidan Inna Hajara ta dade tunda sakata tayi a daki tana ta nasiha har sai da aka kira magriba.

Kafin ta ajiye kayan ta fara tambayar Umma ina yaran, tace

‘Sun bi Hamida gidanta inaga sai gobe za ta dawo da su.’

Bata so hakan ba domin tana so su gama maganarsu da Nurain, amma ta san idan tayi magana Umma ba zata saurara mata ba. Don haka ta ajjiye kayan a dakin Umma ta koma nata dakin.

Tana shiga dakin ta kirawo Hamida, ita kuwa tana dauka ta saka a hands free ta bawa yaran. Gaba daya suke magana duk sun cika mata kunne

‘Uncle ya siyo mana burger da ice cream da chocolate, gobe zai kai mu fun park muyi wasa.’

Haka sukayi tayi mata hayaniya daga baya Hamidan ta karba tace mata sai jibi zasu dawo.

Haka ta hakura ta kwanta tana ta wasi-wasi; ta daina son Mukhtar amma tana son yaranta kuma itama tayi kewarsu. Ta san Mukhtar ne ya aiko Nurain amma wannan ya nuna yana so ta dawo kenan. To ko dai hakura zatayi ta koma ta zauna ko don yaranta?

Haka tayi ta tufka da warwara ita kadai. Ko da AA ya kirawota ma haka tace masa kanta yana ciwo don haka babu wata hira sukayi sallama ya barta don ta kwanta.

Washegari haka kowa ya cigaba da harkarsa yayi banza da ita. Har Sabir ma kin kulata yayi domin ta fara bashi haushi, yana ji a ransa kamar sai ya je ya korawa Mukhtar jawabi sannan zai kyaleta.

Haka tayi ta hidimarta cikin damuwa suna kallonta suna ta shirin biki yayinda ita kuma take musu kallon basa tausayin yaranta.

……

Washegari da yamma Hamida ta hada kayanta da na yaran ta kirawo almajirinta ta bashi ya wanke mata. Bai jima da fita ba ya dawo ya mika mata takardar yana fadin

‘Wannan a aljihun yaronki na sameta inaga ko aikensa akayi.’

Ta karba shi kuma ya koma ya cigaba da wankinsa.

Suna can suna kallon cartoon a falo don haka ta wuce da takardar dakinta ta zauna a gefen gado sannan ta fara dubawa; wasikace a cikin envelope wadda har likewa akayi da gam.

Tana ta mamakin inda Nurain ya sami wasika a envelope haka ta bude ta zaro takardar dake ciki, tana bude takardar mamakinta ya karu musamman da taga an rubuta sunan Safiyya daga sama:

“Safee”

Ta wuce kasan takardar ba tare da ta karanta takardar ba don taga waye zai rubutowa Safiyya wasika.

“Mukhtar”

Shine sunan da aka rubuta a kasan takardar, ta tuntsure da dariya sannan ta mike ta tura kofar dakin ta saka mukulli don kada yaran su shigo su ga takardar, ta koma ta zauna ta karanta kamar haka

“Kafin nace komai ina mai sake baki hakuri, in Sha Allahu duk abinda ya faru ba zai sake faruwaba, nayi miki alkawari.

Ni da yara muna kewarki. Bamu makara ba Safiyya ki yi hakuri mu mayar da aurenmu ko don yaranmu. Na tabbatar ko yanzu kika ce zaki aureni babu wanda zai hana sai dai ke din.

Ina sonki Safiyya kuma ke kin san ina sonki, abinda ya faru jarrabawace daga Allah. Na dan bazaki so ki rushe gidanki kuma kije kina gina gidan wani ba, kiyi hakuri mu maida aurenmu; mu hadu mu kula da tarbiyyar yaranmu kamar yanda iyayenmu suka yi mana.

Don Allah ki kirani a waya yanzu ko kuma ki cire layina daga blocking din da kikayi ni sai na kirawoki, please.

Your’s

Mukhtar.”

Hamida ta kyalkyale da dariya tana juya takardar a hannunta, tace a fili

‘Mugu, Allah ya kama ka.’

Ta janyo wayarta ta dannawa Sabir kira, yana dagawa tace

‘Wallahi akwai wata jarida kazo yanzu na siyar maka da ita.’

Tana magana tana dariya, Sabir yace

‘Wa kika cuta ne haka zaki tsaga min kunne.’

‘Don Allah kazo yanzu.’

‘Allah ya soki da motar Yaya a hannuna gani nan zuwa amma wallahi da bazan zo ba.’

Sukayi sallama suka ajiye wayar.

Kafin wani lokaci ya isa gidan Hamidan. Tana jin tsayuwar mota ta san shine don haka kafin ya kwankwasa ta zo ta bude masa gate din. Yana shigowa ta mika masa takardar tana fadin

‘Mutuminka ne yayiwowa Yaya Safiyya aike a aljihun Nurain.’

Ya karba yana mamaki, nan a farfajiyar gidan suka tsaya ya fara karantawa. Yana yi suna dariya. Bayan ya gama ga dubeta suka kece da dariya yace

‘Mugun kaya, ya ji wuta yana rubuta kalaman soyayya. Kin san ranar da mukaje makarantar su Nurain A.A ya kunnashi da yawa.'

Nan ya bata labarin abinda ya faru a wajen speech and prize giving day din su Nurain.

‘Ai dole ya rubutawa budurwa wasika ya ga za a ci shi yaki har gida.’

Suka kyalkyale da dariya Sabir yace

‘Don Allah kada ki dawo da yaran nan daga nan ki mayar dasu gidansu idan an gama bikin sa dawo, tunda daman ba don Allah ya sa aka kawo su ba.’

‘Ai in Sha Allah bazasu sake gamin Yaya Safiyya ba sai ta zama matar AA. Sun bani tausayi amma haka ubansu ya zabar musu, idan ta koma wahala kawai zata cigaba da sha har bakin cikinsa ya kasheta su zama marayu.’

Ko gidan bai shiga ba daga nan sukayi sallama ya sa wasikar a aljihu ya wuce yana dariya.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA TAKWAS

MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

FIKRA WRITERS ASSOCIATION

BABI NA TALATIN DA TARA

39

Tun Safiyya tana sa rana Hamida zata dawo da su Nana har ta gaji ta hakura. Haka ake ta shirye-shiryen biki amma hankalinta baya wajen, tunda Umma ta gane matsalarta ta shareta suka cigaba da hidimarsu. Bata son ta cewa Hamida ta dawo dasu don kada Hamidan taga bata kyauta ba don haka ta daure aka cigaba da shiri.

.....

Tun ranar da ya sa Aminu ya kaisu gidan su Safiyya yake jiran kiranta amma har yau Juma'a shiru, don ranar litinin din har wajen dayan dare idonsa biyu yana jira Safiyya ta kirawo shi amma shiru. Sai da kyar bacci barawo ya sace shi.

Gashi har kawo yau shiru, ko Hajiya ma tace basu kirawota ba don haka ya san suna can suna jin dadin hutunsu.

Jikinsa yayi sanyi, saura kwana bakwai yau a daura auren Safiyya da mutumin da ya tsana, shikenan yayi nasara ya rabashi da matarsa uwar yaransa. Zuciyarsa a jagule ya kirawo Aminu yace gobe da safe yaje ya dauko masa yaransa.

Washegari wajen karfe goma Aminu minu ya isa gidan Umma don ya dauko su, yana isa aka ce masa suna gidan Hamida ya bari za a dawo dasu. Yace gara dai ya daukesun kawai don haka aka yi masa kwatance ya wuce can ya daukesu.

Tunda Safiyya taji labari sun wuce daga gidan Hamida ta kasa tare hawayenta, don haka Umma ta saka ta a gaba ta ci mata mutunci sannan tace

'Idan mutuwa zakiyi to ki shirya ki mutu tun da wuri don ba zaki koma gidan wannan mutumin ba. Yara muma muna sonsu kuma muna tare da su in Sha Allahu amma tunda aka kawo yanzu to kowa tasa ta fissheshi, Allah ya raya mana su.'

Ta bar Safiyyan a nan tana kukan takaici; da sune suke so ta koma gidan Mukhtar amma yanzu sun tsangwameta saboda sunga tana tausayin yaranta. Ita a halin

yanzu ma bata san me take so ba kuma bata san wa take so ba, so kawai takeyi a barta tare da yaranta.

Gashi AA yana maganar Abuja zai tafi da ita ko Lagos don haka ta san nisa zata yi musu sosai; idan ta tuna sai zuciyarta ta sake karyewa.

Sai da yamma Yaya Hajiyayye tazo ta sakata a gaba da fada da nasiha, ta kifa kai a kan cinyar Yaya Hajiyayye tayi kukanta ya isheta Hajiyayye tana lallashinta daga karshe tace mata

‘Ki kwantar da hankali ki ke din matar AA ce ba matar Mukhtar ba da izinin Allah.’

Saida gari ya waye sannan ta dan fara samu nutsuwa saboda ta kwana tana sallah da addu’a. Aka cigaba da shirin biki domin a satin ne zata je gyaran gashi da gyaran jiki. Haka aka cigaba da shirin biki jikinta a sanyaye, ranar laraba tana kallo aka zabi mutum uku da Yaya hajiyayye suka tafi don gyara mata gidan. Bayan sun fice kuma mai kunshi ta zo ta zana mata mai dankaren kyau; dama gashi fatarta sai santsi da kamshi kawai takeyi. Kafin dare amarya ta fito fes da ita sai dai kawai kana kallonta zaka ga damuwa a fuskarta, domin har wani share kwalla takeyi.

Ranar Alhamis za ayi kamu a nan gidan Umman don haka tun safe su Inna Hajara suka zo da sauran yanuwan babansu Safiyya, nan da nan gida ya kacame da hayaniya.

Tunda amarya tazo gaida iyayen nata Inna Hajara ta san da matsala, ta san ba zai wuce a kan yaranta bane take bata rai don sunyi maganar da Umma a waya. Nan take Inna ta jata suka kule a dakin su Safiyyan da yake babu kowa a ciki. Bayan sun zauna a gefen gado Inna ta dubeta tace

‘Ya akayi ne Safiyya?

Sai kace wadda za ayiwa auren dole? Kina ta wani zare ido.’

Kawai sai ta fada cinyar Innan ta fashe da kuka, sai da tayi mai isarta sannan ta dago ta dubi Innan tace

‘Inna sai naga kamar ban kyauta ba idan na tafi na cigaba da haihuwa na bar yarana tunda ubansu yanzu yana so mu dawo.’

Inna tayi murmushi mai sautu, ta dago Safiyyan ta kalli fuskarta ta share mata hawaye sannan tace

‘Ki bani hankalinki nan Safiyya. Uban yaranki baya son ku dawo, ya dai ga zaki auri wanda ya fi shi, shi yasa ya dawo ya mayar dake cikin wahalar da kika riga kika sani. Idan namiji yayi saki mace in dai da sauran kauna to kafin matar nan tayi wata uku a gida yake mayar da ita, idan aka wuce haka to babu so ko daya.

Shi dinma da ace ya ga wani kaskantacce zaki aura ba zai dawo ba dariya zai dinga yi miki kamar yanda ya dinga yi miki dariya yana tunanin kina cikin kunci zawarci. Yara kuma kowa da kaddararsa, baki da ikon tsarawa kowa rayuwa sai abinda Allah ya tsara don haka ki barwa Allah aikinsa kiyi naki; wato addu’a. Ke kika ce min kinyi istikhara a kan Allah ya zaba miki abinda yafi alkhairi gashi ya zaba miki amma kina so kiyi fatali da zabin Allah, idan kikayi haka kuwa anya bakiyiwa Allah butulci ba? Idan dai kin gode da abinda Allah yayi miki da ya rabaki da kuncin da kike ciki a baya to ki wanke fuskarki ki shirya ki fito yanzu naga kina ta walwala. Kin ji ko?’

Ta gyada kai alamar to, ta fada jikin Inna ta sake rungumeta tace

‘Nagode Inna.’

Da dariya Inna tace

‘Yauwa ta wajena, maza ki shirya ina falo ina jira naga kwalliyar amaryar Abdurrahman ba tsohuwar matar Mukhtar ba.’

Tayi dariya tana goge fuska, Inna ta fito ta rufo mata kofar dakin.

Ta sa hannu ta dafe kirjinta tana ajiyar zuciya, ko babu komai taji sanyi da tayi kukanta a jikin Inna ba tare da an hanata ba. Ta mike ta karasa gaba mudubi, ta kalli fuskarta wadda ta jike da nason hawaye tayiwa kanta murmushi; tabbas ta so ta yiwa Allah butulci duk da tarin ni'imomin da yayi mata domin ita ta nemi zabin sa kuma gashi yayi mata. Ta bude baki tace

'Alhamdulillah.'

Ta sake kallon kanta tayi murmushi, tabbas tana son mijin barrister sai dai soyayyar da takewa yaranta tana saka mata shakku a kan komai.

Wayarta ce da take ajiye a kan mudubin ta dau waka, ta kalli wayar hoton fuskar A A ya bayyana domin da kansa ya saka mata lokacin da ya siyo mata wayar. Ta bi hoton da kallo tana murmushi har wayar ta nemi tsinkewa sannan ta dauka. Bayan ta amsa sallamarsa tace

'Mijin Barrister.'

'Amaryar AA, ina kika shiga ne kike hora ni haka? Tun jiya nake waya bakya dauka. Kin san Allah kin ganni a mota da baki dauka ba yanzu gidan zan taho.'

Tayi da dariyar da ta kwana biyu batayi irinta ba

'Kaina bisa wuyana, a daki nake barin wayar saboda gidan da mutane.'

'Gobe ne fa, kin shirya ko na zo na shiryaki?'

Ta sake kyalkyalewa da dariya irin yanda take saka shi nishadi sannan tace

‘Kaga bari naje na shirya kafin Inna ta biyoni don tun dazu tace na fita wajen mutane.’

Sukayi sallama ta fada bandaki, nan da nan ta gyara fuskar ta sako doguwar rigarta ta atamfa ta yafa mayafinta mai kyau ta fito ta shiga gaisawa da mutane kafin yamma tayi a zo kamu.

…..

Ana idar da sallar la’asar mai kwalliya ta zo, nan da nan tayi mata makeup dan daidai misali wanda ya kara mata kyau, ta saka leshinta kalar maroon. Ta riga ta ce ba zata saka goggoro ba don haka mai kwalliyar ta daura mata dankwalin leshinta irin yanda ake yiwa amare. Ta kawo mayafi irin na amare me ruwan gwal ta yafo tun daga kanta har kasa.

An riga an gyara dakin Umma don a nan za ayi kamu, an riga an gyara dakin an shimfida babban zanin gado ga fululluka an jera an baje carpets, ga turaren wuta mai sanyi kamshi na Xee Yaxeed da aka kunna a kowacce kwana don haka kamshi ne kawai yake fita daga dakin. Ta zauna a kan gadon kamar yanda saraki suke zama a kan karaga.

Saliha da Maimuna ‘yar wajen Inna suka zauna a gefenta suna ta hirarrakinsu.

Basu dade da zama ba aka buga musu kofa aka ce ga ‘yan kamu nan don haka suka gyara suka ja mata mayafi ta rufe fuskarta. Su Hamida da sauran cousins dinsu sukayi ta ciniki da iyayen ango hara aka tsaya a kan naira dubu dari. Suka zaro su sababbi dal ‘yan naira dubu dubu suka mikawa Hamida. Nan da nan aka saka guda aka bude musu kofa suka shiga suka feshe amarya da turare.

Jimawa kadan aka fito farfajiyar gidan inda aka zuba kujeru duk da basu da yawa, nan malaman islamiyyar su Safiyya suka fara lakca aka baje ilimi ana ta tattaunawa ana raha. Ga abinci kala-kala hadadde da aka rarraba kowa yaci ya sha.

Sai gefin magriba aka fara raba souvenir wanda Xee yaxeed ce ta yi musu turare da kasko tare da gawayi aka bawa kowa, aka kwashi na dangin ango aka zuba musu a motar da suka zo da ita. Aka sallami malamai taro ya tashi.

……

Washegari ranar daurin aure tun karfe bakwai ta shirya suka wuce gidan Baban Hotoro, domin a can za a daura auren kuma haka sukeyi duk 'yar da zai aurar sai ta zo gidan. Sai bayan azahar sai yayi mata nasiha ta koma gida.

Sai karfe sha daya za a daura auren don haka saida suka gama hirarrakinsu da dangi suka ci abincin safe sannan amarya ta shirya.

Farar atamfa ta saka wadda aka dinka mata siket da riga sannan ta kawo farin laffaya lace wanda aka yiwa kwalliya da shudi da ruwan gwal ta nade jikinta da shi, nan da nan dakin ya dauki kamshi domin laffayar ta sha turaren wuta.

Karfe sha daya da rabi suka jiyo sanarwa a loudspeaker: “An daura auren Safiya da Audurrahman a kan sadaki naira dubu dari, waliyyan amarya sun karba kuma mun shaida Safiya ta zama matar Audurrahman.”

Nan da nan kuma mata suka karade gidan da guda.

Bayan wajen awa daya suna zaune sun gama hotuna a cikin gida angonta ya kirawota, tana daga waya yace

‘Mrs AA.’

Tayi murmushi kamar tana gabansa, yace

‘Ina falon bakin Baban Hotoro ina jiranki minti biyu na ganki ko?’

‘Ka ga mutane kuwa a cikin gidan, gaskiya ba zan iya fitowa ba fa.’

‘Barin na turo a dauko min ke.’

Tana ta dariya ta ajiye wayar, ai kuwa ba jimawa Saliha ta shigo ta tasata a gaba har falon.

Shi kadai ne a falon yana waya suna shiga ya ajiye wayar ta karasa ta zauna a kusa da shi, Saliha tace

‘Gata nan bari na hado kan dangi sai ku fito bakin gate muyi hotunan.’

Tana fita Sabir ya shigo, yana ganin zaman nasu ya daga waya ya danna video.

AA yace

‘Kin wani sunkuyar da kai kamar mara gaskiya.’

Ta kara sunkuyar da kan kamar zata dungura, ya mika hannu ya kamo habarta ya dago fuskar. Ya bita da kallo yana murmushi, ta sake sunkuyar da kai, ya matso daf da kunnenta ya rada mata

‘fine girl matar AA.’

Tayi dariya ta mike yayinda shima ya mike, ya tsaya a gabanta ya juyota yana fadin

‘Sabir kayi mana hoto.’

Ya janyota jikinshi ta gefe suna murmushi sannan Sabir din ya kashe video din ya daukesu hotuna.

Suka fito cikin Jama’a mai hoto ya cigaba da dauka.

___

A zaune take a falo tana aikace aikacenta na gida. Tunda yaje gidan Baba ya ga Baban sun ci kwalliya shi da Nurain da Aminu wai zasu tafi auren Safiyya ransa ya baci, yayi magana kuma Baban yace wai ya zo suje. Don haka yana fitowa daga gidan ya dawo gida ya kwanta a falo Halimatu tana ta yi masa gwaranci.

Zuciyarsa babu dadi, bai san me zai yi ba shi yasa ya kwanta a nan ko motsinsu zai debe masa kewa. Ya daga waya ya gama zagayawa a Facebook, ya rufe ya dawo Whatsapp. Ya duba sakonnin sa kadan sannan ya fara kallon status, ya bude guda yana kallo yana gatsina baki wani yayi ‘yar dariya.

Bai damu da sunan wanda ya dora ba don haka kallo kawai yake wannan yana wucewa wani ya fara.

Kamar da keta ya buda wani, tun kafin ta dago fuskarsa ya san Safiyya ce. Ji yayi kamar ya rusa ihu lokacin da AA ya mika hannu ya dago fuskar Safiyya. Haka sukayita soyayya yana kallo kuma yaki yan rufe status din zuciyarsa sai suya take yi.

Har hoton ya kusa karewa Jamila da take tsaye a kansa ta mika hannu ta dafe wayar tana fadin

‘Wannan ai kamar Maman su Nurain ko?’

A fusace ya bata amsa tare da rufe wayar

‘Eh itace.'

Har zuciyarta ta bashi amsa

‘Allah sarki ta ji dadinta don da da gani suna son juna, inama ni ce ita.'

Ya juyo ya kalleta a fusace

‘Ina ma ke ce kike auren ko me kike nufi?’

Tar ta kalleshi tace

‘Eh, inama nice tunda kaga ko ba komai da matarsa zai raba mata kwana ba da karuwa ba.’

Ya mike a fusace yana nunata.

‘Bafa na son irin wannan Jamila, wannan ai wulakancine. Ni kike gayawa wannan maganar banzar?’

‘A’a fa! Ba ni na kar zomon ba ratayar ma ba a bani ba. Yauwa, kada ka daga min hankali daga fadin abinda ke raina.’

‘Mtsewwww!’

Ya ja tsaki ya wuceta ya haye saman.

Haka suka koma tun bayan data dawo daga yajin data yi. Ta daina magana a kan neman matan da yakeyi amma fa duk lokacin data ga dama haka zatayi ta yaba masa maganganu marasa dadi, in ya biye mata kuma sai suyi tayi bata damuwa.

Idan abun ya ciyota kuma sai ta shige daki tayi kukanta ta koshi tunda ta daina gayawa kowa matsalarta. Ta riga ta yarda duk matan duniya munafukai ne tunda duka ce mata suke gaba daya maza haka suke da neman mata amma duk wadda ta tambaya

‘Mijinki yana neman mata?’

Sai sauce mata a’a.

Saboda tsabar ta saba har ganewa takeyi idan yayi sabuwar budurwa. Saukinta daya tana zuwa aiki kuma tana karbar albashinta, sannan kuma hidimar gidansa ko ashana bata yarda ta siya sai ya biya don tace bazata yi asara ba, ta kaiwa ‘yanmata nasa kudin ita kuma tayi hidimar gidansa da nata.

Yana shiga ya turo kofar dakin ya zauna a gefen gado, yanzu shikenan yayi asarar Safiyya? Anya kuwa zai iya karashe rayuwarsa da Jamila?

Shi mutum ne da baya son yawan fada da hayaniya, ita kuwa Jamila yanzu bata bari suyi sati suna zaman lafiya, haka kawai sai ta dinga gaya masa maganganun masu zafi har sai ya kulata sun yi fada. Idan sukayi fada kuma sai tayi kwana uku zuwa biyar bata shiga harkarsa.

Ita kuwa Jamila tambaya daya takeyiwa kanta kullum ‘Anya kuwa ta yiwa 'yayanta adalci da ta zabar musu uba kamar Mukhtar? Me zata ce musu idan suka girma suka ga ubansu mazinaci ne? Wannan tambayoyi ba karamin razanata sukeyi ba suna kara mata damuwar da dama kullum a cikinta take.

Idan taga ance mijin wata ya mutu har ji take dama ace itace, Mukhtar ya mutu kawai ta huta.

KARSHEN BABI NA TALATIN DA TARA.MATAR MUKHTAR

Written by

Sakina Yazid

(Innar su Amal)

BABI NA ARBA’IN

40

Sai bayan sallar isha’i aka kawo motocin daukar amarya, mota hudu ce ta zo kamar yanda Yaya Habibu ya gayawa AA; domin yace kai amarya kawai za ayi ba tare da an batawa matar gidan rai. Sosai AA yaji dadin hakan don haka ya bada motoci hudu; daya danginsa ne su uku a ciki wadda anan zasu dauki amarya uku kuma iyayen Safiyya.

Sai da suka gama Lodi suka kama hanya sannan Yaya Habibu ya bar wajen su kuma suka kama hanyar Nassarawa GRA inda a nan ne gidan da za a kai Safiyyan yake.

Babu kowa a part din barrister don a rufe yake kuma babu fitila, don haka sai kawai suka wuce wajen Safiyyan. Ba tare da bata lokaci ba suka shiga suka kai amaryarsu suka fito. Ya riga ya gaya mata yana nan a cikin gidan shi yasa bata damu ba da suka yi mata sallama.

Shi kadai ya shigo dakin yana ta fara'aa da ledojinsa. Har ya gama zolayarta babu abinda ta iya ce masa. Ya kama hannunta ya zagaya da ita ya nuna mata gidan, bayan ta koma dakin tace masa zata yi sallar isha’i don haka ya mike yace

‘Bari na je wajen yayarki na dawo.’

Barrister ta riga ta gaya masa bata son ya kawo mata amaryarsa don haka ma shi ya sa bai yi gigin tafiya da ita ba.

Yana shiga lokacin suma basu dade da dawowa ba ita da yaran; gidan kanwarta ta tafi sai da ta tabbatar duk 'yan kawo amarya sun watse sannan ta dawo. Suka gaisa yayi musu sai da safe ya koma wajen amarya.

.....

Kwananta biyu a gidan amma bata taba ganin barrister ba ko yaran gidan, tana dai jiyo motsinsu kuma tana jin lokacin da barrister take fita da yaran don kaisu makaranta ita kuma ta wuce wajen aiki. Bata san me ya hana su zuwa ba kuma itama bata neme su ba. Bata fara girki ba don ya gaya mata sai bayan kwana uku zata fara girki, kullum fita yake ya shigo da abinci wanda bata san wa ya girka ba amma dai ta san ba barrister ce ta dafa ba.

Ranar laraba ta cika kwana uku, don haka tun ranar Talata ya sanar da ita gobe idan yayi breakfast a wajen barrister zai yi lunch ya zama kwanta, sai an yi kwana biyu sai ya dawo; itama barrister ya sanar da ita wannan tsarin.

Ranar laraba da ya fita sallar asuba kafin ya dawo ta koma bacci, don haka sai kawai ya rage mata AC ya fito daga dakin tunda dama shi bai saba bacci bayan asuba ba.

Sai wajen karfe bakwai da rabi ta tashi, bayan ta wanke fuska ta fito ta same shi a falo. Bayan sun gaisa yace

‘Ashe kin tashi shi yasa na daina jiyo munsharin.’

Tayi dariya ta zauna a jikinsa, yace

‘Bari na karbo mana abincin ko.’

‘Ka bari kawai tunda akwai bread yanzu zan yi mana sandwich in ya so sai na fara girkin yau tunda ba a nan zakayi lunch din ba.’

Ya gyara zama yana kallon fuskarta tana masa murmushi yace

‘Kin iya girki ne?’

‘Bakinka zai gaya maka.’

Ya ja hannunta suka tashi tsaye yana fadin

‘Muje na koya miki.’

Tayi dariya ta mayar da shi ya zauna tace

‘Ka zauna a nan har sai na nemeka.’

Ta fice kafin ya bata amsa.

Ya riga ya siyo duk wani kayan abinci ta gyara ta saka a freezer don haka tana shiga kicin ta debo kifi a freezer ta gyara ta bararraka, ta dafa kwai ta yanka vegetables dinta. Ta dauko butter nan da nan ta hada musu fish sandwich ta zo ta jera a dining table.

Ta zagayo ta bayansa yana zaune a kan kujera ta hura masa kunne, yayi dariya sannan tace

‘Breakfast is served and ready.’

‘Yes my love.’

Ya amsa tare da mikewa. Sai da ta hada masa tea sannan ta zauna a gefen damansa, ya dora hannunsa a kan nata yana kallon idonta

‘Thank you.’

Suka cigaba da cin abincinsu yana ta faman yi mata surutu.

Ba zai iya tuna lokacin da barrister ta hada masa shayi ba balle ta dafa masa abinci, sai dai tana da masu aiki uku da suke komai na gidan. Duk abinda yake so mai aiki ce zata dafa ta jera masa a table yaci, don haka yanzu da Safiyya ta dafa abincin ta zuba ta hada masa shayi jin kansa yake kamar wani sarki.Sai wajen sha daya da rabi sannan yace mata zai wuce wajen barrister don haka ta shirya su je ta rakashi duk da dai an ce kada yazo da ita.

Hijabi kawai ta saka suka wuce.

Bata fita aiki ba yau saboda public holiday ne, don haka duk suna zaune a falo ita da yaran; Sulaiman, Suhaila, Muhammad da kyma Nur; yayin da Cynthia mai aikinsu take kichin tana ta faman soya dankali.

Suna shiga Muhammad ya taso da gudu ya fada jikin Safiyya

‘Anti Oyoyo.’

Ta shafa kansa tana dariya, yace

‘Dama Daddy yace gidanmu zai dawo dake.’

Suka karasa Barrister ta nuna mata kujera ta zauna, ta kirawo talatu mai aikinta tace ta kawo ruwa da lemo.

Cikin mutunci suka zauna, shi kansa AA saida yayi mamaki don ya zata Barrister bazata karbeta ba amma sai yaga suna gaisawa girma girma don haka shima ya zauna Nur ta haye cinyarsa. Ya dubi barrister yace

‘Ga kanwarki nan.’

Tace

‘Godiya nake yallabai, ka ga yanzu na samu wadda zamu dinga gulmarka na huta da yi da yara ma yi da hujja.’

Haka yake ce mata in yaji suna hira da yara suna dariya in ya shigo sai yace gulmarsa sukeyi.

Yayi dariya yace

‘Kwanan nan kuwa zan maka ku kotun koli.’

Sukayi dariya gaba daya.

Ya gabatar mata da yaran gaba daya banda Muhammad da yake zaune a kusa da ita. Dukansu suka gaisheta cikin sakin fuska banda Suhaila wadda take ta faman cika tana batsewa kamar ita akayiwa kishiya.

Ta mike tace bari na koma, barrister ma ta mike tace tana zuwa ta shiga daki. Jim kadan ta fito da leda a hannunta ta mikawa Safiyya

‘Ga wannan amarya, Allah ya sanya alkhairi.’

Tayi mata godiya ta juya zata wuce Muhammad ya riketa yace

‘Anty zan biki, Daddy wajen Anty zan je.’

Yace

‘Anty Kuma sai kace a school?’

Ya nuna barrister yace

‘To ai ga Mommy na ai sai nace Anty ko? Ko da yake kai kace Inna kake cewa mamanka to nima sai nacewa Anty Inna, kaga kai kana da Inna ni kuma ina da Inna da Mommy.’

Sukayi dariya gaba daya, taja hannun Muhammad suka wuce AA ya bi bayansu don ya raka su.

.....

Hutun sati biyu aka bawa AA don haka ranar da zai koma ya dauki Safiyya suka fita, unguwar da take nan kusa da su ya kaita wajen wasu shaguna a bakin titi, ya nuna mata shaguna. Guda biyu a bude suke yayinda hudun suna rufe. Yace ta zabi guda biyu a gyara a mayar mata da su saloon. Ta rasa bakin da zata yi masa godiya sai da tayi kwalla.

Yayi musu sallama Barrister ta kaishi airport ya wuce Abuja. Ya barwa Safiyya mota da direba don kaita aiki da duk inda zata je tunda ita barrister tana da mota kuma akwai direban da yake dauko yara daga makaranta.

_

Sai da Fatima da Ahmad sukayi wata shida suna more amarcinsu sannan ya dauko Jabir, lokacin tana dauke da ciki wata hudu. Da yake ta saba bata da kani a gida sai ta mayar da shi kamar kaninta, haka suka cigaba da rayuwarsu cikin walwala da farin ciki.

Ta manta da Mukhtar gaba daya bata fatan ta sake ganinsa a rayuwarta.

_

Wata biyar da auren Safiyya, lafiya suke zaune da Barrister kawai dai babu ruwan kowa da kowa amma duk wata mu'amala da ta hadasu to da girmamawa suke yinta.

Gaba daya yaran gidan suna girmama Safiyya banda Suhaila, domin ita ko gaisheta bata yi don bata ga dalilin da Daddy zai kawo musu wata Anty ba ace ta zama matar gida.

Shi kuwa AA jinsa yake kamar wani sarki domin bai saba matarsa tana yi masa duk abinda yake so ba saida ya auri Safiyya. Girki kawai da takeyi masa da kanta kuma ta kawo masa ya kara mishi sonta, duk inda ya tafi cikin kewarta yake. Bai saba hira da mace ba saida ya auri Safiyya domin barrister bata fiya zama ba idan kuma tana nan to bata rasa wani aiki na office da takeyi, don haka da yara ya saba hirarsa.

Ita kuwa Safiyya sai ta zauna a falo ya kwantar da kansa a kan cinyarta suyi ta hira suna dariya har sai sun ji bacci.

Babu wadda ta sawa ko wacce ido don haka ma babu wadda ta san me 'yar uwarta take cikiWatansu shida da aure ya sami sauyin aiki zuwa Lagos, ya riga ya san barrister ba zata bishi ba don haka ya shirya tafiya da Safiyya wadda take dauke da ciki na wata biyu.

Saida aka kawo mata su Nurain sukayi mata sati sannan taje tayiwa gidansu sallama suka kama hanyar Lagos.

AA ya sanar da ita nan da shekaru takwas zai yi retire su dawo Kano don haka idan sun dawo Kano ta dauko Nana da Nurain suyi zamansu a wajenta.

Ta san dai za ayi rigima kafin ubansu ya bata su amma ta shirya don dole sai ta karbi yaranta.

_

A yanda Mukhtar ya tsara bai so Safiyya ta sake ganin su Nurain ba, sai dai Baba ya taka masa birki, yace

‘Ban yarda ba, dole a barta taga yaranta duk lokacin da ta so ko suka so. Hakki ne wanda Allah ya bata kuma kai baka isa ka hanata ba, ka ji na gaya maka! Kai wa yayi maka haka?.’

Don haka ya hakura, duk lokacin da ta ke son gani su sai ta tura Sabir ya dauko suya kai mata su suyi kwana biyu.

Bai fasa neman matansa ba sai dai kullum ya canza dabara. Ita kuwa Jamila kullum cikin fada suke da Mukhtar domin kullum zuciyarta a kusa take. Kukanta yaki karewa duk da kullum fata take ya daina amma ita ta san bai daina ba.

Shekarar Halima daya da rabi ta haifi Zainab. Tayi murna kuma taji tausayin yaran, ga halin da mijinta yake ciki kuma ga yara mata tana haifa.

Watan Zainab shida taje aka saka mata implant ba tare da tayi shawara da kowa ba saboda tana jin ba zata iya cigaba da haihuwa alhalin mijinta yana bin ‘yayan mutane ba. Tana fatan wataran dole zata rabu da shi musamman idan bai daina neman mata ba kuma ta san idan ta tara yara da yawa ba zata iya rabuwa da shi da sauki ba.

KARSHE..